Compiled By Umar Dalha Funtua.

Copied By Xayyneb 💤💤

https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp

DA SAURAN KALLO!!!
👁️👁️
🥫🥫🥫🥫
👁️👁️
Fasaha online writers f. o. w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳

story and writing
by
Xayyneb 💤💤

~In the name of Allah the benepeciant the merciful~

Bismillaheer rahmanirraheem.
.....
🅿️🔲
T a shigo gidan nasu hannunta riq'eda wata 'yar q'aramar baby nokia tana waya, kaida kaga yanayin halin da nokiar take ciki kasan ta fara jin jiki dan har da wata 'yar siririyar farar salatif aka nad'e a q'asan ta dashi a wajen sa cajin kenan da wani d'an falan day'a na salatif d'in gudun kada wajen ya ida su6utowa yayo qasa.
amman inkaji yanda heenduh ke faman sake nonnoq'e sanyayyar murya tata tana magana harda wani lumshe idanunta zaka d'auka wata iriyar babbar touching ce take wayar da ita, wannan karan a tsiwace take fad'in
"mtsss haba dan Allah nace ka bari sai next week zamu had'u anan gida dan wlh kokazo yanzun kayi wahalar banza danba wai fitowa zanyi ba uniform d'ina zan goge danma kaji fah, haba ka fiye naci musaddiq wallahi"
daga can 6angaren day'a musadiq ya dafe kansa ya rasa miyasa yarinyar nan ke son had'a masa hyper tention ba da sonta a ransa kamar zuciyarsa zata tsinke yakeji, da q'yar ya bud'e bakinsa yace "to.. to shiknn gimbiya ta heenduh Allah shi kaimu juma'ar lpia ai kmr gobe ne inda saura kwana 2 ko nikeji? "
tana tsoki ta katse wayar take fad'in "ban sani ba nataccen mutum kawai" tana mgnr amman still hankalin ta na kan wayar tana tafiya dan qarasawa cikin gidan nasu,
da yake babu zaure a gidan bika wuce ne.
turo lips d'in bakinta tayi hakan ne kuma ya bawa qwan zuma cwingum d'in dake maq'ale cikin

bakinta da yayi q'atoto damar fitowa ya fashe sannan ta cigaba da rats rats tana cigaba da sakin qarar q'wan cwingum din a bakinta abinda babanta ya hanata kuma knn wato qas qas na cwingum indai yana gida kuwa bata yarda ma ta fara sa cwingum a bakinta saiya fita dan ita kam sam sam batta iya taunar cwingum batareda da tai masa qwai da q'as q'as ba,
tana shirin d'agowa da fuskarta kenan daga saman wayar tata sakamakon sanin jarababben qamshin mutumin da tasan waye mamallakin turaren da tayi.
bata ankara ba kuwa by mistake taji goshinta ya doki gefen chest dinsa, da sauri ta ware masa manyan fararen q'al d'in idanunta a kansa fuskarta cike da mamakin miya kawosa gidansu bayan abinda ya faru jia tsakanin babanta da nasa dud akansa kuma?
ranta taji yayi wani mugu mugun 6aci sosai, nan ta sake ware masa manyan idanun nata akansa bayan ta soke wayar tata a cikin bra d'inta daga saman rigarta ta atamfa wacce ta fara jin jiki.
matsowa tayi da sauri a gabansa ganin yanda yake shirin zagaye ta ya wuce bayan gama binta da kallon banza da ya gama yi shima harda wani ta6e red lips dinsa yayi bayan ya kakka6e gefen farar rigar sa ta t -shert da wani blue hankicerf dinsa cike da qyanqyamin abun, wato a dai dai inda kanta ya d'an gogi qirjin nasa.
cak yaja ya tsaya shima ganin yanda tasha gabansa da sauri hannuwanta na saman kwankwaminta tana binsa da wata iriyar muguwar harara a tsiwace tace "miya kuma sake kawo ka gidanmu eye d'an masu kud'i?
uhm? yaya akai mahaifin ka har yasake barin ka shigo gidan talakawa kamar mu? ko bai san kazo bane em?
dakai nike fa mlm?
wata kalar zazzafan harara taga ya sakar mata tareda sake d'aure girar sa tamm tamm babu alamun fara'a nan danan kuwa tsabar k'warjinisa mai cike wa kowane jinsin mace ko na miji ido ya bayyana garesa, hakan ba q'aramin tsorata Heenduh yayi ba tareda haddasa mata faduwan gaba babu zato babu tsammani, amman sam saita kanne bata nuna hakan ba a fili,
'd'aurarriyar fuska a wajen sa ai ba yau ta saba ganin ta ba daman can bare ta sare.
"mai mugun hali, mutum ko dariya baima san ta inda ake farawa ba bare wani abu waishi ma murmushi indai kaga murmushin sa to tasan suna fira da maman tane ko babanta indai har yazo gidan, inko tana kusa ko haqorinsa day'a bata gani.
abinda ta fad'a knn a qasan la66anta,
"matsa ki bani hanya"
yayi maganar yana mai fiddo mata kalar nasa idanun magargad'a gareta na rashin wargi a cikinsu ko kad'an dud ya tsattsare ta dasu.
kuma har cikin ransa hk abun yk, ga kuma fuskar nan dai still gim da ita,
mamanta dake zaune a qofan daki a saman tabarma masassara ce sosai a jikinta amman dataji abin na heenduh bana q'arewa bane sam sam dan ita kam dai batasan a inda heenduh ta d'auko wannan masifar tsiwar ba a danginsu,
heenduh da batasan mamar na wajen ba sai muryarta dataji tace "bazaka bangaje ta bane kalipha ka wuce koka mammareta inda ita ta maida kowa sa'anta?,,
ta qarashe maganar tana aikawa heenduh da harara bayan had'a idanunsu da sukayi da mamar,, baice komi ba ya zagaye ta ya wuce dan shi baida lokacin yi mata ko day'a daga cikin abubuwan da mamar ta lissafo,, hasalima shi bason mgn yake ba inba kamawa taiba yatsani

mutum mai hayaniya hkn yasa yake mugu mugun jin haushin yarinyar dudda ta kasance sister tasa ta jini kuwa amman babu wanda baiqi jinin kowa a cikinsu ba hatta iyayen nasu sunsan da hakan, hakan kuma ya samo asali ne daga banbancin halayya tasu,
zumburo baki Heenduh tayi bayan ta zauna gefen mamar kamar zatayi kuka tace tace "yanzu wai dan Allah mama har kin mnta abinda baban sa yayi mana kuwa jiya jiyan nan ba har nan cikin gida?'
dubnta maman tayi bayan ta d'anyi tari da qyar sannan tace "heenduh kullum qara nusar dake nike amfanin haquri a rayuwar yau, haquri shine ya kawomu a yanzun, da bamuyi haq'urin nan ba da bazamu kawo i ya yanzu ba, mama ta nisa sannan tace haquri gadadden abuni tun daga annabin farko Annabi adamu (A.s) har ya zuwa ga annabin qarshen zamani Annabi Muhammad rasulillah (SAW).
dan haka kiyi haquri mai haquri zai cimma gaci a rayuwar sa, kije ki zazafawa babanki tuwon sa kinsan ya kusan shigowa yanzun, ta qarashe maganar tana mai maida kanta ta kwantas bisa wani shafaffen filo wnda da gani tun na amarcin ta ne,
kan Heenduh tace wani saiga Khaleefa ya sake shigowa hannunsa dauke da jikkar nan ta likitoci wuyansa sagale da abin awo yunus a bokinsa na biye dashi a baya.
"sannu mama" cewar yunus yana mai zuqunnawa saman qafadunsa, "yawwa yunusa" cewar mama,, Khaleefa kuwa kusa da mamar ya matso yace cikin riqaqqan muryarsa "mama bari na auna naga miye matsalar,,,,, mamah tace "oh ni Khaleefa har cewa nai ka barsa nasan masassara ne zansa heendu kuma ta amso min magani a chemist,,, saida ya waiwaya gefen da Heenduh din ke zaune ya watsa mata harara bayan had'a idanunsu da sukayi tun zamansa wajen, batai qasa a gwiwa ba kuwa ta murgud'a masa bakinta itama ta miqe tsaye tana shirin barin wajen taji yunus na cewa
"headache din doctor namu barka da wuni" harara ta sakarwa yunus tuni kuwa ya sinne kansa yana dariya qasa qasa dan yasan bata son sunan da abokansa suke kiranta dashi, quta tayi ta ida wucewa tana fad'i a ranta "bakuda laifi laifin shugaban naku ne da ya samun sunan, wani takaici taji ya qara shigarta wai itace headache ma gaba day'a ? (ciwon kai)
a haka ta qarasa ta fara had'a murhun garwashin dan zazafawa baba tuwon nasa.
Khaleefa kuwa tuni ya maida hankalin sa ga awon da yakewa mamah, bayan ya gama aune aunen ne ya zare abin awon daga kunnuwansa ya dubi mama dud ransa bai masa dad'i ganin abubuwan da take dauke dasu na ciwuka a jikinta,
bayan gyara farin medical glass din idanunsa da yayi fuskarsa a damuwance yace
"amman mama miyasa kike z.....

~Xexen fasaha~
f. o. w.
[1/17, 3:09 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🥡🥡
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing

by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️📄👁️
🅿2⃣
Bayan gyara farin medical glass d'in idanunsa da yayi, fuskarsa a matuqar damuwance yace "amman mama miyasa kike zama bakici abinci ba gashi ulcer ta kamaki har haka?
sannan mama ga maleria itama?
mama shiru tai bata ce komi ba, dudda tasan su d'in ba masu hali bane amman tasan mijinta bai q'asa a gwiwa ba wajen jajircewan sa akan ciyar dasu koda babu yawa ne kuwa,
Khaleefa a ransa fad'a yake
"why dady!! why dady!! please ya za'ace q'aninka d'an uwanka uwa day'a uba day'a kagaza tallafa masu a rayuwar su yanda ya dace dudda halin da kake dashi? amman zaka iya yiwa wasu alheri why shi bnda shi dady?
runtse idanunsa yayi a hankali gam2 sannan ya bud'esu ya saukesu kan yunus yace "yunus je gida ka fito mana da mota quick please"
 "an gama doctor" cewar yunus d"in, haka ya wuce tuni heendu ta rakasa da harara taci gaba da wanke tuwon a ruwa tana zubawa a tukunya.
mama tace
"a'a bana zama da yunwa mai sunan manya kawai dai nasan hakan nufin Allah ne a gareni, maleria kuma sauro a gidajen talakawa ai sai dai haquri Khaleefa kai dai Allah shi rufa asiri"
"aminn mama" cewar Heenduh data zauna a gefenta tana murza mata tafin hannunta, sannan cikin son bashi haushi tasake cewa"mama kinsan ai masu kud'in nan fa sam su basusan ana q'aq'anikayi ba a wannan lokacin ba saimu talakawa bayin Allah, shiyasa komi zasuga talaka yayi suke ganinsa a raine, amman dai dudda haka muma dai km Alhamdulilla inda bamuje maulan roq'o a gidan wasu ba bare azo ai mana surutu, babanmu ya iyawa talaucinmu kum... buge mata baki maman tayi cikin jin kunyar habaicin dataji Heenduh d'in na sakarwa Khaleefa,, cikin takaici tace "zaki rufemin baki kosai na farfasa miki shi yanzun nan sakarya kawai"
turo 'yan siraran lips d'inta tayi ba ta sake furta komi ba kawai taci gaba da murzawa maman tafin hannun nata dan samar mata da d'umi ga alama maman sanyi takeji na masassara.
dudda yasan wannan maganar shi wannan lazy headache din take jefamawa amman sam bai nuna hakan ba a fuskarsa bama, hasalima wayarsa dake hannunsa da yake dubawa kawai ita yafi maida hankalin sa a kai yana dannawa. duddai kuwa maganganun nata sun masa zafi amman babu komi tarata yake har yanzun.
wayar sa ce tahau ringing,
da'gawa yayi
 "ok yunus gani nan futowa yanzun to"

abinda yace knn ya miq'e tsaye bayan ya d'auki jikkar tasa yace
"mama bari na kawo miki magungunan da yadace kisha" mamar tace "Khaleefa tun dawowar ka q'asar nan daga makaranta yau kimanin sati 2 knn kake ta hidima damu dan Allah ka barsa in mlm ya dawo zai siyo min maganin kaji?"
"a'a mama dan Allah na roq'eki kada kice a'a a karo na biyu kema ai mahaifiyata ce fa" yayi maganar yana mai son a tausayawa kalaman nasa,, ita kuwa Heenduh kyab'e baki tayi a ciki ciki tace "dubesa kamar wani mutumin kirki mtsss harda wani cewa da mamata mamarsa,, hmm! ai wlh Allah sawwaqa mamarka nacen masifaffiyar nan marar kirki can kaje kaji da ita bawai tawa ba, sai nacin tsiya dubi fa dud abinda ya faru jiya amman saida ya dawo gidan mu yau kamar da kudin babansa a ka cika aka siyi gidan, mtss ta qara jan tsaki jin wata zuciyar tace mata "amman ai qanen babansa ne mai gidan ko heendu ? (babanta knn) dan ya shigo laifi ne Heenduh? yatsina fuska tayi a sace ta wani 6alla masa harara sannan ta dauke kanta tace a can qasan zuciyarta take fad'in "haba ni wlh tun bayan tafiyarsa qaro karatun likitancin nan da yayi har tsawon shekara day'a ba qaramin dad'i naji ba da nabar ganinsa shida wannan abokan nasa amman yanzun ya dawo suma sun dawo kuma, ita takaicinta ma yanda suka ci gaba da had'a musu majalissan abokansa a qofar gida a dud ranar weekend kowa na hutawa a gida ranar knn to abinnan ba qaramin takaici yake qunsa mata ba, shikadai ne Allah bai yassarewa nacin kallo ba a majalissar bisaga abokanan nasa masu nacin kallon tsiya, dan wani sa'in kotana son fitowa sai dai ra haqura.
maganar mama ce taji ta katse mata tunanin nata da tace "to shikenan Khaleefa AllAh shiyi albarka ya kuma daidaita tsakanin mahaifanku kaji"
cikin jin dad'in addu'ar maman Khaleefa yace "amean mama,
bari naje na kawo miki magun gunan saiki fara sha ynxun"
yayi maganar yana mai barin wajen da gangan yabi ta saman kan yatsan kafar Heenduh babban ya wuce abinsa kuwa hnkali kwance kamar bai taka komi ba,
yayi hakanne kuma
cikin mugunta da son ya kuma baqanta mata, dan yana lura da murgud'e murguden da take masa tun a lokuttan zamanta wajen "wata qara ta saki kuwa gamida dafe wajen da hannunta,, tana "ashhhh ! wuushh Allah na ya fiddan yatsa mama ynxun!!!"
da sauri mama tace "ke lafiyarki lau kuwa? "takamun qafana yayi mama,, tayi maganar a azabance,,
shikuwa tuni ya fice abinsa inda buqatarsa ta biya harda wani iriyar tsadadden 6oyayyen murmushi ya dinga saki tsakanin le6unansa. mama tace "jimin sakaryar yarinya, kinsan dai da gangan bazai taka miki yatsa ba ko? nasan bai gani bane saikiyi haquri kuma" Heenduh kuwa dmn akwai aukin saurin kuka dan ta tsani abin da ka ta6a lafiyar jikinta sam.
cikin qwallar takaici tace "wlh mama mugu ne yah kaleepa din can kedai ke baki ida sanin halayen saba shiyasa, wlh mama ni nasan da gangan yaimun inda daman ya tsaneni ba sona yake ba tuntuni"
"yaza'ayi mutum yaqi jininsa d'an uwansa banda shiriritanki kuma da kika saba?"
cewar mama, heendu kuwa tayi saurin cewa "to nidai wlh mama ya q'i jini na nima kuma shiyasa naq'i nasa jinin😏"
tayi mgnr tana murgada baki kamar yana wajen. kuma hr lokacin da qwallan a fuskarta.
gyara kwanciya kawai mama tayi tana mai lumshe idanunta ita kam bazata iya biyewa Heenduh

ba tana fama da kanta ma, jin mamar taki tankata yasata miqewa tsaye tana dangishi da qafar tana fad'i a cikin zuciyarta "Allah ya isa nikam dai walh mugu zai kashemun yatsa kawai kaje ka maidani kuturwa ina budurwa ta ka nakastani dan q'iyayya.
kuma nima wlh ynda ka tsaneni nima bn sonka har cikin ruwan raina.
a haka ta qarasa ta sauke tuwon ta kashe murhun ta dawo ta kwanta nan gefen mama ta d'auko wayarta daga cikin bra din tata ta fara neman layin sa'a qawarta dake kusa da gisansu, tana da'gawa sa'a tayi saurin cewa "inye Heenduh yau babu plasging knn, danni nazata plasging din naki ne da kika saba shiyasa nai jinkirin dagawa dan nasan dana d'aga sainasha masifa wataqil ma ciko ya biyo gyartai saina siyi katin hamsin banci bn shaba inda yanzun babu katin shikenan d'an 10 bare mu rage zafi, kai mtn sun wa talaka baqin ciki wlh an lasa mana zuma a baki an janye"
tab'e baki heendu tayi tace "eh ya sonki? yau kiji in gaya miki banna harkan talauci da tsiya dan account balance d'ina cike yake da creedit kamar zai fashe,,, dariya sa'a ta qyalqyata tana fad'in "kai hajiya heendu bari to na lallabo na zagayo nazo amin transfer danga alama musadiq yau ya gwangwajemu da kati available,,
cikin yatsina heendu uwar kakkafi da son iya taku tace babu matsala kawata sai kinzo" kashe wayar tayi tana mai d'an matsawa ta leq'a fuskar mama taga alamun barci take sonyi ma, komawa tayi inda ta taso taci gaba da danne dannen wayarta anan taci karo da d'ubban text message daga samarinta na qwaqwar son suzo wannan satin ciki kuwa harda musadiq nata. dukansu deleting dinsu tayi a fili take cewa a tsiwace kma
"wannan iyayen message ai saiku ida kashen 'yar ragwagwan wayar tawa ko bakusan cewa ba over load na message na kashe ginshinq'in ingancin injin d'in waya da batirinta ba????

~Xexen Fasaha~
f. o. w.
[1/17, 3:09 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🥡🥡
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️🥡👁️
🅿️🚹

W ani d'an siririn tsuka ta kuma saki sannan ta maida wayar ta soke a breazer din nata, ta dawo gefen fuskar mama ta zauna sai lokacin ta lura ashe ma maman ba barci take ba, "tace lah mama nazata ai barci kike ma? yunqurin tashi zaune mama tayi, da sauri heendu ta kama ta ta ida miqewa zaunen ta jingina bayanta da bango, sannan mama tace a hankali tana mai dafe saitin zuciyar ta, "na dan fara barcin ma amman nan ta dafa tsakiyar zuciyarta tace "yawani tuqoni naji kamar zanyi amai mafarin farkawar tawa knn dan sam banjin dad'in wajen" ta qarashe maganar da qyar tana sauya fuska alamun ita kadai tasan ynda wajen ulcer din ke katsa mata, ciwon da wajen ke mata jitake ba dad'i har takasa kwatanta yanda yake kuwa a zahiri ma, "sannu mama insha Allah zaki daina jin komi,,
cewar heendu da take shafawa mamar wajen idanunta cike da qwalan tausayi,,
sallamar baba ne da yayi yasa suka maida hankalin su wajen tareda amsawa.
dawowarsa kenan daga kasuwa ya sawo kayan gwari (su cefane da sauran kayan miya) dayake su yake siyarwa a nan anguwar can bakin hanya cikin rumfarsa,, da sauri heendu ta miqe tsaye ta zaro idanunta waje ganin yanda jini kebin gefen gwiwar baban nata yana zubowa har cikin takalmin qafarsa,, a guje ta qaraso wajen tuni hawayen da suke maqale a idanunta suka samu damar zubowa saman kumatunta ta ida kama masa ya sauke kwandunan cefenan daga cikin yar qaramar baron sannan ta koma kusa dashi hankali tashe take fad'in "baba na miya faru dakai hatsari kayi ne? wayyoni ni baba dan Allah miya faru,, dai dai lokacin mama ta samu ta iso wajen da qyar tana mai bin bango dan itama ganin jinin dake bin qafafun nasa da tayi ba qaramin tayar mata da hankali yai ba, da sauri heendu ta matsa ta ruqota ganin kamar zata fad'i da tayi,, mama tace "baban heendu miya sameka haka,, cikin tsananin tausayin mijin nata take maganar.
baban ya dubesu jiki sanyaye taya zai fara fad'a musu cewa dan uwansa kuma yayansa uwa day'a uba daya ne yayi qoqarin bin ta kansa da mota ya wuce baccin da Allah yasa yayi namijin qoqarin tsallakawa gudan gefen wanda hakan ya jaza faruwar jin ciwon nasa sakamakon kwatar daya danna qafarsa mai cike da yayi a ciki ramin kwatar na qasa bai sani ba,
wani kalar murmushi ya kalato tareda d'ora hannunsa bisa kan heendu yace"kada ku damu Allah ya kiyaye ma ai iya hakan, yanzun ku bari naje can cemist din sabo yai mun dreesing din wajen, da sauri heendu ta jawo qaramar hijab dinta tace "to muje babana sai na rakaka" haka suka fita tana riqe da hannunsa maman ta rakasu da kallo,, bayan ta koma ta zauna zuciyarta cike da wasi wasin ta yanda akai ciwon ya samesa, anya hakan baya rasa nasaba da maganar da yayansa mukhtar yai masa jia a inda yace "wlh isma'il yanda har iyalinka sukai sanadiyyar da har jini ya fita a jikin gudan jinin talliron d'ana Khaleefa abin sona to billahel azeem saina fidda maka naka jinin kaima matsiyatan banza kawai da wofi"!
gaban mama ya tsananta wata azababben faduwa, tagumi tayi tasan hakan ba izin kowa bane face na matarsa hjy fiddausi.
komawa tayi ta kwanta nan da nan jikinta y sake daukar gumi masassara nason rufeta shin kuka ta farayi tana fad'in "haba yaya fiddausi kina tsoron Allah kuwa a rayuwar ki? ,, ina matsayin qanwarki amman kike baqin ciki damu kinasa mijinki na wulaqanta dan uwansa da yar uwarki ni Zainaba? share hawayen fuskarta tayi da hannuwanta 2 sannan ta dagasu sama ta fara addu'a da cewa "ya Ubangijin mu Allahu na kawo kuka na gareka na kalar wannan qadararran al'amari na tsakanin 'yan uwan juna dinnan guda 2 dayake faruwa wanda mace ta haddasa masu shi a tsakani, ya rabbi ya rabbi,,,,haka taita addu'a sannan ta koma tayi

tagumi zuciyarta na cewa sai yaushe badaqalar nn zai zo qarshe ne? rufe idanunta tayi ruff tana tazbihi a cikin ranta kota samu sauqin damuwar dake addabar zuciyarta.

~shekaru 23 da suka gabata~.....

Kuyi Manage pls

~Xexen fasaha~
f. o. w.
[1/17, 3:09 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~My daughter ummu sulaimu writer of sinadarin rayuwar aure, shafin nan mallakarki ne ke day'a qwallin qwal moxynki takice kema tawa ce har gaban abada ana kyawun tare a muddance Allah bar zumunci a tsakani d'aurarre dan wanda keyi dakai to kaima muddin rai dashi zakayi haka duniyar ta gada ay~😘

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️📦👁️
🅿️📲

~Shekaru 23 da suka gabata~.
***
Muku mukun sanyin da akeyi ne a jihar kaduna wanda ya sauko tun bayan gama sallar asubahi hakan yasa da yawa daga cikin masu salla a cikin babban masallacin anguwar tasu mlm Abdullahi sukayi zamansu a masallaci suna cigaba da lazumi har saida gari ya yi sha sannan suka fara komawa gidajen su.
Mlm Abdullahi na tafe shida 'ya'yansa maza samari 2, babban shine mukhtar dan kimanin shekara 30 sai qaramin ismail nada shekara 28,
har suka isa gida suma suka wuce ciki, saida baba Abdullah ya gama musabaha da maqocinsa

baba yawale da mlm zayyanu mai almajirai sannan shima yabi bayan samarin y'ay'an nasa nasa yashiga cikin gidan.
ya taras da matarsa wanda yaran y'ay'an ke kiranta inno,
a gaban murhu take duqe tana kwashe d'umamen tuwon nasu a wata roba mai murfi,,
har qasa ta zuqunna ta gaishesa ya amsa a fara'ance, shikam ba qaramin alfahari yake da hafsato ba a matsayin mata ta gari garesa ba tun zamanin aurensu kuwa, shidai kam Alhamdulilla ala kulli halin yana matuqar farinciki da ahalin nasa sosai,,
"sannu da aiki hafsatou" cewar mlm Abdullah daya duqa ya d'auki robar tuwon da nufin kai musu cikin d'aki dan wajen kwata2 batta zaunuwa saboda sanyi,, da sauri inno hapsatou ta ce "a'a mlm kabari basai na qarashe samun ladan ba in nakai mana abincin d'aka ba?" tayi maganar a kunyace alamun fulanan takar tana kurkusa kenan,, murmushi mlm Abdullahi yayi yace "inason in ragewa uwargida na aiki ai nima ko? to dan haka nike roqon ta data haqura ta barni nakai mana abincin nn d'aki sai nasamu ladar temaka wa nima ko ba haka ba?"
cikin murmushi inno hafsatou ta janye hannunta daga kan robar tuwon tace "haka,, to shiknn mlm aini banqi ace dud aikin da nike cikin gidan nan ba'a raba mana ladar ni da kai da yaranmu ba, kaga sai kowa ya q'ara samu akan nasa ladan ba" murmushi matashin dattijon yayi d'an kimanin shekaru 66 ita kuma inna hapsatou nada shekarun ta 55 sannan mlm Abdallah ya sake cewan "hmn hakane madalla da mata ta gari irinki hafsatou, muje to"
a tare suka shiga d'akin nasu suka zauna.
dudda sanyin da ake surarawa amman kuma d'akin nasu akwai gumi sakamakon rushin garwashin da inno hafsatou ta girke musu a d'akin tuni dakin ya d'auki daddaden gumi kuwa.
saida mukhtar ya sake gaida iyayen nasa sannan isma'il shima ya gaishesu cike da biyayya iriyar tasu wacce iyayen nasu suka d'urar dasu tun farko.
a tare suke cin abunci da iyayen nasu kullum karin safe, yanzun ma tare sukeci bayan sun gama ne mukhatar yaje dakinsu ya shirya cikin kayan aikinsu ganin baiga qanen nasa isma'il ba ya shigo shiryawan shima dan wucewa school dayake sun saba tare suke fita saisu rabu bakin titi shi mukhtar saiya wuce wajen sana'ar sa shikuma Ismail saiya hau school bus ya tafi shima, ganin shiru shiru ismail din bai shigo dakin nasu ba hakan ne yasa mukhtar fitowa dan ya kirasa ya shirya su wucen,
saidai abin mamaki yana fitowa nan tsakar gida ya hango qanen nasa ismail zaune kan wani bokitin qarfe ko sanyin nan baya ji yayi tagumi kansa saqe cikin jikinsa.
cikin mamaki mukhtar ya isa wajen nasa sai lokacin ne ma ya lura da yanda tsigar jikin isma'il d'in ke tashi ta wajen damatsan dukkan hannayen sa wanda mukhtar yasan ba komi bane ya jaza masa hakan face sanyin dake ratsa sa a wajen,
matsawa kusa dashi mukhtar din yayi sannan ya dafa sa yace "q'anina yaban ganka ba kazo ka shirya zuwa school kada kayi late naji jia kuma kace around 8:30 kunada exam ko?, kuma gashi kazo ka zauna waje ga sanyi anayi bakka gudun mura ne ta kama ka?
sai lokacin ismail ya iya d'agowa da fuskarsa wacce hawaye ke bi dan tsabar damuwa,
cikin mamaki mukhtar yake kallonsa sosai,
zuq'unnawa yayi bayan ya kamo hannuwan ismail din fuskarsa cike da damuwa, dan kuwa cikinsu babu wanda keson yaga damuwar dan uwansa mafarin knn a matuqar d'imuwance yake qara ruqo hannuwansa yace "dan uwa na qanena mike damunka? kasan bazan juri ganin damuwarka da kuma zubar hawayenka ba a rayuwa ba dai ko?

sanin kanka ne sai inda q'arfi na ya q'are akan hakan dan naga na faranta ma qanena dan uwa na guda day'a tal hm? , dan haka maza ka gayamun mike damuwar ka?
q'irqro wani kalataccen murmushi ismail yayi bayan ya dauke fuskarsa daga jikinsa yayi saurin goge hawayen nasa dan baiyi tsammanin zuwan dan uwan nasa ba wajen ba lokacin, yace "laaa yaya mukhtar yaushe kazo nan ban sani ba?,
ni babu abinda mafa ke damuna fa kada ma ka damu kanka d'an uwa na"
yaqarashe yin maganar tasa tareda qara son 6oye damuwar tasa can qasan ransa.
kallonsa mukhtar din yake cigaba da yi sai kuma ya girgiza kai yace
"no q'anena kada kaimun qarya nasan bakayi mun ita, dan nasan halinka na kuma san in kana damuwa kokuma kana murna dan haka ka fad'a mun,
Saddar da kansa qasa yayi yana tunanin ta yaya zai fad'awa yayan nasa wannan iyayen kudin handout din da zai siyo kimanin 5000k (dubu biyar)? alhalin yasan ba wata riqaqqen sana'a yake ba, bayaga ta kanikanci kuma ba koda yaushe suke samu ba inda wajen nasu ba wani fice yai ba, kuma dudda shima yaya mukhtar d'in wannan year din yagama karatunsa a A. B. U. Zaria shima da qyar da zufar goshi da kuma temakon baffansu ta hnyar saida saida day'a daga cikin guda 2n gonakinsa da yayi har yasamu yayi degree d'inshi gashi kuma ya gaman aiki yayi wuyar samu dole yaje ya roqa ya samu aikin kanikancin a can bayan tasha,,
kuma duka duka aikin nasa ko wata day'a baiyi da fara sa ba, gudan gonar da ta ragewa babansu itace dud in lokacin noma yayi suke zuwa da baffan nasu suke girbewa amfanin gonar kuma in aka samu baffan yakan rabawa dangi da abokan arziqi kingin kuma a kawo gida aci, kuma tunda yayan nasa mukhtar ya fara aikin shike siyo musu kayan cefanen da za'a saffara abuncin gidan aci kullum, sannan ga kuma kud'in ruwa da kuma sauran buqatu na rayuwa,,
topa tayaya zai fad'a masa damuwarsa ya tayar masa da hankali inda yasan ba halin hakan garesa ba?, jin mukhtar ya sake dafasa a karo na biyu muryarsa hatta fara canzawa sbd bacin rai yace
"wlh q'anena in baka fad'a mun damuwar kaba zanyi fushi dakai har na tsawon minti day'a fa danma kaji"
yana fad'in hakan kuwa ismail baisan sanda dariya ta subuce masa ba dudda halin damuwar da yake ciki kuwa,
dan yasan wannan wani salon sune na wasa tun suna q'ananan yara in day'a na cikin damuwa zai furta wa d'ayan hakan to zakiga nan take sunyi dariya dan sunsan koda dai dai da second d'aya ne bazasu iya fushi da junan suba bare har minti day'a kuma hakan sabon sune tun zamanin childhood nasu knn. murmushin jin dad'i mukhtar yayi ganin q'anin nasa ismail ya saki ransa har yy dariya sannan yasake cewa "to gayamun qanena miye damuwar ka dai yanzun?
cikin kararriyar murya ismail yace"wlh yaya kudin handout ne sukaimin tsaye na rasa yanda zanyi nida da sanaar da zanyi da naje nayi wlh na siyo su, to amman yaya lokaci ya rigaya daya qure min tunda saura kwana biyu knn lectures din zai yi mana exam dasu kai tsaye, kuma gashi yace dud wanda bai siyoba bazai zauna masa class exam ba kuma babban tashin hankalin yaya shine lecture din dake daukarmu topic din inglesh da math kuma yaya Allah kuwa baida mutunci nasan zayana iya bawa dud wanda bai siyo books dunnan ba carry over a exam dinsa to shine narasa ynda zanyi damuwa taimun yawa kuma gashi muna jarabawar qarshe ne ta fita makaranta"
mukhtar zaiyi mgn knn sukaji muryar baffan nasu a bayansu na cewa "ah mukhtar Ismail

mikuke har yanzun baku tafi ba, ni da naji shiru ma nazata kun tafi ay,, ismail zaiyi mgn mukhtar yayi saurin cewa
"eh baffa yanzun zamu fita yayi maganar yana mai yiwa Ismail din alama da ido alamum kada yace komi kawai yaje ya shirya,sam mukhtar baisan iysyen nasu susan da mgnr kudin dan basu ke garesu ba saima suma su saka damuwar hakan a ransu, shi har mmki yake yanda ake cewa free education amman saika je school din kaga ba haka ba dan tafi karfin talaka maras galihu. hakan kuwa akayi saida yaje ya shiryo suka wuce baffan nasu ya bisu da addu'an adawo lpia sannan ya d'auki buta ya fara alwala danyin sallar walha. suna tafiya har suka kai titi mukhtar ya fiddo wayarsa yace
"qanina bani sunayen handout din man" zuba masa idanuwa ismail din yayi sannan yace "yaya nasan bakada kudi ka barsa ni kawai zan haqura da zana jarabawar" yayi maganar kamar zaiyi kuka, girgiza kansa mukhtar yayi yace "kada ka damu qanina inabin salis abokin aikina wasu 'yan kud'i nasan zasu isa na siya maka books din. Insha Allah " da sauri ismail ya rungume yayan nasa baisan sanda hawayen farinciki suke zuraro masa ba fad'i kawai yakeyi " ngd d'an uwa na gari yayana Allah shi qara bud'i nasan in AllAh yai maka arziqi zamuji dad'i yayana kamar yanda kake cewa, murmushi sukai dukkansu kansu rabu saida ismail yakai bakinsa kan kunnen yayan nasa yace "d'an uwa ns Allah yabaka fiddausi,, cikin murmushi mukhtar ya dan kai masa dukan wasa yana fad'in kaiko kan dubamin waya na ko? da gudu gudu ismail ya shige school bus din nasu data tsaya a wajen datake daukar students din yana dariya tareda d'agawa yayan nasa hannu shima mukhtar d'aga masa hannun yake cikin fara'a sannan ya wuce wajen aikinsu yana tafe yana tunanin qaryar dayai ma qanen nasa ns cewar Yana bin salis abokinsa kud'i,, shi kansa yasan babu yanda zaayi ta bari burin qanen nasa nason ganin ya zama malamin makaranta ya kasa cika muddin yana a raye kuwa.
dam yasan burin qanen sane ya zama teacher tun yana qaraminsa yake riqe da wannan burin shikuma yai masa alqawalin tallafa masa harya kai ga gaci muddin ana rayuwa,, to yanzun baccin yasan yanda suke da salis abikinsa ne na qut qut kuma yasan salis din na aron yan kudade a wajen yayan nasa in yana dasu shima kuma haka salis din yana arawa abokin nasa mukhtar kudin dud in buqatar hakan ta taso kuwa, to yanzun dai a haqiqanin gskia babu wasu kud'i da yake bin salis saima shi salis din da yake
binsa dubu day'a daya karba jia yayo cefanen sati day'a yakai gida, dan yasan kafin nan da sati day'a za'a basu kudin aikinsu dubu uku da dari biyar da ake basu dud qarshen wata, kuma tabbas da ismail yasan aron kudin zaiyi wajen salis din dasai ya hanasa danba da san ransa yake amsar bashin ba, shima kuma dole tasa yake karbar bashin sbd ciyar da iyayen nasa tunda yanzun baffa bayya wata sana'a qarfi ya fara tafiya.
koda yaje wajen aikin nasu nan ya iske salis da sauran abokan aikin nasu suka gaisa nan ya fara cigaba da aikinsa wnda yatashi akai jia na gyaran wata mota ta shinkafa,, har sai wajen la'asar sannan yasamu ya ida gyara motar ya koma qasan wata bishiya ya kwanta yana maida numfashi danba qaramin gajiya yai ba, salis ya ajiye sukuddireba din hannunsa bayan ya zauna gefen mukhatar din yace "yadai abokina yau naga kayi weak fa da yawa tun zuwanka naga kamar kana cikin damuwa, mike faruwa ne?
tashi zaune mukhtar yayi yace "so nike in siyawa ismail wasu handout salis guda 2 dubu biyar suke kuma wlh gashi ko sisi bnda... nn mukhtar ya fad'a ma salis din yanda ismail yai masa bayanin exam din akan books din kmr ynda yai masa, shiru salis yayi yace"kashh kuma wlh

abokina ni kaina yau bayaga naira dari hudu da hamsin dinnan bana maganin ko sisi a aljihun nan nawa" ya qarashe maganar yana mai zarowa mukhtar din kudin yana mai nuna masa , sannan yaci gaba da cewa suma yanzun nike jira mai abincin nan ta kawo na sai mana muci, in kuma kanada buqatarsu gasu saika cika saimu haqura da abincin inmun koma gida maci inda yiwa kaine za'ayi ko?
cikin fara'a mukhtar yace "haqiqa salis kacika amini na qwarai ngd da kulawar da kk mana, amman ka riqe kudin nan ai mutum bazai rayu babu abunci ba,
kuma bnda kud'i a jikina duka nera dari da hamsin ne bare nace na amsa na cika na siya masa books din, dana yanke shawara naje wajen oga Daniel ya temaka yabani aron kud'in in yaso in anyi albashi wannan watan da wata mai zuwa saiya fidda kudinsa saiya bani kingin cikin kaima na baka dubunka kingin sainai cefane nakai gida kaga shiknn ay,, kallonsa kawai salis yake cikeda mamakin yanda ashe har yanzun akwai 'yan uwa masu qaunar junansu haka? kalli dai yanzun shi ko tunanin kansa baiyi na buqatar rayuwa na iyayensa da kuma d'an uwansa kawai yake danya faranta musu, shiyasa bai qyashin bashi rancen kud'i dan yasan a hanyar daya dace yake biyar dasu kuma dud mai tallafawa zumuncin Allah bazai ta6a neman alfarma a duniyar nan ya rasa ba koda bai samu wani wajen ba to sai Allah ya buda masa ya samu tawani 6angaren,
dubnsa salis yayi sosai yace "gskia abokina bn tunanin oga daniel zai maka wannan alfarma d'in nan kuwa yanda yake da shegen masifar son kud'in tsiyan nan, kasan fa yare da mugun son kud'i abokina wlh?"
shiru mukhtar yayi yana nazari zuwa can ya miqe tsaye yana kakka6e rigarsa yace "bari naje dai,, 'yar dariya salees yayi yace "Allah a dace abokina daman sai an gwada ay ake sanin na qwarai, jeka ina nan har ka dawo kuma inai maka fatan sa'a"
daga haka bai sake cewa komi ba ya dauki haki qasa yana zane dashi a qasa rairayin wajen, da "amimm mukhtar ya amsa ya wuce,, saman wata mota marar body ya iske oga din yana qilga wasu kud'ade.
ya matsa kusa dashi yace "oga barka da hutawa,, ai danial na ganin mukhtar yayi wuf ya cusa kud'in qasan dam6areriyar cinyarsa guda day'a yace cikin hausarsa mai gargada" yaye ankaye mukhter kabalo aicinka kajo nan wulina kuma yanju?"
mukhtar yace yana d'an shafa sumar kansa ta fulani "am oga dama cewa nayi ka ara mani 5000 thousand a cikin kud'in albashina na wata 2 in yaso in wata 2n ya cika saika fudda kudinka ka bani sauran canjin please oga a temaka ina cikin buqata ne"
fiddo idanuwa waje daniel yayi yace da qarfi " woooo 5000 k? kana nema wulina yanjun? "eh oga help me please help me "!! shiru oga Daniel yayi zuwa can yace "ok na yalda jan baka kutin ammannnn da sharad'i,, cikin tsananin farinciki na muhktar jin oga ya amince babu gargada yace "to oga sharadimmi?"
oga daniel ya d'aga cinyar nn tasa ya fuddo kud'in ya qirgo 5k din ya riqesu a hannunsa ya maida sauran aljihu sannan ya dubi mukhtar yace "inka yalda kingin canjin albashinka na wata 2n wato dubu biyuh jan liqesu a macayin baci da luwa?
zaro idanuwa mukhtar yayi tabbas inyayi haka yasan zai cutu, dami zai biya salis dubunsa day'a? dakuma mi zai riqe a hannunsa na amfanin gidansu?
batareda 6ata lokaci ba yace "a'a abarsa ma kawai na haqura" oga daniel yace "ok no problem go, go,mukhtaro"

haka ya koma ya fadawa salis komi, salis yace " hmm nasan ai za'a rina dadai ba oga daniel bane, amman ka shawara man abokina mizai hana muje kasa wayarka kasuwa ka siyar in yaso saika siya masa handout din kaga nan gaba in kasamu wasu kud'in kasayi wata koya kace? shiru mukhtar yayi dan babu wanda ya fad'o masa arai face masoyiyarsa fiddausi yanzun idan ya saida wayar shiknn bazasu sake firan dare ba na free cull wanda suka sabawa juna dashi kullu?
wata zuciyar tace qanen fa to yaya knn?
tuni kwanyarsa ta cakude yarasa matsaya ta shawara, ana haka kuwa saiga kiran fiddausi a wayar tasa ta shigo, kam ya d'aga harta katse, ganewa yayi plashing knn tai masa, jiki a sanyaye ya runtse idanunsa dudda kwad'ayin son jin muryar tata da yakeyi amman hakanan ya runtse idanunsa ya zare batir din wayar ya fiddo sim dinsa yasa aljihu ya maida murfin nokia din wayar tasa ya rufe yana binta da kallo a haka ya miq'e tsaye ya dubi salis yace "muje ka rakani to kasuwar saina siyar na siyo masa handout d'in daga nan,
kan salis yace wani oga daniel ya qwallawa salis d'in kira akan cewa yazo ya gwada inda ya ajiye tayar Pejo din motar da aka kawo gyara d'azun, haka ya wuce yabar mukhtar a nan gun tsaye zuciyarsa na masa saqe saqe akan shin ya saida wayar nan dai koko. dai???...

Xexen Fasaha
f. o. w.
[1/17, 3:09 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🥡🥡
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

~A Ko ina nake kina raina aunty na ta kaina yayata me sona a koda yaushe wacce battason abinda zai ra6eni muddin ba alheri bane a cikinsa kuwa, my hawwas d'ina nike muku bayani my mom sadeeq tawa Allah bar jini da anta a had'e suci gaba da rayuwarsu muddin rai a lami lpia~❤

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️🥡👁️
🅿️5️⃣
Y ayi zurfi a tunanin hakan sosai har baisan yawan adadin lokuttan daya d'auka ba haka, bai

san sanda ma har salis d'in ya dawo ba sai dai jiyayi an dafa masa kafad'arsa salis d'in yace "abokina tunanin me kakeyi haka inata maka mgn baka jiba kuma? miye abin damuwa kuma inda mun samu maslaha ga lamarin?
kazo kawai muje daman na fad'awa oga daniel zamuje salla inda lokacin sallaer la'asar d'in yayi, kasan bawai barin fita yake ba bada dalili ba kaga daga nan in mun gama sallar sai mu wuce kasuwa mi saido wayar ka siya masa handout d'in"
salis din ya ida yin maganar yana mai duban lokaci a agogon hannun dake jikin hannun mukhtar d'in.
miq'ewa mukhtar yayi yace cikin 'yar fara'a yana mai miqawa salis hannu suka tafa yace "ya ilahi nagode maka da ka had'a ni da aboki na gari, dariya sukayi sannan suka tafi gefen titi inda can masallacin yake anan sukayi alwala suka shiga masallacin sukai salla suka fito lokacin qarfe hudu da kwata na marecen ranar ma.
kai tsaye kasuwar saida wayoyi suka isa shagon ya fiddo wayar ya miq'awa salis, salis ya kar6a shikuma ya nunawa mutumin yace "abokina wannan wayar mukeso ka siya, yayi maganar yana mai miqawa mutumin wayar, amsar wayar mutumin yayi ya hau jujjuya ta a hannunsa yana dubanta ciki da bai d'inta sannan ya d'ago kai ya dube salis yace "wannan wayar dudda dai alamun sun nuna cewa sabuwa sabuwa ce bataji jiki sosai ba to gskia duka duka kudinta bazasu wuce dubu 6 da d'ari takwas ba, sakin baki salis yayi yana jin kamar ya kaiwa mutumin wani iriyar kalar bahaggon kutufo na jini da majina dan takaicin cininkin wulaqancin da mutumin yai musu, kasa magana yayi kawai ya juya yana kallon mukhtar wanda jin kud'in da mutumin yace zai sayi wayar yasa tunanin to shi kansa nawa ya siyi wayar ma duka duka atata wata biyu da suka wuce? dubu 13 da d'ari biyar fa ya siyeta a sabuwan tama shima kud'in da suka rage ne lokacin dayai exam da aka siyar da gonan nan ta babansa bayan ya kaiwa baban nasa ragowan sune baban yace yaje yai wani abun dashi shine kawai ya ajiyesu ga lokacin baiyi komi dasu ba, sai bayan takardun sa sun fito na gama degree ya duqufa yawon neman aiki ko Allah zaisa a dace amman sama da wata guda shiru kkji, shi knsa sai lokacin ya yarda da batun mutane da suke cewa karatun talaka a wannan qasar in yagama yana nemn aiki to ya qwammace ace ya qara maimaita shekarun karatun nasa indai zai samu aiki in eagently da ace yaita yawo ofis ofis ma'ikata ana tozarta tasa, inda dai aikin yanzun daka gama karatu tofa babu mai samunsa a kn lokaci face yaran manyan qasan in kuwa kaga talaka ya samu aiki tofa wannan q'wacen Allah ne yabaka kyauta a garesu shiyasa kullum addu'arsa Allah ya azurtasu da shuwagabanni na qwarai wanda zasu kawo cigan qasa a kowace jiha.
haka ya gaji da neman aikin nn ga lokacin ko masinja na ofis bai samu aikin saba dole ya haqura ya dawo gida, ahaka ya yanke shawara shida ismail akan yasai 'yar wayar zamani mai kafafen yad'a labarai koya dinga tura request din neman aikin nasa a wurare daban daban wataqil ko Allah zaisa a dace tanan 6angare in anyi gamdakatar dacen daukar sabbin ma'ikata kamarsu,
hakan yaje shida salis suka siyo wayar fa kullum yana cikin internet aikin tura saqonni amman shiru kkji, bai damuba inda yasan yarigaya daya tura yakuma isa garesun yasan kuma dud daren dad'ewa zai samu saqon amincewa daga garesu kokuma akasin hakan,, alokacin ne yarasa ynda zaiyi ko sile biyar baya maganinsa a aljihun sa inda ya kwashe 'yan kud'in yasai waya, mafarin knn sai da yaje wajen salis akan yanason yakaisa wajen aikinsu na kanikanci dan yagaji da zamn rashin abunyi haka. akayi sa'a kuwa suna zuwa oga daniel ya d'aukesa

tareda fara koya masa dabarun aiki, har aran mukhtar yaji dad'i yasan aikin daya samu ma harda add'uar da iyayen su ke binsu dashi kullum, dayake Allah ya basa qwalwa nan da nan kuma ya fara koyan aikin cikin nasara harya kaiga ya iyan shima yanda ya dace, hargashi kuma da albashin aikin yake tallafawa gidan nasu shima i yau,
katse masa dogon tunanin daya shiga salis yayi yace "yanaji bakace komi ba kuma?"
dubansa mukhtar yayi bayan ya sauke ajiyar zuciya yace "bansan ya zance bane salis wlh"
duban salis mutumin yayi shima salis ya dubesa ya daure zuciyarsa sannan yace " to yanzun ko 12k bazaka siya ba abokina? ka duba fa dakyau sabuwan modern ne fa babu inda ya koyi qwarzane jikinsa?
murmushi mutumin yy yace "eh na gani, a gaskia na siya 8k bayaga haka bazan qara ko sisi ba, kuma madai bari kuji kasuwar nan dud in zaku kewayeta bazaku samu sama da abinda na siyeta ba wlh Allah kuje nina gaya muku"
salis sarkin zuciya yaja wani tsoki ya fizgo wayar daga hannun mutumin yace muje mukhtar muje wani wajen an fasa siyar wan ma anan"
riq'o salis mukhtar yayi yace "tsaya sarkin fushi inda dai yace haka ya siya a siyar masan ba komi,, ai kasuwa ce ta juri hakan daman, badan ran salis ya soba ya bashi wayar mutumin ya karba ya ajiye a cikin dan akwakun qasan inda sauran wayoyinsa na siyarwa suke yana qirgo musu kud'in yana magana da cewa " mu ai wlh masu siyan wayoyin hannu nan bawai qaramin tasku muke gani bama, yau muci riba gobe mu kur6i asara dan yawancin wanda suke kawo mana siyan wayan dud 6arayi ne suke kawo mana muke saya, wannan harkar ai ataimaki juna sunanta kawai"
cikin fushi salis ya yunquro zai nufo mutumin mukhtar yayi saurin taresa jin salis d'in na cewa "ok mune 6arayin knn kake nufi,,?!! "
tuni mutumin yasha jinin jikinsa dan yasan ko warewa zasuyi babu abinda zai iya d'iba a jikin salis barcin shi yaci qaniyarsa ma ya rure masa jiki, shiyasa yayi saurin cewa "a'a nifa yawancin mutane nace baku ba, amman in ranka ya 6aci abokina to kayi haq'uri ai abin bai kai nn ba"
dai dai nan ya miqawa salis d'in kud'in yana fad'in "gasu ngd... , a fusace salis ya fuzge kud'in a hannunsa har yana datsawa mutumin akaifar hannunsa wajen kar6a a fusacen snn yaja tsoki tareda riqo hannun mukhtar din suka bar wajen. mutumin na cewa a ransa wannan kam shegen zuciyar tsiya ne dashi amman kuma ga abokinsa silent man koya suke zaune tare lpia kuma da juna? ya dafe ha6a tareda furta Allah mai had'a jinin bayinsa dudda banbancin halayar dake a tsakani kuwa.
ahaka yaci gaba da harkokin gabnsa.
salis kuwa suna tafiya a hanya yace "wlh daka barni dashi da sai nayi maganin d'an iskan can, har ya isa yai mana habaici ma?"
mukhtar yace "mutane sai haquri ay abokina mu wuce kasuwar books din kawai dan lokaci na qure mana"
Hakan kuwa akai sukaje kaauwar kusan shago biyar sukaje basu samo littatafan ba sai da wani mai ahagon yai musu kwatancen shagon da yake tunanin akwaisu sai sannan sukaje can din suka samu suka siyo.
daga nan wajen aikin suka koma saida oga daniel yai musi fad'a akan jimawarsu,, koda aka tashi suna hanyar su ta tafiya gida dayake tsakanin gudansu mukhtar da salis babu nesa, dubu

day'a da d'ari biyar mukhtar ya fiddo a aljihunsa ya ya miqawa salis, salis ya Karba yana fad'in "wadan nan fa abokina? cikin murmushi mukhtar yace "dubunka ce day'a dana ara sai kuma wannan bari biyar din na baka kyauta kaima kayi wani abun" girgiza kai sales yayi yace "bazan kar6a ba gskia, yayi maganar yana mai daurawa mukhtar din kud'in saman hannuwansa da suke rungume cikin qirjinsa, da sauri mukhtar yaja baya kud'in ya fad'o q'asa yace "wlh saika karba kamaji na rantse danni banyin kyauta a maidomin kuma banyin rantsuwa na sa6a kaima kuma kasan hakan, dan haka sai nazo anjima bayan ishae zaka rakani wani wajen"
yana gama fad'in hakan ya juya ya d'auki hanyar gida salis ya bisa da kallo sao daga bisani ya d'auki d'ari biyar din ya wuce gida shima.
mukhtar na shiga gida ya taras da inno tana sharan tsakan gidan nasu, bayan amsa sallamar sa da inno tayi da sauri ya ajiye ledar litattafan dake hannunsa ya isa gareta ya kar6i tsintsiyar yace "inno ya isa haka kawo na qarasa miki,, cikin murmushi inno tace
"ka dawo mukhtar ko hutawa bakai ba kabarsa kawai zan ida Allah dai shi yi muku albarka"
aminn inno amman dan girman Allah na roqeki ki kawo na ida sharewa miki, sakar masa tsintsiyar tayi da dad'in "to gashi mukhtar" cikin jin dad'i ya ci gaba da sharan danshi da ismail sun saba damn tuni indai suna gida basu fita ba aikin gida tare suke yinsa da innon tasu.
inno kam kwanukan wanke wanke ta duqa tana wankewa ko kofi biyu bata gama wankewa ba saiga ismail ya shigo, da sauri yaje ya rungume yayan nasa sannan yaje ya gaida inno har inda take, jikkarsa kawai ya ajiye a daki ya sake fitowa ya nafe hannun rigarsa yaci gaba da yiwa inno d'auraya.
har wajen garken tumaki saida mukhtar ya share tas sannan ya dawo wajen wanke wanken shima suna cigaba da daurayar kwanukan shida ismail.
cikin jin dad'i inno ke qara dubansu tana cewa "kuma Allah albarkaci rayuwarku ya baku 'ya'ya na gari masu yi muku biyayya iriyar kalar wacce kuke mun yakuma ci gaba da sa muku qaunar junanku ya tsareku da sherrin mahassada" cikin tsananin farin ciki suke amsawa da "ameeen inno tamu"
saida suka gama tsab sannan suka zauna nan bisa tabarmar kaba tsakar gida inno ta sanyo musu burabusko sukaci tare suka gama suna fira mukhtar ya fiddo handout din daga cikin leda ya miqawa ismail yace "handout dinnan ince sune wadannan qanena?"
jiki na rawa cikin sauri ismail ya kar6a yahau dubawa wani uban tsallen murna yayi
tareda yun sukuwa ya maqale jikin mukhtar yace "wlh sune yayana ngd ngd sosai yaya yanda kk faranta mana Kaima Ubangiji Allah ya faranta maka ka samu aiki mai tsoka yaya na ofis kamar yanda kake da buri kaima, nasan in yayana yayi kud'i mun warke inno yayi maganar cikin zubar qwalla a gefen idonsa day'a tareda duban inno din tasu.
"aminn cewar inno"
amman miyasa kuka? inji inno,,
murmushi mukhtar yayi yace "qyalesa inno kukan murna ne yake ai" yayi maganar yana sharewa ismail din hawayen da gefen qasan rigarsa.
inno tace nifa bn ganeba mike faruwa?
Ismail yace "inno litattafan da zaai mana jarabawa ya siyomim kuma sunada tsada inno wlh shine farinciki yasani kuka" girgiza kai inno tayi tace "bakomi haka ake son 'yan uwa su kasance ay, in dan uwa nada damar taimakawa dan uwansa to yayi dan shine cikar zumunci,, Allah shi bada lada mukhtar,

"Aminn inno baba bai dawo bane?
"eh bai shigoba kasan yanzun sai wajajen magrib yake tasowa daga wajen sana'ar"
cikin zumudi ismail ya miqe tsaye da handout dinsa ga hannu yace "nidai natafi yin karatu nida Mustapa (wani aokinsa ne anan maqotansu dayake level dinsu day'a a school din)
suka amsa da sai ya dawo harya wuce mukhtar yace "kamanta q'anena" juyowa ismail ganun yanda mukhtar ya dunqule hannu kamar haka🤜shima yanda yaga yayi hakan yayi masa(dayake taa'dar sune yin hkn in wani zai fita yabar wani sai sungama sannan suyi masabuha kuma)
to yanzum ma hakan ta kasance sukayi tare🤜🤛 sannan suka yi musabaha 🤝tareda rungume juna suna dariya,...

Xexen Fasaha
f.o.w.
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📄📄
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️📄👁️
🅿️🚾
D a dare bayan sallar isha'e ne mukhtar ya shirya cikin wata 'yar shaddarsa wacce bata wuce arxiqin talaka ba, kalar brown ce, dudda ba sabuwa bace amman babu wani aibu jikinta dan taji guga ta kwanta tayi luf bisa fatarsa ta usulin fulanin yola, fara tas da ita, hakama hular sa daya sanya bata boye lallusan sumar gashin kansa ba daga bayan qeyan sa wacce ke kwance lub lub.
d'an lobia dinsa ya matso ya murza a jikinsa, mukhtar kam akwai tsafta da son q'amshi,, tsakar gida ya iske baban nasa ya durqusa har qasa ya gaishesa, cikin faraa baban ke amsawa, a kunyace mukhtar yace "baba zanje wajen firdausey ne"
tuni fara'ar baban ta qaro yace "af toto yarinyar wajen mlm zayyanu knn? "eh baba" yayi maganar kansa duq'e, baban ya sake cewar "masha Allah,
AllAh ya sanya alheri a neman to,
ai mariqinta mutumin kirkine mlm zayyanu mai almajirai gaskia"

Cewar baban, amman kuma can qasan zuciyarsa yake fatan Allah yasa ita yarinyar firdausey bata dauko mummunan hali iriyan na uwar taba meron tsimbe, dan kuwa dai kaf anguwar tasu kowa yasan mugun halin meron tsimbe.
wanda shi kansa mlm zayyanu tafi qarfinsa wani lokacin.
ismail dake karatu can qofar dakinsa ya d'aga murya cikin tsokana yace "aminn babanmu, yaya a gaisheta in kaje kuma kada ka dad'e fa, dan inka dad'e baka dawo ba gskia biyoka zanyi dan bazan juri rashin ganin kaba indai nasan kana anguwar nan" baba yace "to sarkin surutu yi abinda ke gabanka zaifima, murmushi mukhtar kawai shidai yayi ya miqe tsaye baba yace "kai kuma ka gaishemun da mlm zayyanu din sosai" to baba insha Allah"
da sauri ismail ya biyo bayan mukhtar yace "yaya bari na rakaka waje ko?,
"to qanena aida ka zauna ma kada na tadoka daga karatunka"
yace "a'a nidai yaya muje ai nan da qofar gida ne kawai fa please "
dole mukhtar ya yarda suka fita taren sunajin sanda baban ke cewa inno ta miqo masa tabarma wacce suke zama qofar gida shida su baba yawale suna fira kan goma tayi sannan kowa ya dawo gida cikin iyalinsa .
har qofar gidansu salis ismail ya rako yayan nasa sannan ya juya ya koma gida.
har dakin maman salis mukhtar ya shiga ya gaisheta sannan ya tambayi ko salis na ciki,
maman salis tace " yajima da shiga bayi wanka mukhtar amman nasan yanzun zai fito ya gidan yasu innon taku?"
"suna lpia kuma suna gaisheki ma"
"ina amsawa kam mukhtar" bari na kawo maka ruwa, nan taje ta kawo masa ruwan masu sanyi na randa cikin kofin sulba babu jimawa salis ya shigo dakin mamar tasu shima ya shirya cikin wani yadin shadda kaida ka gansu shida da salis kasan samari ne masu jini a jika,
duban sa mukhtar yayi yace "amman fa ka dade mlm ko so kake muyi dare kn muje?"
yayi maganar yana hararar salis d'in, dariya salis ya saki yace "ina zamu knn?
"ban sani ba" cewar mukhtar cikin sake hararar sa. sai lokacin salis ya gane zuwa wajen firdausey abokin nasa yake nufi.
ta6e baki salis yayi ya dubi mama yace "dan Allah mama ki yima mukhtar dinnan nasiha narasa miyasa dud matan dake anguwar nan yarasa wacce zai ce yanaso zai aura sai firdausey diyar meron tsimbe kiji fa mama dan Allah? ni wlh da ace ma zainab ce yake nema d'iyar mlm zayyanu din da sai na taya sa murnar dace da abokiyar rayuwa ta gari amman wlh firdausey ita kanta da mamanta masifa ne zama dasu kowa yasan hakan" tunda salis ya fara magana mama cikin mamaki take kallon mukhtar sai zuwa can tace "mukhtar da gaske ne abinda naji salisu na fade na kanason firdausey 'yar meron tsimbe matar mlm zayyanu mai almajirai?
kai a sunkuye mukhtar yace
"eh mama hakane"
shiru mama tayi ta fad'a zurfin tunani,
ta jima tana jinjina maganar mukhtar din a kwanyarta sannan ta sauke ajiyar zuciya ta kai dubnta ga mukhtar din tace "ni a matsayin mahaifiya
nake gareka mukhtar dan haka komi zai cutar dakai zan fad'a maka gskia a kansa, amman ga tambayata gareka a karo na biyu da fatan zaka amsamun su?
"insha Allah mama"
"miya kaika neman 'yar meron tsimbe kai kuwa, ka kuwa san halin mahaifiyarta kuwa?

shiru mukhtar yayi zuwa can yafara mgn knsa na kallon qasa "mama ai bata biyo halin mamarta bane shiyasa, shiru maman salis ta sakeyi tana mai cigaba da kallon mukhtar din sosai,
"to inma neman auren ahalin gidan kakeso mizai hana bazaka nemi auren Zainab ba diyar shi mlm zayyanu din ba wannan agolar ba maras tarbiyya?"
wannan karon shiru mukhtar yayi kuma yanayin fuskarsa ke nuna baiji dad'in kushen da maman salim kewa su firdausey ba, kuma ai yasan da Zainab din yace yanason ita firdausey din inda dai shi ba makaho bane, shifa abinnan ya ishesa kowa ne abokinsa sai ya kawo kushen tarayyan su da fiddausi to shi kuma yakega danmi zasuna ta kusheta bacin ba iriyar kalar halin maman ta gareta ba waima?
sarai maman salem ta lura da yanayin sauyin fuskarsa da maganar, ta kuma lura cewan lallai mukhtar yayi zurfi a son yarinyar yayi nesa maran jin kira kuwa har ta soma tunanin anya kuwa meron tsimbe batayi wani abun akan mukhtar ba kuwa dan yaso 'yar tata duba ga yanda dud samarin anguwar babu wanda ya nuna koda wasa yanason irin nata?
yanke shawara tayi kawai ta qyalesa amman gobe sai taje wajen mamarsa inno taji kotasan da mgnr dan yanda ta d'auki mukhtar a matsayin danta bazataso ace ya fad'a tarkon makiran mutanen nan ba,
tashi tayi ta basu waje batareda ta qara furta komi ba,
mukhtar ya dubi salis yace "dalla mlm ni kataso muje in zaka rakani" salis yace "kai wlh bini a sannu sai nace bazan jeba fa"
hararsa mukhtar yayi yace "Allah kuwa baka isa ba ka 6atan lokaci sannan kuma kace bazaka rakani ba" saida salis ya qara jajja masa rai sannan sukaiwa mama dake tsakar gida tana kunna fitilan joni sallama sannan suka fita ta bi mukhtar da kallon tausayi nan kuwa ta fara tuno maganar da sukayi da maman zainab matar mlm zayyanu din dataje gidan dayake aminiyar tace sosai sosai tunkan ma a auro meron tsimbe.
a lokacin suna d'aki itada maman zainab din ta bude mata gwanjon safunan sanyi da riguna wanda ita maman zainab din ke siyarwa kawai saiga ita firdausey din ta bankado labulen jikake kuwa jigib ta kayan shanyar da zainab tayi saman igiya saman jikin mmn Zainab din ko bushewa basuyi ba hasalima har digon ruwa wasu kayan keyi daga cikinsu dayake bata jima da wankin ba ita zainab din maman tata ta aiketa siyo kalanzir bakin hanya, sai jisukayi firdausey din tace "baccin iskancin banza har zata zo ta cika wa mutane igiya da shanyar wasu tsummukaran kayanta bacin nima ga tawa shanyar nan inaso zanyi,, ita kuwa mm salis ganin mmn Zainab din batace komi ba tasan kuwa daman bazata ceban danba qaramin haquri take da ba, mafarin knn ta dubi firdausey tace "haba kekuwa firdausey aida kinyi haquri kayan sun bushe inyaso saiki shanya naki... kan firdausey din tace wani abu kuwa saiga meron tsimbe din kamar an Jefota tsaye saman qofan dakin mmn Zainab din ta kama qugu ta riqe tace "to tsohuwar munafuka anqi a bari kayan su bushe nace Anqi din, inkuma kin isa kizo ki maida kayan saman igiya wlh kiga inban nakad'a miki na jaki ba a gidan nan ba har sai anzo an fitar dake, munafuka to ita kanta Zainab din da kuke cewa itace tar gida firdausey kuma nakawota agolanci inda ba gidan mahaifin ta bane munafukai to wlb bari kuji tafita power ta qarfin iko a gidan nan zayyanu dinma daya ajiyeni yayi kad'an yace zai wulaqanta min 'ya na barsa bare ku cakuri cici cukon benci kunzo dakin kun kulle kuna cin naman mutane danye matsiyata"!!! tana maganar ne tana zazzaro ido da wata qatoton muryanta wacce har waje saida aka juyota hakan yasa mlm zayyanu dake koyawa almajirai karatu a qofar gidan kuwa yayi saurin tasowa yana

nad'e babban rigarsa wajen sauri har carbin hannunsa na zamewa qasa yana duqawa ya d'auka.
yana shiga ya taras da masifar da meron tsimbe din keyi yace "haba mero miya kawoki har bakin qofanta bayaga neman fitina iririyar taki da kika saba? cikin tsawa da hayagaga meron tsimbe tace "masifa anje anyi ai daman nasan da kazo babu wanda zaka bawa rashin gskia inba muba, wlh zayyanu ka kiyaye gamuwanka da mahallaci dan bakai man adalci ka tsaneni nida 'yata a gidan nan"
"ni bn tsaneku ba mero halinkune na rashin da'a ke sa bakwa zaman lpia da mutane ina mai tabbatar muku in kuka gyara halayenku kuka dawo na gari kowa zai soku zai qaunace ku kum....
"dalla ni rufemin baki tshohon banza kawai kaima ai munafikin ne" ta qarashe maganar tana nunasa da yatsa idanunta a tsaitsaye, taci gaba da fad'in shanyace kuma an watsar ayi dud abunda zaayi muna dai dai da kowane banza a gidan nan wlh" tana gama fad'in hakan ta dubi firdausey tace "jeki shanyarki 'yata ba gidan ku bane amman kunfi uban kowa matsayi a gidan nan" cikin dariya firdausey tace "shiyasa nike sonki mama na Allah dai ya barmun ke kicimin uban maqiya na wlh"
"aminn d'iyata fad'i kanki tsaye "
tana gama fad'in hakan ta bangaje mlm zayyanu ta wuce har rawaninsa na tiqan qasa "girgiza kai yayi yace "Allah ya shuryeki mero"
cikin tsiwan masifa tace "shirin jigida ba"
bai sake cewa komi ba harta shige daki tana murza wani shafaffen d'uwaiya nata q'asa q'asa uwa na kura.
firdausey kuwa shanyarta take tana wasu waqe waqenta na futsara wacce rashin tarbiya ce tsantsa kawai a cikinsu amman babu kunya haka take yinsu gaban mmn salis d'in da mmn Zainab sai kuma mlm dake tsaye kansa a qasa,
ya jima a haka sannan ya d'ago ya dubi mmn Zainab yace "jameelatu kiyi haquri nasan kina haquri da mutanen nan, to dan Allah na roq'eki ki q'ara akan nada kinji ko, Allah shiyi miki albarka"
maman Zainab tace "bakomi mlm aminn"
Lokacin da yazo fita daga cikin daki yaji meron tsimbe tace
"mu kuma da ba'a son mu AllAh ya tsine mana ko?
ko sauearen ta mlm zayyanu baiba yai komawarsa wajen almajiransa ransa a 6ace matuqa da mugun halin mero da 'yarta.
mmn salis tace "oni Jameela haka kike zaman haquri daman knn? Ashedai maganar jama'ar anguwar nan da gaske ne na matsin da kike amsa daga mero da 'yarta? kan mmn Zainab tace wani abu saiga Zainab din ta shigo bayan ta ajiye kalanzir din nasu ma'ajiyarsa takai dubnta kan igiya taga babu kayanta data shanya taga saima kallon banza da tsana da firdausey din ke aiko mata dashi.
daurewa tayi tace "yaya firdausey ina kayan shanyata kuma?"
"suna gidan ubanki koni tsarar kice dazakimin mgnr wasu banzan kayan tsummokara naki shegiyar yarinya kawai "
"Allah shi baki haquri yaya firdausey ai abin baikai na zagi ba,
"inma yakai ko zaki rama ne?

mmn Zainab tace "zo nan Zainab baro wajen" haka Zainab ta wuce dakin nasu firdausey ta bita da harara tana fad'in "masu baqin hali"
tana gama shanyar kayanta tai komawarta dakinsu.
Saida maman Zainab ta gama shanya kayan Zainab din a saman qyauren dakin sannan ta dawo wajen mmn salis ta zauna tace "hmm kedai kawai ayi sha'ani mmn salisu, wlh tunda mlm ya auro meron tsimbe ban sake samun kwanciyar hankali ba, takai ta kawo in dare yayi har barci ke qauracemun sakamakon firgitani da akeyi cikin dare da wasu halittu wanda tunda nike ban taba ganin suba, wlh saida mlm yaita mun addu'oen sa nima yabani wasu inayi dare da rana, bana zama jikina babu alwala to sannan na samu lpia fa,
rigimar gidannan da masifar mero bata qaro ba saida ta tusa mlm gaba akan saita d'auko 'yarta ta dawo gidan nan, wlh dawowar 'yar tata gidan nan baqaramin gaggarumin wani tashin hankalin ya qara jefa muba, dan tun mlm na mgn harya kai ga ya daina dan masifarta sai Allah kam, kinga zainab nn wlh jininta saman akaifa yake a gidan nan danko jia saida firdausey ta kwada mata bokitin qarfe a goshinta kinga wajen nan sai yau da safe kunburin ya dan sace dan har yanzun da sauran gululun " tayi maganar tana nunawa mmn salis goshin Zainab din da hannunta,
haquri mmn salis taita bawa mmn Zainab din da taketa faman kuka baqincin mero datake qunsa mata kullum a zuciya,
da tsananin tausayin mmn Zainab mmn salis ta dawo gida kuwa ranar, to shine har take tausayin mukhtar dayakai kansa ga wannan mugun ahali gskia kam dole gobe ma taje wajen mamarsa inno taji kotasan da wannan mummunan al'amari, sauke ajiyar zuciya tayi ta d'auki fitilan ta sawo gidan ta dawo cikin daki ta shiga zuciyarta nata mata saqe saqen.
Mukhtar kuwa wani yaro ya tura ya kirawo firdausey dan babu wayar da zai kirata kamar yanda ya saba in yazo.
salis kuwa yana zaune saman dakalin qofan gidan ransa fal takaicin inda abokinsa yazo neman iri, jiyake wata sabuwan tsanar firdausey na lunkuwa a ransa sbd shan gaban mutumun kirki iriyar mukhtar mai tausayin ahalinsa datai.
babu jimawa kuwa saiga yaron da firdausey a gabansa sun fito, sai wani karairaya take.
"hubbi nayi mamaki danaji kaine kazo bakaimun waya ba kuma? cikin murmushi mukhtar yace "Wlh kuwa wayarce ta samu matsala,, ya kauce maganar da cewa ga salis nan ku gaisa tare muke da shi"
da sauri kuwa takai kallon ta ga salis shima kuwa ya watsa mata nasa kallon cikeda q'iyayya, tuni firdausey tasan cewa salis bai son ta da mukhtar mafarin knn shima tai masa waje a cikin zuciyarta ta sanyasa a layin maqiyanta na sahu sahun farko kuwa,
amman kuma dud rashin kunyarta ga mutane sam batta iya yiwa salis sabida wani iriyar mugun shakkunsa takeyi batareda tasan dalilin hakan ba, indai ko hakane na mawaqin nan da yake cewa wanda rai ke ajikinsa na *da sauran kallo*....

Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️

DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️📦👁️
🅿️7️⃣
D auke fuskarsa salis yayi daga kanta batareda yace mata uffan ba.
itace ma tayi na 'yan duniya tace "salis barka da dare"
daurewa yayi ya amsa mata da "yawwa barka" shima kuma ya amsa matanne saboda kada shi mukhtar din yaji babu dad'i ya zamo yaci fuskarta a gabansa kuma, saidai daga haka bai sake cewa komi ba saima duban mukhtar din da yayi yace "abokina bari na qarasa can wajen su mansir nasha atayi kan ka gama"
Ok to shiknn" cewar mukhtar din yana mai juyawa yana cigaba da kallon firdausey zuciyarsa kal farinciki.
"ya mutan gidan suke ne gimbiya ta? cewar mukhtar din yana sake kai dubnsa ga fuskar tata, saida ta dan tabe baki sannan tace suna lpia lau kam, nace miya samu wayan taka ne haka hubbi d'azun naita kira shiru dud hankali na ya tashi na zata wani abunne? kan ya bata amsa saiga Zainab ta fito daga gidan hannunta daukeda wata leda baqa mamanta ta aiketa can bayan layin sune gidan hjy murja.
tana ganinsu ta gaisheda mukhtar har qasa ya kuwa amsa cikim kulawa ta wuce firdausey ta bita da harara kamar ta shaqeta takeji dan gani take wani ladabin yaudarar ne aka turo Zainab din taiwa mukhtar danta burgesa, batasan ita sam zainab ma maza basu gbnta koda anzo nemnta sai mmnta ta matsa snn take zuwa bare harta cusa knta gasu mazan ma. haka zainab ta miqe hanyar da zata danma sauqinta akwai wuta alokacin ko ina lungun fayau yake da hasken wutar nepa.
mukhtar yace " zainab na burgeni firdausey ga kunya sam bata barima ko idanuwa ku had'a da ita yayin mgn.
kusan halinsu day'a da qanena ismail, kuma wlh suma da zasu had'e knsu da sun dace da juna koya kikace,
zaki bamu qanwarki gimbiyar mata?"
yi tayi kamar ma bata jisa ba saima cewa da tayi "nidai dan allah bar wannan zancen miya samu wayar taka amsar danakeson ji knn nidai ynxun gareka"
kai tsaye yace "na siyar da ita ne"
da sauri cikin mamaki take kallonsa tace "bangane hausan bafa? kasiyar kuma kamar yaya knn?

"eh na siyar da itane na siyawa ismail handout sabida bnda kud'i a hannuna gashi kuma dasu zasuyi exam shiyasa"
Wani gululun takaicin baqinciki taji ya tokare mata a maqoshi batadai ce komi ba.
saishi ne yace "ina fatan kema in munyi aure zakiyi ma qanena ismail dud wani gata gimbiya ta kimaidashi qannenki kema kamarni ina mai tabbatar miki in kikai mun hakan kin gamamun komi na rayuwa dan qanena shine farincikin rayuwata banida wani dan uwa sai shi dan haka muna son junanmu sosai fatan kema kuma zaki tayamu qaunar junanmu gimbiya ta?
cikin karfin hali ta furta cewa "eh insha Allah sosai ma kuwa zan taimaka a zumin cinnan naku q'waran gaske"
"yawwa gimbiyar shiyasa kullum kike qara samun fada a zuciyar nan tawa sabida iriyar lailan q'anena abin sona da kike tayani yi" itadai "hmmmm"!! kawai take cewa amman can qasan zuciyarta Allah kadai yasan tsananin takaicin ismail da takeyi, dan ta lura muddin kuwa suna tare da mukhtar tofa bayya mata zancen kowa saina ismail, ismail dai haba,!! ita kam tasan tanada tsananin kishi sosai sam battason taga wani abinda zaisa mukhtar ya had'a sonta da na wani koda kuwa iyayen sa ne, gskia kam tanajin bazata juri hakan ba da sakal wai anbawa mai kaza kai yace da sakal wlh, to itama kuwa hakan take a wajenta.
haka yaita janta da fira tana amsa masa badan dad'i ba dan ranta yagama 6aci da wayar nan tasa da ya sayar dan wani banzan qanensa can.
bai jimaba yai mata sallama ta koma gida sabida sanyin daya fara saukowa.
da suka tashi komawa gida da salis sai suka canza hanya akan wacce sukabi sukazo.
acan gida kuwa ismail harya gama karatunsa ya jima sosai amman baiga yayan nasa ya dawo ba gashi har tara tayi mafarin knn ya fito kai tsaye daga gidan nasu ya nufi qofar gidan mlm zayyanu mai almajirai din, yana zuwa ya ga babu kowa qofan gidan yayi tsaye cikeda mamaki to miya hana yayansa komawa gida da wuri inda yasan sun saba dud dare tare suke fira sannan su kwanta barci gashi shi kuma yanzun hakan barcin ma yakeji.
jingina bayansa yayi jikin bangon gidan yace a fili "to yaya na ina kaje ne? komadai baka zo nan d'inba ne?
yana shirin barin wajen knn saiga
zainab ta dawo zata shiga ciki da sauri ya tsaidata da fad'in
"Assalamu alaikum baiwan Allah" jin neman amincin da zainab taji mutumin yai mata yasata tsayawa ta juyo tareda amsa "ameen waalaikaslm"
"dan Allah tamvayar ki zanyi nace yaya na yazo nan kuwa? kallon rashin fahimta take binsa dashi danta rasa gane waye yayan nasa da yake mgn akai, ita hasalima fa bata sanshi ba danba wai fitowa take sosai ba a anguwar tasu bare tasan kowa da kowa dake cikinta, mukhtar ma ta sanshi ne ta dalilin zuwan da yakeyi gidan nasu.
ganin sa yai cewar takasa fahimtar abunda yake nufi yasashi tunanin laifinsa ne ai dabai mata gwari gwari ba yanda zata gane.
"afuwan" abinda yace knn sannan yaci gaba da fad'in "ina nufin yayana mukhtar yazo wajen yayarki firdausey ne?"
sai lokacin ta gane zanxen nasa tace "eh ina tunanin ma kuma ya tafi dan dana fito d'azun nan na barsu da yaya firdausey din.
har zata wuce ciki yayi saurin cewa "bakiji ba fa"
shi kansa yarasa miyasa ya tsaidata sai sai yasan cewar zuciyarsa na masa kwadayin sake son

ganin fararen idanun matashiyar budurwar sosai.
juyowa tayi, karaf idanunsu suka sarq'e ana juna saida gaban kowanensu ya buga damm!!! sannan cikin kunya zainab ta mayarda kanta qasa jijinta na rawa rawa da batasan miya jaza mata hakan ba a take.
"dan Allah zaki ce kina sona nima innace miki ina sonki? bansan miyasa naji zuciyata ta harbu dake ba dudda ban ta6a ganin kiba sai yau, kawai naji ina sonki ne har qasan raina wlh da gaske nike ki yarda dani, gashi kuma ko sunan ki ban saniba amman har kikayi qoqarin daukemin zuciyata haka urgently?
a kunyace sosai Zainab ta boye fuskarta cikin hijab ita knta taji abunda yaji a zuciyarta tun kallon junansu da sukayin nan nan take, to mike nn hkn? itama tana sonsa knn?
Jitayi yasaki Murmushi yace " ashe rabo ya tasoni gada gida neman yayana wajen gimbiyarsa ashe nima da rabon nayi gamdakatar da tawa sarauniyar kyawawan a wannan kyakkyawan daren knn? da sauri zainab tanufi cikin gida dan wata sabuwan kunyar tasa ke qara shigarta intaji kalaman bakin nasa zuwa gareta.
da sauri yace "dan girman Allah ki tsaya kiji" cakk kuwa ta tsaya daga inda take kuwa baifi ta qara taku 4 ba tayi cikin gidansu ba.
har inda take yazo ya tsaya sannan yace " kibani amsa dan Allah ko na samu na zauna lpia da zuciyar nan tawa yau" kuma dan girman Allah ki fada mun sunani nidai sunana Ismail qanen mukhtar saurayin yayanki firdausey, a tsananin kunyace tace "sunana zainab maganar amsar ka kuma ka bari sai nan da jibi ka dawo kaji" daga haka ta ruga da gudu ta shige cikin gidansu ya bita da kallon murmushi shi knsa yasan ya samu karbuwa sosai a zuciyar zainab kawai da iriyar abinnan ne na mata masu fulako na maimakon a baka amsa kai tsaye sai an wainaka sannan,
daqyar yabar wajen fuskarsa qunshe da murmushi na shima yai yayi budurwa Lallaikm yaya zakasha labari yau.
zainab da gudu ta fad'a bisa tabarmar dake shinfede qasan dakinsu tana sauke nunfashi maman kuwa cewa take "ke zainaba lafiyanki lau kuwa?
da sauri zainab ta daidaita nutsuwarta ta dubi maman tace
"laa babu komi mama, " a'a Zainab indai da wani abun fad'a mun kinsan yanzun babu sama da ni wanda zakiyi maganar sirri dake dashi dan haka ki fad'a mun" saddar da kanta Zainab tayi qasa cikin kunya tasake cewa " to mama ki bari sai abun ya daidaitu zakiji koma miye" tana gama fad'in hakan tayi kuryan dakinsu da sauri,
murmushi mama Jameela tayi kawai a zuciyarta tace " to Allah shi tabbatar da mafi kyawun alherin " sai kawai taji daga bakin qofar dakin nata ance "mtsss muna funci dai uwa da 'ya matsiyatan kawai baku iya koman kuba face munafurci a d'aki"
muryan firdausey knn da mama Jameela taji sai lokacin tayi saurin kallo bakin qofa taga wucewarta tabita da kallo wato yanzun ma harda la6e ake masu kenn?
"Allah shi kyauta muku" cewar mama Jameela taci gaba da goge kayansu.
firdausey kuwa tana shiga dakinsu saman cinyar meron tsimbe uwarta ta kwanta tana faman zage zage mero tace "miya faru ke kuma? "nida wadannan marassa mutuncin mutanen mana mama, wai dan tsabar iskanci d'azun muna waje sanda mukhtar yazo saiga wannan shegiyar yarinyar zainab ta fito tawani maqe wannan mummunan qaraman muryan tata da wannan shegunayen farin idon nata tana wani yin rawa dasu take gaida mukhtar har yana wani yabawa

da ita shikuma"
mero ta zabura tace "kam uban malhwar hular mlm zayyanu,, kujimin 'yar iskar yarinya hasararriya, toke kuma dan ubanki daya haifeki uwar wa tasa baki dauke mata haske ba (mari) a lokacin? firdausey tace "haba kekuwa mama yaya zan mareta a gabansa? ai saiya gasgasta gaakiyar rashin mutuncin namu da mutane keta fad'a masa ay ko? meron tayi shiru tace "kumafa hakane kinyi dubara kuma, abarma wannan zancen matsiyatan ni yanzun, miya baki yau shi mukhtar din dayazo?
tsuke baki tayi tace
"ke mama wlh kin cika son abin duniya da yawa Allah kuwa (kuji rashin tarbiya d'a ya iya furtawa uwarsa wannan mummunan kalma hankali kwance.
nikam nace duniya dai firdausey)
daq'uwa mero tai mata tace "dan uwariyonki waye bai son alheri koya baki kin b'oye dan nasanki da mugun hali?"
"nifa wlh mama babu wani abunda ya bani ki yarda man, ni haushinsa ma naji wai d'azun yaje ya saida wayarsa ya siyawa qanensa handout wlh mama bakiji ba kamar na kashe kaina naji sanda yake fad'a mun abinnan,
mama mero tace
"ki iya takunki fa firdausey kada ki kuskura ki nuna masa kina jin zafin alherin da yakewa wani nasa dan ina mai tabbatar miki zaki rasashi yanda na fahimci mukhtar bai daukar tozarci ga wani bare kuma ahalinsa ma, dan haka kiyi musu kwantan 6auna har mu samu ayi auren kinga daga nan komi kikayi dai dai da kene fatan kin fahimce ni? (kuji mummunan hud'ubar uwa ga 'yarta wacce zatakai gidan miji? Allah tsaremu da iriyar halayen iyayen nan masu 6ata 10 2 bata gyaru ba).
kashewa sukayi da uwar firdausey cikin dariya tace "kai kina masifar wuta mama wallahi kin iya komanki fa"
meron tsimbe tace "ahaf naci duniya ninan da kike gani ba qaramar 'yar bariki bace ninan da kike gani bata wasa bace ko ubanki marigayi wlh shima ya q'arda da halina dan kanya rasu kadanne daga cikin azabobin fitinonina ban kwankwad'a masa yashanye ba, danma ya mutu faqiri matsiyaci babu gadon uwar da yabar mana na arziqi, da yabar mana wani abun aida bnga tsautsayin dazaisa na auri zayyanu ba wlh da gida zan kama naita facaka ta da kud'i na zamo hajjaju dan zuwa mecca wlh akan kari dud hajji"
6ata rai firdausey tayi dan ta tsani zagin da mero kewa ubanta haka nan dudda ya rasun ma bazata shafa masa lpia ba ya samu salama.
lura da 6acin ran firdausey meron tayi tace "tofa an ta6o masu son uba ko? sai kiyi haq'uri ay kinsan dai bakina ba haila ne dashi ba komi yazo kan harshena na kowace iriyar magana ne tofa saina furzosa waje fit nike samun lpia"
"to amman mama inda ya rasu saiki qyalesa ai yamaji dabaqin cikin da kikaita qunza masa kanya rasu, kin korar masa mata da yara har kika d'ora masa hawan jini wanda yakaisa ga faralise ta samesa yana halin hkn ne har ya rasu haba mama ai masifar ta isa haka, dan ni dai gskia da inada wayau ne lokacin banbari kiwa babana haka"
banza mero tai mata taci gaba da cin kwadon tuwonta mai daddawa danshi akayi gidan da dare harda almajirai na mlm din.
"kizo kici abunci shine ya fiye miki da wannan shegen surutun naki marar ma'ana" cewar mama

meron.
"nikam bazanci tuwon mai daddawa ba bakina yaita wari" mero tace "inye sannu d'iyar obama, zakiyi kwanan yunwa knn dan wlh ko sile bazan baki ba ki siyo abinci waje kici"
Firdausey tai komawarta quryan daki ta bude jikkarta ta fiddo wani dan qaramin lemon roba da biscuit tahau cin abinta tana kurbn lemonta hankali kwance.
koda mero ta shigo dakin ta iske saura kad'an lemon da biscuit din ya qare aiko takai musu wafta ta warcesu daga hannun firdausey din tace"dan ubanki ai bake kad'ai zakiji dad'in ba, tayi maganar tana mai tura biscuits din a wawagegen bakinta tana korawa da ruwan lemon ta ce
"anya kuwa firdausey zakiyi jinqai na in kika samu gidan nera kuwa?
"eh man mama ina mai tabbatar miki innayi kud'i kema kinyi su ai, dan sawa zanyi a gina miki qaton gida kema ki fantama a cikinsa.
hararta meron tayi bayan ta tillar da empty din robar tace "au a hakan kina 6oyewa d'akan kina danq'arar dad'i nikuma kin barni can da tuwo mai daudawa zakice hakan?
"wallahil azeemu da gaske nike mama ki yarda dani indai nayi kud'i kuwa zaki shaida hakan, banfa da kowa saike"
murmushin jin dad'i mero tayi dan tasan kimi firdausey ta rantse dashi tofa zatayi abun kuwa.
"yawwa d'iyata aminn to inko haka ne zaa wulaqanci da hura hanci dan tsab mlm zayyanu mai almajirai zai dawo nice mijin shine matar dukknsu suka bushe dariya har suna ta6awa.....

Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📄📄
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️📄👁️
🅿️🚪
M ukhtar kuwa suna rabuwa da salis gida ya wuce, anan qofar gidan yaga babansa da su baba yawale maqotan su, saida ya durqusa ya gaishesu sannan ya wuce ciki,, kai tsaye dakin su ya wuce ganin baiga qanen nasa ba yasashi tunanin koyana dakin innon tasu mafarin knn yasa kai dakin inno din bayan yayi sallama,
zama yayi ganin inno dun tana salla yasan shafa'e ne take yi, inno kam nada q'oqarin ibada

hatta ta cikin dare kam bata shallaketa saita tashi tayi sallolin dare na nafiloli ta roqi Ubangiji Allah buqatunta na alheri akan mijinta da iyayenta da suka jima da rasuwa da kuma 'ya'yanta da kuma sauran jama'ar musulman Allah.
saida ta sallame ne ta yi lazuminta tareda addu'a sannan ta shafa ta juyo tana duban mukhtar d'in tunkan tace wani abu yayi saurin furta"inno ismail bayya gida ne? inno tace "nikam dai ban saniba mukhtar nida ina cikin d'aki, ka duba d'akin naku kaga bayya ciki ne?
"na duba inno ban gansa ba, " qilan ya dan fita ne to" cewar inno din.
"ga alama dai kam inno bayya gidan dn nima yanzun na shigo"
"halan daga wajen salisun kake taron tuzurai ko?
wai nikam mukhtar har yaushe zakusan kun girma kaida salisu ne har ku ajiye iyali kuma em? yanzufa ba kuba ko ismail da yayi aure da yana nan da iyalensa shima bare ku" mukhtar ya maida kansa qasa yana murmushi yace " nifa inno kin gane ko nafiso na fara samun aiki tukunna in yaso saina fara ginin gida dan matsalar matar da zan aura babu ita inda na sameta harma mun daidaita kanmu"
inno tace "rabani da wani zancen samun aikin nan mukhtar kaji, yanzun kana nufin zakaita zama ne har sai kasamu aiki zakai aure? wannan kam ba maganar ji bace, d'azun da safe bayan fitarku munyi magana nida baffanku cewa wannan d'ayar gonar tasa zai saida ta ya siya muku gidaje wanda aka gina guda biyu 'yan madaidaita, saurin kud'in kuma sai a baku kuyi hidimar biki dasu koba shikenan ba?
cikin sauri mukhtar ya dubi inno yace
"amman inno baffa zai siyarda gonansa tomi zai kama kuma? inda yanzun dai wannan gonar ita kad'aice tai mana saura fa"
 Inno tace "mun tattauna akan wannan zancen shima, kaga ai munada garken awaki da raguna da kuma tumaki ko?, to akansu zai koma kasuwanci dud ran kasuwa yana kaiwa yana siyar da jariran da suke haifa insun tasa fatan ka fahimce ni?"
girgiza kai mukhtar yayi, matuqa gaya yaji dad'in hakan a ransa koba komi zai rayu da firdauseyn sa nan bada jimawa ba ya mallaketa mallaka kuwa ta har abada, kuma itama yasan zataji dad'i sosai inya fad'a mata manya zasu shigo cikin lamarin nasu.
dan haka cikin kunya ya ce "inno mun gode to Allah shi saka muku da alheri akan iriyar wnn kyautatawa da kuke mana muma kuma Allah shi azurtamu mu dad'ad'a muku fiye da yanda kuma kukai mana, Allah kuma shi jiqan iyaye"
cikin murmushi inno take furta "aminn, shima in ismail din ya dawo saika shaida masa hakan shima daganan in yanada wacce yakeson kaga da ya gama qarashe jarabawar makarantar sai a had'a ayi bikin naku lokaci day'a a huta, ko muma ma samu muga jikokin namu kafin muyi qaura daga duniyar,
jikin mukhtar yayi sanyi jin maganar da inno tai na mutuwa, dan haka sai yace"inno kikasan ma komu rigaki tafiyan ma? , Murmushi inno tai tace "kayya dai mukhtar babu wanda yasan *gawar fari* ay tsakaninmu, fatanmu dai Allah yasa mu cika da kyau da imani,,
sai lokacin mukhtar yasaki ransa yace "aminn inno,, amman ban tunanin ismail nada budurwa dan sai nikega ma tsoron matan yake bai iya musu mgn ma inno"
murmushi inno tai tace "miyasa kace baida budurwa to? yace "da kuwa yanada da nine mutum na farko da zan sani inno" dariya inno tai tace
"hmm komi zai iya canzawa lokaci day'a mukhtar,

kai bagashi kaima da banyi tsammani kanada budurwar ba daga ta6oka da zancen aure har kayi azarbabin fiddota to bare shi ma saurayi mai quruciya bisaga kai tuzuru?"
dariyar kunya kawai mukhtar yayi yace "baffa ya ta6a ganinmu wajen gidansu rannan amman na boye a ranan amman kuma jikina ya bani ya ganni inno fa shareware kawai yayi" yayi maganar yana 'yar dariya itama inno dariyar take sai daga bisani ta dubesa tace "ince kai wacce kakeson auren nan kusa take dai ko?"
"eh inno nan qasan layinmu take ma ay, yarinyar gidan mlm zayyanu mai almajirai ce ma ai" Inno tace "to to af kaddai ince Zainab d'iyar jameela,?
kai amman ko kayi sa'ar mace mai tarbiyya Allah yasa alheri..... "aa inno bafa ita bace,, mukhtar ya katse inno da fad'in hakan, tace "ikon Allah, tofa wacece a gidan knn? "
yace "inno d'iyar matar mlm zayyanu ce ita sunanta firdausey mamanta kuma meron tsimbe ake ce mata, da ita tazo gidan mlm zayyanu din dayake baban yarinyar ya rasu."
cikin tsananin fad'uwan gaba inno tace "mukhtar???! meron tsimbe fa kace?! amaryar mlm zayyanu mai almajirai? wannan matar da kowa yasan halin rashin kirkinta shine zaka jajibowa kanka iriyar wannan *babbar annoba* haka? to nikam dai ban yarda ba ban lamunce ba kamaji na fad'a maka kafita harkan wadannan mutanen marasa mutunci dan haka maza tashi ka bani waje kuma mlm zai shigo saina fad'a masa halinda kakeson tsoma kanka muma kuma ka tsoma mu a ciki wanda ba mai 6ullewa bane.
haka mukhtar ya miqe fuskarsa taf taf da hawaye ransa na masa zafi yabar dakin ya shiga d'akinsu, kwanciya yayi zuciyar sa na cewa "hoooo kaiko mukhtar miyajaka yin abinda har ran mahaifiyarka ya 6aci akan wata mace wacce batasan dukkanin d'awainiyar da mamarka tai dakai ba tun kana cikin ciki har zuwa sanda ta haifeka itadai kawai ta ganka da girman kane har kuka fara soyayya.
to kayi gaggawar samarwa kanka mafita,, a fili ya furta "kiyi haquri firdausey kiyi haquri na barki na barki kiyi rayu.... jiyayi an dafa sa ta baya,
da sauri ya goge hawayen da sukayi nasarar zuraro masa a kuncinsa guda day'a kuma yayi shiru.
Ismail ya zauna gefensa fuskarsa wacce ke ciki da farinciki amman ganin yanda yayan nasa keta sabbatun damuwa ne yasashi jin jikinsa yayi sanyi zuciyar sa nai masa babu dad'i kwata2.
"mike damunka yayana" ismail ya tambayesa,, amman sai ganin mukhtar yayi ya qaqalo wani sanyayyen murmushi yace "babu komi qanena ina ka tafi ne inata nemanka dana dawo,, girgiza masa kai ismail yayi yace "a'a yaya mukhtar dud yanda akayi akwai abinda ya faru dan girman Allah ka fad'amun mike damunka yaya na, wlh zuciyata har bugawa take ganin hawayen daka share a fuskarka yanzun" runtse idanunsa mukhtar yayi yajawo dan uwan nasa ismail yana firarda qwalla, rungume juna sukayi cikin rawar murya mukhtar yace "q'anena inno bata amince mun na auri firdausey ba kuma ni na haqura da ita koda kuwa son ta zai zama ajali na kuwa bazan ta6a bujirewa inno ba wannan alqawali ne"
da sauri ismail ya janye jikinsa yana duban yayan nasa sannan yace"kuma baffa yasan da hakan? gyad'a kai mukhtar yayi yace "a'a bai basani ba" miqewa tsaye ismail yayi yace bari ma dawo yaya" da sauri mukhtar ya jawo hannunsa yace "ina zaka qanena kuma?
"yaya wajen baffa zanje in durqusa gabansa na roqesa akan ya lallashi inno tabarka ka auri za6in zuciyarka" murmushi mukhtar ya qaqalo yace "zauna nan qanena kaji" bayan ya zauna yasake dubnsa yace "qanena kaga inkajewa baffa da zancen nan inno zatai tunanin bata isa

damu ba inda gashi mun kaita qara wajen baffa ko? shiru ismail yayi zuwa can yace "hakane yaya to kaikuma fa" Murmushi mukhtar yayi yace " mu kwanta hakanan qanena barci nikeji gobe in AllAh ya kaimu saimu yi maganar ko"
dubnsa Ismail yayi yace idan kuma har goben tayi baka bari mun qara tattauna maganar ba tofa sai nayi fushi dakai na tsawon minti day'a yaya" dariyan qarfin hali sukayi dukknsu bayan sun riqe hannun juna alamun amincewa.
badon yasoba ismail ya kwanta saman shimfidarsa shima mukhtar kwanciya yayi, daman yayi hakanne dan yasamu yayi kukansa a 6oye koya samu radadin zuciyarsa tai masa sauqi.
haka suka kwanta barci zuciyar kowa na masa saqe saqe.
washe gari dukkansu suna dakin inno bayan sun gama karin safe kamar yanda suka saba har zasu tashi suje su shirya baffa ya dubesu yace " ku koma ku zauna zamuyi magana daku"
kowanne saida gabansa ya fadi tsakanin ismail da mukhtar, musamman ma mukhtar da yasan komi ma dai za'ace tofa akan sane baffa zaiyi maganar.!

Xexen Fasaha.
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️📦👁️
🅿️📱
S aida baffa ya d'an yi shirun daq'iqa biyu sannan ya sake duban kowa dake wajen da duba, sannan daga qarshe ya tsaida fuskarsa kan mukhtar yace
"mukhtar kana jina kuwa? cikin mummunan fad'uwan da gaban mukhtar d'in keyi yace " eh baffa ina jinka"
 baffa yace jia da na shigo da dare innonka ta fad'a mun maganar da kukai da ita gameda matar da kake so zaka aura hakane?
"eh baffa hakane munyi maganar da inno jian har ranta ya 6aci wanda hakan yasa ban samu barcin kirki ba sabida ban so ace nine sanadin 6acin ran nata akan yarinyar dan haka na yanke hukunci na fad'a muku cewa na haqura na janye daga batun nawa, ya dubi inno yace cikin rawar murya

"inno kiyi haquri ki yafemun 6acin ranki dana yayi dan girman Allah, kuma nai miki alqawalin ki za6a mun ko wace mace dake duniyar wacce ranki ya kwanta da ita wlh inno komin tsufanta zan aureta domin farincikin ku shine nawa" yana maganar ne wasu hawaye na zuraro masa ta idanunsa.
har cikin ran inno ta qarajin tausayin mukhtar d'in sosai har tayi dana sanin fushin ta data nuna masan ga jiyan dan itama tasan yaranta masu tarbiyya ne koda bata nuna fushinta akan abuba muddin ta nuna qyamarta kan abun tofa sun barsa knn komin sonsu da abun kuwa, muddin ba itace tace si dawo ga abun ba tofa sun basa baya knn badawa ta har abada, jiyayi baffa yace "a'a mukhtar ay bama akaiga hakan ba, tun jia mun gama mgnr da ita kuma Alhamdulilla ta fahimci zancen nawa sosai, na nuna mata shi aure hadin Ubangiji Allah ne tun fil'azal abinda Allah ta qaddaro babu mahani garesa, dan haka inma kace zaka hana yuwuwar abin rabo mai tsanani sai yazo ya kaudaka daga rayuwar ma gaba day'a kuma azo ayi abun bayan ranka, anan ta nuna mun cewar daman ita bawai ta hana bane dan son ranta a'a taguji ne ko ace ita yarinyar ta biyo halin maman tane, to nikuma sai nike nuna mata duda munsan halin ita babar yarinyar batada da kirki kowa ya sani a anguwar nan, to saidai kuma ita yarinyar babu wanda ya ta6a cewa ga wani abun assha datai masa a anguwar nan dan haka wannan nikega ba hujja bane dazata sa ace ba za'a aureta ba, dan muna kyautata zaton cewa bata d'auko halayen maman tata ba, dan haka komi mutane zasu ke fad'a to akan ita maman tane bawai kan yarinyar ba, dan haka itama maman tata muke mata adduar Allah ya shuryeta ya ganar da ita hanya madaidaiciya (niko nace ayya baffa firdausey kam ta rigaya da ta tsotso mugun nono dan haka Allah dai shi kyauta kam, dan abinda Allah yayi kam Annabi kuma sai dai ceto).
mlm Abdullah yaci gaba da cewa "dan haka nike mai shaida maka kaje kaci gaba da neman yarinyar Allah ya sanya albarka a lamarin, kuma insha Allah zanma su yawale magana cikin wannan watan dan muje wajen mariqinta mlm zayyanu din atsaida ranar bikin naku" farinciki kamar kamar me mukhtar yake jinsa a ransa kannewa kawai dai yayi yace "Allah shi qara girma baffa da inno" ismail dayake cikin farinciki shima na ganin komi yayi normal tsakanin iyayen nasu yace "aminnn yaya baffa mun gode inno kema mungode" yayi maganar baki gar kunne.
inno tace "ba godiyarka muke so ba amsarka muke sauraro kaima " cikin mamakin rashin fahimta ismail yace "amsa kuma inno tami? duban mukhtar inno tai tace "au mukhtar badai baka fad'a masa maganar da mukai ba jian nan? cikin kama baki mukhtar yace "ya subhanalla,,,! wlh inno na mance ne,, cikin zuciyar ismail ya kalli yayan nasa yace "ba dole ka mance komi ga jiyan nan ba yaya kaji zancen za'a rabaka da masoyiyanka, nima nan da nike farin shiga har mafarkinta tawa na dingiyi kan gari ya waye bare ku da kuke tsofaffun hannu a harkan.
maganar da mukhtar keyi masa ne yasashi dawowa tunanunsa, mukhtar yace "inno tace in fad'a maka.... nan ya kwashe komi na maganar da sukai jiya da inno akan shima ya kawo tasa matar ahada ayi bikin tare.
Ismail baisan sanda wani Murmushin farinciki ya baibayesa ba, Lallaikm Zainab haske ce a rayuwar sa, daga haduwarsu jia sai batun aure kuma dudda bai ajiye ko sisi ba? lallaikam na maganar mutane da suke cewa hidimar biki temakon Allah ne ga marassa shi zai buda musu ta inda basu tsammani dan albarkacin raya sunnar manzon tsira dan samun zuri'a ta gari wacce zai alfahari dasu ranan gobe.
gurgiza kafadansa mukhtar yayi cikin murmushi yace "kaifa muke sauraro mlm" tuni ismail ya

fara sosa q'eya yace
"na.... nam ya.. yaya ehmm..." sai kuma yayi shiru yakasa mgn kansa na qasa cike da kunya,, zaro idanuwa mukhtar yayi yace "laaaaaa qanena kaddai maganar inno ta zamo gskia kanada budurwa ka boyen"? da sauri ismail ya dubi yayan nasa yace"wayyo yaya mukhtar wlh jia kawai muka fara ganin juna da ita fa ka yarda dani ban boye maka ita ba"
dariya mukhtar dasu baffa sukai masa ganin yanda ya duburce lokaci day'a.
tsaida murmushin fiskarsa mukhtar ya dan rage ya qara duban ismail din yace "naji to amman ka bawasu inna bayani akai to dan su fahimta a ina ne ita ahalin yarinyar yake ko?
cikin kunya gamida saddar da kai qasa ismail yace "eh to ku nimadai ku bani kwana biyun kamar yanda nima tace mun in bata kwana biyu sannan na dawo naji amsar amincewar ta gareni, sannan kuma 'yar nan anguwar ce kuma zainab qanwar firdausey ta gidan mlm zayyanu mai almajirai d'iyarsan"
ay yana gama fad'in hakan ya tashi ya gudu d'akinsu cikin kunya shi dariya ma kunyar tasa taci gaba da basu a haka mukhtar ya biyosa dakin ya iskesa zaune sai murmushi yake, bayan mukhtar ya zauna gefensa ne yace "amman dai qanena indai haka ne kaima to kayi dacen tsarkakakkar mata ta q'warai, dan ni ganau ne ba juyau ba akan tarbiyya ta zainab, kuma nasan koda tace makan ka bari nn da kwana biyu ka dawo nasan kunya ce ta hanata baka amsa nan take, amman ai qanena yanda ya had'un nan babu wata yarinya wacce zai nuna yana so taqi amunce masa ko?"
murmushi ismail yayi yace "kaima indai batun haduwa ne da gayu ai ban kai yakai ba yayana"
Murmushi mukhtar yayi yace "mu tashi mu tafi dai kada time ya qure mana danni yau inada aiki sosai ma" kwanciya yaga ismail yayi harda jawo malullubi yace "nikam yaya sanyin safiyan nan bada niba yau, dan yau banda exam sai
2:pm."
"ayya qanena kace yau sanyin nan zai qara mun yawa inna fita, dan koba komi indai muna tare dakai sai na kanji sanyin nan ya ragemun yanda kasan ana lullu6eni haka nikeji kuma nasan hakan ba komi bane yajazasa face jinina dake gudana tareda matuqar qaunar qanena shiyasa".
Zumbur kuwa ismail ya yakice mayafin tareda miqewa tsaye yace "muje na rakaka yaya, bai jira komi ba ya fice mukhtar yabiyo bayansa har suka fito tsakar gida mukhtar ya leqa dakin inno yayi musu sallaman saiya dawo su kuwa suka bisa da adduar Allah temaka adawo lpia. sun fara tafia a hanya mukhtar ya lura da yanda tsigar jikin qanen nasa ke tashi sabida sanyi sakamakon wata riga marar hannu da ya ke a jikinsa, yarasa yanda zai masa yasan koda yace ya koma gida bazai koma ba inda yace har wajen aikin nasu zai kaisa ma, gashi kuma yasan qanen nasa da tsananin jin sanyi dole ya gaqura har saida suka isa wajen aikin nasu suka tarar da oga daniel da wasu sauran ma'aikata rsirarru dan yanzun ake ta zuwa ko salis ma kansa bai iso ba.
shima ismail gaisheda ogan yayi cikin ladabi kamar yanda yaga yayan nasa yayi har zasu wuce oga daniel daketa kallon ismail cikin mamaki ganin tsabar kamarsa da mukhtar sun koma masa ma tamka
'yan tagwaye dan bada wani abi sosai mukhtar din ya d'ara ismail ga tsawo ba,
oga yace "ahh mukhtaru wannan brother naki ne ko?
cikin murmushi mukhtar yace "yes oga" oga daniel yace "bamta6a gani nasa ba kuma to,
mukhtar yace "hakane oga dayake yana zuwa school ne amman yanzun haka dhis month ne

suke yin final year nasu a school din"
dubn ismail oga daniel yayi yace "ok no problem amman mi dai hana qane nakan nan shima yajo nan muna aiki tale dashi muna bashi albashi nasa in ya gama jalabawan nasa?
cikin tsananin farinciki mukhtar yace "ok thankyu sir thankyu,, shima ismail yai ma oga godia sannan suka jiya suka bar oga din yana cigaba da aikin sa na seta body na wata mota da yake gyara.
har inda su mukhtar suke aikinsu sukaje sannan cikin fara'a mukhtar yace "kaga amfanin adduar iyayenmu akan mu ko q'anena? kaga zuwanka alheri ni anan inda kaima gashi ka samu aikin kamawa, cikin murmushi ismail yace "hakane yaya na shiyasa kullum muma muke masu addu'a kamar yanda suke mana, amman yaya burina a rayuwa shine inganni a class ina koyar da students lesson wato teacing to kuma gashi ban samu ba inda na samu wani aikin" yaqarashe maganar fuskarsa tadan canza,, dafasa kad'an mukhtar yayi yace " wannan dinma daka samu ka godewa Allah q'anena, dan wlh wani ma Yana cen bai samu iriyar wannan dinba, batun son aikin teacher naka ni kamanta buri na ne? kallonsa ismail yayi a ransa ya tunano tun suna qananu kowanen su yakan cewa itayensu ga abinda yakeson zama inya girma, iyayen sukan fara da tamvayar yayan nasa mukhtar akan wane buri ne dashi na aiki idan ya girma, saiyace shi burinsa inya girma tasami aikin government yagansa a babban office nasa yana aiki tareda samun albashi maqudai wanda zai dinga kai su baffa da inno mecca cikin jirginsa da ya siya domin su da qanensa.
shikuma ismail saiyace " nikuma baffa so nike inna girma burina shine na zama malamin makarantar boko, nima inga ina koyarwa kamar yanda malamin mu ke koya mana yayinda yake mana rubutu da alli ga allo, insun fad'i hakan iyayen kan dinga bunsu da adduar cikan burin nasu na alheri ga rayuwa.
ta6asanda mukhtar yayone ya maidosa daga d'an balaguron tafiyar tunanin da yayi, ya sake maimaita masa da cewar " kamance ne q'anena? girgiza kai ismail yayi yace "ban mance burinka ba kaima yaya" mukhtar yace "to danmi zamu zauna babu abinyi alhalin Allah ya bamu wani? kawai kazo ka fara koyon aikin da zaman da zakai tayi in yaso kana aikin kana kai takardunka neman aikin teacing din a haka saikaga Allah yasa an dace wataran kamar yanda nima ban fidda tsammani ba, kaga daga zarar mun samu offer ta samun aikin aikaga sai mi saki wannan mu tafi can koya ka gani q'anena?"
miqa masa dunqulallen hannun sa ismail yayi shima mukhtar ya miqa masa nasa sukai 🤜🤛ta'adar su sannan daga bisani suka cafke hannun juna🤝sukai musabaha, cikin dariyar farinciki ismail yake cewa "hmm✔idear yaya na,, dariya mukhtar yayi shima baice komi ba ya cire jibgegiyar rigar sanyin dake jikinsa ya tsaya dagashi sai singlet kawai sai 'yar rigar aikinsu dake saman singlet din kawai.
mukhtar yayi hakanne danya kare qanen nasa daga sanyin daya lura yana addabarsa sakamakon qanqame jikinsa dayaga yanata yi tun d'azun, shi ya gwammace sanyin yai masa koma miye ajiki dadai ya ta6a lafiyar qanen nasa dan haka gudun kada ismail ya zargi wani abu ya sashi cewar "q'anena ka tafimin da wannan sweater din tawa gida ka ajuyemun dan banjin dad'in aiki da ita sabida nauyi" cikin tsananin mamaki ismail yace "to yaya yakuma zakayi da sanyi?
konaje gida na d'auko maka tawa qaraman wannan ne kasa? "
"a'a q'anena hakanma yayi ai, yanzun dai zan yi aiki kaje gida haka, Allah sarki dudda ismail

baisan ta kan aikin ba sai yace " to yaya gwadamun yanda kuke aikin nima saina tayaka ko?
d'agowa daga kwance qusan da mukhtar ya zuqunna yafarayi na wata taya ya dubesa yace "hmm kabari in lokacin koyon naka yayi zaka koya kaji ko q'anena? yanzun dai katafi gida dan Allah kaga sanyi fa"
badon ismail yaso ba yasashi furta kalmar "to taya" mukhtar yace "yawwa dan qanen" muryan salis sukaji a bayansu yana cewa "ah yau baqon student mukai knn?"
murmushi ismail yayi cikin girmamawa ya gaisar da salis din ya amsa,ya dan qara jimawa sannan ya wuce gida sakamakon uzzurawar mukhtar da yai akan ya tafin.
bayan tafiyarsa ne mukhtar ya dubi salis dake cin waina da miya wacce yayo musu guzurinta daga gida yace "yau narigaka zuwa abokina"
bai samu salis ya amsa masa ba saida yakai komar wainar cikin bakinsa ya hadiye sannan yace "bismillah fa kasan ban jira nidai Indai akan ciki nane shiyasa kan na fara dumamuqan wadannan qarafan saina cika tumbina tsaf tsaf sannan na q'addamar musu a lafiye wallahi "
mukhtar yace "to nidai kam yanzun bannajin yunwa ci kawai ka ajiyemun nawa sai anjima naci"
salis yace "to lpia lau, nima abinda yasa na taushe hannu bari nai mama ta qarasa ida wainar sannan kuma daga nan na ajiyeta gidanku da mashin dina saida na shiga na gaisar da inno sannan kuma na yo nan".
wani d'an siririn murmushi mukhtar yayi yasan maman salis taje gidan nasu ne dan maganar sa da firdausey, hankali kwance yake tafiyar da aikinsa dan yasan baida matsala ga batun inda baffa ya daidaita komi yau.
hakan kuwa ya farun bayan maman salis sun gaisa da inno nan sukaita labarinsu har ismail ya dawo gida shima ya gaisheta sannan ya wuce dakin su, jiyake kamar ya jawo gobe tazo ko zai samu hankalin sa ya qara kwanciya daganin masoyiyar tasa da kuma samun amsarsa gareta zuwa garesa. sai gab da maman salis zata tafi har inno ta rakota nan tsakar gida sannan ta dubi inno tace
"nace inno daman tambayar ki nike sonyi,,,,,? shin da saninki mukhtar yafara neman auren yarinyar nan kuwah firdausey d'iyar meron tsimbe matar mlm zayyanu mai almajirai ? dudda halin mamanta kuwa marar kyau? bakkwa gudun nan gaba ta haifar muku da tarwatsewar iriyar wannan kyakkyawan ahalin naku mai cike da tsantsan son junanku? to wlh basuda kirki ko kad'an mutanen dan bai dace ace kamar mukhtar mai mutunci da d'a'a yaje neman aure wajen mero ba, ni na d'auki mukhtar kamar salisu ne, dan haka dud wani abu da nasan zai kawo cikas a rayuwar sa gameda danginsa bazan so shiba, shine nace bari nazo naji ta bakinki shin da sanunki koko?"
haq'iqa jikin inno ya qara yin sanyi dajin bayanan ta game da mero, tabbas kuma tasan gskia maman salis ke fad'a, dan mero kam abin gudu ce ga al'umma saboda munanan halayen ta maras kyau wanda babu wanda bai sansu ba kaf anguwar.
to amman kuma yaya zatayi inda har mlm ya amince wa batun an gama mgn?.
tuni zuciyarta ta shiga tunane tunane na anya bazata canza shawara ba kuwa?! daman tunda mukhtar yayi mata maganar auren firdausey tun jiyan nan gaban ta keta faman dukuwa kamar kamarmi, jitake a jikinta kamar wani babban al'amari marar dad'i yakusan kusantowa garesu a rayuwarsu haiq'an,,,,!

Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: . 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️📦👁️
🅿📖
I nno takusan munti uku cikin tunanin mafita maman salis ta ta6ota tace "in kuma kina ganin babu matsala a ganinku to shiknn babu komi Allah sa hakan kuma shi yafi alheri"
har zata wuce inno tayi saurin kamo hannunta tace
"tsaya kiji innar salis, dakatawa tayi tana kallon inno tace " to shikenan ina sauraranki rabi'a"
inno ta girgiza kai tareda sakin qarfaffan ajiyar zuciya sannan tace "maganar da naiwa mlm knn ga jiya gameda hakan wlh, dan nima Allah ne shedata ina matuqr shakkun mero da jinsinta, amman kinsan kowa da tunanunsa, shikuma mlm a inda yake nunawa bamai yi sai Allah, aure nufin Allah ne, dan haka a fawwalawa Allah komi babu abinda zai faru insha Allah, harya ke cewa yaji ai dud abinnan da ake fada gameda ita uwar 'yar a anguwar toshi bai ta6a jin komi dangane da ita yarinyar ba na wani hali marar kyau knta, ga alama wai bata d'auko halin ita mamanta meron ba" kama ha6a mamar salis tayi tace "a ina mlm Abdallah yaji wannan zance na iriyan gskiyar halin yarinyar? ta6 gskia kowa kuwa ya fad'a masa hakan ba shakka bai masa adalci ba ya fad'a masa san ransa ne kawai, amman dai shiknn, ni bazanyi ta jayayya ba inda shi mai gida da kansa ya goyi bayan auran ai babu matsala, Allah kuma ya bada zaman lpiar kamar yanda muke fata d'in, nina wuce sai anjima" daqyar inno ta had'iye wani maq'alallen yawu tace"aminn maman salis ngd sosai saina zagayoki"
ahaka maman salis ta wuce tana mai fatarwa mukhtar d'in zaman lpia a gidan auren nasa idan Allah ya nufi auren nasa da ita firdauseey d'in.
zama inno tayi saman tudunkar d'akin nata dake kusa danasu mukhtar d'in tayi tagumi dan gaba d'aya kwanyarta a tushe take da ga tsoro ga tunani.
Is'mail dake zaune cikin d'aki shima kuma yaji komi da suka tattauna da maman salis, jin shirun da yaji ne ya tabbatas mata da fitar maman salis d'in daga gidan nasu, fitowa yayi shima jikinsa a sanyaye, dan harga Allah yana q'in dud wani abu dazai raba tsakaninsa da d'an uwan nasa komi yeshi kuwa, amman kuma yafi son ganin farincikin d'an uwan nasa akan nasa farincikin, dan haka yasha alwashin bazai ta6a nunawa kowa na gidanba baison auren firdauseey da

yayan nasa danshi kansa yanajin labarai wajen abokansa gameda halayyar firdauseey da mamarta, inda suke cewa masa wlh ba fata ba in ba'ai sa'a tsaf firdauseey da uwarta zasu iya janye musu d'an uwa, danma sauqinta shi mukhtar din bamai kud'i bane aida abinda suke fad'a masa saiyafi hkn, cewar abokan nasa, shiyasa tun lokacin shima jininsa yake shaye ga batun, basaja kawai yake bai bari a gane,
Inna dake zaune saiji tayi an dafa gwiwowinta an zuq'unna gefenta.
duba takai wajen da idanunta, ismail ne yace" inno dud naji komi gameda maganarku da maman salis da wannan zan ce inno kedai kibi mgnr baffa kamar yanda yace insha Allah babu abinda zai faru ga auren nasu sai alheri to muma kuma muna masu fatan hakan inno,dan Allah kuma ki daina damun kanki kan batun" sauke ajiyar zuciya tayi koba komi taji dad'in tunasarwa da d'an nata yai mata ga lamarin, da haka wani sabuwan ajiyar zuciya din ta sake saki ta dubesa sosai cikin fara'a tace "madalla da d'a na gari Ismail, qwarai naji dad'in hkn kuma ngd Allah shiyi maku albarka dai gaba dayan ku" "aminnn inno nima bari naje na karbo littafina wajen nuhu clasmate dina ne so nike na dubasa nima" inno tace shiknn to adawo lpia Allah shi taimaka kuma" haka ya wuce bayan ya zura takalmansa yana fadin aminn inna.
gashi cikin ikon Allah har ranar da zaunab ta dibarwa ismail akan ya dawo tazo, tun safe yaketa zumudi ayi magrib koya tafi, I mukhtar kuwa sai dariya yake masa yana fadin "ina ruwan sabon shiga"
shima dariyar ismail ya mayar yace" baji yaya komi zakace, dan nasan yanda ka saba nima hakan zan saba"
koda magrib tayi yaje wajen Zainab itama cikin kunya ta ke maida masa raddin kaunar da take masa, ay farinciki tuni ya mamaye zuciyar ismail, baibar wajen ba saida ya tabbatas daya qara dasawa zainab tsantsar qaunarsa a ranta, daqyar suka rabu a ranar.
haka ta kasance dud bayan kwana 2 sai yaje zanje, tuni firdauseey ta tseguntawa uwarta mero wai qanen mukhtar ke zuwa wajen zainab, anan uwar ke ce mata "to miye ruwanki? mi na sama yaci bare ya sakowa na qasa? sai ki bari muga iya gudun ruwansu, I qarshenta dai yace zai aureta kuma saimi danya aureta,
ni daman ai nafison matsiyatan suzo nmn aurenta dan na tsani inda Zainab zataje tai aure ta huta ta barki cikin wahala, to qwamma dud ku auri matsiyatan tare inda shima ke kika nacewa ma"
tuni firdauseey ta zunburo baki tana mai dana sanin fad'awa uwar hkn dan gashi itama har ta samu nata rabon wulaqancin, nikam nace kamataddini ta danu ay.
haka rayuwar taita tafiya yanzun mukhtar da Ismail tare suke zuwa zancenma kowa ya ke6e da tasa in lokaci yayi su dawo gida kuma.
tuni har mlm Abdallah yaja abokinsa baba yawale sunje sun kai kudin neman aure ga yaran nasa an kuma saka rana wata 2, dayake yanzun shima ismail d'in yana gama exam d'in ya soma bin yayan nasa zuwa aikin kanikanci yana samun abun rufawa kai asiri, wnda a cikin albashin ne har yakewa Zainab siyayya ta kyaututtuka da dama kamar ynda inno dinsu ke cewa su yawaita alhero, dan ance sadakin so kyauta.
tuni har baffa ya siyarda gonansa ya siyi gidajen 'yayan nasa guda 2 kamar yanda yace, can qarshen layinsu baffa gidajen suke.
har an musu fante dayake bikin Saura mako daya yanzun.
yanzu biki ya rage saura kwana biyu danginsu baffa da inno 'yan yola dud sunzo nan da nan

aka shiga hidimar biki gadan gadan babu kama hannun yaro.
anyi biki lpia an gama lpia amare sun tare a gidajensu,
yau kimanin wata d'aya kenan da bikin nasu,
yau ta kama ranar juma'a ne da safe misalin qarfe 7:50 Am, mukhtar ya gama shiryawa cikin uniform dinsa sauri kawai yake yaje ya karya dan gudun kada mukhtar ya bugo masa waya kanya fito su wuce, yana fita ya tarar da firdauseey din a madafi tagama sheqa kunun gyad'a tana juye wa cikin plastic yaja ya tsaya cikin murmushi yace "amarya bakkya laifi, miqewa tsaye tayi, tayi dariya tace
"badai fita zakaiba baka karya ba, dan tabe baki yayi yace "sauri kawai nike gudun kada ismail ya jira ban fito ba, tabe baki tayi a ranta tace "nina tsani Ismail dinnan wlh kuma ba kowa yaja masa hakan ba face shegiyar yarinyar nn Zainab, amman a fili sai tace "gskia bazaka fita ba sai kayi kalaci" bata jira komi ba ta miqa hannunta ta riqo nasa suka koma d'aki ta zuba masa kunun gyad'a din yasha sosai sannan ya fita waje anan ya iske Ismail d'in waje cikin mamaki yace "ah qanena kana nn ashe? mimakon kamin waya na fito kokuma ka shigo"
murmushi Ismail yayi ya tuna jia daya buga waya firdauseey ta dauka kai tsaye tace " kada ya damar mata miji inya shirya ya fito,lokacin mukhtar din wanka ya shiga baima san an bugo ba, kuma tana gama wayar ta goge kiran.
shiyasa kawai yau yaqi kiran nasa gudun kada a maimaita 'yar gidan jia,, shi bama wannan ba farinciki kawai yake sakamakon kiransu da akayi interview na sabbin malaman makaranta da za'a dauka jia da aka nuno a labarai, haka suna tafia a hnya yake bawa yayan nasa labari, qwarai mukhtar ya matuqar yin farinciki yahau yiwa qanen nasa fatan alheri.
har suka isa gidan su(dayake kullum sai sunje gaida iyayen nasu sannan suke wucewa aiki.) nanma koda su baffa sukaji maganar interview din sun yi masa addua matuqa nan suke cewa kaima mukhtar Allah ya cika maka burunka ns samun aikin d kk son" aminn baffa cewar su mukhtar d'in.
daga nan suka wuce wajen aiki.
cikin ikon Allah ismail yaje interview yakuma samu nasara a inda ya samu aikin koyarwa a wata bsbbar makarantar secondary schcol,
kankace miye tuni harya fara zuwa aikinsa da yake fannin social studes yake koyawa kuma ga albashin nasa har kusan dubu 30 ne zai dunga dauka a lokacin.
wayyo mukhtar yaji dadi harda hawaye dan ganin yanda dad'adden burin qanen nasa Allah ya cika masa shi.
wata biyr knn da fara aikin Ismail, dud inya kwashi albashin sa kuwa komi zai saya na abinci kashi uku yake siyansu komi yawansu da tsadarsu kuwa, kashi daya yakaiwa su baffa kashi daya ya baiwa yayan nasa sannan kuma kashi daya ya ajiye gidansa, yasamu qarfin gwiwar yin hknne daga shawarar da Zainab matarsa ke basa masu kyau na maimakon yadinga basu kudin qwamma yasai musu abinci, harta qara da cewa "kuma teacher (dayake haka take ce masa mlm tunda ya fara koyarda karatu itama)saika dunga bawa yaya mukhtar koda dubu bibbiyu ne bayan ka siya musu abincin dan kaga shima iyalinsa, koba komi yanzun nauyi ya qaru shima inda yanada iyali,
haka Ismail kuma yaji dadin shawarar tata, dan haka saiya bari ma dud inya gama siyayya to kudin da suka rage masa suma uku yake kasasu yabawa su baffa kashi d'aya
mukhtar kashi d'aya shima saiya riqe kashi dayan, da basu amsar kudin dole tasa suke amsa

sakamakon kukan dashi Ismail din ke shirin yi musu in sunyi nufin qin karbar, firdauseey kuwa baqinciki kamar ya kasheta danjin zafin budin da Allah yaiwa Ismail da Zainab qanwar tata dudda iriyar alheran da ismail ke masa kuwa sam batta gani sam bnda huznu babu komi a ranta da'iman hk tk.
ahaka har Ismail ya d'auki shekaru biyu da fara aikinsa na teacher.
yau ta kama ranar litinin da misalin qarfe biyar da rabi na yammacin ranar
da sauri mukhtar ya shigo gidan nasu dan dama yasan ismail na can, yana shiga kuwa ya taras da ismail shida inno da baffa zaune a tabarma suna fira,
yana shigowa ya rungume qanen nasa yace "baffa inno qanens kutayani murna yanzun aka turomin text na anyi accepting dina a matsayin ma'aikacin government a wata babban ma'aikata na fitar da tsirran amfanin gona da sauransu, dan yanzun nan daga can ma nike, sunce takarduna sunyi matuqar kyau sosai, kai qanena kaga ofis din kuwa? ga tv plasma da easy komi baja baja fa, gashi sati mai zuwa sukace zan fara zama kujerar office din nawa dan gudanar da ayyuka. kai alhamdulilla"
tuni ismail ya daka wani tsalle ya qwaqwume yayan nasa yana kukan dad'i yake cewa"dan Allah yaya da gaske? Wayyo ni Allah Alhambdulilla daka cika mana buruknmu a rayuwa, yana maganar yana qwallan murna jikinsa har rawar farinciki yaketa yi.
sosai suka rungume juna suna kukan farinciki.
baffa da inno nan take addua sukaita kwararo musu akan tabbatuwar alheri mai daurewa ga lamarin ayyukan nasu.
sai gashi kuwa sati na zagayowa mukhtar ya d'are kujerarsa ta office ya zauna,cike da adduar iyaye ya fara gudanar da aikinsa cikin nasara da qwarewa...

Kuyi hqr busy nk shiyasa kuka jini shiru,
Ynxunma n smu likaci ne

Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

W asa wasa yau kimanin wata uku knn da fara aikin mukhtar, buhunnan shinkafa dasu kuskus macroni superghety indomi sha'er da dai sauransu haka mukhtar ya cikawa su baffa d'aki dashi,kuma haka shima yaje gidan ismail ya cike masa waje ma'ajiyar abincinsa dasu taff, hatta abokan baffa su baba yawale saida suka shaida da arziq'in mukhtar dan saida yayi musu kyauta suma,
kan kace mi tuni anguwar ta dauka labarin cewar mukhtar yayi kudi,
alherin mukhtar bai yankewa ga jama'a shiyasa kowa zakaji yanda yake yabon kirkinsa a anguwar sukance sam baida qyamar marassa shi kamar yanda sauran masu kud'i sukeyi,, tuni mukhtar ya sabarwa kansa dud ranar juma'a bayan antaso masallaci zakiga ya zauna a qofar gidansu shida ismail yana bada sadaqar Dari biyar biyar yayinda ismail din ke tayasa,, bazai bar wajen ba har sai ya tabbatar da kowa kuwa ya samu sanna.
salis yaji dadi qwarai da arziq'in abokinsa da Allah ya basa shi a cikin dare daya shiyasa shima mukhtar yaso salis din yabar aikin da yake yazo nan ya basa wani aiki ya dungayi a ma'aikatarsu amman sam salis yaqi yarda danshi a ganinsa mutane zasuyi surutu gameda hkn shi bama wannan ba yafiso ya samu aiki da qashin kansa kamar yanda shi mukhtar din ya samu kunga kowa saiya tsaya kan qafafunsa,
dan salis yana tsoron ai masa alafama gudun juyin rayuwa iriyar na mutumin yau. shima yasan bai fidda rai ba, inda shima ay ya bada takardunsa tuntuni cigiyar aiki gun wani qanen mmnsa dake bauci shima ma'aikacin government ne, danma ya riga bayarda cigiyar aikin nasa akan mukhtar daya bayar daga baya,
mukhtar kuwa ganin salis yaqi amince wa hakan ne ya sashi haq'ura dole amman kam yana masa kyaututtuka matuqa dan kaf fadin garin kaduna baida babban aboki sama da salis.
yau lahadi ta kama weekend kowa yana gida babu fita, mukhtar ya na zaune a dakinsa yana faman cike wasu daga cikin takardunsa n office, dan kam gaba daya hankalinsa ya tafi ga wajen lissafin abubuwan da yakeyi, saiga firdauseey ta fito daga quryan daki jikinta sanye da wata atamfa super English ta zauna kusa dashi fuskarta ahad'e ta dubesa tace "yalla6ai ina son magana dakai" bai dago kai ya dubeta ba saida ya ida had'e dukkan calculating din sannan ya kauda document din gefe ya juyo y zuba mata idanunsa yana kallonta cikin wani murmishi, hannunsa yasa ya kamo nata yace "ehm emmm to sarauniyar mata, amman kafin nan wai miye sirrin ne? nike ta jinki zam zam haka kwanan nan?, gashi kuma kin d'anyi haske dudda kalarki choculate color ne amman ta q'ara smooth fa sosai, kodai da ajiyar baby nane anan?" yayi maganar yana goga kuncinsa a saman cikin nata cikin wata fara'a.
ture kansa tayi tace "nidai ba wannan ba dan Allah ka saurareni dan maganar nada muhimmaci sosai,, tuni ya maida nutsuwarsa gaba daya gareta yace
" to ina sauraranki"
saida ta qara bata fuska tace "yanzu dan Allah yalla6ai dud iriyar wannan arziq'in da Allah yai mana yanzu mu ba abin kunya bane aganmu cikin iriyar kalar wannan dandaqaqqen gidan ba? dud gurori a cikin wajensa?
kuma gaskia byn haka ma gidan nan yayi kadan dan inna haihu taya mutane zasu wala a cikinsa ma tukunna dai wai?"

sai lokacin ya yi saurin cewa " oh my god,, are you pregnant my Queen? kinada ciki ne daman baki gaya munba?, yayi maganar cikin mamaki,, wani dan murmushi tayi tace "jia munje asibiti nida mamana sakamakon zuwa danai gida daga naci abinci naita amai kamar zan mutu wlh lokacin shiyasa hankalin maman ya tashi tasa mukaje asibiti a lokacin anan doctor ya min gwaje gwaje har suka tabbar da ciki ne a jikina d'an kimanin wata shida da kwana hud'u"
da sauri mukhtar ya rungume ta yana firda qwallan dad'i tareda godia g Allah da sauri ya ruq'o ta jikinsa yana fadin "firdy na mikeso na miki wanda zaisa kiji dadi dan wannan kyakkyawan albishir da kika zomun dashi?"
cikin kwarkwasa firdauseey ta wani karkace kai tace "nidai kawai inason mubar ckn anguwar talakawan nan mu koma layout da zama inda bb hayaniya can bare su hanani renon baby na cikin pic nutsuwa" sakato mukhtar yayi kawai yana kallonta yace cikin tsabar takaici
"inbar iyayen nawa ina da d'an uwa na to inna bar anguwar?, look bari kiji inke baki son zama kusa da iyayen ki da 'yan uwanki toni inso domin hakan shine bugun numfashi na, kuma wannan gidan da kike cewa bakkya sonsa toni bnda kamarsa a abinso na gida inda kudin mahaifina ya zuba a ciki ya siyamun ba kudi na ba gashi kuma har kin rayu cikinsa dan haka ina alfari da kyautar mahaifa na kima sani i don't go anywhere I swear"!
yayi maganar ransa a d'an bace.
tuni firdauseey tafara matsar kwalla tace "hmn ai nasan daman haka zaka ce kai kenn da an yi maka magana zakace iyaye d'an uwa towaye baida sune?" nan taci gabs da kukanta, wanda a zahiri ba kukan amsar daya bata takeba kukan tsabar baq'inciki take yanda yadamu da iyayensa da d'an uwansa bisaga ita matarsa shine kawai fa faman cin ranta.
"kiyi haquri fiedy na, bawai gidan bane bazan fad'ada saba na gyara no oready dmn na yi magana da masu qaton filin nan na kusa damu akan zan siya kinga saina qara fadada mana gidan namu amman gskia na fad'a miki bazan tashi daga anguwar nan ba, danko wajen aikinmu da sukace munaso a bamu d'aya daga cikin gidajen government mu zauna da fami namu ko kudin mukeso, tonidai gskia kudin na buqata kuma suka turan a account dan nikm bazan bar mahaifata ba ina nan da'iman hayat"
kamar tai kukan baqinciki najin wai anbasa kyautar aljannar duniyar gida amman sabida wannan gajarabils d'in tsoffin ya qiya, q'utawa tayi ta danne 6acin ranta sumburo baki tayi tace "naji to ammanfa to gskia inka tashi gyara mana gdn harda fa benaye nakeso aimana ciki a ko'ina?"
yayi wani guntun murmushi yace
"kada kidamu komi za'ayi dan so nike nasa ayi gyaran dasu baffa ne da Ismail suma a fad'ad'a musu gidajen nasu amasu gyaran zamani suma" tuni wani gululun baqinciki ya sake tokarewa firdauseey maqoshi a karo na barkatai har batasan sanda ta fashe da kuka ba, da gudu tabar wajen ta koma d'aki.
binta yayi ya zauna gefenta yace "mike kuma ske faruwa ne haka wai firdy na?" sam taqi mgn dud nacinsa haka ya haqura ya bar d'akin kai tsaye waje ya fito ya nufi gidansu tun a hnya mutane suketa miqa masa qoqon bararsa mabuqata,
yakance musu su bari saiya fito daga gidansu sannan, yana isa kuwa qofar gidansu ya zaro wayarsa jikin aljihu ya kira ismail babu jimawa ya daga yace "q'anena kana mainhouse namu ne koko? daga can ismail yace "a'a wlh yaya na muna kan hanyar dawowa nema daga hospital yanzun ma haka"

da sauri mukhtar yace "subhanalla waye babu lpia?, baki har kunne Ismail yaketa dariya yace "Zainab ce mukaje anso result wajen doctor yayana"
"result nami knn?, cikin kunya yace "ay ciki ne gareta yaya, da sauri ya kashe wayar waishi kunya, murmushi kawai mukhtar yasaki yarasa yanda akai dud alherin daya samu d'an uwan d'aya to shima dayan babu shakka zai samu kwatan kwacinsa alherin Allah kenan hakan.
cikin gidan nasu ya shiga ya zauna gefen baffa dake kishingid'e a bisan
tabarmar kabarsa yana sauraron radio dinsa.
baffa ya amsa gaisuwar inno ta fito daga d'aki ta zauna saman kujerar qarfe 'yar tsugunno bayan ya gaisheta yace "baffa magana nike so muyi,, baffa yace "to shiknn mukhtar ina sauraron ka" yace "baffa daman in bazaku damu ba zan yi muku gyaran gidannan ne dana Ismail amman baffa nayi magana da mai shagon nan nakusa da gidan namu akan zai siyar mun dashi sai a rushe ginun gidan ayi muku sabon gini na zamani asamu foundation sosai" kan baffa yace wani abu saiga Ismail ya shigo gidan da sallama Zainab na biye a bayansa, bayan sun zauna suka gaisheda su baffa sannan Zainab ta koma dakin inno ta zauna, btatare da yn qasa a gwiwa ba mukhtar ya sake maimaita wa Ismail maganar rusau na gidajen nasu da yake shirin yi, baffa yace "mu wane gini zaka sake yi mana kuma mukhtar bayan wannan? kai dai Allah shiyi albarka kaji ko? tsufanmu da wannan gidan ya dace" yayi maganar cikin fara'a, inno tace gskia dai kam kadai gyarawa dan uwanka danshine d'an zamani mu kuma muna kurkusa da q'abari tsufa ya kawo jiki inamu ina wani kayan qawa na duniya,, hidimar da kake damu ma mun gode Ubangiji Allah shi sanya alheri a arziq'in mai amfani gaku da kuma jama'ar annabi Muhammad SAW ya qara muku bud'i na alheri kuma" dukkansu suka amsa da "aminn mukhtar ya kalli inno yace "dan Allah inno to koda baku yarda na siyi shagon nanba na hade muku dashi to ku bari na gyara muku gidan asa tayils da esi da sauran kayan more rayuwa a ciki dan Allah baffa,, da sauri Ismail yace "hakane dan Allah su baffa ku amince ma burin yaya in bai muku ba a duniyar kukaji dad'i miye amfanin samuwar kud'in?, dan Allah mun roq'eku ku amsa masa da to kada kuce masa a'a karo na biyu"👏🏻
ya qarshe maganar tasa yana mai hada hannuwansa biyu alamun roqonsu.
sauke ajiyar zuciya baffa yayi ya dubi inno tai masa alamun ya karb'a musun, gyaran murya yayi yace "to madalla mungode Allah saka muku da alheransa" cikin jin dad'i q'warai suke amsawa da
"Aminn baffa"
inno ko murmushi kawai takeyi daga nan kuma mukhtar yasake gyara zama yace "kuma baffa hajjin bana hardaku za'aje insha Allah, dan na tsara mana tafiyar ne kaida inno, Ismail da matarsa sai kuma nida firdauseey insha Allah, tuni fara'ar dake fiskar iyayen nasu ta qara qaruwa sukaita zuba musu addua kamar ba gobe, baffa da inno harda qwallan farinciki suka share na ganin cewa ashe sunada rabon taka qasa mai tsarki ta sanadiyyar yaransa lallaikam haka abun yake zakaran da Allah ya nufa da cara ko ana muzuru ana shaho sai yayi.
ai ismail rungume yayansa kawai yayi yana faman kuka kashirb'an yana cewa "dukiyarka kada ta zamo tamu yaya dan Allah ka tsahirta haka" mukhtar ya goge qwallar farinciki shima na ganin yanda yasa iyayensa da d'an uwansa kukan dad'i, shima yace "dukiya ta takuce qanena har abada dan haka koda ran rasata rankatakaf d'inta sabida kyautata muku billaheel azeem bazanji komi ba, dankune raina farinciki na da kuma bugun numfashi da farincikinku nike rayuwa mai dad'i q'anena dan haka kada kadamu,.

kasa mgn Ismail kawai yayi sai dariyar dadi kawai take yana godiya ga Allah haka suma iyayen sukaita godia ga mai sama daya azaurtasu da 'ya'ya masu jinqai.
koda su ismail suka fita daga gidan sakamakon jawo hannun sa da mukhtar yayi inno komawa tai d'aki wajen Zainab shi kuma baffa buta ya dauka ya shiga bayi.
suna fitowa kuwa mukhtar ya iske mutane dafifi qofar gidansu mutane sama da 30 dud mabuqata kuwa, nan ya fiddo bandir na yan dubu dubu ya baiwa Ismail danya tayasa kason, haka suka dinga raba musu kudaden nan wani ya samu dubi biyar wani bakwai wasu takwas har goma in Allah yaci dakai samu zakayi wajen kuwa, mukhtar baibar wajenba saida ya tabbatas da kowa na wajen yasamu sannan. mutane saisa masu albarka suke daga nan kowa ya kama gabansa aljihunsa na nishi na marowa da yayi a iriyar wannan lokaci da aljihun mutane ke rama aisu kam sun godewa allah Allah shi qara bud'a masa, abinda kowa ke fad'a knn.
ashe lokacin da mukhtar suke tsaka da rabon kudin nan meron tsimbe ta wuce zuwa gidan 'yar tata amman sam basu lura da ita ba, dan sabida jama'ar da suka rurrufesu bazai basu damar ganin wanda ya wuce ta hnyar ba, haka mero ta wuce ta isa gidan tana cijen leb'e zuciyarta a hasale cikeda baqincin yanda taga mukhtar ke rabawa al'umma kudade haka kamar bayyaso.
Koda suka bar wajen gidansu salis suka wuce nan mamarsu salis ke cewa ai jia kawunsa wato qanenta dake bauci yakirasa akan maganar aikin daya samar masa amman zai dawo cikin kwanan nan, nanma mukhtar saida ya cikata da kudi taitamurna kuwa dasa alheri daganan suka wuce cikin gari kuma.
Meron tsimbe kuwa a fusace ta bankada qyauren gidan mukhtar ta shiga tana faman qwallawa firdauseey kira da cewa "ke firdauseey ke fiddau kina inane maza fito, ta zauna saman kujerar falon gidan himmm da ita uwa saniya sai bud'a hancina take tana numfarfashi.
da sauri kuma ta miqe jin kakarin da firdauseey keyi daga kewayen waje, can ta nufa kai tsaye kuwa, taraswa tayi firdauseey nata sheqa amai kamar zata amayo da 'yan cikinta a waje saida ta gama tsab sannan suka dawo suka zauna, dubnta mama mero tace "kedai wannan jarababben cikin bnda azabtar dake babu abinda yake, in bazaki iyaba zan kawo miki magani kisha saikiga ya fita salun alin babu wata sauran wahala kuma gareki" yamutsa fuskarta tai tace" kai ina wlh bazai yiyuba mama inason cikin nan kamar raina dan haka kibar zancen baras da shi.
tave baki mero tayi tace" saikije kita kaya ay, ...
ta canza salon maganar da cewa koda yake wannan d'an shine arziq'in mu, inda Allah ya kawosa cikin daula da jin dad'i kinga uban koda kuwa mutuwa yayi to dukiyarsa rankatakaf dunta ta yaron ce kuma muma tamu"
ni yanzun wani qaton gululun baqincikin takaici naji, zuba mata idanuwa firdauseey tayi tace "miya faru mama ne"? Minenema bai faru ba, wai shi dan Allah mukhtar kudin nan da ciwon sadaq'a suka zo masa ne? "miya faru to mama nike tamvayarki fa? mero tace " hmm! ay gashi can qofar gidansu ya tara uwayen jama'a sama da maitan yana basu kud'i shida d'an uwansa sirikin wannan uwar kinbibin ga miji sai bayarwa suke,
Quta wa firdauseey tayi tace hmm to nan mikika ganine mama? baida aiki sai kyautatawa sheggun tsofaffin iyayen nan nasa da d'an uwansa mutane kuwa kullum sai sunzo gidannan wajensa sama da aqilga, hmm wlh mama jia fa ina jinsa yana waya da dare wai ma'aikatarsu ta basu kyautar kujerun mecca mecca har guda 6 wlh mama inaji yace babansa da mmnsa ya

basu kujera 2 sai nidashi 2 sai kuma qanensa da wannan shegiyar Zainab din biyu,, tuni mero ta dafe qirji tareda bugunsa da hannunta baffffff idaninta sun firfito tace "kutumar bala'en kan uban can kayyasa kai!! yo nifa? harda fa zainabu kikace fa? tuni idanun mero suka kawo ruwa jikinta har ciri yake tace 'ca6 to billaheel azeem da sakal, dole asan nayi, taff,, takama hab'a tai shuru, firdauseey tace kuma kinga azumi baifi saura kawana 2 ba a fara kinga knn salla na bada baya za'aje hajji din, kai gskia mama wlh dada yanda zanyi dasai na saki a jerin layin tafiyar nn na fidda matsiyaciyar zainab dinnan a tafiyar nn, d'agowa mero tayi tana huttai tace "to wlh kuwa nagaji da iskancin nan na mukhtar lokaci yayi da zaisan ainahin wacece meron tsimbe!, zaisan kala na, zai kuma san had'a iri dani ba alheri bane dan dud wanda ya had'a alaqarasa damu tofa ya d'ebo ruwan dafa kansa billaheel azeem sai nasa boka na marakusa ya juyar mun da kwanyarsa garemu ya mayarmana dashi bawanmu yazamo sai abinda mukeso zai aiwatar" dariya firdauseey ta kwashe dashi suka kashe tafi da uwar snn tace"dakyau mamana mai maganin kuka na shiyasa banda matsala indai kika fuskanci damuwata, wlh mama ba qaramun baqincikin nake jiba innaga yanawa iyayensa da dan uwansa wannan kyautatawar, kamar na kashesu nakeji dan baida lokacin na sai nasu kullum hk ake tafiya, meron tsimbe tace " hm ravu da matsiyata zasusan ni suka haifawa washi kuwa, waya fad'a musu barno gabas take wakuma yaje lafira yaddawo, babushi wlh, dan haka zaisan ya nemi iri wajen meron tsimbe d'oyin kashi mai gume ko'ina har a kasa rab'ar wajen wallahi nice nan kuwa hkn..

tofa jama'a labari yanzun yahau hnya sosai dankuwa dai gskia
da sauran kallo,
kudai kucigaba da kasance tareda alqalamin
👇
 Xexen Fasaha.

Afuwan ansamu type error dadama a pg 10
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🫁🫁
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

B affa dai shiru yayi bai ce komi ba kuwa sai zuwa can yace"dole ne daman adinga yiwa mutum uzuri a rayuwa mukhtar bare ita da dalilinta ma mai qarfi ne dan saida lpia ake iya aikata komi"
inno ta ce "hakane mlm mudai adduarmu Allah ya sauketa lpia itada Zainabu inda inaga ai dud ma kusan lokaci daya ne haihuwar tasu zai kama"
"aminn dai"
inji baffa.
mukhtar yace
"baffa ko kana da wanda zaka bawa kujarar ne danni bnsnma wanda zan tattago yanzun cikin qurarren lokacin nan ba baiyi latti ba, dadai salis nanan saina kirasa ko exchange na kaya sai muyi a jakana to gashi bai gari kuma"
baffa yace
"to Masha Allah lallikam bawa baya ci sai rabonsa ka bawa babanka yawale itan saimu tafi tare, sai kaje kai masa bayani dan daman bamu jima da rabuwa dashi ba yanzun yana gida".
inno kanta tayiwa baba yawale murna itama,
haka mukhtar yaje yasamu baba yawale a gida yai masa bayanin tafiyarsu mecca nanda lokaci kadan, Allah sarki saiga baba yawale yana kukan farincikin yake shirya wasu
 'yan kayansa yanata yiwa mukhtar addua da fatan gamawa da iyayen sa da duniya lpia da arziq'in mai d'aurewa.
sai gashi babu jimawa baba yawale yagama parking d'insa nan mukhtar yakira yaransa wani daga cikin yaransa na ma'aikatarsu kan yakawo musu mota yanzun zai kaisu airport, kan ado masinger yazo har sungama kimtsawa su baffa da Ismail da zainab nan sukaita shisshiga maqotansu suna yi musu sallama babu jimawa ado yazo nan suka sanya kayansu a booth suma suka shiga motar zuwa camp d'in alhazai,
jama'ar dake tsaye dan ganin tafiyar tasu sukaita d'aga musu hannu tareda fatan alheri har sai da sukaga motar tasu ta 6ace daga titin anguwar tasu sannan suka koma gidajensu cike da sha'awar ahalin.
koda suka isa airport babu jimawa jirginsu yafara yin louding batareda 6ata lokaci ba komi ya kammala cikin yardar Allah suka d'aga zuwa q'asa mai tsarki.
Meron tsimbe kuwa
kamar jira take subar airport d'in dan sune 'yan rakiya, daga nan sukayi shatar mota sai qauyen 'yan maraya.
dole suka cewa mai motar ya ajiyesu nan gefen hnyar da zata sadasu da inda gidan boka marakusa yake dan mota bata isa wajen.
tafiya suke cikin duhuwar tsaunukan kamar ba'a jeba, sunyi tafiya sosai sannan suka fita daga cikin duhuwar bedukan basu qara wata tafiya mai tsawo ba kuwa sai gasu tsaye dai dai bukkar boka marakusa wanda wajen ke kamar bola sakamakon tarin tulin kayan q'azantar dake danq'are a wajen.
meron tsimbe ta dubi 'yar tata tace
"ke anya kuwa dai firdauseey marakusa na nan dan banji alamunsa ba wajen... kan ta qarasa

ida maganar tata sukaji an wani qyqyace musu da wata iriyar qaqqafar dariya mai ban tsoro wacce gaba d'aya saida dajin ya amsa da wata iriyar kuwwa mai tartsatsi,
Ai babu shiri su meron tsimbe suka zube wajen tareda qanqame juna itada firdauseey, sai ihun kuka suke dn harga AllAh saura kad'an subar hayyacinsu dan tsoro da firgici.
a qalla sun d'auki sama da mintuna ashirun da biyar sannan sukaji an tsagaita da dariyar ance "marmaza ku juyo nan dangin shed'an ubana"
ai kuwa babu shiri a gaggauce suka juyo har suna karo da fuskokin juna suka ida zubewa a q'asa sosai sukai zaman dirshan.
wata dariyar ya qara kecewa musu da ita sannan yace "kai ku natsu sosai dan dud wani mutum mai tsoro da kuma d'an 6urbushin imani baya zama inwa d'aya da marakusa bokayen hatsabiban duniya."
dole suka nutsu suka daina kyarman jin muryarsa da kuma gamdakatar da sukayi da mummanar suffarsa marar kasa misiltuwa.
meron tsimbe ta bude baki knn da shirin yi masa bayanin abinda ya kawosu wajen taga ya d'aga mata hannu yace "dakata ja'ira in kika kuskura kika ce uffan gameda abinda ke tafe daku sai d'an tsimbirbirin aljani yaci q'aniyarki kuwa, dan bai son ai masa shisshigi a lamarin kai saqonsa dan dud wanda yazo nan shike fad'a mana matsalarsa bawai sai kai ka fad'a ba da bakinka ba"
tuni meron tsimbe tai saurin datse bakinta har tana datsewa da harshenta wajen rufewa aikuwa babu shiri tasaki wani d'an marayan fitsari daga nan inda take yashe a zaune kamar mai neman gafara,
ga mamakinsu sukaji boka na zayyano musu bayani akan mukhtar a inda yake cewa "ku arna kunzo nan da buqatar a shafe muku tunanin mukhtar mijin firdauseey daga kan ahalinsa da kowa nasa gamida sa musu zazzafar q'iyayyar su a ransa yazamana bazaije wajensu ba da alheri face sherri shima kuma babu wanda zaije wajensa yayi masa wata alfarma, sannan ya zamana sai abunda matarsa ta umarcesa zaiyi koba haka ne buqatar taku ba?"
cikin rawar vaki suka dinga cewa "e... eh e... marakusa hakane"
6at sukaga ya 6ace sun daina ganinsa babu abunda yaci gaba da tashi a wajen kuwa face dariyarsa,wannan karon hatta d'an dake cikin cikin firdauseey saida ya hautsina dan firgita aikuwa ta dafe cikin tana faman "wash2"!!! na azaba, gani sukayi walll!!! bokan ya dawo kamar walqiya ya dawo zaune a inda ya 6ace, hakan yasa tayi saurin danne ciwon jin yana cewa "munan magani d'aya rak muke badawa ba'ai mana jeka ka dawo dan mun yarda da maganinmu"
gani sukayi ya bud'e tafin hannunsa babu komi a cikinsa ya turasa cikin wani makeken kunnensa sai gashi ya fiddo wani ganyen magani qwara daya yana cigava da tofa wasu d'asimai na suddabaru akan ganyen sai sukaga ya wurgasa a sama ya6ace 6at ganyen, amman a haka bokan ya dinga sambatu idanunsa na'a rufe bayan ya dantsi k'asa dake wajen ya watsa ta a sama saiga ganyen nan ya dawo k'ulle cikin wata farar leda d'anye shakab dashi ya juyo ya miqawa firdauseey yace "ungo nan wannan ki tabbatar dud sanda ya dawo qasar nan inda tsumvirbiri yace mana bai nan to dud sanda ya dawo ki tabbatar kinsa masa sanwa da wannan ganyen a ciki yaci sa"
cikin rawar baki firdauseey tace

"to boka ganyen bazai yi komi ba in aka dafa san knn? tsawa ya daka mata yaxe "ke!! kul!! kada ki mana zancen iska anan kinji ko?"
"kayi haquri boka" cewar meron tsimbe tanawa firdauseey daquwa ta cikin gyalenta akan ta kiyaye harshenta. boka yace "wannan ganyen da kike gani koda zaiyi shekara talatin kina sanwa dashi bazai canza ba, abinda yasa nace kiyi masa sanwa dashi kuwa shine sabida maganinki na jikinsa, dazarar kina sanwa dashi a abincinsa tofa sihirin zai dinga bin jikinsa a hankalin harya girmana, yanda zakiyi amfani dashi kuwa shine inya dawo zakiyi masa sanwa dashi tsawon kwana uku to daga nan saiki saka ganyen a cikin masai to nan d'an tsimbirbirin ajlanina zaije ya d'auko manshi ya kawo mun, kinsan shi a wajen najasa yake rayuwa, shikenan faqat aikinki yaqare dan wannan sihirin indai ya cisa saiya dauki tsawon shekaru da yawa bai sakesa ba dazarar kuwa kinga alamun zai sakesa kiyi marmaza ki dawo nan saimu qara baki irinsa,
Hahahahahaha!!! bokan yasake kecewa da wata dariya sannan yace "ku ajiye mana kud'in anan ku wuce arna banza ga wasu cotumers din na nan tafowa" jiki na rawa firdauseey ta bude jikka ta d'auko damen kud'i 'yan dubu dubu guda 3 ta ajiye suka tashi suka bar wajen da tafiya da jan qugu kamar yanda marakusa ya umarcesu dan haka yakeyiwa dud wani wanda yazo kuwa wajensa indai zai tafi to saiya nad'e buje dajan qugu yake varin wurin dud nisansa kuwa gashi kuma wajen da qayoyin gaske shiyasa dud saida suka jimasu ciwo musamma ma firdauseey da batta iya d'aga jikinta sosai sakamakon cikin dake jikinta.
haka suka fito waje suka iso har inda motar taxi dinnan tasu take suka shiga daqyar suka d'osa na dan duwawukan dud sun farfashe musu a hanya dan azaba.
kai tsaye gidan mlm zayyanu mai taxi din nn ya tsaya sakamakon gwada masa matsaya da meron tayi nan suka biyasa suka wuce cikin gidan.
 mlm zayyanu yana salla nn waje suka wucesa kawai suka qarasa cikin gidan. dasauri firdauseey ta dauki bokitin ruwa da kwandon sabulu tayi bayi dan qyanqyamin daudar da ta kwaso takeji a jikinta.
maman zainab ce dake sanwa tsakar gida ta lura da yanda zanen mero ya 6aci da jini daidai inda qayoyin nn suka sossoke mata d'uwayyu tace "yaya meri jini a jikinki kije ki gyara knki" dan ita harga AllAh maman zainab tasa jinin al'ada ne mero keyi basaan na masifa bane kuwa.
dan haka mero tace a fusace"emhem to 'yar sa ido bazan gyaran ba, nace bazan gyaran ba, ah kujimin mata dan allah da kafirin sa idon tsiya, uwarwa yakai kallonki kan d'uwawukan nawa eye ma?"
 "Allah baki haquri" cewar Maman Zainab d'in tana ida kashe wutar girkin danya dafu dama alwala tayi tanufi d'aki dan tayi salla, aiko mero ta bita da cewa"matsitaciya ahaka dai zaki q'are wajen kinbibin tsiya, ke ni nafa lura ma da cewa tun sanda aka ce anba 'yarki kujerar mecca kike tada wa mutane hanci a gidannan to bari kiji billaheel azeem kinyi kad'an kice zaki raina mun wayau a gidan nan, ta dadin abunma a jikin sirikina meccan ta fito matsiyata kawai" itadai ko kallonta maman zainab bata sake yiba fad'i take aranta "AllAh dai shi shiryaku in masu shiryuwar ne, in kuma akasin hakan ne to AllAh yai mana maganinku ya shiga tsakanin na gari da mugu".
koda firdauseey ta fito daga kewaye daqyar tana nishi ta shiga d'akin uwar ta zauna.
itama mairo batayi qasa a gwiba ta shige kewayen ta gyara jikinta sannan ta fito, ta shigo d'akin ta zauna tareda fad'in "washh kai komi zaka nema a duniya saika sha azaba wlh"! firdauseey

data fara samun dama dama a jikinta ta dago kai ta dubi uwar tace "bagashi mun samun ba mama, ai daman ance bayan wuta sai dad'i ay, to ynxun wuyar ta yanke dad'in ne ke zuwa mana"
mero tace "hakane gaskiyarkin nan" firddausy tace "hmm wlh mama jinake uwa inje in dawo dasu nafara gudanar da aikina tun yanzun"
meron ta dago daga shan ruwan faro dinda ta keyi tace "tukunna tukun dai mai saurin kuka ai bazai shiga gasar shad'i ba"
nan suka raba dare basuyi barci ba suna faman maganar yanda al'amarin nasu zai kasance.
tun bayan tafiyar su mukhtar da sati daya nan masu gyaran gidan sukazo fara aikinsu.
yayinda firdauseey tasa aka kwashe kayan gidan duka ta kai d'akin mero ta ajiye mata su dan tace ta bayar dasu dan itama sabbi zata siya mata, masu gyara kuwa basu jirkinta ba akasa mota ta rushe gidan babu wasa aka fara aiki, abinka da angama biyan kudi na komi nan suka hau aiki babuji babu gani wanda ya d'aukesu har tsawon satittika sannan suka kammalasa duka. gidan babu abinda ba'a saba irinsu esi kuwa ko ina kabi ta gidan saika sameta uwa uba kayan dake falon da kuma saman dakunan zaka rantse da allah cewar inka kalli fuskar gidan zuwa gate dinsa isuwa harabar farfajiyar makekiyar barandar su ta wajen gidan harya zuwa dakuna tofa zakace gidajen qasashen waje ne aka d'auko aka ajiye musu shi sak.
wannan kam shi ake kira da a ljannar duniya cewar meron tsimbe da tazo ganin gidan dud tabi ta rud'e ta gigice da santin gidan,bama ita kad'ai ba har 'yan unguwa maganar qanqararren gidan mukhtar sukeyi.
firdauseey tuni ta tare a gidan ko tadan jira alhajin gidan ma ya dawo ta gagara.
kullum mero tana gidan har kwana takeyi tun mlm zayyanu na mata maganar rashin dacewar kwanan nata harya gaji yai shiru sakamakon harshe datake finsa.
kullum kuwa sai firdauseey tayi waya da mukhtar amman koda wasa bata ta6a cewa ya bata su baffa ba su gaisa, kuma shima baima kawo komi a ransa ba inda gani yake insun gaisa dashi kmr sun gaisa dasu baffa din ne. yauda gobe inji yan magana asarar mai kwana har gashi an fara d'auko alhazawa 'yan makka.
dan yau kam tun safe firdauseey ake rawar jikin yin girki dan jirginsu mukhtar gab yake da sauka qasar Nigeria.
bata jimaba ta kammala masa hadaddeyar fridrice dinsa mai hadin coslow na barma a cikinsa, sannan tai masa tuwon shinkafa miyar ganye da kuma lemummuka har kala uku wanda tayi da kanta kuma dud cikin girkin babu wanda batasa masa ganyen maganin nan ba kuwa a ciki, yayin da ta girka wasu baffa suma abuncinsu na daban dudda ya kasance kuwa iri d'aya ne dana mukhtar d'in dandai su banbancin kawai bata sa ganyen maganin nn ba a cikin nasun, abinda kuwa yasa ta girka musu iri d'aya kuwa tasan mukhtar na iya cewan kalar abincinsa shi su baffa zasuci suma.
dan kokadan bai yarda yaci abu mai dadi ba batareda ya kawowa iyayen nasa nasu kason ba qa'idarsa kenan kuwa kullum leda uku yakeyi yakawo daya gidansa daya gidansu daya gidan Ismail cike da kaji yhugurt ice-cream dss.
hakama abincin karin safe da rana da akeyi da nama zu6u zu6u a ciki dole saiyasa an dibar musu yakai musu, hakan kuwa ba qaramin k'onawa firdauseey rai yake qara yiba da kuma tsanarsu baffan da ismail.
biyar dai dai su alhaji mukhtar suka dura airport, bada jimawa ba motar kamfaninsu tazo ta

kwashesu da manyan jikkunansu na tsaravar mecca, gidan su mukhtar din suka sauka gaba d'ayansu. dudda mukhtar nason xuwa yaga firdauseeyn tasa dajin dumin babynsa amman kasa tashi yayi sabida jama'ar dake shigo musu barka da dawowa ciki kuwa harda surukansa maman Zainab da mlm zayyanu.
baba yawale bai jimaba yatafi gida dan hutun gajiyar
hnya, baifi minti biyar ba da fita saiga firdauseey ta shigo gidan cikin shigarta mai kyau wacce ta karb'eta, cikinta kuwa ya fito sosai dan wata matsayi ne take haihuwa, jar atanfa tasa riga da zani sai farin gyale mai ratsin jaja a cikinsa, nan taiwa su baffa barka da dawowa a zuciyarta cewa take "hmmmmm samun farincikinku ya kusan qarewa indai kuwa daga mukhtar ne tsoffin kawai"
ko kallon zainab bataiba bare ta tnka mata babu wanda lura da hakan kuwa wajen face Zainab din da ismail.
haka firdauseey ta ajiye musu abincin tadan jima a gidan sannan ta tashi ta fita ta koma gida.
shi kansa mukhtar yayi mamakin jimawarta gidan nasu dan zai iya q'ilgawa da aurensu zuwan firdauseey gidan basu kwata kwara baufi sau uku ba shima a tsattsaye, itakuwa yana lura da zainab matar ismail kusan dud ran juma'a da alhamus nan take wuni wajen inno, shiyasa ko shaquwa sunfi yi sosai tsakanin zainab da inno akan ita din firdauseey .
yaso ya cusa mata ra'ayinsa na zuwa kaida kai a gidan nasu dan su saba da inno itama sai iai daya lura bataso saiya barta dan babu takurawa a lamarin kowa yagyara dan kansa ay a cewarsa.
ganin baffa ya dubi abinci yakaiwa baba yawale yadawo nan inno da zainab sukai 1 plate baffa da ismail suma suka zuba nasu nan, har mukhtar yayi nufin sanya hannunsa cikin nasu baffa yaci aiko baffa ya dakatar dashi yace dole sai dai yaje can gidnsa yaci nasa wajen matarsa, ganin baffan bada wasa yake masa ba shiyasa ya tashi ya wuce zuwa gidan nasa, shi knsa gidan ba qaramin burgesa yayi ba matiqa gaya daya shiga cikinsa.
saida yaji dumun matarsa da babynsa sosai sosai sannan ya rabu da ita ya miqe tsaye tareda d'aura towel
Wanka kawai yayi tareda salla yana gamawa ya kuma nufi dining table dunsu inda firdauseey ke zaman jiransa yaci abinci , yana zama cikin murmushi ta matso da kujerata kusa da tashi tace.
"hm mikakeson fara ci ne alhajina?" murmushin shima ya mayar mata yace "ni wannan qamshin abuncin yayi dad'i fa hajiyata, fara samun fridrice ma dai to dan yau abincinnan naki mai dad'i yanda nai missing din nan nasa dud yau saina cinyesa rass"
 fari tayi masa da ido tareda sakin 'yar dariya sannan ta fara zuba masa lemo ta ajiye masa agabnsa taresa tura masa plate din Friedrich din kamar yanda yace, babu wata wata ya d'auko spond da nufun fara ci tace "waitt alhajina aiki nane ay ciyar dakai" murmushi yayi ya sakar mata cokalin datake qoqarin kar6a garesa, nan ta d'ebo abuncin tasa masa abaki ya karb'a tareda taunawa a hankalin harda lumshe idanuwa alamun dad'in girkin yayi masa sosai, cup din lemon data hada da ganyen sihirin nan ta d'ora masa abaki nan shima yafara shan lemun, sannan daga bisani ya karb'i cokalin daga hannunta yana mai cigaba da cin abincinsa da kansa ita kuwa sai faman kallonsa take tana sakin murmushi na cin nasarar tasu ga alama...

Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️

👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~Dedicated to my mom Sadeeq hawwass~.

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️ 👁️
🅿️
T a q'arashe maganar cikin huhhutai da mugun dukan qirjinta da hannunta.
firdauseey tace"kwantar da hankalinki mama nasan zamu sameshi yanda mukeso fiye ma da hakan inda har kika sanya boka marakusa a wannan zancen komi yazo ending ay, hmm mukhtar kenan nayi maka alkaqawalin saika manta da muhimmanci iyayenka na tsawon shekaru da dama"
"wannan haka shike fad'i ki q'ara dai kam d'iyata yar albarka mai iriyar hakin uwarta sakk".
nan sukaci gaba da had'a mugun nufin su ga bayin Allan da basuji basu gani ba. mero bata bar gidan ba har saida dare shima dan mukhtar d'in ya dawo gida sannan ta wuce.
hm ko kunya ta baje gidan d'iya suna fira suna shewa kamar qawarta, da yake dai abubuwan mamaki basu ta6a qarewa a duniya akwai masu hkn sosai na budurwar zuciya.
fitar da sukayi d'azun mukhtar da salis wajen camp din alhazai suka je cike wasu forms daga nan kuma sai suka dawo, mukhtar daga nan yaje inda masu ginin zamani suke yai musu bayanin ginin gidan nasa, nan batareda b'ata lokaci ba kuwa suka d'auko masu albums albums na gini mai kyau da tsari tamkar a turai, ismail yace ya zabar masa, nan take kuwa ismail ya zab'ar masa wani tsantsararren ginin gida wanda daga wajensa dud iriyan wannan manyan duwatsun ne masu jone da cut silver tayils, sannan ga wata makekeyar harabar cikin gida, can kuma gudan gefen wajen runfunan tampals tampals har guda 3 ne na saka motoci, sannan aka budo musu shafin tsarin falo.
suma d'akunan falon masu benaye ne hawa kusan biyar a kowane d'aki dake cikin falon, wato bedrooms, gashi kalar fentin gidanma abin a tsaya a kalla ne,
nan take kuwa yasa sukayi masa bill din kudin anan sukai masa shi kuma ya tura musu alert nn take da sharadin bayan tafiyarsu mecca bayan qaramar salla zasuje gidan sufara aiki in yaso kansu dawo an kammala komi, har zasu fito daga ckn ma'aikatar maginan manajan yace oga

banda new fenuters modern ne xaku zuba a iriyan
Wannan gida haka? Mukhtar yace "za'a sanya su amman zan nema ai,,, manager din yace "ai muma nan muna dasu oga, zamuyi maka gini kuma ka siyi funature a gurinmu dud wanda kakeso shi zamu sanya maka a gida harda labulaye yan waje dud muna da".
nan yajasu wajen kuwa, sukai arba da kayakki iriyar na wajennan set set babu kalar da babu na q'asashen waje nanma ismail da kansa ya zab'arwa yayan nasa kayan daki, har set guda biyar, dan d'akunan ne guda biyar a saman benen ga yanda ginin zai kama inkun tuna.
suna dawowa kuma mai hilin kusada gidan Ismail mukhtar yasa a nemo masa dan suyi ciniki sbd ayi gyaran gaba daya sai dai kuma anyi rashin sa'a mutumin yayi tafia zuwa umara ance bama zai dawo ba sai bayan qaramar salla in yayi hajji sannan,
dole mukhtar ya haqura badan yasoba, ammam yaso ayi musu gyaran tare yanda da sundawo meccan kowa zai tare a sabon gidansa.
har saida Ismail ya nuna masa wannan ba abun damuwa bane inda duka saura kwana 2 azumi kenan hajji baifi wata daya da yan kwanaki ba,
dan haka koda mukhtar din ya koma gida yana gwadawa firdauseey yanayin ginin gidan da za'a musu tuni ta mnta da wani fushi da takeyi dashi ta dinga farinciki na dariya ganin qirar gidan dud a layin anguwarsu babu kamarsa a tsarin kyau koda kuwa a fuskar gidan nrma bare ciki, dudda akwai masu kudi da mnyan gidaje a anguwar kuwa amman na mukhtar end ne in aka zo, yanda kasan a qasashen qetare haka gidan yake ciki da waje dan komi na cikinsa dark pink ne, and white colour.
watan alfarma na ramadana ya kama har gashi anfara azumi cikin ikon Allah yau kwana 6 knn da farasa, a lokacin ne kuma aka fara gyara gidansu baffa yayinda suka dawo nan gidan mukhtar din da zama kamar yanda ya roqesu alfamar hakan dan baffak am yaso su koma gidan babban amininsa kuma maqocinsa baba yawale inda matarsa ta rasu shi daya ne a gidan kan aga gyara musu nasun,
koda wasa kuwa firdauseey bata nuna wa iyayen nasa ba mugun halinsu kamar yanda uwar ta gargad'eta akan cewa kada ta nuna musu komi harsai halin hakan ya bada sannan,
inda marakusa bai nan da taje, amman anmata bayani zai dawo garin in angama azumi dan shi bai iya zama garin indai watan ramadana ya kama kuwa, danji yakeyi a jikinsa kamar ana babbakasa da wata iriyar azabtacciyar zazzafar wuta mai q'una ne shiyasa yake had'a 'yan komatsansa yabar gari yakoma can cikin daji sosai a wani yanki2 na tsibirin matsafan yamma bazai yadda yadawo qauyen garinsu ba kuwa har sai an gama azumi sannan yake samun zama lpia.
shiyasa komi su inno sukeso take musu babu gardama sai bayan idanunsu taita tsine musu tana d'ura musu ashir tareda cewar lalatattun tsoffi kawai kunzo kun rashe mana a gida kun hanani rawar gaban hantsi hmmm! dani kuke zancen randa kuka tabvatas da cewa d'anku yabar hannunku ya dawo namu a lokacin ne zakuga samfur samfur na tozarci na d'aya bayan d'aya wlh muna fukai kawai.
ahaka azumin Ramadan yaita tafiya lpia lau cikin ikon Allah har yau gashi an kai na 22 ,a ranar ne kuma aka gama wasu baffa gyaran gidan washe gari kuma suka koma, gida kam Alhamdulilla komi yaji banda tsiya a cikinsa, su baffa su kansu abun ya burgesu kai lallaikan babu wanda yaqi wajen hutu dajin dad'i a duniya koda kuwa mukwan lpia ne kai wajen tsufa.
lokacinda aka shiga goman qarshe kuwa baffa kullum masallaci yake kwana yana adduoe da

roqon Ubangiji Allah akan ya tsare sa da iyalensa da dukkan kullihin musulman Allah yakuma basu lpia mai d'aurewa ga ibadarsa, kullum adduarsa naga daurewar zumuncin 'ya'yan nasa ko bayan ransu kuwa,
a haka aka gama azumi lpia, azumi kuwa na bada baya yan mecca suka fara shirin tafiya, yau litinin kenan
ta kama ana ya gobe za'a tafi to adaren ranar bayan meron tsimbe tazo gidan sunyi magana da d'iyar ta tafi mukhtar na dawowa katsam firdauseey tasa masa kuka wiwi,, da sauri kuwa ya nemi waje ya zauna yaduveta sosai dud a rud'e ga tunaninsa ko ciwon cikinne yad'an juya mata dayake cikin yanzu ya shiga wata na bakwaiy ne yanzun kullum yau ciwo gobe sauqi haka take, ganin yanda ya rude ne yasa ta faki idanunsa tai masa gwalo(ashe daman sun shirya da mero kan zasuje wajen boka namarakusa goben tare kamar yanda ya buqata, inda ya dawo gari tun bayan gama azumin ma.
to tasan kotace masa bazata bisa mecca ba akwai matsala danzai tuhumeta akan dalili shiyasa kawai suka shirya itada uwar akan cewa zata zauna shan magani saboda bata da lpia inyaso daga baya sa koma tareda shin).
haka taci gaba da kukan munafunci kamar gaske, dan kuwa fuskarta tai kacan kacan da hawaye sai da qyar ta bude baki tace
"toni yama za'ayi naje mecca da wannan turtsetsen cikin mai bani wahala wanda ko tafiya ma daqyar nikeyi dud nabi na qara kunbura, ni bnma iya ibada dashi bayan kasan yanda kwananan yake wahalar dani ko yanzun ni bnma lpia ni kadai nasan ciwon da nikeji a jikina"! taqarashe maganar tana taune leb'e da daddafe ciki da qugu kamar gaske, dasauri yace "sannu to fiedy na ko muje asubiti ne yanzun? saurin girgiza masa kai tayi tace "a'a zan koma gida wajen mama ne dan tace zata dinga bani magunguna ina sha har ku dawo nasan zan samu sauq'i lokacin"
cikin rashin jin dadi yace"gida kuma fiedy?!, bakya gudun kije kinashan magungunan dabakan tsarin na likitoci ba aje kuma asamu matsala? muje asibitin zaifi kawai nikega ko?"
cikin murmushin yaudara na q'arfin halin qarya tace "kada ka damu mama tasan kowane magani daya dace mai ciki ta sha su fa to dan inganta lafiyarta indai na hausa ne kuwa dan tasansu kuma ta saidasu a baya ga jama'a da dama"
badan ya sova ya haqura sakamakon matsawa datai kan batun.
washe gari yaje ya fad'awa su baffa komi yaqara da cewa "ni baffa ma bansan wanda zan bawa kujerar tata bama, gashi baifi saura awa biyu ba yanzun jirgin namu ya tashi bafa.....

To dears wa za'a bawa kejerar nan ta mecca din nan datai saura?? Plss bnda rigima ku tsayu ku fidda gwani cikinku😜.

Takun daice wato👇🏻
Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🥡🥡
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️🧻👁️
🅿️1️⃣
saida mukhtar yaci abincin nan kuwa sosai, jin cikinsa na barazanar fashewa dan cikarsa shiyasa ya d'agawa abincin nan qafa fa.
koda ya gama cin abincin kai tsaye gidansu yaje ya kirawo Ismail dasu baffa harda baba yawale sukazo sukaga gidan sukaita sa alheri sannan suka juya, ismail ne kawai yai saura bai tafi ba inda suke tsaye cikin garden din gidan(lambu) suna q'ara yawatawa shida mukhtar din.
ismail yace "wlh yaya gidan nan yayi mun masifar kyau baka jiba, hmmmm Allah kuwa yaya kamar gidan turawa fa, gskia maq'eran gidannan sun baje iya fasahar su kam" mukhtar yayi murmushi sannan yace"wlh qanena in kana son gidan nan zan iya barar maka shi sai nasa ni a gina mun daga baya, danni komi nawa naku ne a rayuwa" da sauri ismail ya zaro idanunsa tareda kama baki cikin mamaki yace"wlh yaya bazan kar6a ba kamaji na rantse"
tuni ismail yayi hanyar gate din gidan da niyar ficewa dan har ga Allah ransa baison haka da mukhtar ke masa, ace ko yaya ya nuna abu yana burgesa indai mallakin yayan nasa ne saiya nemi barar masa shi? wannan ai abun yayi yawa danshi har kunya ma yakeji dudda kuwa yana yayansa, shiyasa kullum son junansu da shaquwa take qara ratsa dukkan zuciyoyinsu gaba daya so zalla bamai algush ba kuwa a ciki.
da sauri mukhtar ya bisa ya riqo hannunsa cikin damuwa yace "miyasa zaka tafi ka barni qanena?!, mukhtar yana gama fadin hakan kuwa take yaji gabansa yayi wani kalar mummunan faduwa kansa kamar yana jujjuya masa da sauri ya dafe kan tareda zuqunnawa wajen yana fadin
"ya salamullahe!,,, innalillahe'wainna'ilaihurraji'un,,, a zabure Ismail ya zube gabansa ya ruqo hannunsa daka saman kan nasa a rude yake cewa "subhanalla subhanalla
"yaya na?
yaya na miya faru dakai ne haka fad'a mun dan Allah, yana maganar muryasa na kyarma, mukhtar kuwa da kansa ya daina juya masa zuwa yanzun,yana dawowa hayyacinsa yaga Ismail zaune a gabansa riqe da hannuwansa da sauri kuwa ya fizge hannunsa daga na ismail din ya miqe tsaye danji dayai bai ma son ganin Ismail a lokacin yafi buqatar yaje ya kwanta ya huta dan har yanzun yanajin ciwo a tsakar kansa, jikinsa ma gaba daya yaji ya saki ya sauya masa kamar ba nasa bama.

ismail shima miqewa yayi yace "yaya fad'a mun mike faruwa dakai dan Allah?"
yayi maganar yana qoqarin sake ruqo hannun mukhtar din, jikin mukhtar na rawa ya goce hannunsa ya dubi ismail fuskarsa a sauye yace"kaje gida qanena kaina namun ciwo zanje nasha magani na d'an kwanta"
"to yaya sannun Ubangiji Allah ya baka lpia,,,, tunkan ma ya ida maganar mukhtar ya wuce baice masa komi ba yana shiga kuwa ya maido qofar tasu ya rufe da qarfi, haka Ismail yabi yayan nasa da kallon tausayi shi kansa yasan gajiya ne kawai ke d'awainiya da yayan nasa, haka dai badan yaso ba yatafi.
wasa wasa kwana uku ras a jere saida firdauseey ta ida ciyar da mukhtar abincin sihirin nan sannan taje ta jefasa a kwaminsu na toilet tareda floshin dinsa yayi qasa.
yanzun haka mukhtar ne zaune shida firdauseey bayan dawowarsa daga office sai faman manne masa take tana masa fira.
zuwa can tace "alhaji na yadace fa ace mamana itama an gina mata gidan zamani haka wanda zata dawo ciki ta zauna ko?'"
cikin fara'a batareda shayin komi ba yace "kin kawo shawara Matata,, to amman awane anguwa ne kike ganin yadace ace za'ai mata ginin ne ta zauna?"
saida tad'an muskuta tareda qara kwanciya sosai a jikinsa tana wani shafa fuskarsa yayinda shi kuma ke shafa cikinta wanda haihuwa yau ko gobe.
jiyayi tace"hmn ay alhajina inma ka tada su baffanka daga gidansu ka gyara mata can ai abun zaifi kusa nikega da ace kuma tai mana nisa in zata zo kuma zata sha wuya, kaga qwamma ace sudinne sukai maka nisan wato su baffa. babu musu mukhtar yace "lallai kumafa wannan gskia ne, yanzun abunda za'ayi zanje nasan yanda zanyi kan maganar gidan su baffan da tashin nasu kuma" farinciki aran firdauseey kamar zai kasheta kuwa, a zuciyarta kuwa tuni tabawa boka marakusa number daya daga cikin hatsabiban bokayen dudduniya dan gaba daya taga hankalin mukhtar yabarsa inba haka ba harya zai yarda yana'a cikin hayyacin sa ya tashi iyayensa daga gidansu, gidan daba mallakinsa ba shi 1?
ta6 lallaikam dole ta sara masa kuwa, cikin murmushi tace "nagode alhajina sosai" 6ata fuska yayi yace "haba matata miye kuma na godia dukiya ta fa dani kanki mallakin kine"
danta tsokanesa tace "amman kuma banji kace komi ba tun dawowarka gameda ginin da zakasa aiwa qanen namu ismail fa?"
gani tayi take yanke fara'ar dake fuskarsa ta gushe gaba dayanta sakamakon ambatar Sunan isma'il da tai"
fuska a daure yace "nafasa bazan yi masa ba, shima ay yana aikinsa na gobnati inyanada buqata ya tara kud'insa shima yaje ya gyara gidan nasa dan nama fad'a masa hakan shima. kaini su baffa mafa kansu nayi dana sanin biya musu mecca da nayi sai naji da kudin na karba na kejerar tasu dana ida shurye shuryen bude gidan mai na da na fara ginawa" firdauseey tace "gskia kam dai asara anyita nima banji dadin faruwan hakan ba alhajina sai dai kuma a kiyaye na gaba dan kuwa dai wannan yarigaya daya faru"
q'utawa mukhtar yayi yace "hmn ai anyi na farko anyi na qarshe dan q'wadala ta bazan qara 6atarwa kan su ba, barima naje na dawo nasan abunda zan musu na rage asara."
(kai jama'a! kuji fa?)
yana gama fad'an hakan kuwa ya miqe ya fice daga falon.
wani iriyan dariya firdauseey tayi har saida dan cikinta ya wuntsula kuwa,

a fili tace "hmnnnn wnda rai ke a jikinsa nada sauran kallo, billaheel azeem su baffa wannan somin ta6i ne kuka soma gani ma daga garemu".
tana gama fad'an hakan ta jawo wayarta takira uwar tata ta sheda mata ai mukhtar yazama nasu harta bata labarin ginin da za'a fara mata itama, karkaso kaji yanda meron tsimbe ta kwarara wani uban ihun farinciki.
Mukhtar kuwa yana fita gidansu ya shiga kai tsaye ya fad'a ko sallama babu, anan ya iske baffa da inno suna zaune tsakar gida suna fira kwalin dabinon ajwad ne a gabansu suke ci.
tsaya musu yayi aka "sannunku su baffa" abunda yace knn ya kama qarfen barandar gidan nasu ya riqe, baffa ya dubesa sosai yace "ah mukhtar ya bazaka zauna ba kai tsaye haka akanmu?, fuskarsa kijin kijin ya dubi baffan yace "eh baffa hakanma yayi dama zuwa nai nace muku zansa a fidda kayanku zuwa gidan isma'il za'a dan d'ora muku wani sabon gyaran ginin ne na sama in yaso aka gama sai ku dawo.
Inno tace "aa mukhtar barmu haka dan iya haka ma ya ishemu wannan gida dai zaman duniya bana q'iyama ba ai yayi"
baffa ya amshe da cewa "gskia ne, dan haka mukhtar kaje mun gode AllAh shiyi albarka mungode hakanma" dai dai mukhtar zaiyi magana saiga isma'il ya shigo gidan yana ganin yayan nasa sai jikinsa ya qara sanyi dan tunawa da abinda ya faru jia, abunda ya faru kuwa jia ne lokacin mukhtar ya dawo office da marecen ranar yana qoqarin tura hancin motarsa gate din gidan nasa dan har ma maigadi ya bude masa wawakeken gate din, to shikuma ismail shima dai dai lokacin d'an aca6a ya saukesa daga mashin dawowarsa kenan ma daga makaranta dayake gyaran makarantar ake musu shiyasa aka maidata ta marece kafin a gama su koma ta safen.
da sauri ya bawa d'an mashin din kudinsa ya qarasa gefen motar mukhtar din yace "waitt yaya, yana maganar ne yana gyara jikkar sa da lititttifansa na koyarwa ke a ciki.
dakatawa mukhtar din yayi Amman sam ko kallon isma'il d'in ma baiba still hanunsa na bisa styarin na motar dukkansu.
Isma'il yace "yaya harka dawo sannunka da dawowa, ya kuma qarfin jikin, kan mukhtar yace wani abu saiga alhaji tanimu yazo wucewa cikin motarsa shima, alhaji tanimu shine mai filin nan na kusa da gidan isma'il wanda mukhtar ya nema a kwanaki akace yaje mecca, dan haka parking yayi kusada motar alhaji mukhtar din daga cikin motar yace "alhaji mukhtar barka da ganinka, sai nan fa alhaji mukhtar yasaki fuskarsa yace "yawwa dai alhaji tanimu ya iyali da harkoki"
"Alhambdulilla haj mukhtar, dama naji ance kana nema nane, haj mukhtar yace "eh a kwanaki ba, akwanaki ne na nemeka dan inason siyen filinka ne, haj muntari yace ok wanne filin kenan nawa daga ciki? haj mukhtar yace nanan anguwar amman yanzun ma na fasa ay"
yana fadin haka kuwa Ismail din ya dubesa da sauri saidai baice komi ba ya maida kansa qasa sakamakon hada idanuwa da sukayi yayan nasa ya hangi wasu abubuwan marassa fasaltuwa a qwayar idanun nasa,
haj tanimu yace "shikenan to babu damuwa" nan sukayi musabaha sunadaga cikin motocin nasu sannan haj tanimu din ya wuce.
a sanyaye isma'il d'in yace "yaya naji kace ka fasa siyen filin kuma? baccin nina fad'a wa haj tanimu din kana nemnsa kuma gashi kagansa kuma kace a'a?
cikin isa da taqama gamida gadara mukhtar yadubi Ismail yace "eh na fasa, dukiyar kace koko

dukiya ta??! dan haka kai tsaye nace bazanyi ba, kaima ai kana aikin kuma kana samun kud'i to kayi da knka, kai bari ma kaji kasan da sanin cewa daga rana mai kamar tayau dinnan kada ka qara tunanin zaka mori qwandala daga cikin arziq'ina, dan bazai yiyuba kudasu baffa da sauran jamaar anguwa kun maidani Baitul mali gidan tatsar kudi ba, dan haka kaji ma ka q'ara ji" yana gama fad'a masa haka ya bad'e isma'il da qurar wajen ya shige gidansa mai gadi kuma ya tura gate d'in gidan ya rufe...
da kallo kawai isma'il ya bisa yana tunanin kuwa anya wannan yayansa ne koko dai wani mai kama dashi ne?!...

by
Xexen Fasaha.
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🥡🥡
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️🥡👁️
🅿️5️⃣
dan haka jikinsa a sanyaye ya wuni yinin ranar.
dan koda ya koma gida Zainab taita tambayarsa akan "mike damunka?" taga jikinsa sukuku haka "bakomi" kawai yake cewa da ita.
mafarin knn daya shigo gidan nasu yanzun yaga yayan nasa abun ya fad'o masa arai.
isma'il yaji baffa yaci gaba da cewa "ida qarasowa isma'il, haka isma'il ya qaraso ya gaida iyayen nasa ya miqawa yayan nasa hannu yana mai cewa "barkadai da warhaka yaya" ga mamakinsu gani sukayi mukhtar din yaqi miqa hannunsa ga isma'il kamar yanda ya buqata, saima kallon su baffa da yayi yace "ku shirya kayanku waje d'aya zan turo yara su fiddasu sukai gidan isma'il d'in"
yana gama fad'an hakan ya juya yai ficewarsa babu ko sai anjimanku. dukkansu da kallon mamaki suke binsa dashi inno tace "isma'il waimi ke damun yayanka ne kwanan nan? yanzunfa yau kwanansa 2 baima leqo mu ya ganmu ba"

baffa yace "nimadai abunda nake gani knn tun dawowarmu na lura kamar ya canza koko yanada damuwar wani abunne yake 6oye mana allahu ta'ala a'alamu"
cikin murmushi isma'il ya zauna cikin son kare d'an uwan nasa wajen iyayensa yace "kuyi haquri baffa ba shakka al'amurrane na rayuwa sukai masa yawa shiyasa bai samun shigowan kai da kai" baffa yace "koyanzun mafa daya ma shigo yana daga tsaye ko gaishemu baiba yake mana zancen tashi daga gida wai zai mana wasu 'yan gyararraki ne komi"
isma'il ya q'ara bin gidan nasu da kallo yace "gyara kuma anan gidan baffa?" ni banga inda keda buqatar saba ay, inno tace "ehem kaimadai kace ay, wai cewa yai ko rufin kwanon asama zaisa asa na gini? shiru isma'il yayi dan shima yanzun baisan inda alqiblan yayan nasa ya dosa ba a taqaice ma. amman dan gudun kada ya goyi bayan su baffan ya zamanto angwasale wa mukhtar bajintar da yake son qara nunawa iyayen nasu na kyautatawa ya sashi kallonsu yace "baffa dan AllAh ku karb'i tayin yaya mukhtar, yana son gyara muku ne a matsayinsa na iyayensa sai naga bayyajin dadin inya yunquro zai muku abu kuma kuna sagar masa da gwiyoyi kuyi haquri baffa dan Allah yayi abinda yace din zai muku"
shiru su baffa sukayi, isma'il yaci gaba da cewa "nasan baza'a d'auki tsawon lokacin nan ba ana aikin bazai kai kamar yanda akai na gyaran gidan ba"
ajiyar zuciya baffa ya sauke yace "ni bawai naqi bane kawai dai bancika son qyale qyalen nan ba na rayuwa wanda zaisa ka rafkana da bautar Ubangiji AllAh cikin lokaci, dan jiya fa saida muka makara isma'il wajen sallar asuba sakamakon wannan abar da aka sanya ta cikin d'aki mai gumi daman ga sanyin da ake"
ya dubi inno yace "yama sunnta?" Inno tace "aaaaa mlm niko yazan san sunnta wannan ai saisu 'yan boko kaga mu kuma da bamu sani ba ai saimu kirata da na'urar d'umama d'aki cikin sanyi ko?
isma'il kuwa baisan sanda ma dariya ta kucce masa ba dan ya fahimci na'urar d'akin su suke mgn wacce mukhtar yasa musu wacce ke bada hot a weather ta sanyi,
sai da qyal dai ya shawo kansu suka yarda, sannan kuma suka wuce zuwa masallaci shida baffan sakamakon kiran sallar magrib da sukaji anayi daga babban masallacin anguwar tasu.
mukhtar kuwa yana fita daga gidan nasu sai yayi wani tunani kawai sai ya nufi gidan alhaju tanimu mai filin nan,
yayi sa'a kuwa ya samesa shida wani abokinsa sunyi sallama zai koma ciki ganin mukhtar din yasa alhaji tanimu tsayawa nan suka qara gaisawa, anan mukhtar ya nuna masa yadai dawo kan maganar filin ne babu b'ata lokaci kuwa sukai ciniki ya siyar masa dashi yaje cikin gida ya d'auko masa takardun filin yai sign ya miqa wa mukhtar ya karba nan ya tura masa kudin ta account dinsa sukai bankwana ya koma cikin gida shi kuma mukhtar ya nufi gidansa.
da daddare ne bayan sallar isha'e nan mukhtar ya miqawa firdauseey takardun filin ta karba tareda dubnsa tace "aa alhajina wannan fa? cikin murmushi yace "fili ne na siya wanda zan ginawa mama sabon gida fil a leda"
cikin jin dadi da salon yaudara tace "ayi haka alhajina kuwa?
kada hidimar tai maka yawa ay, qwamma dai kabata gidan nasu baffa kamar yanda muka tsara"
"kada ki damu ay matata wannan filin ma anan anguwar yake zanma iya cewa baifi gida 7 ba daga nan kafin namu" rungumesa tayi cikun dariyar dadi tace "tnccckyu alhajina,,,,,,,,,, to nace amman kuma maganar gidan naku fa wanda kace gashi canma kasa ana fidda kayan nasu ana

kaiwa gidan Ismail? ya ya knn? basai ka barsun ba inda ka fasa?, dubanta yayi fuskarsa a sauye yace "bazan canza ba dan inada buqatar gidan nima, mizakai da wannan gidan alhaji na to? saida ya kauda fuska daga kanta amman hannunsa na bisa cikinta yna shafawa dan har cikin jinin jikinsa yake qaunar babyn cikin firdauseey, sanda ya sumb'aci cikin sannan yace cikin halin rashin damuwa "sawa zanyi a rushe gidan duknsa inda gidan qato ne babba dan zan had'a sa da wani filaye guda 4 da na siya a bayan gidan sainasa ayi man shaguna nasa 'yan haya a ciki kota nan na huce hushin kud'ina na mecca dana kashe musu"
dariya firdauseey ta qyalqyace da ita sosai dan ta lura kam mukhtar yanzun yayi nisa bayyajin kira, saida ta ruqo hannunsa guda biyun sosai tana shafawa tace "naji dadin hakan sosai kuma nima na goyi da bayan hkan alhaji na dan gskia kam asara bata da dadi koda kuwa ta miyan barci ne bare ta kud'i"!.
miqewa mukhtar yayi yace "mtss bari ma naje naga in sun gama kwashe musu kayan dan gobe goben nan nikeson ganin gidan ya koma fili".
"to alhajina saika dawo saimu tsara yanda za'a ginawa mama nata gidan ko?, yace "eh saina dawo d'in" tace "to adawo lpia amman dan Allah ka tabbatar komi an rakasu baffa dashi can sabon masau kin nasu a gidan isma'il" yace "zan tabbatar miki da hakan kuwa matata"
abinda yace knn ya fice daga falon.
yana isa gidan nasu kuwa dai dai lokacin da masu kai kayan suka fiddo fridge da katifa, yayinda shi isma'il ya fito daga gidan shima yana cewa musu "kai kai ku tsaya banda wnn kayan d'akin ai zaku fitar, inda kun gama fiddo na wajen kubarsu haka kawai, kamar daga sama yaji muryar mukhtar yace "injiwa yace su d'in ba za'a futar dasu ba?,
yadubi isma'il cikin kallon tsanarsa dayake ji cikin ransa fiye da kowane mahaluqi kuwa a duniya yake tambayar tasa, Allah sarki isma'il da sauri ya matso wajen yayan nasa cikin fara'a yace"ah yaya ne yaushe kazo bn gnka ba ai, dan ni ina nan tun lokacin da aka fara fitarda kayan ma" ko kallonsa mukhtar baima qarayi ba bare ya basa amsar tambayarsa kawai saima ya dubi yaran da suke tsaye da kayan yace "kai ku wuce dasu kukai su can inda kuke kaiwa ku tabbatar da cewa ko tsinken tsintsiyar kwakwa nasu bai kwana a gidan nan ba"
sukace "angama oga tuni wasu daga cikin yaran suka koma cikin gidan dan kwaso sauran kayan yayinda wanda suka d'auko fridge da katifansuka fuce dasu gidan isma'il,
isma'il kuwa cewa yake a ransa "miye haka yaya ke fad'a harda cewa koda tsintsiya kada ta kwana saikace ana tada 'yan haya? 'yan hayar ma kuma marassa galihu? dudda haka ismail bai daddaraba da shariyar da yayan nasa yai masa ba yasake kusanto dan uwan nasa yace "yaya amman sai nikega da ba'a fidda kayan d'akin nasu ba inda kace ginin sama kawai za'a d'an dora masu.
kuma yaya... wata mugunyar tsawa mukhtar ya sakarwa isma'il da fadin "kaiiiiii jahilin mutum kaimun shiru bansan jin wasu banzayen kalamanka, wai bakasan cewa
na tsaneka ba?! bansan ganunka?! naqi jinin ace mani kai d'an uwa nane?! nifa zaman nan da ake banqi ace baka cikin doron duniyar nan ba Ismail wlh kona huta ma da ganinka" cikin rawar baki da wasu zafafan hawaye jikinsa na kyarma kyab kyab kyab Ismail yake fad'in "innalillahe'wainna'ilaihurraji'un yaya?! minai maka?! nifa dan uwanka ne?!, dan girman AllAh ka yafeman innai maka wani laifi kayi haquri ka fad'a mun yaya"
cikin dolen wani wulaqantaccen kallo mukhtar ya gewaye isma'il yanufi cikin gidan dasauri isma'il ya riqo hannunsa yace plsss yaya ka tsaya ka saurareni dan Allah kaj.... afusace

mukhtar ya juyo a zafafe ya d'auke isma'il da wani wawan mari a kumatunsa guda biyu sannan yasa qafa ya doki cikinsa saiga isma'il duqe wajen a qasa baki ya fashe jini na futowa ta hancinsa sakamakon ha6on daya sauko masa babu shiri.
cikin azaba ya dafe gefen cikinsa yana salati saida yadauki tsawon minti 15 ahaka sannan ya dago yaga mukhtar din bai wajen ya shiga d'aki yanawa yaran magana akan suyi sauri su qarasa aikin soyake ya kulle gidan, wani ruwan hawaye ne sukaita cigaba da saukowa isma'il aransa yake cewa "mike faruwan ne a rayuwarmu?! yau yayane yakaiga dukana?! abinda bai taba faruwan ba a tsakaninsu tun lokacin yarinta bare yanzun da kowa ya mallakin hankalin kansa yake shirin fara ajiye iyali?!" amman dudda haka isma'il bai sare ba danshi yafi tunanin wani laifi ne yaiwa yayan nasa wanda bai sani ba haryake hukunta sa da wannan iriyar kalar mummunan d'anyen hukunci.
dan haka a daddafe ya qarasa miqewa tsaye ya nufi bakin famfo ya wanke fuskarsa ya nufi dakin harkusa da mukhtar sannan ya tsaya yace yaya k.... afusace mukhtar ya juyo ya kallesa tareda nunasa da yartsa
Yace "wai kai dabban mutum d'in inane??! nace kadaina mun magana sannan kuma kada ka kuskura ka qara kirana da yayanka danni ba yayanka bane, I hate you in my life dan Allah, haba I'm tired,, kai wane iriyar mayen mutum ne nace ka rabu dani kaqi ko? to wlh dud illar danai maka konasa akai maka kai kajawa kanka, kuma koda a hanya ka sake ma ka ganni kada kasake ma ka kalleni dagayau barema ka nuna cewa ka sanni, kuma wannan gidan da kake magana to inma baka sani ba ka sani yanzun, daga yau ba naku bane mallakina ne ni daya na amshesa ne sakamakon in huce hushin asarar takaicin biya muku mecca danai dan haka na karb'i gidan ya zama mallakina wannan saqo ne na baka kaje ka fad'awa su baffa hakan inkuma kunyi musu kuna iya d'aukaka q'ara har kotun q'oli ina nan ina saurarenku.
In kuma sunada buqatar gidan nasu to suzo muyi list na kud'ad'en da na kashe muku dukkanku na mecca ku biyani saiku karbi key d'in gidan.
tuni ismail yaji kansa yafara jujjuya masa dan girman Allah wannan wace iriyar jarabta ce haka ta samesu ne? tamvayarda yakewa kansa knn.
Wai yanzun yayan sane ke masa iriyan wannan cin mutuncin da iyayensu dan yayi kud'i komi ne?
Kuma wai har yake iqirarin cewan yayi garkuwa da gidan su sai anbasa kud'i? Kai duniya ina zaki damu???
girgiza kai yayi bai qara gigin cewa komi ba danya lura da kallon qiyayyar da yayan nasa ke aiko masa dashi zalla ko sirki babu.
a kuma dai dai lokacin ne mukhtar ya gama sallamar yaran da suka gama kwashe kayan tas dai dai da tsinken sakace basu bari ba kuwa kamar yanda shi mukhtar d'in ya umarcesu dasuyi.
suna fita shima isma'il yafara qoqarin fita daga gidan daqyar yake jan qafarsa ma dan mutuwa da jikinsa yayi amman dudda haka saida mukhtar yace"dalla mlm yi sauri ka fitar mun daga gidana zan rufe, juyowa isma'il yayi ya zubawa yayan nasa jajayen idanunsa yarasa mashi amsar dazai basa dan takaici, daqyar yace "yaya yanzun hakan kaga ya fiye maka ka mallaki gidan daba haqqinkaba kai d'aya alhalin su baffa na raye a duniya?
wani banzan qazamin kallo mukhtar yayi masa sannan yace "ok in kanason kaima ka mallaki gidan saikaje ka kashesu baffan inyaso saimu raba gidan tare" zaro idanuwa isma'il yayi waje gabansa na sake bugawa anya kuwa qwalwar yayansa bata samu mix ba da jini ba a cikinta?

dan abubuwan nasa kam it's over yanzun, kuma ya shallake iyaka tareda tunanin manazarci. Abunda yake tambayar ransa kenan yana cigaba da kallon yayan nasa, mukhtar ganin ismail d'in yaqi fita ya tsaya yana kallonsa kawai sai yasa hannuwansa duka buyin ya ida tunkude isma'il d'in k'ofar gida harya gicce qasa tareda d'an matumbili dan faduwar dayai qasa warwas, daqyar ya samu ya miqe da taimakon baba yawale daya iso wajen yanzun, bayan d'agasa dayai tsaye, baba yawale yana fad'in "kai kai subhanalla mukhtar ya haka kuma? Ko kallonsa mukhtar baiba ya dubi isma'il ya nunasa da keys din gidan yace daman tuni batun yauba na lura kana min baqinciki da qyashi gamida hassada a kud'ina da nayi to wannan kuma matsalar kane nidai nasan nai maka nisan da har gaba da abada baza kamo niba,banza matsiyaci kawai, a razane baba yawale har carbaharsa da carpet d'in sallarsa dake hannunsa suna zamewa daga hannunsa zuwa qasa dan daga masallaci suke shida baffa tun bayan gama isha'e suke tare a masallacin sai yanzun suka fito shi baffa ya wuce gidan isma'il shi kuma yayo nan gida, yace "haba kaikuwa d'ana mukhtar miyake damunka kake ciwa dan uwanka mutunci haka ta hanyar gaggayya masa magana?, a fusace mukhtar yace "kai tshohonnan babu ruwanka fa badakai nikeyi ba, in kuma kaima kanada buqatar in amshi haqqi nane na kudin mecca dana biya maka ta hanyar amshe maka gida to kacigaba dasamun baki da katsalanda a cikin lamurrana, isma'il daransa ya 6aci matuqa yakoci kwalar rigar mukhtar yana girgiza sa take fadin
"billaheel azeem bakai arziq'in dazan maka hassada ba, waikai yaya bakada mutunci daman ashe? yanzun baba yawale wanda ke matsayin uba d'aya a garemu kobayan ran baffa shi kake neman zagi?, to wlh bari kaji in kaimun
nina jure wlh bazan juri kaiwa iyayenmu ba"
tuni rigima da buge buge kuwa ta kaure
tsakanin masoyan 'yan uwan biyu ada maqiya kuma a yanzun.
tun baba yawale na rabasu iya qarfinsa har saida suka gajiyacceshi suka yardashi qasa wajen kaiwa juna bugu da naushi uwa 'yan dambe kowa naji da qwanjinsa kuwa, kankace miye wannan tuni jama'ar anguwar sunyi musu zobe daqyar aka rabasu dud sunjiwa juna ciwuka a jiki inda mukhtar ya farfasawa ismail gefen wuyansa da kunnensa, shikuma isma'il ya kwantarwa da mukhtar jini a idanunsa guda daya da kuma bayan wuyansa g
har d'an kumburi yayi,, mutane saicewa suke "haba kaikuwa alhaji mukhtar yada girmanka da darajarka zaka fito rariya kake haka da qanenka? qanen kane fa miya faru da zafi ne haka?
a fusace mukhtar yace"niba jinina bane shi din danma na tsanesa kuma daina had'a ni dashi,haqqina nazo karba kuma na karba dan haka kowa yasan inda dare yai masa kona kwaso muku bataliyar sojoji billaheel azeem kowa kuwa sai ya kwana gidan army barrak dinsu tareda azaba mai tsanani banzayen mutane kawai daku magulmata"
aiko da wanda suka zo rabo dan Allah da 'yan ganin qwam d'in kuwa tuni suka yaye suka bar wajen sumi sumi jin maganar sojoji. mukhtar har kusada isma'il ya matso sunata huci kuwa kamar zakuna, yace "blllahil azemu kuwa isma'il yanzun qazamar gaba ta qullu tsakaninmu bani bakai ba ahalina babu naku, ko saman hnya ka ganni inma kallo nakai Allah ya isa bare harka tanka mun" a fusace shima isma'il yace "saimi? yo aje a hakan saimi? koka dauka kaika d"aine dan zafin kai"
banza mukhtar yai masa ya duqa qasa ya dauki keys dinsa ya wuce wanda daga haka bai qarabin ta kansu ba, kamo hannun isma'il baba yawale yayi suka nufi gidan isma'il din, koda su baffa sukaga halinda isma'il take tuni suka rude suna cewa kai isma'il "miya samu jikinka haka

jini gefen bakinka da hancinka?
sai lokacin ma isma'il ya tuna dako babu shakka jinin dazun ne ya dawo wanda mukhtar yayi masa habo tun cikin gidan nasu ma, zubewa qasa yayi yana kuka yake shaidawa su baffa dud abinda mukhtar yace a gaya musu, yaci gaba da kuka yana cewa baffa "wannan ba yaya na bane mai sona kodai an canza mana shi ne?!,
ya cigaba da maimaitawan cewar "baffa ya qwace muku gida yace saikun biyasa kudin makkansa fa? sannan yace kuma babu ahalunmu babu nasa haihata haihata ko magana karna qarayi masa bare na nuna nasanshi to dan Allah baffa ku gayamun wannan halin yaya nane?"!
salati su baffa sukeyi harda baba yawale dasai yanzun yasan makamar zancen shima.
gani sukayi baffa ya miqe tsaye inno da jikinta gaba daya ya saki kamar zatai kuka tai saurin cewa "mlm ina kuma zaka?"
"ina xuwa"
abunda yace knn ya fit.
kai tsaye gidan mukhtar ya nufa ya qwanqwasa kofa saiga mai gadi ya leq'o ganin baffa ne yasashi zuqunawa har zuwa qasa ya gaidashi,baffa ya amsa sannan yace "mlm sani yimin mgn da mukhtar inyana ciki"
tuni mlm sani mai gadi yahau sosa kai dan kunyar abinda zai cewa baffan kmr yanda mukhtar yabasa sallahu yanzun daya shiga gidan.
daurewar Mlm sani mai gadin yayi yace "sai dai kayi haquri baffa dan alhaji yace kowa yasake zuwa gidansa indai daga bangarenku ne kada aqara bari ya qara shigar masa gida ciki kuwa hardaku yace"
Allah sarki jin hakan da maigadi yace tuni sansanyar zuciyar baffata qara karewa babu zato baffan yaji hawaye suna sulalowa daga kuncinsa,da saurin sa ya gogesu da hannunsa sanin dayai cewar masifar dake faruwa inhar iyaye na zubdawa yayansu hawaye, haka yajuya ya tafi.
daman shi bawai maganar kwace gidan da mukhtar din yaiba yazo yai masa ba, a'a zuwa kawai yayi dan yaji dalilin dukan isma'il d'in da ayi da kuma tambayarsa miyasa yake son canza halayensa na gari zuwa akasin hakan??
haka baffa ya karya kwanar gida yana tunanin wannan wane *rubutaccen al'amari* ne ya samesu wannan lokaci?.
haka yaci gabada tafiya yana goge hawayen fuskarsa da suka kasa daina zubo masa har lokacin, dudda qoqarin hanasun fitowa dayakeyi kuwa amman abun ya faskara!! ,,,

by
Xexen Fasaha.
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📄📄
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️🗞️👁️
🅿️🅱️
B affa da qyar ya samu hawayen suka tsagaita masa ya shiga gidan isma'il d'in wanda har lokacin suna zaune a inda ya barsu.
zama yayi tareda zuba tagumi batareda yace komi ba, baba yawale ya dubesa sosai yace "mlm Abdallah badai wajen yaron nan kake ba?"
baffa dai baice komi ba saida ya zauna sannan ya dubi kowa dake wajen kana ya tsaida fuskarsa ata baba yawale yace"eh can naje yawale, saida ya dan dakata yana mai sake jin ciwon cin mutuncin da mukhtar yasa akai musu, hmm duniya knn wai ace d'anka? d'anka na cikinka ke cewa in kazo gidansa kada a kuskura abarka ka shiga ciki dan yayi kudi komi ne? kuma bama wai iya kaiba harda 'yan uwansa ma?, baba yawale ya katse wa baffa tunanin da yakeyi yace "to masha Allah babu laifi ai, dan nasan indai mukhtar din yaga kaine kaje masa da knka dole ya haqura ya daina halayen da ya tsirowa kansa ya saurareka"
'd'agowa baffa yayi sosai yace "yawale nayi dana sanin zuwa na gidan mukhtar ba kadan ba, dan ko arziq'in ganin sa ban samu nayi ba sakamakon wani mummunan sallahu daya barwa maigadin gidan nasa wanda yace a fad'a mana idan daya daga cikin ahalinmu yaje masa.....
atake kuwa baffa ya fad'a masu komi da mukhtar yace gameda barin zuwa gidansa.
babu wanda jikinsa bai qarayin sanyi ba na tunanin cewa lallai ko abun na mukhtar yayi mtqr girmama.
baffa ne kadai ya lura da kukan da inno keyi yayi saurin cewa"subhanalla inno ki daina masa kuka dan hawayenki garesa masifa ne dan zai qara dorasa awata iriyar masifar ma wacce tafi haka" cikin shessheqar kuka inno tace "ai abinne da ciwo mlm ace kamar kai da yawale mukhtar zai wulaqanta ku? gskia ban haifi d'an da za'a ce ya wulaqanta mu ba kuma sannan inci gaba da riq'esa a mazaunin d'a na gari ba, indai kuwa haka ne daga yau wlh na zare mukhtar daga cikin yarana dana haifa da ciki na,,,,,,,!" tuni baba yawale da baffa suka qara fadin "subhanalla Allahuma ajirni fi musibati wa khalapni khairan minha kada kice haka inno, kiyi tunani ai ada ba haka yake ba"
Allah sarki kuwa isma'il d'an uwa rabin jiki, jin abinda inno take shirin yankewa mukhtar din baqaramin cira ta rawar jiki ba ta sake sauko masa ba nan take, dan haka yana hawaye ya kwantas da kansa kan cinyar inno yana cewa "dan Allah inno kada kice zaki tsine wa yaya mukhtar dan wlh inaji ajikina bayin kansa bane tursasa akayi ba halinsa bane kuma koma wanene kuwa yai mana sanadin faruwar rushe mana farincikin zumuncin mu wlh bazamu ta6a yafe masa ba"
zainab da tun lokacin da aketa maganganun tana gefen inno banda hawaye babu abunda ke

surnanowa daga kuncinta na tausayin su baffa akan wannan masifar data samesu tasan ko rantsuwa tayi bazatai kaffara ba wulaqancin da mukhtar yaiwa iyayensa dasa hannun yaya firdauseey matarsa dumu dumu kuwa dansu kowa yasan haka suke baza'a
taba hada zama inwa daya dasu a kuma wanye lpia dan sai sun rarwatsa na cikin inwar nan gaba daya sannan hankalin su ke zama nasu ita da meron tsimbe mahaifiyar tata.
har lokacin isma'il kuka yake kada inno ta tsinewa mukhtar sai lokacin ne tace"ni bawai nufi na in tsine masa nadai kawai ciresa daga sahun yarana har sai ya dawo da halayen sa masu kyau kamarda, wannan shine magana ta" tana gama fad'an hakan ta tashi tsaye ltada Zainab suka koma d'aki aka bar su baffa nan su uku jugum jugum sai da baffa yayi qoqarin yakice damuwarsa ya saki fuskarsa tareda nuna wa baba yawale da isma'il komi mai wucewa ne bnda ikon Allah dan haka su daina damuwa abinda yafi su taya mukhtar da addua dan ita yafi buqata a halin daya tsoma kansa a ciki, sun jima a haka sai daga bisani baba yawale yai musu sallama ya tafi.
nan baffa ya sa isma'il ya tafi dakinsa shima ya kwanta kan dole isma'il ya miqe tsaye jiki babu lakka ya wuce dakinsa shi kuma baffa ya daura alwala ya shiga d'aki shima.
mukhtar kuwa yana komawa gida bayan ya fadawa mai gadi abinda yace ya fadawa su baffa kai tsaye falo ya wuce ya hau samansa ya wuce toilet ya watsa ruwa sannan ya fito ya kwanta a gado zuciyar sa sai zafi take da tunanin wai har shine isma'il zai ware dashi suyi fad'a? lallaikam shima yace wani abu kuwa,, firdauseey ce ta murda kofar dakin ta shigo da turtsetsen cikin ta tafiya daqyal, zama tayi tareda dafasa sai lokacin mukhtar yasan ta shigo dakin ma, zuba mata idanunsa yayi da sauri ta riqo fuskarsa tana shafa idonsa da zuwa yanzun jinin cikinsa daya kwanta yadan fara washewa nn ta fara tambayarsa a rude da cewa "wayyo ni firdauseey mijina miye yasamu idonka ne haka? dud tabi ta gigice kuwa, daurewa yayi tareda qalato murmushi yace "kada kidamu wifey na, wannan ba wani abu bane ba ay, qwace hannunta tayi ta miqe tsaye tace "nidai fad'an gskia dan Allah"
kwata kwata baisan 6acin ranta dan 6acin ranta hana masa shaqar numfashi yake cikin hankalin sa dan haka yai mata bayanin fad'an da sukai da Ismail yanzun.
nan take ta fara masifa dacewa"wannan wane kalar dan iskan yaro ne wai? miyakeji dashi dahar zaice zaiyi fad'a dakai? yana talakkansa lis shida matsiyatan iyayensa har sunada qarfin gwiwar ciwa mai kudi kamarka mutunci, to wlh bazai yiyuba dan haka gobe goben nan za'a rushe gidan nasu muga ta qaryar iskanci da rainun wayau in kuma sun isa su 'yan kansu ne suce wani abu wlh kuwa da gaba dayansu zansa ka watsamun su a magarqama suda fitowa kuwa saidai a lahira" kamo hannunta mukhtar yayi yana cewa"zauna haba kiji uwargidan mukhtar ai bakida matsala abunda kikeso shi mukhtar yake so, dan haka gobe zansa a rushe gidan jibi a hau ginin sabbin shagunan da zan bude miki kisa 'yan haya koba haka ba matas? yayi maganar cikin murmushi dason burgeta.
abinka ga mai son abun duniya da nuna ita watace nan ta kalaimayesa da manaqisarta kala kala wai taji dadi dan haka kuwa wanshekare kamar yanda suka tsara saiga masu tarakta dinnan ta zybda gidaje tazo ta saita gidan baffa ta kuwa rushesa tsaf kamar titi ta maida wajen sannan ta tafi,
su baffa basu san mi ake ciki ba sai dai kawai ganin isma'il ya shigo gida hannuwansa dafe bisa kai yana kuka sosai ya zube gabansu baffa, a zabure baffa da inno sukai ta tambayarsa mike faruwa, kwata kwata ya kasa magana dan tsabar baqinciki sai saqyar ya iya dubn iyayen nasa

yace"baffa ashe yaya mukhtar da gaske yake zai rushe muku gida, wlh gashi can ya gama rushewa ku taso idanunku su gane muku,, aida sauri baffa ya fita inno ma ta janyo mayafinta suka fita suna isa wajen kuwa daqyar suka gane inda mukhtar yai musu ta'adar kuwa sakamakon mutane da suka iske wajen dayawa suna kallon abunda mukhtar yasa akaiwa gidan nasu dan yana tsaye lokacin har aka gama kuwa snn ya tafi.
nan kowa yaita tofa albarcin bakinsa, gameda rashin mutuncin mukhtar a yanzun kuma.
Allah sarki inno tana yin arba da filin gidan nasu ba gida ba tuni ta zame qasa ta sume, a rude jama'a sukai kanta ana mata fiffita amman shiru inno bata tashi ba, aida gudu isma'il ya sa6eta a kafada ya nufi wani asibiti dake tsallaken titin anguwar tasu, cikin tsautsayi wajen tsallaka titin baisan mota ta tafoba tuni kuwa ta kwashesu ta watsar shida inno din a gefen titi, mai motar kuma maimakon ya tsaya saima qarawa motar tasa gear da yayi sanin dayai koya tsaya aljihunsa ne zai koka haka ya wuce batareda ya damu ba shin mutanen nan daya buge ko suna raye ko suna a mace ba.
dudda mutane sunso kamo sa amman abun yaci tura baffa da baba yawale kamar su katse dan tsuma ganin jinin dake fitowa jikin isma'il da inno d'in.
nan aka ida isar dasu asibiti bayan an kai zainab gidansu wajen mamarta sakamakon gigicewa datayi tana shirin fara naqudar dole a saman titi.
daqyar likitoci suka tsaida jinin nasu,
saidai sunyi asarar jini da yawa saida aka qara musu jinin baffa da na baba yawale sannan aka dora musu drip.
saidai sakamakon gwajin da akaiwa inno ya nuna cewa jininta yayi mugun hawa ba kadan ba, dan haka likitan yaja su baffa office ya nuna musu cewar dud wani abu dazai sa hankalin ta ya dinga tashi to su kiyayesa matuqa dan zata iya rasa ranta ta sanadiyyar hakan.
wasa wasa saida su baffa suka qulla sati 3 a asibiti amman kuma mukhtar ko leqe tame AllAh bai leqosu ba dudda yaji labarin hatsarin kuwa.
a sati na hudu ne aka sallamesu suna shiga cikin anguwar kuwa sukaga har angama ginin shagunan inda gidan nasu yake har shago kusan ashirin da wani abu kuwa sakamakon wasu filin daya hada dasu ya siya din kmr ynda yace, yanzun haka fenti kawai ya rage a qarasawa gidan, AllAh sarki su baffan kallon wajen kawai sukayi tareda girgiza kai suka wuce gida kawai.
haka rayuwa ta dore mukhtar kwata kwata ya d'auke qafansa da zuwa gidan iyayensa suma kuma sun haqura sunsa masa idanu indai duniya ce ai tafi bagaruwa iya jima kamar yanda mutanen anguwa suke cewa knn ga mukhtar a vayan idonsa, dan yanzun taimakon ma da yake wa jama'a ya rage sosai saiya ga dama yake bayarwa.
watan haihuwar firdauseey ya tsaya dan haka kullum cikin saurare suke kamar yanda itama Zainab take sauraran tata haihuwar tunda satin ya kama bata komi face naqudar tsattsaye danma Allah yasa tanada juriya, gashi kuma itama ta kowane 6angare tana samun kulawa su inno da baffa da mmnta gakuma isma'il dan baffa kam cikin ragunansa daya siya guda uku harya bawa su isma'il din biyu yace a yankawa Zainab inta haihu, hakan kuwa ba qaramin dad'i yasa isma'il ji ba dan daman gashi duka duka yanzun wata yayi rabi bare yasa ran samun albashi har ya siya mata ragon sunan, danma sauqinsa sunada abinci da mahad'ensa.
yau Monday tun da safe su mukhtar da firdauseey suka nufi wata qatuwar private hospital wacce akwai mnyan likitoci a cikinta. harda baqin turawa maza da mata kuwa a cikin likitocin nata qwararrun gaske wanda suka qware ta kowane fanni. sakamakon ciwon da firdauseey ta

kwana dashi a daran jia wanda kamar zata mutu, suna zuwa wani babban likita ya dubata yace nan da rabin awa zata iya haihuwa, shiru kakeji rabin awa ta koma awa daya, awa daya ta koma biyu biyu ta koma uku, abudai har marece bnda 'yar banzar azaba babu abinda take sha dole likitoci suka sa mata ruwan naq'uda sannan ta fara nishin gasken gasken na haihuwa, tasha baqar azaba kuwa dan aqarshe tana yin wani bbn yunquri kan baby ya fito likitoci na ida janyo mata babyn ita kuma tana sumewa.
mukhtar na waje amman hankalin sa baqaramin tashi yayi ba jin wani ihun kukn azaba da firdauseey keyi, jiyo kukan jaririn dayai ne yasashi hamdala dasauri ya nufi shiga dakin aikuwa security suka hana sa dole ya haqura ya tsaya, acan kuwa sunyi matuqar qoqari sannan firdauseey ta farfado.
haka suka gyara kyakkyawan jinjirin yaron wanda suka tabbatar ya zuwa yanzun yanada matsala danko numfashi ma saida qyar yake yinsa, nn suka ta masa aune aune har suka gano inda matsalar take.
wani baturen likita ne ya fito daga labour room d'in ya kira alhaji mukhtar d'in zuwa babban office dinsa bayan ya zauna nn ya dubi mukhtar yace cikin yarensu"yalla6ai babynka yasamu matsalar toshewar numfashi wanda har matsalar ta shiga cikin wasu hanyoyi dasuke da dan gan taka da numfashin sa wanda yake shaq'a, to zamu sanyashi a cikin wasu einges na na'ura har tsawon sati biyu dan munada tabbacin 2 in akai masa hakan zai dawo normal, zai yiyu kuma ya rayu ko akasin hakan"
cikin rawar jiki mukhtar yace "doctor ban... bangane ba? kamarya zai rayu bazai rayu ba?"
baturen doctorn yace "eh, ina nufin a qa'ida naurorin sune zasu fudda masa sanyin da mamarsa ta dunga shayar dashi a ciki lokacin ta hanyar kayan sanyi data dunga sha, yanzun haka,
so yanzu zamu baka uniform saikasa kashiga ka gano su dan mu ba,a shiga room din saida uniform na hospital namu a jiki, haka kuwa aka bawa mukhtar wasu tsanwayen kaya da sunn hospital a gabn rigar sai wata farar hular leda yasa yashiga room din da sauri.
yana isa kan gadon
firdauseey yaganta rungume da jinjirin ansa masa kayansa blue amman sai kuka take, karbar yaron yayi.
"ya subhanalla" yace ganin gaba daya yaron kamar baffansa ya d'auko sak.
 dogo ne sosai fari tas ga hanci sannan gashin kansa da jikinsa kwance laya laya alamun na cikakken fulanin usuli knn.
Amman kuma sai dai kash dud wannan baiwar kyan sura da AllAh yaiwa babyn bayya numfashi saida qyar da qyar yanda kasan bazai qara koda second ba kuwa a duniya saboda hatta mad"igar babyn nasa ana ganin tashin bugawarta.
kuka firdauseey take tana cewa "dan AllAh mukhtar kada yarona ya mutu ina sonsa wlh zuciyata zata fashe nima wlh inbisa, dutta rude ta gigice sai sambatu take.
 rungume jinjirin mukhtar yayi a jikinsa ya zauna bisa wani gado dake gefen na firdauseey saboda yanda yaji son yaran na ratsa b'argo da tsoka na jikinsa kaishi fa jiyake baiqi a halin da ake yanzun ba ace yabada komi nasa ba saboda d'an nasa yasamu ingantacciyar lpia kamar kowa.
kawai sai qara rungume jinjirin mukhtar yayi yana kuka.
suna haka saiga wata 'yar tsamurarrar baturiya ta shigo room din ita da 'yarta.

nan baturiyar
ta cirewa firdauseey drip din ta fita yayinda 'yar tata ta matsa kusada mukhtar ta dan riqesa ganin yana kuka kamar qaramim yaro yasata fadin "oh sir yi hakuri kada ka damu babyn ku zai samu sauqi insha Allah"
amman ina kwata kwata mukhtar baisan ma tana yiba kuka kawai yake firdauseey na tayasa dan ganin
da suke a yanzun rashi zai risqesu dai dai lokacin da sukaga samu Allah kenan!

By
Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🥡🥡
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

```Masoyana na gskia da gskia wanda na sani da kuma wanda bn sani ba ina godia gareku matuqa da nuna qauna, ina roqon Allah kuma alherin Allah ya isar muku kamar yanda nike samun managartan addu'oe daga gareku kuma```.
👁️🥡👁️
🅿️🚾
M ukhtar kam sai da qyar doctor merzan ya rarrashesa tun shigowan sa shima kuwa ya iske sa halinda yake.
kan dole mukhtar ya haqura ya basu d'an ya fita ya canza kayansa ya zauna nan office din doctor merzan kamar yanda ya umarcesa daya jirasa nan.
babu jimawa saiga likitan ya fito yayinda firdauseey ke biye a bayansa har zuwa lokacin fiskarta share share take da hawaye. mukhtar nan shima yaji zuciyar sa ta q'ara karewa dole yasa hankicerf wannan karon yana tafiyar da hawayen nasa a cikinsa.
bayan firdauseey da likitan sun zauna nan doctor merzan ya dubi mukhtar yace "ka daina saka damuwa a ranka kaji? babynka zai samu lpia insha Allah so dan yanzun haka mun kaisa can dakin da na'urorin suke mun kuma sanya sa ciki, sai dai kuma a qa'idar asibitin nan indai muka
```

kwantas da iriyar wannan patient d'in to ba'a zama wajensa kuma adadin satikan da muka d'iba sai lokacin ake dawowa so dan hka be careful zaku iya tafiya sai nan da sati uku zaku dawo ku iske sakamakon, sannan ita kuma maman babyn munga babu wata matsala a jikinta kuna iya komawa gida yanzun tare da ita wannan shine cikakken bayanin zaku iya biyan bill namu sannan ku tafi"
da kuka firdauseey tabar office d'in shi kuma mukhtar saida ya biya bill na komi sannan ya fita daqyar ya rarrasheta suka shiga mota direbansu yaja su har gida.
koda suka koma gida bnda sabon kuka babu abinda firdauseey ta dasa dan gaba daya ta hayyaci kanta ta hana kanta sukuni.
dole mukhtar ya kirawo mairon tsimbe tazo.
tana zuwa kuwa ko sallama batai ba ta fad'o cikin falon gagaf tana fad'in "wai yaya ne mike faruwa nikejin kukn firdauseey ta?"
cikin ladabi mukhtar ya fito daga bedroom din ya gaisheta ko kulasa batai ba dan ita ta 'yarta kawai take da sauri ya matsa yabata hnya ganin yanda ta cusa kai cikin bedroom din nasu har tana qoqarin turesa.
firdauseey na ganin uwar tata da gudu ta miqe tsaye ta isa jikinta tana cigabada da kuka tana fadin "mama babu babyn babyna zai mutu ya barni mama? ita mero ma sai lokacin ne ta lura da babu cikin jikin firdauseey dan haka wata uwar ashariya ta ingizo tareda fadun"tooo ana wata ga wata fa, bantar ubancan,! gidan uwarwa aka kai mini jikan nawa eye? a fad'a mun inda aka saka mun jikina komuma billaheel azeem na rigizazo muku August a gidan nan" tayi maganar tana dukan qirji tareda cin d'amara da mayafinta tana duban mukhtar alamun dashi take.
kasa magana yai dan baq'aramin tsoron meron tsimbe yake jiba matuqa a rayuwarsa, dan haka muryarsa na rawa rawa yace
"ai...ai mama yana hospital ne.... "uban ubanmi yasa aka barosa a sosbitel d'in?, cewar meron tsimbe data katse mukhtar d'in dudda mukhtar na halin tsoro saida maganar mero taso basa dariya danjin dayai ko sunan ma hospital din takasa fad'a banda zagi babu abinda bakin ya iya da cin mutunci.
kamo hannunta firdauseey tayi suka zauna gefen gado nan suka zauna firdauseey ta fad'a mata da cewa "mama babyn ne bayya da lpia dana haifosa kuma.... nan ta kwashe komi ta fad'a ma uwar ta qarashe da matse qwalla tana cewa "wlh mama bakiga kyakkyawan babyn ba, AllAh kuwa mama inna rasa sa kema zaki rasani ne" kama hab'a mero tayi dayake zuciyar ta ta jima da qeqashewa shiyasa bataji ko d'ar na tausayin firdauseey dawani jinjirin ba, kawai fizgo hannun firdauseey tayi ta girgiza tace "toke dan ubanki uwar waye yace baki fad'a mun ta waya ba nazo munje asibitin tare? kuma uban waye yace kitashan abin sanyin ne eye bare kizo kifasawa mutane makoki?,
to wlh can saman kanki kuma marmaza kije ki d'umma jikinki da ruwan zafi dan maijego batta zama babu gashi"
haka firdauseey ta miqe ta nufi toilet amman gaba daya zuciyarta naga babynta, mero ta miqe tace "naga sanya kikewa batun bari kiga in shigo kewayen in gasaki da kaina dan ban yarda da kiyi ke kad'ai ba dan wannan in aka barki zaki lalata kanki ki
zama maras amfani fanko ga miji saidai yaje ya nemi wata kokuma ya aura kinaji kuwa kina gani kin zama foto a cikin gida bayanda zakiyi"
haka mairo taita sakin magana ko kunyar mukhtar dake wajen batayi ba harta bi firdauseey

toilet din ta maido kofar ta rufe.
zama mukhtar yayi gefen gado tareda dafe kansa yarasa yanda akayi son babyn nn yai masa wawan kamu, zumbur kuma sai
ya miq'e tsaye ya koma falo ya d'auko wayarsa yahau kallon foton babyn bai aune ba sai yaji hawayen sa na d'iga bisa screen touch din wayar.
yajima a haka sannan yayi shirin office akan dole sakamakon wayar da aketa masa tun dazun akan zuwan wasu baqinsu haka yahau mota jikinsa a mace yabar gidan.
A can toilet kuwa kukan da firdauseey take tana kiran babynta kada ya mutu shine ya hassala meron tsimbe ta kufula tace "tace ke dan kan mataccen tsohonki kukan nn ya isheni haka, haba anyi d'iya sai shegen naci? kuma madai naga yaron nn bai mutu ba bare kita asarar hawayenki ko?, to inma ya mutu q'asanki amfanin ubanmi yake miki dabazaki qara iya daukar wani cikin ba ki haife?,,
shiru firdauseey tayi amman sai faman gunguni takewa uwar qasa qasa tareda satar hararata, basu baro kewayen ba saida meron tsimbe ta gashe firdauseey fiyeda qema ta qara shan wata azabar kuwa saida ta bud'e sabon famfan kuka sannan uwar ta barta.
haka ya kasance kullum mero ke kulaw da firdauseey kuma basu fad'awa kowa haihuwar ba dan a cewarsu sai sati ukun sun cika sun koma asibiti suga yanda lpiar yaron take ko akasin haka.
cikin ikon Allah kuwa yau Monday yacika sati uku knn da haihuwar firdauseey kuma yaune suke shirin komawa asibiti dan meron tsimbe saboda zumud'in ganin jikan nata datazo jia nan ta kwana gidan firdauseey kuma a bisa gadonta tayi shame shame a bisa uwa saniya wanda hakan tasa mukhtar dole barar musu d'akin ya kowa d'aya daga cikin d'akunan saman benen, dayake babu abinda babu a d'akunan dudda ba zamnsu ake ba.
6:22pm a hospital din tai musu suna nn zaune har saida lokacin yad'anja wajen 8 da wani abu sannan fa manyan likitocin suka fara shigowa asibitin cikin motocinsu, suna a haka saiga doctor sera ta shigo wato mamar yarinyar nan baturiya wacce ta rarrashe mukhtar jia dayaita faman sakin sambatukan kukan nn. Still 'yar tata raja tana biye da ita, raja iriyan matan nan masu 'yan mnyn shekaru a fuska amman jikinta ya b'oye mata hkn danko mama bata dasu yanda ya dace shiyasa ake kllonta qaramar yarinyane. bayan sun gaisa ne mmnta take cewa "kuna jiran doctor mezan ne ko?"
"eh cewar mero data riga kowa harshen mgn a wajen, sai tace "ok to ku qara haquri nan da mintuna 10 zaku gansa"
"ok ba matsala doctor thanks" cewar mukhtar su juya suka wuce yayinda meron tsimbe tabi 'yar baturiyan nan wato raja da kallo aiko saita bushe da dariya tana fadin 'o'o ni Allah mai halitta ita wannan jibeta da fuskar manya amman dubi qirjin kamar anyi shafen suminti akai... kanta qara cewa wani abu saiga doctor merzan yashigo aikuwa da sauri mukhtar da firdauseey suka miqe daidai nn doctor d'in ya iso garesu suka gaisa yajasu office dinsa ya aijye brifcase dinsa a side tareda zama kan kujera ya dubesu cikin fara'a yace"congrats ina tayaku murnar babynku ya samu lpia jia muka fiddasa a engies d'in yanzun kam bayada matsalar komi numfashinsa it's very very normal dan yanzun haka ma zamu iya zuwa ku d'auki babynku" tuni suka hau murnar gasken gaske kuwa sai hamdala mukhtar yake haka doctor merzan ya kaisu dakin da babyn yake ai mero na arba da tsantsar kyawun yaron saita dubi firdauseey tace" 'yar banza dole ki haukace kan jinjirin nn ashe? yaro kamar yasha hatimin annabi yusuf shima dai? itadai

firdauseey batabi ta kanta ba shayarda yaronta kawai take kamar yanda doctor ya bata izini.
sai kallon yaron suke Itada mukhtar sai wutsil wutail dinsa yake na jarirai cikin kayansa an kuma nadesa a showel kaida ganin babyn kasan lafiyayyen baby ne, yanda kasan ka tabasa jini yai tsartuwa haka yake, danba qaramin kyau ya qara ba akanma wanda aka haifesa dashi d'in .
basu jimaba aka basu sallama da yake ranar suka kar6o babyn dan haka sai aka maida rad'in sunan yaron da kuma bikin sunansa rana ita yau watau Monday mai zuwa, tuni mero ta dunga fadawa yanuwa da aminan arziq'in haihuwar firdauseey kankace miye mutane sukaita shigowa ganin jariri kuma dud wacce tazo abunci da namomi da juice s saita ture kuwa dan masu aiki har uku mukhtar ya zube musu sannan dud wacce zata tafi sai an mata kyautar 1k sannan.
aIkuwa shiyasa a ranar mutane basu katsewa zuwa gidan danjin labarin kud'in da ake badawa wane yaji ga wane knn, kai baka bayarba kaje an baka tomiyafi wannan dadi cewar mutane.
koda wasa mukhtar bai taka q'afarsa yaje yafad'awa su baffa haihuwar ba dan tsanar sa da ismail bazai bari yaje gidan nasa ba, suma su baffan ya runtse idone kawai haryayi tunanin gaya musun bawai dan matsayinsu yakai ba na sujin a cewarsa, amman ya yanke hukuncin a ranar daren suna zai je wajenda su baffan ke firar dare saiya fad'a masa faqat yarage ruwansa yaje zanen rad'in suna ko kar yaje shidai yafita haqqi a ganinsa.
saidai abinda bai saniba har su baffa ma sunji haihuwar saidai sukayi shiru abinsu batareda sunyi gigin tunkararsa da wani abu wai shi barka ansa mu qaruwa ba,suna masa adduar Allah raya. to mutumin dayace babu kai babu shi babu ahalinsa babu naku kuma ya hanaka taka gidansa tomi zakaje kayo? suna matsa yin iyayensa aisu yakamata yabi basu su bishi ba kodan gobensa tai kyau, dan haka inda bai zo ya fad'a da kansa ba ai huta roro waken gizo yayi 'ya'ya cewar inno da suke tattauna maganar da baffa da ismail.
dan yanzun harsun manta ma su rabonda dasusa mukhtar idanunsu dama basusa aka ba bare abun yadamesu, danma musamma ma inno dake da hawan jini, takan qara da cewa "inda ya zabi mace akanmu ai shiknn haka duniyar take ay ba kanta farau ba haifarwa mace namiji tana masa fatan shirya dai.
suma kuwa abun Allah a ranar ne bayan gama sallar isha'e Zainab ta suntulo musu kyakkawar d'iyarsu mace barikallahu Masha AllAh, su baffa baqaramin dadi sukaji ba da Allah ya nuna musu d'an isma'il wanda bai yarda suba, shiyasa har nafila sukai ta godia ga Ubangiji,, ranar kam sunyi kwanan farinciki, danko washe gari aka farfado haihuwar maqota akaita shigowa kuwa tayasu murna dasa albarka kowa ya amshi jinjirar nan kuwa kamar karya badata yakeji dan yanda kasan zubin larabawa haka Allah ya basu ita.
mutane basu katsewa zuwa gidan kuwa kullum saboda sake ganin jinjirar zainab, dan kuwa wasuma dawowarsu ganin jaririyar yafi a qilga dudda sun zazzazo kuwa, mutane suknce dudda kyan da Allah ya qawata jinjirar dashi saida ya qara mata da farin jinin mutane ta ko'ina, Allah kenan buwayin sarki shi daya gagara misali, haka akaita zaman barka har yau gashi daren suna.
kamar yanda shi mukhtar ya tsara haka kuwa a daren suna yazo har wajensu baffa inda suke zama da baba yawale waje sallama kawai yayi batareda ya gaishe suba face "sannynku"' da yace yana daga tsayen sa kuwa, amsa sallamar baffa yayi shima dan ya zama dole kam, amman daga haka ko kallon mukhtar din baiba yaci gaba da jan carbinsa.
baba yawale yace "mukhtar kazo ganin jinjirar d'iyar qanen taka ne a fiddo ma ita ka gani?
Mamaki mukhtar yayi daman har matar isma'il ta haihu bai gaya masa ba,(kujifa shi ya fad'a

masa ne?)jiyayi nan take ya sake tsanar su gaba daya jiyake dazai iya raba jikinsa ya kwashe jinin jikinsa ya maida masu baffan abunsu dayayi koya huta da tunanin cewa dansu ne shi kuma shi dan uwan isma'il ne!
(ya subhanalla gskia mukhtar an nemeka an samu da yawa, AllAh shi kyauta dai to).
duan baba yawale mukhtar yayi jiyake kamar ya ida qarashe tsohon ta hanyar yi masa zazzafar shaqa danjin zafin mgnr dayai masa nawai yazo ganin jaririya wancen gidan da talauci da babu dake mamaye dashi.
shi koda yarinyar ma ta girma kowani yaji zaima je neman auren yar Ismail gidan aisai ya zugesa yadaina zuwa.
kuma ma ya d'auki alqawalin yar isma'il indai ta girma itada yin aure saidai taga mata nayi dan kuwa kowa yayi nufin aurenta zai sa mutanen sa su zugesa ne in kuma yaga mutum ya nace tofa numfashi zai gintase a rayuwar sa dan ya tsani dud wani cigaban isma'il koda na farinciki ne kuwa.
gani yake inyai masa hakan wata sabuwar hanya ce wacce zaisa maza su guji yarinyar insukaji lavarin kowa yazo neman aurenta yana mutuwa kuwa. tunanin hakan dayai ne yasashi sakin murmushi ya dubi baba yawale da baffa yace "baffa damn nazo fad'a muku zanen suna d'ana ne a babban masallaci bayan gama sallar asuba" ga mamakinsa saiyaga baffa yayi murmushi yace Masha AllAh damn gobe ake rad'in sunan 'yar isma'il kaga sai ayi duka a wuce wajen,
baba yawale yace "gskia ne Allah dai shi kaimu lpia, aminn cewar baffa,
Juyawa mukhtar yayi yace "sai anjimanku" baba yawale ne kawai ya amsa masa baffa kuwa shiru kawai yayi yana cewa aransa "hmm ta yaro kyau take bata qarko ay."
Nansu baffa sukaci gaba da firarsu har lokacin tashinsu yayi sannan kowa ya wuce gida danya kwanta.
ana gama sallar asuba kuwa akai sanarwa a masallacin na zanen suna inda d'an mukhtar yaci sunan khaleepa, 'yar isma'il kuma taci sunan heenduh haka aka yi addu'a mutane suka fara fita yarage daga baffan sai baba yawale sai kuma mukhtar da baffan yace ya tsaya kada ya tafi, ala dole ya tsaya kuwa yana tunanin mi baffa zaice masa a masallacin bayan ko jia sun had'u?. babu zato yaga baffa ya miqa masa hannun damarsa yace bani nan mukhtar?"
cikin mamaki mukhtar ya dubi baffan nasa yace "baffa mizan baka, dan jikinsa harya soma rawa ganin yanda fuskar baffa ta koma babu alamun wasa a cikinta ko masassaqo.
baffa ya qara tamqe fuskar sa yace"dud abunda ya sawwaqa cikin aljihunka indai kud'i ne su nikeson ka bani banson wani ja'inja bani kawai kayi abinda nace" mukhtar bai sake cewa komi ba ya tura hannunsa aljihu yaji babu wasu kudi komi face takardar dubu daya dan jallabiya ce kawai ya fito da ita a jikinsa, haka ya miqawa baffa.
baffa ya kar6a yace Allah sanya alheri cikin ta dan mafi qanqantar sadaqi yana habbaka albarka ta aure ai daman fiye da mai yawan ma, juyawa baffa yayi ya miqawa baba yawale dubu dayan shima baffan ya fiddo dubu daya cikin aljuhunsa ya riqe kowa sai binsa da kallo yake tsakanin baba yawale da mukhtar din dan basusan manufar maganar baffan fa, baffa yace "yawwa yawale inason kai ka zama waliyin jinjirin mukhtar wato dansa khaleepa .
ni kuma zanzama waliyin heenduh yar isma'il yanzun nan basai an matsa ba za'a daura wa jariran aure dan bazan juri ganin tarwatsewar zumunci tsakanin yayana ba ina raye ban mutu ba, kaga innai ma yaran aure tun yanzun kaga zumunci bai kauba dan zuri'ar mu zata qara yawa" ya juya ya dubi mukhtar daya daskare jin abunda baffan yace gaba daya jikinsa ya kab'e

da kyarma ko motsi ya gagara yi, baffa yace "yawale kazama shaida ko bayan raina wallahi tallahi narantse da izzar mulkin Ubangiji Allah kuwa muddin mukhtar yasa d'ansa kaleepa ya saki heenduh yar isma'il dan wargajewar zumunci na har abada kamar yanda yk fata to wlh mukhtar kaji da kunnen ka indai ka kuskura kai hakan Allah ya isa!
Allah ya Allah isa!! Allah ya isa!!! tsakanina dakai dan haka ka kiyaye wannan umarni nike baka bawai shawaraba" mukhtar yanaji yana gani a haka kuwa nan take baffa da baba yawale suka daura auren jariran da basusan abunda ke cikin duniyar ba, suna gamawa suka tashi suka fice daga masallacin suka bar mukhtar nan wanda yayi qaramar suma zaune awajen yanaji kamar bugun zuciya zata kashesa a wajen jin yanda zuciyarsa ke bugawa fat! fat! fat! zai iya rantsewa da Allah inda wani zaizo kusa dashi tofa zaiji sautin bugun zuciyarsa a wajen.
wannan aishi ake kira a mareka a hanaka kuka kuma, rasa abinda zaiyi yayi yaji dadi koya samu zuciyarsa ta daina bugawa kawai saiya daura hannunsa 2 aka ya fashe da kukan baqinciki na auren dansa da heenduh yar maqiyinsa,
Mukhtar cewa kawai yake tsakaninada ismail Allah ya isa nasan shi zaisa baffa yaimum hkn, haba baffa miyasa? wlh bntaba jin inda akai wannan auran ba tunda nike ace ranar rad'in suna jarirai nan take kuma a wajen a daura wa jinjirai d'in aure ba,! wayyo ni Allah na zubewa qasan wajen yayi, yayi goho yana dukan knsa da hannun sa yanamai fidda zafafan hawayen baqinciki da takaici yana cewa "firdauseey zokiji danyen hukuncin da baffa ya yanke mana a rayuwa wanda bai gamda muba"!!!!!!!!!!!!,
tunanin kawai toshi yanzun tayaya zaijewa da firdauseey da wannan zancen wane kuma hukunci zata dauka akansu baffa kuma intaji???

By
Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🥡🥡
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas and sis ayush ilyasu musa amaryarmu Ubangiji Allah ya kawo zaman lpia mai dorewa da zuri'a d'ayyaba fatan da muke miki knn ala kulli halin.~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

W Ih bantaba jin inda akai wannan auran ba tunda nike, ace ranar rad'in sunan jariran nan take kuma a wajen a d'aura wa jinjirai d'in aure ba!
wayyoni Allah na!"
zubewa q'asan wajen yayi, yayi goho yana dukan kansa da hannunsa yana mai fidda zafafan hawayen baqinciki da takaici yana cewa"firdausy zokiji d'anyen hukuncin da baffa ya yanke mana a rayuwa wanda bai gam da muba"!!!!!!
tunanin kawai toshi yanzun tayaya zai jewa da firdauseey da wannan zancen wane kuma hukunci zata d'auka a kansu baffan kuma in taji??
dole ya miq'e daga wajen yabar masallacin ko ganin gabansa baiyi sosai sakamakon wani mugun jiri da yakeji a lokacin, da qyar yasamu ya isa falon gidan nasa ya zube bisa kujera yana huttai.
lokacin kuwa qarfe bakwai da mintuna 50 na safiyar ranar.
gida yan suna suna waje sai ida hada delicious na abuncika akeyi da drinks kala kala. mai jegon ce ta sauko daga benan jikinta sanye da wani swice lace kaida ginensa kuwa kasan nera basai an tabbayeta ba gu siyensa, awarwaron mnyan zinarai ne sanye da hannuwan ta sai kunnen ta da wuyanta suma sun shaida nasu golds d'in kuwa.
har kusa da mukhtar firdauseey ta zauna sai baza qamshi take ko ina.
"yalla6ai yabaka shirya ba?
ai yakamata kaje kai wanka ka shirya sosai inda an gama zanen sunan ko?
dubnta kawai yake da kansa dake barazanar fashewa, shin tayaya zai iya dubn qwayayan idanunta yace an d'aurawa jaririnta aure da jaririyar 'yar abokin gabansu ne abin q'insu kuma mawai tukun?
runtse idanunsa yayi bayan yasa hannuwansa ya shafo tundaga saman kansa har zuwa fuskarsa da wuyansa sannan ya sake dubnta daqyar ya iya furta "akwai matsala firdauseey" arazane ta dubesa, haba ba banza ba takejin faduwan gaba tun dazun kam, cikin tsurewa da faduwan gaba gamida rudewa tace "mi... Mmm. mim. mine ya faru kuma? dan Allah yi maza sanar dani wlh daman sai faduwan gaba nikeji ba kad'an ba"
Saida ya qara sauke qarfaffan ajiyar zuciya, ransa bnda tuquqin baqinciki babu abinda yakeji, shifa jiyake daman mutuwa yayi ya huta dayasan zaiga wannan baqar ranar da har baffa zai iya jefa d'ansa gidan matsiyatan nan dan sake hada wata sabuwar dangan takar data wartsake kuma da jimawa ma.
muryan firdauseey ta katsesa inda yaji tana fadin "haba mukhtar kawa girman Allah da manzonsa ka fad'a mun abinda ke faruwa danni ka barni a duhu babu kyau iriyar hakan fa"
"baffa ya yanke mana mummunan hukunci yau firdauseey inda ya had'a auren khaleepa da 'yar tsinannen yaron nan isma'il yanzun nan bada jimawa ba a masallacin anguwar nan bayan gama rad'in sunan su"
wata mummunan hantsilawa firdauseey tayi wajen miqewa wanda har kallabin dake kanta wanda tayi coge dashi wato wanda ake kira tunkud'esa kaga tsiya yana fad'owa qasa amman kota hakan bata biba dan kwanyarta ma ta daina aiki na wucin gadi jin maganar tai mata dirar mikiya a gaggauce kamar ana faffaska mata tafi takeji a kunci. bayan dawowarta hayyacinta tace "wai tukunna madai wane khaleepa din kake magana ne mukhtar???!! khaleepa na fa? "

shi kansa abin mamaki yake basa dan tun sanda suka fara soyayya da firdauseey bata qara kiran sunnsa ba gatsal amman yau gashi sai maimaita mukhtar take a bakinta batareda taji ko d'ar ba, amman yasan dole tayi ma fiye da hakan ma a yau inda an tab'ota.. babu zato yaji ta cacumo kwalar jallabiyarsa tana girgiza wa da qarfi idanunta sun yi jajir hawaye na fita ta gefensu tana cewa"wadannan matsiyatan za'a had'a min d'ana da 'yarsu aure? ai wlh bazan yarda ba wlh sai an raba wannan q'addararren auren ko ai kashe kashe a anguwar nan"
ran mukhtar a matuq'ar 6ace wannan karon ya fizge hannun firdauseey daga kwalan sa data shaqa, ransa ya b'aci da abinda tai masa matuqa dan yaso lallashenta amman jakin dinsa datai yasa yaji bama zaiba kuma bazai biye mata ba tsinuwar iyayensa tabisa ba a banza a wofi, dan haka ya dubeta idanunsa sun sake kad'awa sunyi jajir yace " kije kiyi komi ma zakiyi nidai bazan bijirewa umarnin mahaifina ba inda harya tsine mun akan indai nasa aka raba auren nan"
yana gama fadin hakan ya haura samansa ya wuce d'aki ya barta nn tana haukan 6a6atu, data gaji zubewa tayi wajen ta d'aura hannunta bisa kai tahau kururuwa tana fadin a ceceta dan gaba d'aya q'arar ihun kuknta ya cika falon gidan, aiko saiga mata 'yan suna wanda suka fara shigowa lokacin suka baro dayan falon da gudu suka shigo babban falon gidan suka isketa baje qasa dutta tuttuje kwalliyar jikinta ta yar qasa hatta dankunnen kunnenta shima bai tsira ba, ta 6alle zanen jikinta sai undie dogo kawai ta bari, ta koma kamar mahaukaciya dan yanda ta dinga kuka da hawaye shate shate gashi sai dukan knta take tana fizgar gashin knta dan azaba ko zafin hkn bataji ihu kawai take tana tsinewa su baffa tana sake cewa Allah ya tsine muku wlh, bazan yarda ba shegunayen mutane kawai wlh saina dauki mummunan fansa akanku gamida abinda kukai mini matsiyatan banza makwadaita, daqyar hajiya Hadeeza aminiyar firdauseey ta kori sauran jama'ar wajen ganin yanda sukewa firdauseey kallon mahaukaciya, suna fita tasamu ta kulle musu qofan falon ta dawo ta zauna kusada firdauseey bayan ta, samu ta rarrasheta tayi shiru daga haukan kukn nata da takeyi takoma zubda zallar hawaye kamar fanfo dankuwa banda zunga da zugugin ciwo babu abinda zuciyar take mata hatta kejin ma inazata ma iya hadiyan zuciya ta mace kota huta tunanin wannan mummunan qaddarar data samesu yau.
Hjy Hadeeza tace "haba aminiyar miyasaki haka har kika janyo hankalin mutane kanki? dan AllAh kiyi haquri inma wani abinne ke damunki fad'a mun yanzun nan zami samu mafitarsa(hajeeya Hadeeza wata sabuwar aminiyar firdauseey ce wacce basu jima da dawowa daga anguwar ba dan itama tanada hali kamar nasu firdauseey din bata da son dangin miji bare iyayensa dan tsakanin ta dasu sai wulaqanci da fad'a kaca kaca kuma ta zagesu tas shiyasa batada farin jinin su kokadan gashi kuma ta hana dan uwan nasu qara aure dud tabi tayi kane da dukiyarsa sai fantamawa take da ita son ranta, daman ance sai hali yazo sannan ake mummunan abota gashi kuwa dan gaba daya sunsan sirrin junansu kaf hatta da mugun asirin da sikaiwa mukhtar na rabasa da iyayensa da d'an uwansa saida firdauseey ta fadawa Hadeeza, kuma itama Hadeeza ta fad'a mata tariga ta gama da mijinta alhaji bala, shiyasa yanzun kansu a hade yake battada amiyar data wuce ta itama haka.
Kuma itama hajeeya Hadeezar ko kwana goma batai ba da haihuwa itama yanzun haka wannan kenan).
dan haka firdauseey tana hawaye take cewa"masifa ta saukar min a wannan rana aminiyar babbama kuwa, gashi kuma mama mero taje qauye yau da sassafe dan kaka musa baida lpia bare na fad'a mata musan mafita dan Wlh bazan bar abinda akaimun ba,

tab!!!!! Inkuwa har harma na barsu kenan ma sunshani a basilla"
Hajeya Hadeeza tace "nifa kin sani a duhu ki famitar dani man kona fahimta"
Saida firdauseey taqara matse hawayen ta sannan tace "wannan mugun tsohon ne man baban mukhtar yatashi ya had'a d'ana aure da 'yar qanensa"
zaro idanuwa hjy Hadeeza tai gaba d'aya sannan ta dafe qirji tace "badai isma'il ba teacher din nan?"
"shifa wlh"
"tab lallai kam indai hakane qawata an cutar mana yaro wlh, nida naso insun girma a hada su aure da 'yata zarah dan koba komi nera zata gogi nera"
cikin quta qatuwa firdauseey tace "hmm gidan matsiyata? marassa shi?! masu jiran albashi sannan suci abinci?! nan aka bawa dana 'ya?! aka cusa masa?! yaron da baisanma uwar mi ke duniyar ba amman dayake jahilai ne q'auyawa
shine sukai mana wannan yankan q'aunar"
to wallahil azeem bazan haqura ba, qawata ki bani shawara, ko mubari mama mero ta dawo ne saimu makasu wajen boka marakusa aiki da cikawa? dan wlh shine kawai zai mana maganinsu"
hjy Hadeeza tace
"haba qawata kina dani fa a hannu kokin mnta ne? wannan tsoffin kingin mutuwa har sai mun wani sha wuyan zuwa wajen boka a kansu? ai wanna aikin naki ne ke zaki yisa da knki" cikin mugu mugun mamaki firdauseey tace "kamarya kenan aminiyar kefa bom ce wlh"
hjy Hadeeza tace "hmm kawo kunnen ki kiji aminiyar "
nan take kuwa firdauseey ta miqa mata kunnen ita kuma tafara d'ura mata mungun nufinsu akansu baffa.
tana gama fad'a mata kuwa suka kashe da tafi firdauseey tace"kai naji dadin wannan zazzaqar shawarar wlh kuwa"
hjy Hadeeza ta karkace baki tace "hm in kikai hakan sai muga tayaya zasu qara ganinsa bare har su sashi wani abu makamancin haka, ahto yanzun kuma dai aiki ya rage naki sai yaushe zaki qaddamar musu dashi ne?"
firdauseey tace
"a daran nan danma wannan jama'ar da ke gidann da yanzun zanje na gama aikin aminiyar sake tafawa sukayi hjy Hadeeza tace "hknm yayi abarsa a daren dan zaifi sirri, amman da har zaki wani tsaya b'ata mana ranki akan wasu banzaye qananun qwari, sannan kuma kada ki manta kiwa Alhj mukhtar managar danai miki"
babu matsala qawa kedai Allah barmu tare kodan shawarki mai wuta.
dariya suka qarayi nan sukaje daki ta qara shiryawa kamar ba itace ta gama borin ihun kuka ba, dan haka koda suka isa cikin jama'a kowa ya tambayeta abinda ya sata ihu haka d'azun amsar da hjy Hadeeza ke basu qadangare ne ya shigo falon ya firgita ta,sudai jinta kawai sukai dnbasu yarda ba.
ahaka akaci gaba da buduri da bured'e d'e na suna awunin ranar.
hankalin firdauseey kwance danta gama samun matsaya ta ramuwa da maganinsu baffa.
baffa kuwa koda ya koma gida nan yatarasu isma'il da zainab harda inno zaune a wajen ya fad'a musu auren daya daura tsakanun jikokin nasa dan qarfafa zumunci, matuqa gaya inno taji dadin hakan har taita sanya albarka ga auren jariran kuwa harma tarasa inda zata tsoma ranta

dan murna nan take taje tai alwala ta bada nafila dan nuna jin dadinta ga faruwam hakan.
yanzun tunaninta ya tsaya cak na cewa zumuncin mukhtar da d'an uwansa yanzun ma aka farasa kenan, bisa ga da datai tunanin zumunci ya datse ganin mugun halin da mukhtar din ke tsurowa dashi, yanzu kam jitake koda yau Allah zai karb'i ranta itadai kam burinta ya cika Alhamdulilla harma takejin ta yafewa mukhtar abinda yai mata kmr ynda baffa ya jima da yafe masa shima a wata tattaunawa dasukai kwana 2 da suka wuce, sun masa afuwa dan sunsan dan nasu ba haka yake ba a da wataqil ajizanci ne na mutum shiyasa kullum suke masa adduar dawowa madaidaiciyar hnya yaci gaba da kulawa da kowa nasa kamar da.
Ismail da zainab kuwa jin bayanan baffa dayai yinin ranar sukuku sika yisa dan sun san km *da sauran kallo* ga wannan al'amari kam wnda basusan iya halin da zai sanyasu ba suda su baffan kuwa, shiyasa kwata kwata basuyi farinciki ba dan sun tabbata akwai mabi baya daga su mukhtar yanda suka qisu dinnan sunsan da sauran rina a kaba.
a ranar kam bayan taron suna ya tashi inno da wata maqauciyarsu hawwa'u suka gyara gidan yadawo fes kamar ba'ai taro ba, sannan ta tafi gida inno ta rakota har waje tana godia dashi albarka sanna koma daki,
sai kuma ta fito ta leqa dakin mai jego zainab daga bakin qofa tace "zainabu ince dai akwai shauran tuwon suna dan nida mlm kam shinkafar nan ta ishemu zainabu ku yara kuma na lura batta isarku ko" inno ta qarashe maganar cikin fara'a.
zainab tai saurin tasowa cikin murmushi bayan ta ajiye heenduh tace "wlh inno ban sani ba amman bari na duba miki naga ni" tana maganar ne tana qoqarin zuro qafarta waje inno tai saurin tareta tace "kul zainabu ai mu bamu barin mai d'anyen jego fita inba wanka ba, da wani uzurin na jikinta kuma, bayaga haka komi kuwa komi zatayi a daki zatai muna fiddawa waje mu kuma, dan haka yi zamanki d'aki bari naje na duba madafin naga"
haka inno ta wuce zainab ta bita da kallon batasan mi zata sakawa inno dashi ba tasan inno na qaunarta ta riqeta kmr ynda ta riqe isma'il sam batta nuna mata banbanci tsakanin su bata dauketa suruka ba kokadan, wasu yan siraran hawaye zainab taji sun sauko mata batareda tasan dalilin zubowar tasu ba.
komawa tai ta zauna ji heenduh ta motsa tana shirin yin kuka tana zama ta dauketa tareda sa mata nono a baki tafara sha ita kuma.
Inno kam ta duba kicin cikin manyan languna da aka zuba shinkafa taga ta rage nan ta rufe tareda bude dayan langar taga tuwo yayi sauran mulmile uku saidai babu miya, shiyasa ta d'aura sanwar miyar kan baffan ya dawo da yake har an fara kiran sallar isha'e shiyasa tana had'a jajjagen kayan miyan ta barta kanta tafaso saitayi alwala tashiga d'aki dan gabatar da tata sallar ishae d'in.
a kuma dai dai wannan lokacin ne firdauseey ce sanye cikin baqar after dres da gyalanta ta nade fuskarta da wani baqin niqaf ta fito daga gate din gidan nata danko jaririn na hannun hjy Hadeeza badashi ta fito, yanda take sauri sauri kasan ta qagara ta aiwatar da abunda ya fiddota lokacin.
kai tsaye inda ake siyar da shinkafar 6era ta nufa ta siya sannan aka had'a mata da fiya fiya original din marar sirki ta zuge jikkarta ta sanyayasu ciki ta wuce da wani d'an saurinta kai tsaye gidan isma'il ta nufa daman kunsan qofar babu zaure shiyasa tana zuwa kawai tasa hannu ta turata a hankali bata kaiga shigowa ba ta zuro kanta a tsakar gidan tagan shi wayam babu kowa da sauri ta ida kutsa kai cikin sanda ta ida shiga tsakiyan gidan taja ta tsaya a tsakar

gidan dan tarasa inda madafin nasu yake damba zuwa take gidanba bare tasan kansa, kallon gidan kawai take a ranta take cewa matsiyatan banza da wofi harni zaku so d'ana to wlh yafi qarfinku d'ana ba kalar auren 'yar talakawan 'yarku bane dan kuwa yau gaba d'aya zanyi maganinku kowa saiya baq'unci lapira yau dinnan tsinannu zakusan ni firdauseey bala'e ce masifa ce a gareku da kuma qazaman rayuwarku ta talauci.
da sauri ta boye jikin bayan qyauren qofan waje dan motsi da taji.
ta leqo sai taga qanwarta zainab ce ta fito da lullu6in zane da buta a hannunta ta nufi qofan bayi ta shiga ta rufe,
hango hayaqi na fitowa ne daga wani tsukakke waje wanda ke nesa da bandakin kadan da firdauseey taine hakan ya tabbatar mata da nan ne kicin dinsu, cikin sand'a ta isa wajen ta iske yar qaramin tukunya a wuta sai tafasa take dasauri ta bide tukunyar taji qamshin daddawa a ciki da cefane tuni ta tabbatar da miya za'ayi ga lokacin, murmushin cin nasara ta saki dan haka a hanzarce ta bude jikkarta ta fiddo kwalbar fiya fiya din duka ta juye musu ita tareda shinkafar 6eran ta d'au muburki ta motse su ciki ta snn ta maida murfin tukunyr a hankali ta rufe tai saurin ficewa daga gidan har tana kaiwa qyaure karo a dai dai nan ne kuma inno ta fito ta shiga kicin din da kuka a hannunta cikin leda, nan ta duq'a ta d'auko muburikin ta bude murfin ta fara zuba kukan tana murtsukawa saida ta gama tsab miyar ta dafu sannan ta zuba tuwon a roba ta juye miyar akai ta koma d'aki, tasake fitowa tana cikin gyara wajen knn zainab ta fito daga kewaye da addua dauke a bakinta nan taiwa inno sannu ita kuma ta amsa sannan ta wuce d'aki.
ana gama sallar isha'e kuwa baffa ya dawo ya shigo da sallama har d'aki nan ya iske inno sai fifita tuwo take da mafecin kaba dan tasan baffa baison abu da zafi in zaici, akai sa'a kuwa duka zafim ya fita, bayan ya ajiye buzun sa da carbinsa ya zauna gaban tuwon yana cewa "kai Allah shi miki albarka innon yaranta kamar kuwa kinsan dama yunwa nikeji ta tuwo aamn, murmushi inno tai tace "hmm ai gashi saikasa hannu muci daman kaina tsaya jira, yana gyara hannun rigarsa bayan ya gama nad'eta yace
"sannunku aiyau kunsha aiki ya hidima da jama'a na suna?,
yayi maganar tareda sha'afa wajen bismilla sai kawai ya tura lomar abuncun a baki, itama inno dai dai ta gama had'iye lomar tata tuwon tace "Alhambdulilla anyi taro lpia an tashi lpia kuma mlm" masha Allah abinda baffa yace knn nn sukaci gaba da cin tuwon, baffa yace "kash kaga mantuwa iriyar na d'an adam ko, wlh nmnta bnyi addua ba, inno tace wlh nima na shafa'a mlm kuma kaga yaune kawai aka samu akasin dan bismila aita zame mana jiki kam" baffa yace kinsan addini sauqi garesa yanzun ma bamu makara ba sai muyi tare ay, nan take yace "bismillahe fi awwalihi wa'a khirih,,,,,,, tsit yai ya
kasa qarasawa jinda yai a lokaci guda cikinsa kamar an daddaure masa hanji waje guda kuwa, kankace mi baffa ya fara fita hayyacinsa tuni
le6una sa sika bushe suka koma fari fat dasu sai shaqquwa yake, bnda salati bashi komi lokacin, inno na shirin yunqorowa itama taji cikinta ya kame kam kwata kwata babu dadi abun kamar ana jujjuya ta takeji tuni suka kwanta wajen sai wutsil wutsil na billaye sukeyi dan zuwa yanzu kam abun yakai geji dan har wani kakkauran kunfa kunfa fari tass mai sirkin jini jini ya fara fitowa daga bakunansu idanunsu a kakkafe rai yazo maqwar qwara madakata suna kallon sama sun kasa motsi kalmatisshahada suke yi daqyar Allah sarki kankace mi su baffa har rai yayi halinsa, dai dai nan aka dauke wutan nepa, babu jimawa da dauke wutar zainab ta fito da fitila ta dakinsu inno da nufin kai musu ganin an dauke wuta kuma inno batazo karba ba,

sallama tai tashiga dakin tana cewa inno ga futilan taku nak.. Sakin fitilar tai tayi kansu inno a gigice ganin da tai musu a halinda suke aciki shine ya tabbatar mata da cewa babu alamun rayuka a jikinsu ko. sakin fitilar tai qasan wajen takuwa fasa wata mummunan qara ta fadin wajen tana shure shure kanta daina motsin itama.....

By
Xexen Fasaha.
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🧯🧯
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️🧯👁️
🅿️🚺
I sma'il ne ya shigo gidan bakinsa dauke da sallama yana rungume da itacen daya bayar aka faskara masa shine yanzun daya fito daga masallaci yaci karo da mai faskaren ya kawo masa su cikin baro, dan haka yana ajiyewa saiya qara komawa waje ya qara d'auko wasu itacen ahaka har saida ya kwashesu tas ya sallami mai faskaren sannan ya shigo cikin gidan kai tsaye wajen famfo ya nufa ya bude sa dan dauraye hannunsa da gaban rigarsa daga qurar iccen sai dai kuma kashh basu maido famfon ba, dan haka matsawa yayi ya d'auko wata butar qarfe ta baffa yaji ta da ruwa a ciki kuwa, to dasune yasamu ya gyara jikin nasa sannan ya wuce dakin Zainab ganin bata nan sai jaririyar ce kawai kwance a tanason yin kuka shiyasa ya dauketa ya rungumeta a jikinsa bayan ya zauna gefen gadon yahau jijjiga heenduh danshi a zatonsa ko Zainab d'in ta zagaya ne ban d'aki. ganin shirun tai yawa yasashi miqewa da nufin zuwa dakinsu baffa kan ta fito bayin harzai fita da heenduh sai kuma ya dawo ya ajiyeta sanin dayai dare ne idan inno ta gansa zatai masa fad'a ne kan ya fito da jaririya da dare.
yana fitowa ya, shiga dakin tuntuben da yai da mutum ne shiyasa gabansa faduwa yana shirin duqawa ya d'auko fitilar dake yashe wajen qasa danya haska yaga waye wajen saiga hasken nefa wall sun maido, sai kuma suka qara daukewa kuma suka qara daukewa alamun wasa suke da wutar layuka nason faduwa.

girimm yayi tsaye wajen kamar butum butumi dan ganin mutanen dake yashe wajen a, qasa sai yake ganin kamar a mafarki ne yake ganin abubuwan.
sake maido wutar akayi wannan karon basu dauke va, I zubewa isma'il yayi gabansu baffa a rude yake tatta6asu dan yanzun kam ya tabbatar da abinda kwanyarsa yake gaya masa, dan haka yasake gigicewa yahau dadin "baffan inno Zainab ku tashi dan Allah,, wai mi yafaru daku ne eye? kutashi dan Allah aida gudu ya tashi yabat gidan ya je gidan baba yawale ya tasosa sao gasu sun dawo tare, Allah sarki baba yawale shima dud yarude daqyar ya dubi isma'il yace "jeka taro tasi muje asibiti,, haka kuwa akayi aka kamo su baffan da taimakon wasu jamaar dake zaune nn wajen aka shigar dasu baffan taxi dud da hakan saida mutane suka bi wata taxi din dan babu wnda bai girmama baffa a anguwar nn kaf babban mutum da, yaro shi kowa nasa ne, dan haka suna shiga asibiti aka kai su emergency koda likitoci suka auna baffa da inno tuni suka tabbatar da jimawa da rasuwan su saidai Zainab da tai nasarar farkowa tahau kuka kamar zata mutu sai kiran inno da baffa takeyi, haka likitan ya fito ya shaida musu tsoffin kam sun rigamu gidan gskia saidai haquri daga haka ya wuce.
kuka Ismail ya fashe dashi ya fad'a jikin baba yawale da shima yake kukan rashin babban amini na qwarai a, rayuwar sa gaba daya.
jamaa yan unguwa suma da zazzo asibiti banda share hawayen rashin mutanen kirkin basu komi, kan dole suka haqura aka d'auko gawarsu baffa aka dawo gida.
Zainab da isma'il kamar ba a hayayacinsu suke ba, daqyar baba yawale yaita nusar dasu sannan suka daina kukan haka suka kwana azaune waahe garin ranar talata aka sallaci gawar wakin guda biyu akaje aka rufosu dan isma'il yana ganin yanda aka kamo baffa akasa a cikin rami zubewa yayi wajen a sume mukhtar ma baisam sanda ya fashe da kuka ba a karo na farko ganin dayai cewa da gasken dai su baffan sun tafi, I amman dus halin nn da ake ciki ko magana bata had'a sa da Ismail ba, I daqyae aka samu isma'il ta farko sannan aka juyo da makarorin nasu baffan bayan adduoen da dubban jamaar suks ryfesu dashi bayan gama sasu qabarburan nasu.
abun mamaki baya qarewa a, duniya indai kana da rai a jikinka tofa kana da sauran kallo, ana dawowa sam mukhtar yaqi zams zamn amsa gaisuwa qofar gidan Ismail dan zafin qiyayyar sa, sai dai kawai yasa aka daura masa qaton tamfal a harabar qofar gidansa shida mutanensa nan shima yai zmn amsa gaisuwarsa wato wajen amsa gausuwar yazama guda 2 knn kai duniya kuma yan ywa ciki daya uwa daya uba daya 😭.
haka akaita fito da abincika kala kala gidan mukhtar hardasu ruwa faro da lemuka sai wasu daga cikin makwadaita na, wajen Ismail sukaita dawowa wajen mukhtar gamin yanda namomi keyawo a kan ainci wanda shi isma'il ko tsoka daya babu a nasa abincin, dan fara da mai ce ma shi aka fito musu dashi cikin gida.
ahaka saida akai kwana bakwai ana zaman makoki sannan aka daina zaman, I saida meron tsimbe tai kwana 15 sannan ta duro cikin garin kaduna a ranar lahadi, kai tsaye ko jikkar ta bata ajiye ba ta nufi gidan yar tata, I qearai firdauseey tai murna da ganin uwar bayan ta huta ne firdauseey ta fad'a mata rikicin da akai gameda daurawa danta aure. wata mulmulallar ashar mero ta yi sannan tace amman kinmin dai dai da kika aika yan iska barzahu wlh, I firdauseey tace"hmm wkh naso ace harda Zainab da shegen isma'il dun nn sukaci abuncin nan dana huta da ganin baqinciki, mero tace ko iya hakan ma da kikai musi ai ya ishesu takaici hakane mama, dan yanzun kam dari dari suke ma kada jamaar susan da aure tsakanin yaranmu gudun rasa

yarsu.
mero tace kamarya bngabe ba, I firdauseey tace qawata hjy Hadeeza ce ta bani wannan shawarar nikuma na fadawa mukhtar, sai gashi ko yasa waau yan tauri nacan saman anguwar nn sun dura wa isma'il din cikin dare suka tsattsare su da muggan makamansu sukaimasa kashedin cewa muddin ya kuskura ya sanarwa da yarinyar sa tanada aure a knta inta girma kokuma suka sanarwa wani tofa bsbu shakka sai sunxi sun daddatsa yarinyar a gbnsu, kuma suka qara cewa mukhtar yace a shaida musu billaheel azeem shida knsa zai harbesu da bingarsa muddin suka fiddo mgnr auren ga yaran konan dashekara nawa ne kuwa yana sauraransu.
dole suka firgita suka dau wannan alqawalin kuwa dudda sunsan mukhtar dinne ya turosu kmr ynda ogan yan daban yaxshaida masa aiken yayansa ne kmr ynda yace musu su sanar masa in sunjr, I inkunne yaji to gnfar jiki ta tsira knn, I kum daga nn suna fitowa suka fad'a gidan yawale shima suksi masa barazanar kisa da 6ata masa suns a anguwa na cewar yana 6ata yara qanana dole shima ya ride yadauki alqawalin bazai tada maganar ba dan shi ba mutuwar yake tsoro ba bata masa suna dazsuks smbata zasuyi kyma yassn zasu iya inda yan isksn titi ne komi aka hiyasu kudi aksn suyisa zasuyi sa bsbu fashi kuwa.
firdauseey na kawowa nn suka kashe tafi da mero tacr "yawwa yata lakkaikam yau na shaida kedin da kika shs nono na bski zubar ba, I kums gobe goben nan zan koma wajen bhokammu akan ya qara qaimi wajen zautar mans da mukhtar yazamo takalmn sawarki firdauseey sai yanda kika saitasa snn, I firdauseey tace ai Wlh mama hjnma bakiga ybda yake rawar jiki ba inna nuna bn son abu, yanzu haka ma dana bude masa wuta doke yasa aka qaro maaikata dan aikin gudan da zaki dawo, miqewa tsaye mero rai tace kinyi sai dai ki qara matsa number dan nima inason zuwa qasashen turai ibga turawa, I firdauseey tace aa mama kikace haji kuma zaki?
tamushe fuska mero tai tace "nafasa wajen turawq zanje un gnsu a fiki ba cijin tv ba alquran, I ke daga can ma har birnin qudus zani in gano qarshen bangon duniya inda ance daga nn babu nisa, I firdauseey kuwa dariya kawai takewa uwat har saida mero ta d'auko jikjarta tabar gidan tana fitowa ta bude jikkarta taji babu sigarinta dan haka saita tsallaka titi wani shago ta siyo kwalin tabar tazo tsallkowa knn ta jiyo qarar harbin bundigogi daga can nesa a titin kawai sai gani ayi dud mutanen dake wucewa a samn hnyar suna kwanciya rubda ciki plat a qasa tareda mimmiqe hannuwa qasa ita kuwa sai abun ya burgeta ta.washe baki tana hngo wata baqar mota mai budadden jiki ta nyfota wndaga alana nn ciji harbun bindogin ke futowa , ashe wasu muggan yan fashi da makami ne sukaje suka fasa wani bankin da ake canjun kudi da rana qiri qiri suka saki wuta dud suka karkashe maikatan tsarob wajen suks kwaso iya sonsu da suka fito ne sukaci gaba da sakin wuta a bakin titi murane sai boyewa suke wazu na kwanciya qasa san sunsan kalae giggan yan fashun nn basu so ana kallonsu, I wani bawan Allah kuwa fitowarsa knn daga masallaci da carbinsa a hannu baisan mike faruwa ba dan sun zata kallonsu yake shiyasa babu wata wata dasuka dags qatuwar bibdigar nn tasu sai saitin cikinsa suka dinga sakar masa harsashi har saida gaba dayan hanjin cikinsa suka fito waje ya fadi nn qasa matacce nn sukaci gaba da tsala gudu a motar tasu basu damuba, dud wanda suka gani kwance kife a qasa babu ruwansu dashi ana haka kuwa suka isko wajen meron tsimbe I wacxe ke tsaye tana washe baki butunta kawai tayi arba da masu varin wutar nn kota jinjina musu da raahin imaninsu klr nata aiko batai auneba ta dinga jin saukar bullet mnya mnya akota ina cikin

jikinta saida sukai mata daga daga jini sai zuba yake kmr an yanka shaniya suka wuce abinsu mutanen dake kwance jin kalar harbin da akeyi a lokacin ne yasa jikinsu qara tsuma saida sukaji shiru ne nasama da kusan awa daya snn suka tashi sukayo kan mairo da jikinta yai fisis fisis, I kai daban hannu daban qugu daban cinyoyi daban yanda kasan an tada mata bom a jijinta haka maau raunin cikinsu sukaita zybewa wajen a sume dan tsabar firgita na ganin ynda aka ciccirewa matar jikinta dan basu ma ganeta ba har saisa aka gama hada jikinta waje guda ne kana wani maqicin mlm zayyanu mijinta yace "innalillahe,,, wannan ai meron tsimbe ce matar mlm zayyanu mai almajirai,, I nan waau daga cikin jamaar wajen wanda mero tasha wulanqata wa suka dara zamewa suna tafiyasu tareda mata Allah qara sannu a hnkali dud saida kowa na wajen ya yaye aka bar gawar mero da mlm isihu maqocinsu sai wani malami shima ya tsaya sun rage su 2 knn, nan mlm ke cewa ashha shiyasa akeso mutum ya kyautata alaqarasa da mutane amman wannan mata ba haka ba, nima nn na tsaya ne bn tafi ba sbd taimakon musulinci vawai dan ita ba danni kaina wlh ta taba turen rawani a gabn jamaa I kn na mata waazi svd tana zagin mlm zayyanu mijinta, mlm isihu yace wlh nima haqqin maqota kawao yasa na tsaya da muka mutuncib mijinta amman daba haka ba bxn nuna ma nasanta ba, I danni nn wanban baiwar allahn cin mutuncin datake mn da iyalaina kusankullum Allah yai yawa dashi, mlm yace babu koni ai dan Allah zamuyi mata, I nan suka tsaida mai amalanke aka kwashi fisis din jiki I mero aka watsa a ciki aka nufi gidan mlm zayyanu mai almajirai ko kare kiwa bai biyo bayan suba, hmm AllAh knn, yanzu mero kinga iyakar ta duniyar ko?ina wulaqanta mutane ynxu da sauransu?? cewar mutumindaya baada aron baronsa sabida malamin nan har ta samu alvarkacin sanyata a ciki ma.
shiyasa akeson ka gyara gobenka dan gbnka tai kyau, I daga haka bai sake cewa komi ba har suka isa qofar gidan ya juyeta qasa kamar kayan banza qudajesaibinta suke abun qyama, I daga nn yaja baronsa ya tafi da nufin kaita wajen wnki dan dud ta 6aci da jinin mero baq'i q'irin dashi kuwa ...

By
Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

```Afuwan page d'inda ya gabata an samu type errors, mntawa nayi na turo muku shi bawanda naiwa editing bane ashe```•

babu kalar haukan da firdauseey bataiba da taji mutuwar meron tsimbe uwarta, tanaji tana gani wasu yan tsirarun mutane da basu fi su 10 suka wa mlm zayyanu kara akaje rufo ta.
iyakar ta duniyar kenan mero aje a girbi abinda aka shuka a lahira cewar wasu daga cikin mutanen wajen.
saida firdauseey tai sati d'aya sannan aka fara samun kanta daga d'an q'aramin haukan data somayi,
tana qara dawowa hayyacinta kuwa banda kuka babu abinda take sai da sannu sannan ta dangana dan ganin cewa meron tsimbe fa tatafi bawai dawo mata da ita za'ai ba, kuma ita yanzun in zata ganta ai sai
iya wajen inda gudun ceton ranta ya tsaya dan babu wnda ya ta6a mutuwa ya dawo bare a fara ta kanta. ahaka dai har aka kwashe watanni har bakwai da rasuwar meron tsimbe ko, lokacin firdauseey ta murmure tasaki ranta gaba d'aya ta kuma d'ora daga inda ta tsaya na rura wutar qiyayyar isma'il a cikin zuciyr mukhtar kullum kuma cikin cin nasara take.
amincin su kuwa tsakaninta da hjy Hadeeza gaba kawai yake dan ynzun hjy Hadeeza ke zuwan musu wajen boka tana karb'o wasu qarin magungunan suyita bankawa mazajen su kuwa, ynxu kam duniya ta zame musu sabuwa dal a leda.
kullum mutane suna q"ofar gidan alhj mukhtar maula wanda zuiyarsu take a mace knn, wataran inya fito ya basu wani lokacin kuma yaqi fitowa harsu gaji da zmn jirnsa qofar gida su tafi suna masa Allah wadai.
wannan abun kuwa na matuqar qonawa firdauseey zuciya ita tafison taga shima isma'il yabi layin 'yan maula a wajen mukhtar yanda zatai masa dariya kuma taji dadin sake wulaqanta sa amman sam yaqi zuwa, wannan yasa a daren ranar ta samu mukhtar zaune a falonsa yana kallon labarai na legos ta zauna kusa dashi khaleepa na hannun ta, da sauri mukhtar ya karb'esa yana masa wasa amman sam yaron yaqi dariya yanda ya kamata, mukhtar ya dubeta yace "gskia madam yaron nan naki saraki ne dan inya girma ba qaramin miskilin mutum za'ai ba, yanzun kalli fa sai dai yaimun murmushi innai masa wasa bawai dariya ba" firdauseey tace "hmm alhajina knn, kai dan yana ganinka nema kullum shiyasa kasamu ma murmushin amman in baki suka shigo bakaga yanda yake komar musu ba, kadan daga halayan khaleepa na knn tun tuni nima na fahimci hkn, shiyasa nike masa laqani da mai tsada na, hmm amman dahar wani za'a cutar man wannan kyakkyawan yaron nawa a had'a sa aure da 'yar gidan matsiyacin nan wanda kansa ma nazo mu tattauna yanzun hakan nan, mukhtar yace "wannan ai tsohon zance ne kada ki damu madam dina, dan angama wuce wajen tuntuni bana tunanun suma basu mance wannnan jinjirin auran ba da baffa na ya daura kan ya rasu dan matuqa sunji tsoron abunda nace zan aiwatas garesu muddin suka sake *gskiyar magana guda d'aya* ta fito daga bakinsu, dan haka in sun gaji da ajiye tar tasu sayi gaggawar aurar da ita a cikin adalcina na
```

cewa zan 6atata ga maza a tambarin dud wnda yazo nmn aurenta danace zan sa a 6atar dashi un bai jiba amman yanzun taci albarcin auren d'ana dake kanta dan haka yanzun sunada right din aurar yarsu ga kowa ma amman badai gold boy dina ba" cikin jin dadi firdauseey tace "wlh kuwa suje can su qarata matsiyatan" mukhtar yasake cewa "mman wane batu zamu tattauna game dashi din kmr ynda kika ce yanzu kuma?
harda gyara zama firdauseey tai tace
"naga wannan dan aikin teaching din nan da matsiyacin isma'il dinn keyi yana kar6ar wasu 'yan kud'i can nasa runtse ga hannu to shine na lura sai faman tadawa mutane kai yake knsa, yana alfahari dashi to inada buqatar kasa a koresa daga school din kwata kwata alhajina sai muga ta tsiya da feleqe iriyar nasa muga dami zaiyi taqamar ne? dan wlh so nike inga abinda zaici saima ya gagaresa ya zamanto mana a qarqashin mu zaizo nema mukuma musa q'afa mu hauresa in munso mu watsa masa tsaba ya tsattsaga in munqi kuma mu watsa masa garwashi ya fuce da gudu kamar karenmu lega na bakin gate din can"
wata 'yar q'aramin dariya mukhtar yasaki yace "indai dan wannan ne an gama madam din"
hakan kuwa ta kasance mukhtar yaiwa makarantar da isma'il ke teaching tsinke tun kan ya wuce office nasa ma, yaje ya sakarwa shugaban makarantar kudi akan maganar korar ismail, dayake an samu marar tsoron Allah principal din dudda yasan isma'il na sahun farko daga cikin mnyan malmai da suka bada babbn gudummuwa ta wadataccen ilimi ga yara a makarantar dan har award aka basa last year na nuna haziqancinsa da jajircewarsa amman bai duba wnn ba ya nuna qarfin ikonsa na matsayinsa nan take kuwa principal din yasa aka nemo takardun Ismail akai masa kaca kaca dasu dajan biro kora ta wulaqanci akai masa babu fansho babu garatuti gashi an bata rakardun nemn aikin da mummunan sheda a kai ta yanda indai anan Nigeria ne babu ynda za'ayi government ta sake daukarsa wani aikin kuma.
Haka mukhtar yabar wajen ko a jikinsa, ismail kuwa yana zuwa aka basa takardar kora batareda wani dalilіba ya kuma tanbayi ba'asin hkn nan take frincipal din yace
"d'an uwanka ne ya biya akai masa wannan aikin kuma yace in kazo in gaya maka in kanada buqatar wani aikin to yana neman mai kula da karensa lega a gidnsa zaka iya zuwa ka fara ma aikin kula da karen daga yau ma in kaso, wannan saqo ne ya bani zuwa gareka kuma gashi na isar cikin ikon Allah dan haka zaka ita ficemun daga office na"👉🏽 yayi maganr yana mai nunawa Ismail din qofar fita a wajn da hannunsa.
Allah sarki Ismail rayuwa tai masa halin nata na rashin tabbas dan haka ko yana hawayen baqinciki yabar makaranta tareda mata kallon qarshe.
koda yaje gida ya fadawa zainab tausar sa taitayi tareda nuna masa amfanin haquri ga dan adam, inda take cewa indai yaya firdauseey ce tasa mukhtar kewa qanensa haka to da sannu zataita ganen qarshensu inda gashi ta fara ganin alamun hkn daga mamarta marigayya meron tsimbe.
dole tasa isma'il fara sana'ar gwari can bakin hnya tun lokacin, hkn kuwa ba qaramim faranta ran mukhtar da firdauseey yayi ba ganin qasqantar isma'il din hartakai haka, shiko isma'il baiji komi ba dan dayaje yana maula ana tozartasa qwamna ya yi sana'arsa komun qanqantarta indai zata dauki nauyin sa da kuma na iyalensa haka yaita sana'arsa kuma Allah ya sanya masa albarka ga abun dan shi kadai ke kalar sanaar wajen shiyasa dud kusan jamaar anguwar wajensa suke siyan kayan miya ga kuma sauqi da sauqaqawa dan sanin dayai tsada bata kawo riba, kuma kad'an mai amfani tafi mai yawa albarka.

a haka a haka dai kuma rayuwa nata tafiya babu abunda ya sauya daga muguwar qiyayyar da mukhtar kewa isma'il.
zuwa yanzun ma kuma mukhtar ya qara samun girma a office dinsu shiyasa arziq'insa kullum qaruwa yake, babu wnda ya kamo qafarsa a kudin dud doguwar santar anguwar sun nan dudda akwai masu halin kuwa a cikinta da kuma marassa shi remix ward knn.
wasa wasa kwanaki na tafiya har yau gashi shekara 23 da haihuwar yaran nasu..
haka khaleepa ya taso dason d'an uwan mahaifinsa tunda ya mallaki hankalin kansa kuwa, kullum sai yaje gidan tun mukhtar na masa fad'an daina zuwa har ya gaji ya barsa danba qaramin so suke ma khaleepa ba.
saidai kwata kwata khaleepa kokadan basushiri da heenduh ko shiga gidan yy iyakar mgnrsa da mama Zainab ne, dan ya fahinci heenduh akwaita da tsiwa, fad'a kuwa koda uban waye yinsa take inya 6ata mata, saidai tana shakkun khaleepa da kuma haushinsa na ganin girman kansa it's t much ga jama'a musamman mata, kodan yaga yanada kyau ne da kowace budurwa a anguwar take bada knta a kansa shi kuma yake yarfata da rashin ko'in kula kalar nasa ne oho. kuma dud intaso tana shiga godan babanta mukhtar tadauko kalar abin sha data keso ta fito tun firddausy na zaginta tana korarta harta haqura takoma cemata mayya yanda taga koda fakar ido ne sai heenduh tazo gidan ta dauki abinda takeso itada qawarta snn su fice inta ga dama kuma saita kwashe wata daya ko qofar gidn bata kalla ba bare taje, kuma in taje komi takeso bata roqon zata dauka saidi lawai ta dauka tasha ta wullar musu da robarsu nn tai fitowarta dan mmnta tai mata kaahedin kada ta qara daukar abunsu ta kawo mata shi nn ckn gida inda ita batajin mgn, heenduh kan turo red lips dinta jawir wur dasu tace ' to mama na daina' hkn kuwa bazai hanata gobe ta koma gidan ba inta kado mata, dan hatta yan aikin gidan sunsan da zaman heenduh headache kamar yanda sukaji yalla6ai khaleepa na fad'a mata dud in sun had'e ckn gidan nasu, ita kuma takan yatsuna masa kumatu tai gaba dud intaji yace mata ciwon kai din nan kuwa.
dayake khaleepa karatun likitanci yake shiyasa kwata kwata bai samun zama a gida inba weekend ba da zasu zauna shida abokn sa su yunus a nan barandar kofar gidnsu smn kujeru suna fira, abinda heenduh ta tsana knn kallo intazo wucewa ta wajen zuwa gidansu sa'a qawarta sukuwa abinda suka sarewa gaba knn kallon dud budurwar da taxo wucewa kuwa, musamma ma ita da suka fiye sawa ido dan cut cheif baby suke ce mata, dan heenduh kam ba qaramin kyakkyawan gaske bace, sautari itake tsokanar khaleepa fada inyazo gidnsu ammn shi ko kulata baiyi bare ya tanka ta, qwamma yai shirunsa yafiye masa in yaje gidan inya iske mama na wani aikin dadai ya biye matan harta sashi mgnr dole. danshi bb wata ma mace dake zaune rayuwarsa gaba daya bare yasa damuwar ta a ransa dan yasan karatun sa nada son nutswa addabarsa datake ne lokutta da dama shine fa harya sa mata sunan headache to dagann kuma kowa saiya dauki sunn daga cikin aboknsa yana ve mata hkn, musaman babban abokinsa yunus.
lokacin da heenduh aka zama yan mata sai rawar kai ya qaru dan tana jida kyaunta kamar ynda kowa ke fada mata cewa kalar kyanta ba kowane Allah yaiwa baiwarsa ba a 'alumma, shiyasa feleqe iyayi rangwada tsiwa fafa da nuna ita din babban yarinya ce babu wanda heenduh battayi wannan ne ke qara sawa khaleepa jin haushinta a ransa danta kula kan heenduh ya fiye rawa ba kadan ba.
ahaka har ya tafi qasan waje dan qaro karatunsa wanda hkn ba ba qaramin dadi heenduh taji

ba, dan ganinta kusa dashi baqaramin laluri take daukar abun ba, kuma koba komi sun daina takurata da wannan muguwar majalissar tasu ma.
saida ya shekara d'aya cip sanna ya dawo Nigeria cikin wannan satin da kwalinsa na cikakken likitan mata ta kowane fanni wannsn kenan, doctor khaleepa ya qara girma yazama cikakken namiji qaqqarfan gaske
sabida ya biyo jikin babansa mukhtar dogo qaqqarfane sosai ko ina kuwa na jikinsa a murd'e yake cikeda yalwar gashi a faffaden qirjinsa da jikin hannuwansa gaahine kwance lu6 lu6 a kyakkyawan farar fatarsa, yanda kasan balaraben mutim iriyar na musura dun nn tofa haka doctor khaleepa ya koma sak, tsare gida kuwa da rashin bada fuska ga mata sai abunda yaci gaba, koda yadawo yaga heenduh yanda ya barta haka take dan bazata wuce iya kafad'arsa bama a tsayi, saidai yaga ta qara masa hske da kyau sosai komi nata yaqara cika dm dam dasu alamun maqerin budurci nata kera mata siffofinta kowane kwana, samari kuwa kamar su kashe heenduh dnma bawai kulasu take ba saidai saurayinta musaddiq daya nace mata kamar qarfen qafa dudda rashin kulawa da take nuna masa kuwa, kudi yake kashe mata bana wasa ba, wai nanma dan bata karba sai taga dama, dan harso yk ta dunga tambayar sa abu kai tsaye, amman taqi dan batada halin roqon maza ita dud rawar knta kuwa wannan kenan.
dawowar khaleepa wannan satin ne iyayensa ba qaramin had'a masa fatittitika na murnar kammala karatunsa sukai ba, khaleepa har aransa yaso kawunsa isma'il yazo wajen amman sanin halin dadynsa yasa yai shiru tukun.
kwana d'aya daya wuce ne wato jia mukhtar yaiwa ismail dirar mikiya a gidansa karo na farko tun rasuwan iyayensu kuwa, yai rashin mutunci akan sunbawa yaronsa abinda ba cimarsa ba yasha wuya harya ce saiya ramawa dansa,
ran heenduh ya qara 6aci ganin ynda ake cin mutuncin datake iyayen ta kan wancen dan qa'idar, dudda haqurin da baba ismail ke basa kuwa amman saida ya raunatasa a yau din sakamakon turesa da yayi da
motarsa har ya kaisu suka tafi cemist shida heenduh dan ayi masa dreesing.
in baku manta ba masu karatu a nan aka tsaida labarin.

An dawo labari yanzun labarin
zaici gaba da kasantuwa.....

By
Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁🥡👁
🅿2⃣1⃣
T afe suke heenduh na riq'e da hannun babanta cikin tsabar sake tausaya masa ganin yanda yake jan q'afar cikin dauriya, tuni idanunta suka sake cikowa da ruwa, abu ga mai saurin kukan nan dai taku, ba 6ata lokaci kuwa hawaye suka fara zubo mata kuma a fuska. baba Ismail sarai ya kula da hawayen da heenduh d'in ke masa hakan ne ya sashi dakatawa da tafiyar tasa a dai dai q'ofar gidan baba yawale, dybanta yayi yace "heendu na inda bazaki daina mun kukan nan ba to shiga nan gidan baba yawale inje amin dreesing d'in ni kad'ai na harna dawo, dan nikam dai bazan jera mi tafi dake kina mun kuka a hanya ba ki jawo muna hankulan jama'ar anguwa akan muba"
yayi maganar yana kallonta.
da sauri heenduh ta share hawayen tace "yi haquri babana na daina kukan Allah kuwa to mu tafi kaji ko? "
murmushi baba Ismail yayi a ransa yace "hmmm heendu badai tausayi ba"
amman a fili sai yace "yawwa ko kefa, ya kalli gidan baba yawale yaga alamun yana ciki, bai shiga ba amman ya q'udurta a ransa cewa in suka dawo daga dreesing d'in zai shiga gidan ya gaishesa kamar yanda ya saba a kullum, dan yanzun yasan inya shiga tayarwa da baba yawale hankali kawai zaiyi da raunin jinin qafarsa.
basu q'ara wata klr doguwar tafiyar ba suka iso cemis din haruna.
haruna mai cemist saurayin matashin ne shima, kma yayi matuq'ar mutuwa akan son heenduh shima kuwa ba kadan ba, amman sai dai har yau ya gagara samo zuciyar gimbiyar heenduh dan bata ta6a basa damar halattar zuwa qofar gidan su ba koda wasa dudda tasan yana son nata kuwa dan yasha fad'a mtn
amman ko kadan bai gabanta ita,
ina ruwan manya heenduh.
dan haka haruna na ganinta da sauri ya miqe daga saman bencin majalissar su shida abokansa sakamakon ta6osa da wani abokinsa isa kabeer yayi ta hanyar cewa "kai haru gafa gimbiyar mata nan tafe da tsofonta may be wani abun za'ai musu"
yana isa kuwa har qasa ya gaisheda baba Ismail sannan ya miqe bayan baba isma'il din ya amsa haruna ya fara magana yana mai kallon qafar baba isma'il din cikin tausayawa yace "subhanalla baba ciwo kaji ka qaraso to sai ai dreesing din wajen sabuda shigar qananun 6oyayyun citukan tetones a ciki" baba isma'il yace "wlh kuwa ciwo ne kuma abinda ya kawo ni kenan nima wato dressing din"
nan take haruna ya daga murfin nasa na katako wanda zai shigar dakai cemist din ya shiga ya d'auko hydrogen da auduga da bandj nan baba isma'il ya zauna kan wata farar kujera har aka gama masa dreesing din wajen sannan ya miqe tsaye yace "yawwa mlm haruna sannunka ngd

fa nawane kudin naka mlm haruna?" cikin murmushi haruna yace "haba baba wlh Allah sawaqa na kar6i kudinka, aiko wani ka kawo bazan karba kudin kuba koda ban san shiba kuwa, kaje kawai Allah sawaqa baba ,zan zo bayan kwana 3 na kwance maka dreesing din insha Allah a gida" ya qarasa maganar yana mai miqawa heenduh wasu magunguna yace "heenduh su baba zai dunga sha safe rana da dare"
godia baba isma'il yake masa da sauri haruna yace "baba ka daina dan Allah bakomi ay"
haka baba isma'il ya juya ya fara tafiya yana cewa "nagode sosai to haruna AllAh jiqan mlm musa" (mahainsa)
"aminnn baba"
ganin da haruna yai heenduh na shirin tafiya tabi bayan babanta yasashi saurin cewa "ah hm gimbiyar kyawawan matan duniya ko zama baki ba da kika zo kinata tsayuwa fa?
wata q'atuwar harara heendu ta sakar masa daman tun zuwanta wajen dud take a tsarge sakamakon wannan shegunayen masa'idawan idanuwa na abokan haru din na nan majalissar sa da sukaita binta dashi uwa mayu, dan haka cikin mafisar sauke hushinta akan haruna din ta sake watsa masa fararan tas qwayar idanun tan nan tace "anqi a zauna d'in, koko zama ya kawo ni ne bare kace in zauna cikin qatti ko ance maka ni yar iska ce?,, da sauri haruna ya kama bakinsa da hannun sa guda na haggu yace "tooo afuwan gimbiyar mata hjy heenduh abin baikai haka ba wlh ba haka niki nufi ba ni sam dam wlh, nasan tsayuwar ne babu dadi ay kuma shiyasa kikaji nace hakan"
wata sabuwar hararar ta sake sakar masa bayan ta saki qugunta taja tsoki tace"wannan kuma ya rage ya ruwanka mlm"
daga haka bata sake furta masa komi ba ta bi bayan babanta daya fara tafiya a hankula sabida taka qafar.
tana barin wajen kuwa abokan haru suka fasa ihu da sowa,,, isa kabeer yace "kai billaheel azeem ajin yarinyar nan yaimun a duka rayuwa fa sosai" musa dake gefensa yace "hm kaima ke fad'i anaji ay"!
nan kowa yaita tofa nasa tawun a wajen kuwa.
zama haru yayi yace "to yabon nata ya isa haka 'yan karere bansan iskanci fa kun zauna sai mgnr matata kuke"
isa kabeer ya doki kafadansa yace "kai d'an iska matarka da ubanwa ye ya baka?,,,, ko damuwa ma batai dakai ba ka zauna kanata kyarmar jiki kan mace" haris da sai yanzun yasake bude bakimsa yayi mgn sakamakon wayar daya gamayi da budurwarsa yace "kai ku qyalesa dan rawar jiki ga mace kamar henndu namiji zaiyi fiye da hakam ma, dan kaf samarin anguwar nan babu wanda baiyi yaqi wajen waccen zazzafar babyn ba ya gaji ya daina badan yaso ba, kai bari in taqaice maka ciki har dani wlh amman ganin danai babu sarki sai Allah dan yarinyar tanaji da kyaun ta bata sauraran kowa shiyasa na haqura na sami tema ta, danna lura qilan sai manyan 'ya'yan manyan mutane take saurara irinsu musaddiq dan gidn Alhj musa kaita".
fashewa matasan suka karayi da dariya suna cewa "gaskia ka bada maza fa hakan yawa ne fa, wayace maka ana gudu kan neman kalar su heenduh beauty?
gskia haru ka qara wuta kada ka sake ka rabu da waccen hurul aini din har sai inda qarfinka ya qare" dariyar jin dadi haru yayi harda shaga dan dogon gemunsa daya aje yana cewa "Yawwa abokaina ai sainaga abunda ya turewa buzu nadi,
Hari's cikin dariyar mugunta yace "ai kam dai ina mai tabbatar maka abokina babu abunda zai

turewa buzu nadin nan nasa face wahala wacce kake sa kanka a ciki akan heenduh beauty wlh, kaje kuma gata ga kana nn ay, zakaga wulaqanci kuwa inda har bata gayyaceka ba kk shirin sa mata kai a rayuwar ta, hmmn koda yake hausawa sunyi gskia da sukace mai rabon shan duka bayajin kwa6a sai yasha tukun, dan haka kaje insha maka Allahumma kuwa munanan zaka zo bamu lanarin ketaka da yarinyar can zatayi, zanga hmm sarewar ka ranar" duka haru yakai masa gamida cewa "mugu dan baqinciki sainayi power kuwa a gunta saidai baqin ciki ya kasheka,,, isa kabeer yace "wlh kuwa abokina saidai baqin ciki nasa fa ya kashen sa, yaci gaba da cewar guys
wai ashe har doctor khaleepa ya dawo? haru yace "eh man ya dawo wajen sati biyu knn ma" musa yace "kai guy din ai yayi wlh akwai harkar girma wacceb babu qaranta a cikinta sai dai kuma shegen fadin ran masifa ne dashi,,, dariya suka qara kwasa a wajen haru yace "mazaje mazaje mazajen kenan ay, danni wlh guy din takunsa yana burgeni kai kominsa gaba daya burgeni yake over2, cikin tsokana hari's yace "inda yana kam burgeka mizai hana kaje ka basa shawarar ya auri Sister dinsa heendu dan wlh dud duniyar nan in maka na babban mahaukaci to sunyi masifar dacewa da juna bil haqqi nike fad'a maka hakan haru"
Isa yace "bala'e knn, kai km yanzun kana nema dauko dala ba gammo knn, alhj mukhtar din zai bari hakan ta faru yanda ya tsani qanen nan nasa dama talakawa duka tab? ai kama daina wanga zance d'an saurayin " kowa na wajen yace "wannan gskia ne isa qilan in za'ayi auran ma kuwa saidai in alhj mukhtar bai duniyar nan anje can qasan qasa".
haru yace "ku rabu da d'an isakan mai mummunan fata insha Allah heenduh beauty tawa ce" dariya kawai haris yayi a haka matasan sukaci gaba da firar su kan dai..
heendu kuwa tana iske babanta ta kama hannunsa sukaci gaba da tafiya mutane a hanya sai yiwa baba isma'il sannun ciwon nasa suke har suka isa gidan baba yawale kuwa.
nan suka iskesa yana sallatul tazbihi.
zama sukai nan kan buzunsa baba isma'il cikin maganarsa ta yanda bazai takura baba yawale dake halin sallar ba ya dubi heenduh yace
"heenduh gskia kam haruna ya....

By
Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

Z ama sukai nan kan buzunsa.
baba isma'il cikin maganarsa yanda bazai takura baba yawale dake halin sallar ba ya dubi heenduh yace
"heenduh gskia kam haruna yaron kirkine dubi fa dan AllAh iriyar alheran magunguna daya bamu haka d yawa batareda ya kar6i ko sule namu ba"
baba isma'il yayi maganar yana mai cigaba da duba sunan magunguna, itako heenduh ta6e 'yan red lips d'inta tayi tace"baba dan ya bamu wannan 'yan magunguna din, shi yaga dama ya bayar ai ba wai dole mukai masa ba, to dan haka ni banga abin a jinjina masa ba inda dai shi yaga daman badawa ba kuma uzzurasa mukai ba ko babana?"
d'agowa baba isma'il yayi ya dubeta ya girgiza kansa kawai yayi murmushi,
sam shikam wnn halayen n heenduh wani zubin yakan kasa fassara mata su da awane matsayi ta dauki kanta?, yanaga heenduh data fito tsatson masu arziq'ina iyaye to daba haka ba,
shikam ya godewa Allah dabai basa mahaukatan kud'i ba da zaisa 'yarsa tana jin ita watace wataqil har hakan yasata yaga jama'ar annabi danya kula diyar tasa akwai son taq'ama kalar ta 'ya'yan manya na masu dashi, banda haka har yausher wanda yai maka abun arziq'i ita a nufinta abun yayi qanqanta da agode masa knn koko?, murmushi ya sakeyi yace a ransa "heenduh wannan halin dai naki ba nawa bane bana mamanki bane heenduh,, hmm rigimammiya ta, yarinta ne kawai ke d'awainiya dake nasan wataran zaki yi hnkali ki daina dud randa kikaje dakin mijinki zaman aure har kika fara hayyafa,
ina roqon Allah daya bani qarfin gwiwar ciyar daku da tufatar daku batareda gajiyawa ba har na gaza ya rabbu nakaiga sarewa ba amimn, hmmm rayuwa knn, lokacin daya tuno su baffa da inno da kuma abubuwan da sukaita faruwa na lokuttan farinciki da iyayensa da yayansa mukhtar amman yanzun gashi yazamo kmr ba aiba sam, Allah ya kawo mana qarshen abin.
"aminn babana" cewar heenduh baisan addu'ar tasa ta fito fili ba.
sauke qarfaffan ajiyar zuciya yayi sannan ya dubeta heenduh yace "q'warai kuwa heenduh haruna ya cancanci godiya matuqa nidai a wajena, dan dayace kud'i zai kar6a da bansan yanda zanyi ba inda bani da isassu na siyan adadin yawan iya magungunan daya bani dan dud nayo siyayya da kud'in a kasuwa, duka duka a cikin aljihun nan nawa in q'ididdige kud'in ma zanyi sam bazasu gaza naira d'ari biyu da saba'en ba, to ki gayamun d'ari biyu da saba'en zata saimun maganin ne har haka kala shida fa heenduh na?
kan heenduh ta ce wani abun sai sukaji muryan baba yawale na furta cewa
"assha ya ilahi isma'il rauni kaji haka dayawa ne a q'afa?, juyowa baba isma'il yayi cikin q'ara sakin fuskarsa yace "wlh kuwa baba abinma yazo cikin sauq'i kuma, na fad'a rami mai kwata ne batareda na nasan dashi ba a wajen" baba yawale yace "ayya Allah kyauta gaba to" "amunn baba, daman munje dreesing ne nida heenduh ta raka ni to shine nace bari na daure na shigo na gaisheka daman naga ban shigo gaishen ka ba yau sammakon zuwa kasuwa saro kayan

miyar da nayi" baba yawale yace "ai daka ma zaman ka isma'il dan ciwo ai ya kauda komi ko" murmushi baba isma'il kawai yai baice komi ba,
baba yawale yakai dubansa ga heenduh dake 6oyewa bayan babanta dan tasan tsiyar data zo ta shuka ma baba yawale din d'azun bawai mntawa yayi ba, dan hk ya d'aga carbinsa kamar gaske zai shauda mata aiko ta fasa q'ara ta ida shigewa jikin baba isma'il tana fadin "wayyo mairan qarfe kayi haquri,(sunan da take kiran baba yawale dashi knn)
baba isma'il najin hakan yasan da abinda tai masa kuwa sababbar, dan haka saiya fara dariya yana qoqarin rabata da jikinsa ya nufi miqawa baba yawale d'in ita amman taqi yarda da hkn, jiyayi baba yawale yace "kaji ja'ira 'yar albarkar yarinyar nan isma'il d'azun waini zata firgita batasan indai wannan tsoron ne ni maraba nike dashi ba konaje na tadda abokina ba dahar gobe rashinsa baibar bimin jiki naba (baffa marigayi),
miq'o mun ita na tsautsaula mata carbin nan inda ta maisheni kakanta na rugar su, wai fa in gaya ma isma'il yarinyar nan kawai tazo lafemun a cikin quryan daki ta sake maq'e waccen qaramin muryar tata wai itace mutuwa idan na shirya yanzun zata d'aukeni sauri take dan akwai sauran wujajen da zata je amman nine na farkon ziyara shiyasa tafara yowa nan wai na jima ban tafi ba yanzun lokaci na yayi... haba baba isma'il dariyar abun kawai yake da gudu heenduh ta hantsala ta miqe tsaye ta nufi q'ofa tana haki ta tsaya ta juyo ta dubi baba yawale tace cikin qyalqyatawan dariya wacce har fararen haqoranta suka fito reras dasu gwanin burgewa "cab kujimin tsohon nan nizai daka da wannan dogon carbin yasamun ya fasan jiki ya cuci masoyina ta66 walle kam Yaseen bazan tsaya ba wlh kuwa,, mairan qarfe naso ka tsorata ka gudu insha dariya a d'azun din nan ay"
girgiza kai baba yawale kawai yayi yace"hmm kedai kika sani ay da shirmenki zan kuma riqeki da hannuna in saki mari sai maaoyin naki yazo belinki kinga daman sai ingansa inda daman rowarsa ake mana,dariya heenduh tai tace "ko aiko indai masoyina na haqiqa zaka gani kenan kana da sauran kallo a gaba dan ni kaina ban sansa ba bare na sanarwa wani dashi shi"
yatsina fuska baba yawale yai yace "zancen 6ur knn, ashe abunma dud wobuwa ce da hayaniya, inda dai bakida saurayin kizo na taimaka miki mu qulla auran nan namun nan" turo baki tayi tareda juya fuska gefe bayan ta kaso kallabinta har goshi sannan taxe "ta6 Saidai na had'a ka da goggo dahara(wata tsohuwa ce nan maqotan su heenduh dun take mai saida zogale da kuli kuli da man gyad'a kuma, batada miji danta daya kuma ya rasu ita kadai ce zaune a gidan sau tari sa'a da heenduh can suke zamansu na fira dan sun saba da ita sosai.
qyaleta baba yawale yai yadanyi murmushi tareda duban isma'il din yace "yarona isma'il tashi jeka gida haka ka huta rabu da shirmen heenduh, Ubangiji Allah ya sawwaqa kaji" "aminn baba" cewar baba isma'il yana mai miqewa tsaye a hankali da qafar tasa, saida ya fita sannan heenduh ta juyo ta kalli baba yawale ta kashe masa ido guda d'aya na tsokana tace "byeee mai ran qarfe sai gani na uku ko wajen kawo sabuwar ziyara dan nasan ka tsorata kadai mazge ne ka b'oye walle kuwa" yunq'urowa baba yawale taga yayi kamar zai nufota da doguwar carbin nan nasa aiko ta d'age siket dinta na atamfar nan sai kusada babanta dayake gabda shiga gida ta dura, dariya kawai take tuntsurawa dan matuqa takejin farinciki dud intana wajen baba yawale, wataran suyi firar arziq'i abinsu hankali kwance, intaja ruwa kuma nan take firar tasu zatai kwab'a ya korota gida.
suna shiga gida suka iske mama zainab zaune nan inda suka barta tana q'oqarin tashi zaune ne da sauri heenduh ta q'arasa ta riq'eta tace "sannu mama jikin yayi sauq'i dai ko? "yaya jikin

naka mlm?"! tambayar da mama taiwa baba isma'il knn dan sam ita tafi damuwa da nasa ciwon akan nata.
"da sauqi zainabu dan wajenma da akai dreesing ya rage ciwon ba kamar d'azun ba da jinin ke zubowa" cewar baba isma'il din.
sosai mama zainab taji dad'i dan ya q'ara kwantar musu da hankalin da kansa ya tashi yaje ya d'auko musu zazafen tuwonsu na jiya wanda heenduh ta d'umama masa d'azun.
saida ya matsa sannan suka sa hannu sukaci dan mama Zainab baifi datai ci biyar ba taji cikinta na zafi dole ya haqura ya barta tad'an kwanta nan babu jimawa barci ya kwasheta sakamakon magungunan ta data sha wanda khaleepa ya bata.
bayan baba isma'il ya wanko hannunsa ya dawo ya zauna nan kan tabarmar ya dubi heenduh dake gyarawa mama Zainab lullu6in zanen data yane jikinta dashi yace"heendatu yau bakije school bane banga kinje ba?" saida ta d'an lawangwa6e kai sannan tace "eh baba bamuda lecture ne yau sai gobe sanna" sauke ajiyar zuciya baba isma'il yayi yace "to shiknn Allah shi kaimu lpia"
"amunn baba, kaima ya kamata ai kaje ka huta kan akira la'asar, tayi maganar tana duban qafar tasa. miqewa tsaye yayi yace
"hakane heenduh na bari na shiga d'aki to na d'an runtsa dan na gaji sosai"
"to babana afuta lpia saika fito"
daga haka ya wuce ita kuma taje ta kai kayan gwarin baba ma'ajiyarsu daga saman hnya data d'auke su, tana gamawa ta dawo ta d'an kwanta nan q'asan wajen tabarmar da mamar ta ke akai tana danna 'yar q'aramar gwaramar wayar nan tata tna tunanin miya hana sa'a kuma zuwa ne har yanzun?".
Khaleepa kuwa suna barin gidan saida ya jima nan zaune q'ofar gidan su shida su yunus sannan ya kwashi laptop d'insa da jikkarsa ya wuce cikin gida.
main falour nasu ya wuce kai tsaye saman dakinsa ya haura ya zube saman mahehen gadonsa laptop d'in na saman q'irjinsa idanunsa lumshe sai dan ya matuqar gajiya yau da aiki dudda ya kama ranar weekend ne kuwa amman saida ya fita aiki tun safe. wanka kawai yake son yayi koya samu jikin nasa ya warware masa gajiyar daya kwasa, bazato bare tsammani sai jiyai kawai ana shafa masa gefen kwantaccen sajen fuskarsa zuwa sumar kansa wacce ke kwance lub lub a saman kansa baq'a q'irin da ita kuwa wanda kaida gainta kasan ba qaramin kashe mata kud'i guy d'in
yake yiba wajen gyaranta, jin abun yaqi qarewa yasa da sauri ya bud'e idanunsu amma still yanadaga kwancen sa bai miq'e ba, caraff suka had'a ido da zarah 'yar hjy Hadeeza aminiyar firdauseey.
sosai ya tamq'e fuskarsa bayan ya miq'e tsaye ya zuba mata idanunsa fess bumisa fuskarta a kausashe,
tuni jikinta ya fara shaking dan ganin mummunan kallon da yake binta dashi, wai ita yaya zatayi da son khaleepa ne a rayuwar ta? tana tsoron fa kada hakan ya illata mata zuciya da yawan tunanin da zuciyarta takeyi na kaikawo a kansa, har jitake a iriyar sonda take masa babu abinda zai nema a gareta ta kasa mallaka masa shi koda kuwa gangar jikinta ne ya nema ta tabbatas to zata sallama masa ita dan wanna ba wai baq'on abu bane a gareta lura da yanda suke qazamtacciyar soyayyarsu da samarinsu na school kises in every were are her body and hugs wanna ba wani baq'on abu bane a gareta ba muddin zai nema a shirye take data sallama

masa knta indai zaiyi farinciki harya kulata dai dai na munti daya cikin sakin fuska ba wannan fuskar shanun da yake ba kullum,
shiyasa ake tunanin jawo hankalin khaleepa ta wanna hanyar amman sam ko fuskar haka ta gagara samu a wajensa bare ta cimma burinta dan a haqiqanin gskia tana masifar son jin yanda zumarsa take danda gani zakin mazaje ne a iriyar kalar k'irarsa zai 6atawa mace tunaninta ta yai mata formating nasa gaba daya indai ta wannan fannin ne komin jarumrarta kuwa, shiyasa kawai ta shagala da kallon qirarsa dudda tsoron da takeji na kallon banza da take samu daga garesa ga kuma tsabar qwarjininsa dake kada hanjin kowace mace kuwa data yarda har ya saka mata kalar idanunsa cikin nata idanun.
anasa 6angaren kuwa dubnta yake sam ya tsani mace marar kamun kai a rayuwar sa, bare ita daya sha ganinta da 'yan iskn samarinta suna yanda sukeso kuma dud halinda ta ke ciki yasan tabbas mamanta tana sane ammam sabida tsabar son da take nuna mata ya hanata katsa mata, kuma shi koda habitat nata masu kyau ne sam batta daga cikin kalar suffar halittar macen da yakeso matarsa ta kasance dasu na jiki, ko daya batada shi amman sbd tsabar ta rainasa har take iya shigo dakinsa ta dunga ya mutsa sa ma knn, amman taci sa'a ta kuma godewa Allah dabata mallaki surar dirin kalar matar da yakeda buqata bane da saita raina kanta yau yau dinnan a hannunsa tabbas, dan a yanda yasan kansa baida excuse ga dud macen data shiga hannunsa, shiyasa bai cika son shiga harkar matan ba dan kiyaye kansa daga abunda ke sake girmama a jikinsa tabbas tabbas tabbas shi yasan yanada sha'awa bata wasa ba, hakan yasa yake dauke kai ga dud wata mace gudun kada ta rusa masa budget dinsa dan ya d'aukarwa kansa alqawali zai zama virginity shima kamar yanda zai karbi na matarsa shima zata kar6i nasa a ranan zata fara sanin sa itama, hmmm kunji fa, shiyasa ya qudurta worning zai bige wa zarah kan zuwan masa d'aki dan ko muddin ta ci gaba da taba masa jiki da wannan qazamin hannun nata wlh sai jikinta ya gaya mata, dan haka nn take ya q'ara fiddo idanunsa waje gaba daya tareda daka mata wata tsawa sai kuwa gata bakin qofar futa daga dakin yace "ubanmi ya kawoki d'aki na? yayi maganar yana mai zazzaro mata idanunsa waje, jikinta na buga rawa ta fara magana murya na sarkewa "ww.. wlh yaya khaleepa momynka ne tace nazo naga in kana ciki,,
"ok dan ina ciki shine akace in kinzo ki dinga shafa ni ke qaramar 'yar iska ko? yana maganar ne yana q'oqarin kwanto belt d'in jeans d'insa aida sauri ta sauka q'asa batareda ta q'ara cewa uffan ba.
wani dogon tsoki yaja tareda wurgar da belt d'in tsakar d'akin ya koma ya zauna bakin gadon nasa ya sa yatsun sa cikin sumar kansa ya dunga yamutsata sosai idanunsa a lumshe sam ya tsani yawan magana yanzun kwaratsin da ta sanyasa ji yake gefen kana na buga masa d'al d'al d'al ciki ciki, shifa harda haka ne yasa sam ya tsani harkar mata shiyasa babu shiri ya miq'e zuwa ma'ajiyar magun gunan sa ya d'auko na ciwon kai babba guda daya ya tura a baki tareda daura kofin ruwa akai ya hadiye maganin ya ajiye cup din cikin deep freezer dinsa sake kwance wajen, cire kayansa yai ya daura towel a iya qugunsa nan take faffad'an qirjinsa ya bayyana mai cike da mayalwacin kwantaccen gashi sai sheq'i yake, toilet ya wuce kai tsaye bai jimaba ya fito ya shirya kansa cikin wasu qananun kayan, baqin jeans ne sai Blue din riga mai qaramin hannu rigar tabi jikinsa ta kwanta ta yanda dud wasu zubin damatsam halittar karfi ta cikakken namiji gogaggen d'an boko kuma suka bayyana a kansa,
Black cambus dinsa yasa kalar na 'yan q'wallo amman su wanna new designer ne, bayan ya

gama d'aure mad'auran takalman nasa ya d'auko wata farar rigarsu ta likitoci ya d'ora saman sheet din jikinsa ajiye medical glass dinsa yayi gaban aljihun rigar sannan ta fito daga dakin sa zuwa babban falon gidan nasu dake q'asa sai baza qamshin sa yake, taku yake cikin takunsa daya saba.
cin karo yayo da momynsa tana qoqarin shiga kicen dan ita bama ta gansa ba, dan haka a hankali ya sad'ad'a ya lallab'a tareda kai bakinsa ta bayanta daidai saitin kunnenta yace "momyyy na!!!" da sauri ta juyo tana murmushi tace "mai tsada na ka b'oye ina ka shige yaune? tayi maganar tana kallon had'adden saurayin matashin d'an nata kwalli d'aya wanda dud sonta na rayuwa yana garesa duka, shiyasa gata na gidan duniya babu wnda khaleepa bai samu daga iyayensa cikin ma samin wasu yake, kan ya bata amsa sukajiyo muryar dadynsa mukhtar daga gefensu yana fadin
"Masoyana fira kuke ne batareda an gayyace niba?" dariya sosai hjy firdauseey tayi shiko uban garin rungume dadyn nasa yai yana cewa "barka da fitowa dady, zama sukai kan kujerun falon hjy firdauseey tace "kagansa nan kyakkyawan saurayin d'an nan naka alhajina tun safe daya bar gida saifa yanzun na gansa alhalin yasan bana jure rashin ganinsa na sa'oe muddin ba yana office ba dan haka na kawo maka qararsa ya fad'a maka inda yaje dan nasan yau weekend ne babu hospital bare nace can yaje" Alhj mukhtar wani murmushi yasa ki sosai tareda dubn khaleepa dake wani langwave kai kamar maiji barci nanko tsoron klr doguwar tambayar da dadyn nasa zai fara masa ne gameda hkn gashi shi kuma ba gwanin doguwar magana ba bare ya basu amsa cikakka fatansa dai shine AllAh sa dadyn nasa ya taq'aita tambayer tasa domun yaji dadin basu qwararriyar amsa guda d'aya, shi kansa Alhj mukhtar yasan halin d'an nasa da kwaikwai wajen magana dan haka sai ya had'a masa tambayarsa waje d'aya a dunqule a sauqaqe tareda cewar " to my done boy kaji mmnka ta kawo qararka kan ka je ka dad'e a waje ina kaje amsar da take buqata knn? yaqarashe maganar cikin raha. sam bai iya qarya ba baisanma ta yanda ake yinta ba dan haka kai tsaye yace "dady momy nifa yau naje hospital bayan na tashi da safe, shine naje na yiwa wata mata ne 'yar qaramar Theatre dan ranar nai alqawalin zan mata so kuma dady bacin na dawo ne na je gidan small father (isma'il) na iske maman bata lpia shine fa na dubata tareda zuwa samo mata medicines dana futo ne kuma ina nn zaune waje nida freands nawa shinefa na shigo yanzu nai wanka zan koma hospital din na duba matar naga kota farko" gaba d'aya saida zuqatan su suka soya fuskarsu ta nuna hakan sakamakon ambatan zuwansa gidan isma'il kai tsaye da yayi dudda abinda ya faru jia kuwa dud a knsa,
to amman da yake firdauseey 'yar duniyar gske ce sai tayi gaggawar q'aqaro murmushi a fuskarta danta kula dud sanda ta 6ata masa rai akan maganar gidan matsiyatan can wuni yake yi mata fushi ita kuma fushunsa quna ne mai ciwo a gareta cikin zuciyar ta. harda mukhtar ya zuciya zai balbale khaleepa nan take a wajen da fad'a da sauri firdauseey ta girgiza masa kai alamun a'a kul kada ya soma.

By
Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️

👁️👁️

DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁🥤👁
P23
Sauya fuskarsa mukhtar din yayi kawai yayi kwana da maganar da fadin "ok done boy jeka take care AllAh ya tsare mana kai" saida khaleepa ya d'an duq'o sumb'aci iyayen nasa a gefen fusakokinsu sannan ya fice da sauri yana fadin "ameen dady na da momy"
bayan fitarsa ne mukhtar ya dubi firddausy yace
"miyasa kika hanani aiwatar da manufata?
murmushi tayi sannan ta d'an kurb'i ruwan lemon hannunta sannan ta dubesa tace" hmmn, lokaci yayi da zamu canza taku akan abubuwan da mukewa su Ismail a gaban khaleepa kasan miyasa?
girgiza mata kansa yayi, saida ta taso ta zauna jikinsa sosai tana shafa tafin hannunsa sannan tace"na lura adud sa'ilin da muka ciwa matsiyatan mutanen can mutunci tofa mai tsada na yakan d'auki tsawon lokaci kan mu fara gane kansa a gidan nan, jiya fa abunda kaje kai ma isma'il a gida nasan saboda shine yasa hkn ransa ya baci harya fita da safe batare da ya nemomu ba abinda bai tab'a yi mana knn ba, to kaga knn in dai har muka ci gaba da yin hakan gaba yaya knn? munaji fa muna gani d'anmu zai gujemu a kansu, shiyasa yanzun abunda nikega yafi kawai shine mu daina masu abinda muke musu na rashin mutunci akan idonsa, koba haka ba? dan gskia ni bazan juri ganin bacin ran d'ana ba akan wasu mutane qasqastun bayi ba marassa madogara wanda hatta abunda zasu ciyarda kansu gobe tofa saisun nemesa a ranar sanna suci, hmmm wlh naji baqincikin baq'in abuncin daya ciwo gdn nn jia wlh bakaga iriyar kalar haraswar da ya dinga yiba uwa zai amayo yayan ciKnsa waje fa,abinci ne suka dura masa wanda bai saba cinsa ba dan mugunta fa? hm amman harya iya hanawa aje ai musu magana kmr ynda yace, wai ba laifinsu bane shine ya nace sai yaci sannan suka bar masa yacin, hmm! kai jama'a abun nn na d'aure mun kai fa alhajina wlh tsoro nike kada su janye mun yaro na dud sanda yasan cewa akwai auransa akan wannan shegiyar aljanar yar tasu mai tsinannen kyaun tsiya uwa Aljana, kaini abun nan na damuna wlh gashi sam bata da tsoro yarinyar alhajina karfa ce wlh kada kaso kaga ynda nike daga akan ta daina shigowa mun gidan nan amman na kasa hana shegiyar 'yar nan ta fiye naci.
sauke ajiyar zuciya mukhtar yayi yace "naji komi kibar batun wai zai gane cewa matars ce dan

wannan wani kuma shudaddiyar tsohuwar magana ce data gabata shekara da shekaru dan haka kima daina sa damuwar hkn a ranki, kuma gameda zuwana gdn jiya dandai kece ma kikasa naje a bayan hkn da ni rabon dama nasa dan iskan matsiyacin a idanuna nama kwan 2 kinsan ni yanzun batashi nikeba ayyukn gabana muhummai nafi sawa gaba na dan wlh ni har ma mntawa nike dashi a rayuwa bare nasa damuwar hkn a raina, sannan kuma gameda shigowar 'yarsa gidan nn ki qyaleta ta gaji ta daina wataran , dan komin abunta dai bazata dawwama a gidan ba in tazo dole ta koma gidan matsiyacin ubanta ta kwana kuma zataita ganin abubuwa da mahaifinta bai mallakesu ba a gidan konan taji haushi ai mun qaru da hakan, dan baqinciki nasu mu shine farinciki a garemu, to dnnhaka ki janye komi na nuna wata damuwa a ranki ki fita harkasu madam d'ina kamar ynda na fita kada tunanin hkn ma ta jaza miki ciwo please forget them kinji ko, murmushin jin dadi firdauseey tayi tace "yass alhajina an gama hakan kuma za'ayi shawarar ka abun dauka ce" sun jima sannan ya tashi ya wuce toilet dan yayi wnka ita kuma ta wuce kicen dan cigaba da bawa masu aikin order kan ayyukan da suke gudanarwa da kuma dinner din da suke shiryawa.
khaleepa kuwa yana isa hospital d'insu yayi parking a moto park nasu na ma'aikatan nan ya fara tafiya harya shiga cikin asibitin nan yaita gamuwa da nurse sunata kawo gaisuwa da fad'in "barka da yammaci sir" da "yawwa" kawai yake amsawa yana cibgaba da tafiyarsa batareda yako kalli inda suke ba, dayake yawancin sisters d'in da nurse nurses d'in asbitin dud 'yan mata ne wayayyu aka zuba 'yan bokon gasken gaske ma kuwa, shiyasa kowacensu kesaon ganin tasamu shiga a wajen wannan had'adden handsome likitan matashi mai jini a jika ta ko'ina baida matsalar rayuwa a cewarsu, saidai kuma dai dukknsu tsabar kwarjin da yake musu ne yasa suke kasa shishige masa kamar sauran mazan doctors d'in, dan ko gani yayi doctor sun kirasu ana conversation to indai yana wajen barin wajen yake fuskarsa a kame, jiyake qwamma yaje office d'insa ya kunna kallo a laptop nasa yayi daya zauna wajen yakeji, babu wnda baisan hln muskilan cin doctor khaleepa ba kaf hospital din nasu kuwa,shiyasa yana shiga d'akin Theatre ya iske matar ta farko Alhamdulilla aiki yayi kyau, nan ya rubuta mata wasu magunguna a wani d'an kati wanda za'a siya mata ta dunga sha,
bai jima ba a cikin asibitin ya fito ya shige motarsa dan q'agare yake ya koma gida yaje yaga ya jikin mama zainab dan tun d'azun daya baro gidan still tana ransa shiyasa yana shiga anguwar tasu motarsa kawai ya shigar harabar gidansu ya sake fitowa ya nufi gidan. harya wuce wani waje da ake suya su naman kaji sai kuma yayi tunanin bari ya siya ya tafarwa mama Zainab dashi koda Zataji dadin bakinta taci, nan ya tsaya ya sa aka sa masa guda 3 cikin leda mai layi layi sannan ya wuce gidan kai tsaye ya shiga da sallamar sa, yaji shiru babu amsa, zama yayi nan bisa tabarmar bai jima ba saiga mama Zainab ta fito daga cikin d'akin jikinta sanye da hijab alamun sallar la'asar ta gama, cikin fara'a ta zauna tana fad'in "yi haquri khaleepa kana sallama kaji shiru gashi kuma ina salla ne nazata ma ai heenduh na nan inda nan na barta zaune tana latse latsen wayarta sanda na farka, kaga ashe to tama fice babu mamaki wajen sa'a ta tafi kai wannan yarinyar Allah shirya dai" wani d'an guntun murmushi ya d'an saki wanda iyakar leb'ensa na q'asa ya tsaya sannan yace "yaya jikin mama? "jiki kam dai Alhamdulillah khaleepa dan ina tashi daga barcin
nan bayan shan magungunan nan bakaji yanda naji sauqin lamurran ba sosai cikin yardar Allah, kuma gashi na samu qarfin jiki na yanda ya kamata, Allah shi albarka dai ngd fa"
a ransa ya amsa da aminn amman a fili ledar ya ajiye mata yace "mama gashi ko zaku buqaci

wannsn keda small dad shine na kawo muku, nan mama Zainab tace
"kai ayya khaleepa d'awainiyar nn kada tai ma yawa haka damu dan Allah ka rage wasu abubuwa kaji?"
cikin muryarsan nan din kuma yake cewa "to mama jinike in bnmaku ba wanike da a dud anguwar nan daya fiku?, ku daina cewa komi dan Allah mama" shiru mama Zainab tai tana tuna tsananin kirki iriyar na khaleepa sam bai d'auko halin mamansa da bbnsa ba ta wannan fannin tunani take ita rabonsu ma da cin wani abu mai dad'in azo agani a gidan harta mnta watan ma na shekar bare ranan, zuwa can
dai tace "to shiknn khaleepa mun karba mun kuma gode qwarai da gsk... sallamar baba isma'il ne ta katsewa mama zainba mgn, nn suka amsa masa sannan baba isma'il ya zauna nan kan tabarmar dayake iriyar ta gidan biki din nn ce tabarmar tanada girma amman dutta fara farfashewa sbd jimawar datai.
cikin girmamawa khaleepa ya gaishesa cikin murmushi baba isma'il yace "yawwa dai bokan turawa ykk kaima?' "Alhambdulilla small dad"
yayi maganar yana kallon nad'in bandage dake q'afar ta baba isma'il d'in.
bai q'asa a gwiba cikin tsabar tausayawa ya sake cewa "small dad sannu ciwo kaji ne, miyasa baka kira ba nazo munje hospital namu ba?"
ganin yanda ya damu yasa baba isma'il din yin murmushi yace
"a'a kwantar da hnkalinka likita namu bawai wani west ciwon yaiba kuma bagashi anmun dreesing ba, kada ma kadamu kaji ko?"
"to small dad AllAh baku lpia dukanku" amunn suka amsa, khaleepa ya sunkuyar dakai qasa yace "kuma dan Allah small dad kuyi haquri akan abinda dady na yai muku jia dan Allah, nasan nina jawo muku bacin ran,
da sauri baba Ismail yace "kaji ka, nifa harma na manta da hkn dan haka kada ma ka damu knka kaji?" mama Zainab tace "komi ya wuce khaleepa Allah dai ya sasanta tsakanin iyayen naku aminn"
Nan wajen yai tsit na yan mintoci kan baba isma'il ya tashi ya je d'aki nan yabar mama zainab tanawa khaleepa q'arin godiya akn d'awainiyar su. shidai bai sake cewa komi ba,
suna haka saiga heenduh ta shigo hannunta riqeda handouts guda 2 tana ganinsa kuwa bayan had'a idanu da sukai akaron farko tareda sakarwa junansu kallon banza wani d'an siririn tsoki suka ja a tare, sai dai dud abin nan kuma ashe da sukaiwa juna mama Zainab na kallonsu, ita kam tarasa miya jaza wannan qin da sukewa juna?sam bassa shiri bare a jitu.
itads mlm sunsha tsawatar musu akan hkn amman kmr ba gaya musu ake ba girgiza kai kawai tayi dan gskia har cikin ranta bataso taga rashin jutuwarsu yayi tsawo kamar na iyayensu fatanta a koda yaushe Allah ya had'a musu kan 'ya'yan nasu kar abun yayi yawa kuma gana iyaye ganasu ai sai abin yayi yawa kuma.
kai tsaye heenduh tayi hanyar d'aki dan ganin sa datai wajen yasa taq'i yowa nan kuma.
mama ta bita da kallon takaici tace "ke zonan heenduh" tana tuquburi da turo baki ta dawo can nesa da tabarmar ta zauna tace mama gani,
"daga ina kike da izininwa kika fita? kinsan dai bannason wannan yawon marar dalili ko?"
mama naje fa wajen sa'a nefa aro handouts zan duba sbd ance munads test gobe a school shiyasa na aro sabida zanyi karatu an jima kan na kwanta amman kuma kiyi haquri mama"
mama tace "babu laifi to ni daman yawon ne banso, kuma bakiga d'an uwanki bane zaki wuce

d'aki bazaki gaisheda Shiba?, wai heenduh yaushe zakuyi hankali ne keda khaleepa har kuso junanku a matsayinku na makusantan 'yan uwa na jini emm? cikin sake turo baki heenduh tace "tofa mama shine ai bai wa mutane mgn ni sai nai masa?
"ni yimun shuru sakaryar banza baya girmeki ba? na gaya miki bansan wannan shashancin zaki gaishesa koko saina buge wannan bakin naki na tsiwa wa mutane?
Sake duban sa tayi a karo na biyu suka sake hade ido wanda tsananin hasken fararan idanunta daya gani sosai yayinda baqin cikinsu shima yake baqi sosai yasashi wani saurin d'auke fuskarsa daga tata yanna wani tabe lips kamar yaga abun qyama amman miyasa gabansa ya fadi ba a haduwar idanunsu a wannan karon. hakan da heenduh ta gani ne yasata q'ara quluwa akan abunda yai matan kamar yaga kashi dai? Quta tai a ranta tace wlh baccin mama kai kayi kad'an dana tanka maka d'an rainin hankalin mutum kawai, kamar bata so ta bude baki daq'yar tace "sannu"!!!!
bata jira komi zaice bata kwasa taqara gaba zuwa cikin d'aki daman tasan ba amsawar zaiba koda ta gaishesa saiko gashi ile bai amsan ba saima taji ya miqe tsaye bayan shigarta d'aki yanaiwa mama sai anjima, tanajin fitarsa ta miqe tana fad'in "dubesa kawai d'an mannin sense, ni ai gidan ka iske indai kan halinka ne toka samu dai dai kai dan wallahi ko can wahala tana ga matan da suka mato maka suka damu dakai wlh badai niba heenduh dankuwa nafi qarfin tunanin ka fiye da, q'ima.
jin kiran da maman ta ke mata yasa ta matsawa daga gaban tagan dakinsu wacce ke nuna mata waje bayan gama leqen ficewar khaleepa da tagamayi.
"gani mama" abunda tace knn bayan ta iso wajen, hararta mama tai tace "je leqa dakin babanki kiga in barci yake"
"to"
tna zuwa ta iskesa yana kishingid'e da carbinsa yana ja tace "laaaa baba ashe ba barci kk ba?, tashi zaune yayi yace "a'a heenduh na ba dai barci ba ai babu kyau ma barcin bayan la'asar dan yana haddasa b'acin rai da dai sauransu"
kan ma heendu tace wani abu saiga mama Zainab ta shigo d'akin baban hnnunta daukeda ledar kazar da khaleepa ya kawo musu.

By
Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️🧻👁️
🅿️2️⃣1️⃣
Z ama tayi tareda ajiye ledar Lazar gaban baba isma'il din tace "mlm gashi d'anka ne ya kawo mana" tayi maganar tana mai bud'e masa ledar a gbnsa.
tuni wajen ya gume da q'amshin kajin wnda hakan yasa heenduh had'iye muyau babu shiri dudda taji haushin ambatar cewa khaleepa ne ya kawo ta, to ance musu suna yunwar nama ne dazai kwaso musu shi suga mayu ko kamar yanda uwarsa ke fad'a mata in taje gidan a lokutta da dama ma.
baba isma'il yace"khaleepa dai?
mama Zainab tace "eh mlm da harna gardama wajen karb'a gudun
kada a koma 'yar gidan jiya shiyasa kawai na karba dan wlh bakaga ynda ya koma kalar tausayi ba, kuma gashi munce komi ya wuce gameda abinda babansa yai mana kaga knn idan mukaqi kar6a zaiyi tunanin mun qullaci abun kenan har yanzu a ranmu"
heenduh tai zubut tace"to mama inyai tunanin hakan na cewa an qullaci abun ai mun huta saima ya daina shigo mana gida d'an qa'idar😉"
hararta mama tayi tace"sannu marar kunya kinji? koko an tsomo dake cikin zancen ne em? sannan da kike cewa yabar shigo muku gida ke ba kina d'aukar q'afa kije gidan nasu ba? shashan yarinya kawai duk kunbi kun qyamaci junanku keda khaleepa, hm basai kuje kuyi ta yiba lokacin da zaku had'e kanunku bamuda labari saidai muga alamun hakan tartare daku inda lokacin da muke cewa kuso junanku a matsayin 'yan uwan juna kun q'iya sai kuje kuyi tayi ai, na ma gama tanka muku kan batun in kun gaji kwa 6aras ay"
tuni heenduh ta cino baki tana fad'in a ranta"cabb nikam mam Allah sawaqa na shirya da wannan muskilallen mutumin dan ba halinmu d'aya bama sam sam bazamu ta6a jituwa dashi ba Inaga"
kuma danma yaga kwana 2 na daina caja masa qwalwar sa shiyasa yake
mun kallon uku saura kwata mako?
Hmn Allah kaimu gobe kuwa zaka gani"
abinda heenduh ke fad'a kenan a ranta.
miqewa tai zata bar dakin mama tace "nace ki dawo ki zauna ki kar6i naki ko?
"ni fa mama na q'oshi kuci kawai"
sai lokacin baba isma'il yace "aa heenduh na abun kusa da baki ne tsaya ki amsa dan Allah inda Allah ya kawo mana saban tuwa"
tsaye tai batace komi ba, kuma harga Allah ita tanason cin naman sai sai wanda ya kawo san ne yasa taji kanta kazar ma haushin cinta take.
mama tace "inda tace battaci barta mana malam bakasan hali na yarinyar nan bane ni nasan abunda yasa tace bazata cinba bakomi bane kuwa yasah hakan face jidatai maqiyinta ne ya kawo mana ita".

murmushi baba isma'il yai baice komi ba yasa hannu ya d'auko wata baqar leda cikin kayan sa na cefane sannan ya duq'o ya d'auko kazar nan guda d'aya ya saka ta cikin leda ya miqawa heenduh yana fad'in cewa "amshi kije kici heenduh na q'yale mamanki 'yata"
haka heenduh ta kar6a ta fice tana jin sanda mama ke mitar cewa yacika goyon bayan 'yar tasa, shikuma murmushi yasakeyi yace "dole naso abata dan ita d'ai ce dani babu q'ari, tanaji sanda maman take magana murya a taushe take cewa baban 'oh ni kenan an ware ni yanzun an daina myn soyayyar nan ko?!, caraf taji babanta yace "zainabu ta aike ta daban ce tafo nan ma kiji wata mgn dan sonike aiwa heenduh q'anwa haka nan itama"
aida sauri ko heenduh ta ida gangarewa zuwa dakinta a kunya ce, ita kam soyayyar iyayenta na burgeta, tana matuqar son miji wanda yayi masifar sanin kansa wajen love, jawo filo tai ta rungume sa q'am a jikinta tareda lumshe ido ita da zatai karatu saigata ta 6uge da rungume filo, wata zuciyar taji tace da'ace zaki samu saurayin da zai zama mijinki kamar dai khaleepa da kin dace dan tsarinsa ya nuna cewa zai iya fiye da yanda kike ma tunanin samun mijin.
zumbur tai tareda wurgar da filon ta miqe zaune tana yamutsa fuska a fili take fad'a da zuciyar tata da cewa "tur!! tuf tuf!
da wannan kalar mummunan tunanin naki dud ki rasa wanda zaki kawomin tunanunsa ma a daidai lokacin da nike tsaka da jin dad'i sai wannan mai mummunan halin? gskia my heart banji dadi ba"
miqa hannunta tai ta janyo handouts dinnan ta yakice tunanin komi ma a ranta ta fara karatun ta, sai gab da magrib sannan ta ajiyesu ta miqe tsaye tana yin miq'a dan ta gaji sosai daga nan kuma ta fita tsakar gida saiga sa'a sunci karo da ita, rungume juna sukai suns murnar sake ganin juna.
anan sa'a ta shiga d'akin mama tai mata ya jiki sakamakon heendu dataje gidan nasu dazun take fad'a mata maman bata lpia, anan sa'a tace mamanta ma na mata ya jiki zata shigo dubiya kuma insha Allah.
mama Zainab tace"bakomi sa'adatu ngd ai"
nan suka tattara suka koma d'akin heendu ko zama basuyi ba aka kira sallar magrib sa'a tace "kai limamin nn qawata da azarbabi yake ina lura dashi fa da zarar lokacin sallah yayi wlh ko second d'aya bazai mana gyaransa ba zakiji ya wani d'ale mumbari yana kira"
qyalqyacewa da dariya heendu tai tace "ke sa'a kiji tsoron Allah fa, yanzun sa'idon naki har yakai gasu baba yawale liman? hmm to nidai wlh daga nan kada ki qara ta6omin baba yawale na.
zama sa'a tayi tace "hmm AllAh jiqan mlm tsalha shiyasa nike yinsa kan ya rasu zakiji har sai masallacin cikin anguwar nan wasu daga ciki sun kira salla sannan zakiji sa shima, anman tunda ya rasun nan aka nad'a wannan kakan naki yadaina mana gyara wlh haba babu wanda yaqi bati fa qawata"
heenduh tace "hmn anman da cikin azumi ne kinfi kowa qagarar ya fara kira"
dariya sa'a ta saki tace "ah aikuma cikin azumi masifar son baba yawale nike yanda kikasan nai miki qwacen sa na aure maki shi fa kodan kiran sallar da yake mana da wuri"
wata dariyar suka sake yi heenduh tai kwanciyar ta tace "mudai Allah ya d'auke mana dan ko ni hutun salla nike wanda na farasa daga yau.
wani qarar ihun sa'a ta saki wanda yayi dai dai da wucewar mama Zainab ta gefen dakin ns heenduh, alwala tayo, dan haka dakin ta shiga ta dubesu tace" ku kuma ihun miye kuke haka

da dararraku saikace baqin mahaukata? maza ku fito kuyi salla kada lokacin ta ya qure muku"
heenduh tai saurin cewa "sai dai sa'a taje tayi tata sallar mama danni bannayi hutu nike"
wata hararar mama ta sakar mata tace"to rasa kunya nace ki kawomin laluri ne?
shiru heendu tai tareda kanne dariyar ta ganin yanda sa'a tayi wiqi wiqi tana sosa jiki alamun sanyin ke ratsata gashi tana shirin ta6a ruwa.
dole sa'a tabi mama zuwa waje nanta dauro alwala ta shigo d'aki tana kyarma saboda sanyin daya qara saukowa a lokacin.
dariya heendu ta saki tace"shiyasa
nike son harkar hutu wlh qawata hmmn musamman ma lokacin sanyin nan fa, kinga knn tab'a ruwa sai naso znyi" sa'a tace "hmmn kedai qawata bari, bari dai na gama sallar tukun"
bata jima ba ko ta sallame nan ta koma ta iske heendu gefen katifarta dake shimfid'e a q'asa tana cigaba da qara duba littafin handouts dinnan.
zama sa'a tai tace "nifa ko karatun test din nan banyi ba qawata dan narasa gane wane abu zanyi choice? kinsan malaman nan muggai ne abunda ka karanto bashi zasuyi maka test akaiba shiyasa kawai na haqura innaje ai muna a together dake banda matsala, bare yanda lectures d'in nan su mlm bala yakeda da tsinannen zafafawa kan test, wlh kuwa ya baqinsa ya baqin halinsa tsohon kawai"
heenduh tace "yanzun sa'a bazaki karatun ba da gaske?
"Yaseen kuwa bazan ba qawata"
shiru heendu tai jin wayar ta na ringing sunan musaddiq ne ya fito, lumshe ido tayi tace a fili "Wayyo ni Allah wannan karon Allah ya had'a ni da super glue fa"
leqowa sa'a tayi ganin mai kiran ne yasata cewa "yi maza yi maza qawata kiyi holding kada ta katse"
tsoki heendu tai taq'i d'agawa saida ta katse ya q'ara kira sannan ta d'aga da cewar"wai miye haka dan Allah musaddiq?! waiba d'azun mukai waya ba kuma miye naka na q'ara kirana?!
sakin baki sa'a tayi tana kallon heendu jin wulaqancin datake kartowa musaddiq din yanaji kuma, baida zuciya dai to.
to ina laifin ma wanda ya ce yana sonka?
girgiza kai kawai tayi tace "qawata har yanzun banga gwanin da zai miki gwanunta ba Indai ta fannin maza ne, amman zanso inga gwaninki gskia konan da wane lokaci ne kuwa.
abunda sa'a take cewa knn a ranta.
saida heendu ta gama wayar ne ta dubi sa'a tace"hmn wai kinsan mi yace ne qawata ? cewa yai wai gashi yazo shagon da ake siyarda manyan wayoyi ya rako abokinsa siyawa budurwarsa wai dan Allah in fad'a masa wacce nikeso saiya suyomin ni kuma nace yabari inna tashi koda yaushe ne zan fad'a masa saiya suyomin sbd yanzun banda buqata" tayi maganar tana dag'e kafada 🤷‍♀️.
wata raruma sa'a takaiwa wayar heendu itako tai saurin sanya wayar ma'ajiyarta wato cikin bra dinta ta kwanta ko luf,, sarai tasan sa'a tsab zata kira musaddiq ta basa sunan wayar, saiko gashi ile sa'a tace "wlh qawata bakiyi ba, dan iskanci arziqi na kiranki tsiya na hanaki? shike nn ai kin kwafsa da yanzun kin rabu da wannan rakani kashin banza kawai,, mtsss Wlh kinma b'atan rai tafiya zanyi," da sauri heendu ta janyota tace "haba qawata banson class dina ne fa ya zube shiyasa na nuna bnda buqata amman bawai dan wani abu ba" tsoki sa'a tai tace "kina sane fa da bikin qawarmu hafsat bala da zamuje cikin satin nan kuma sanin kanki ne 'yan boko

na qarya zasu halacci wajen ga kuma yan school namu da suka sa mana ido kuma kinsan dole ai qaryar touching phones a wajen gashi kuma dagani harke d'in babu mai touch bare muma muyi bagarar nan da ita, gashi kuma an mana tayi abun yazo a sa'a kin mana baqinciki kince masa a'a mtss wlh banza ce ke tanan fannin"
heenduh tace "ke dalla malama shouting din nan naki wlh ya fara hawar mun kai, dole sai munje da wayar ne? yanzu waya ai tazama ruwan dare babu wnda zai damu kanada ko baka da, ai yanzun abunda zakasa kaje gidan buki shi akeyi ynda za'a maka daukar girma bawai wata waya can ba, ni matsala ta yanzun ina zamu samu qananun kayan nn ne wlh muyi ranting d'insu na rana d'aya dai?
sa'a tace" kuma fa q'awata da gskiyar ki, gashi kuma ba atamfa ko less ne za'a saba bare mu je wajen mutuninki sani tela ya ara mana mu biyasa kamar ynda muka saba in biki ya kama bamuda kayan q'awa can muke masa tsinke ya satar mana cikin na masu kawo masa dinki customers nasa ya bamu ranting mu biya, to kinga matsalar baida qananun kaya kuma shi Wlh, yaya knn kikega zamuyi qawata?
shiru heenduh tai ta zurfafa tunani sai zuwa can tace "yesss i'have idea, nasamu mafita qawata saidai banda kudi a hannuna enough bansani ba ko wajenki baza'a rasa ba?"
sa'a tace "yanzun dai ba maganar kud'in ba wane mafitar ne kika samo mana?.
murmushi heendu ta saki sannan ta dunga jujjuya fararen idanunta da wayarta a hannunta ta dubi sa'a tace"wannan karon wajen madam lera mai boutique din bakin titin can na anguwar mu zamuje muyi ranting kayan" sa'a tace "wow gud idea yayi qawata, dan kuwa madam lera kafurin son kud'in tsiya ne da ita da zarar mun bata wasu 'yan q'alilan di kudi la shakka zamu samu kayan,
amman hannuna yanzun inada dubu daya dako hamsin ne? to kema kinga saiki kawo na hannunki mu had'a mata mu bata musamu zafafan inglesh-wears na gudun wuce sa'a qawata" heenduh tace
 "taf wooo danq'ari!
kamar nawa kike ganin za'a bata ne? danni wlh bnda kudi fa sosai shekaran
jiya na siyo gesha naci muda mama daman cikin wanda nike tarawa ne na school wnda baba ke bani ma fa"
sa'a tace "kamar 2k zaiyi ai in muka batan ko nikega?
heenduh ta miq'a hannunta ta jawo jikkarta ta d'auko 'yar pos d'inta mai gidan zips ta dinga shiga cikin zifa zifan tana dubawa duka dai kudin da ta had'a su basu wuce dari biyar da talatin ba, hakanan sa'a ta amsa da nufin goben in sun dawo school sai suje wajen madam lera din sumata mgnr.
heendu tace "amman qawata wane kaya zamu saka ne gobe zuwa school kinsan jami'a fa inbaka d'aukar wanka tsab za'a renaka" sa'a tace haba qawata kowa ya dubi zubinki ai yasan babu wasa a lamurran mu, kawai musa atamfar anko din sadiya bala kinga ai wancen satin ne muka yi bikin kuma daman bamu sanyata munje school da ita ba" tace "to qawata hakan za'ayi, anman ki tafo min da red din gyalenki" "to qawata shiknn" cewar sa'a din daga nn sukaci gaba da firarsu harta tafi gda ta rakata ta dawo ta kwanta kota kan kazar data cillar bayan katifarta batai ba.
hakan kuwa akayi washe gari bayan sun gama test din su sun fito sun zauna nan capeteria nasu na makarantar suna hutawa kan zuwan next lecture dinsu saiga hafsat wato qawar tasu

wacce za'aiwa bikin nn ta fito daga class itama alamun ta bada test dinta ta zauna nan kusa dasu dayake dud 'yan group dun heendu ne danma sauran basu fito ba daga class da wajen groups din nasu zaka gansa cike da mata wayayyu ana caskewa.
dayake group dinsu yafi na kowa class a cepeteria din nasu in sun zauna, shiyasa hafsat bala na isowa wajensu tace gayu gayu mutanen Allah, yaya test d'in ne?, heenduh ta yatsuna fuska tace "kinsan mu test ko exams no wahala nike jinta" zama hafsat tai tace "aike queen heenduh daban kike, so yaya maganar partyn nawa, kunsan dai kalar dreesing din da zamuyi dan taku bnda matsala inda nasan heendu queen ba harkar qaranta shiyasa nabaku matsayi na daban a cikin abokaina dan banda case daku" sa'a tace ai kada ki damu dan kalar wankan da zamuyi muje wajen nan dud wajen nan baza'a samu masu doke muba"
"ke mune fa mukayi gayun ma da knsa kokin mnta?" cewar heenduh tana yin fari da idanunta q'ar q'ar d'in nn dasu. kashewa sukai tareda shewa dukkansu, babu jimawa sauran 'yan matan suka fito nan aka zauna akaita mgnr dreesing d'in bikin hafsat har second lecture d'in tazo suka shiga.
qarfe biyu dai dai suka hau bus din school d'insu suka dawo gida, dai dai bakin titi aka ajiyesu nan suka wuce shagon madam lera mai boutique kai tsaye dansuji yanda zasu kaya zata amshi tayin gayun 'yan mata su heenduh koko?....

~Hhh yan group din Xexen fasaha dana Gital da sauran groups mm xee group kozakuyiwa wannan yan matan agajin inglesh-wears ne zafafa klr d suke so~•

By
Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️📦👁️

Suna shiga nan bakin shagon daga ciki suka iske madam lera zaune kan wata 'yar farar kujerar ta tana fmn lissafin kudi
tana ganinsu ta washe baki tana fadin cewa
"hhh yea welcome costomers sannun
ku da zuwa kaya kunason siya knn? muje to sai ku dudduba cikin shagon ko?
heendu ta Kalli sa'a sa'a ma ta Kalli heenduh da saura kad'an su fashe da dariya ganin ynda madam lera d'in tayi gaba zuwa shagon sai faman su6ur su6ur take sakamakon fat datai mata yawa.
heendu taima sa'a alamun su bita aiko suka shige har cikin shagon nan sukaga kaya na gayu kala kala kuwa q'arshen wanka ko kume ince zoda wankan ka kawai saika zura su acan kenan.
sai gwada musu wasu kalolin take dan a ganinta kalar dake nn batai musu ba ganin yanda suke ta ruwan idon dube duben nemo qarshen wankan, duban heendu madam lera tai tace "you're beautiful baby,,,, yhu choice dhis colur clothes becouse i'know zasu maka cau sosai" kallon kayan heendu take taga wata riga ce top golden colur mai tambarin wasu stones farare cike a gaban qirjinta amman kuma hannunta gajere ne iya cinyar hannuwa suke, kuma rigar iyakarta saman cinyarta mai gidan hips ce da bra haka desiner nata yake ita.
sai wandon rigar shima pencil roba ne amman har qasa ya sauko shi,
sa'a ma ta matso ta duba kyn da heendu ta dauka tace "kai gskia ne q'awata zasu amsheki kayan nan kawai ki dafesu nima ga wanda na d'auka nan amman dandai ni top rigar batakai naki sulb'i ba amman naso nasamu kalar naki ko akwaisu ne madam? madam tace "no costomers babu shine dai daya wanda ya rage mana anan sai an sake kawo mana washu kalar kuma" sa'a ta q'ara duban kayan sosai dan sun burgeta dudda haka.
heenduh tace
"sumafa sunyi kyau sosai knn qawata?" kan sa'a tace wani abu sai ji sukayi ance musu "gaskia ko sunyi kyau kuma zasu dace da kalarku musamma ma ke baby, gskia kin hadu matuqa.
yayiwa heendu maganar tareda kallonta.
duban saurayin matashin mutumin suka hauyi wanda ga alama d'an masu dashi ne kuma alamu ya nuna shima siyayya yayi wajen, madam lera tace "ah harka dawo to bari na d'auko maka ajiyar naka" nanta shiga cikin q'uryan shagon, dayake kaya ya siya yabarsu nan akan cewa tai masa total nasu yanada uzuri yanzun kn ya dawo, to shine fa ya dawo yanzun,
khames kenan d'a ga wani babban d'an kasuwa mai suna hasan gwanda, yaro ne dabaijin komi ya kashewa mace maqudan kudi indai tai masa bayajin qyashin hakan, dan haka shigowan sa yanzun ganin heendu dayai ba qaramin shigar sauri yarinyar tai masa ba a zuciya, karo kuma na farko kenan dayaji yana sha'awar aure koya bar bin yan matan sa dasuke rayuwa.
d'auke fuskarta heendu tai tareda jan q'aramin tsoki ganin ynda ya q'ura mata ido kamar wani maye sai wani lasan lips yake.
batasan kuwa shi haka halinsa yake ba muddin yaga macen datai masa sai yayi wannan ta'adar sarar tasa.
dai dai nan madam lera ta fito tace "gashi to" yace "yawwa madam so nawa ne balance naki da kikai total? tace balance ya kama dubu hamsin da biyar" yace "ok in aka had'a dana su wannan 'yan matan nawa knn?
madam lera ta dubi kayan dake hannun su wnda suka za6a tace nasu kuma ya kama 30k knn" a tsorace heendu da sa'a suka fiddo idanuwa waje jin kudin da aka tsagagawa kayan.

nan ko ya zura hannunsa a aljihu ya d'auko kudin curr ya bawa madam tuni ta damqe tana dariya ta dubi su heendu datake ganin zuwansu shagon alheri ne ya qara saukar mata tace"ah ladies ku kawo kayan to sai a sanya muku a leda ko,suko tunda sukaji madam lera ta ambaci iyayen kudin kayan jikinsu yayi snyi ashe ba kayan qananun mata bane wajen? wannan wajen ga alamu tafe yake da umarninsa kam, saika shirya wa wajen sannan zaka nufosa, dan su tuni ma harsun fara sarewa akan sun fasa mata maganar renting din dan suda sukazo da kudi runtse da hannu wato dubu daya da dari bakwai sai gashi ana musu maganar dubu 30? amman jin da heendu tai saurayin ya siye musu kayan tuni ta kauda wani d'ari d'ari a ranta ta doje tana yamutsa fuska ta dubesa tace"aida ma bakai whlr da knka ba dan munzo da kudinmu enough zamu siya koma kala nawa mukeso hakan ba damuwa bane. sakin baki sa'a tayi ta kallo heendu jin yanda ta karkace ta tsantsaro q'arya alhalun basu da abun nan? kai heenduh shegiyar yarinya ce Wlh abinda sa'a tace knn a ranta, heenduh taiwa sa'a alamun kada ta badasu man tayi normal itama, nn tk kuwa sa'a ta doje itama tace "qawata kin fad'i gskia fa daka barsa mlm ay zamu bada kud'in"
murmushi khames yayi yace "please and please nasan
zaku iya biya duka amman naji na yarda abarmun nasamu ladar biyan nan nima to" yatsune lips heendu tai ta zuba masa fararen idanuntan nan wanda yasa khames yaji yaqara shiga a kan wannan yarinyar, dan gskia ta hadu kyanta na daban ne cewarsa.
jiyai tace"ok babu damuwa inda ka matsa"
"amman ina fatan bamu takura maka ba?" cewar sa'a.
cikin 'yar dariya yace "a'a ni ai bnda matsala haka nike"
dai dai nan madam lera ta kawo musu kayan suka amsa sa'a na niyar yimasa godia heendu tai saurin fizgo hannunta suka nufi barin wajen, a hankali take cewa sa'a "kefa banza ce miye naga kina shirin masa wani godia? mu mukasa ya siya mana ne? wlh bazan bari ki gode masa ba kawai kije ki 6arar mana da class ai iriyar wannan ba ai musu godia, suna shirin tsallaka titi ne zuwa anguwar tasu sukaga saurayin ya biyosu da sauri harya qaraso wajen dasuke yace "har zaku wuce bansan sunayenku ba friends?
banza heendu tai taqi ma kallonsa sai saitin anguwarsu datake kallo caraf kuwa cikin ikon Allah idanunta suka fad'a cikin na doctor khaleepa wanda ke zaune saman but din motarsa yayinda yunus abokinsa yake rubuta wani abu cikin wata farar takarda da alama da abinda ya tsaidasu wajen knn, d'auke fuskarta tai daga tasa gamida tab'e lips.
dai dai nan sa'a tace" hakane ni sunana sa'adatu, wannan qawata kuma heendatu sunanta amman muna kiranta da heenduh queen yan school dunmu, kuma mu anan anguwar muke dan haka wnn shine taqaitaccen bayaninmu dazan maka" wow nice names,nikuma sunana khames ina zaune ne nima a garin nan naku kd amman bnjima da dawowa daga karatu ba last year,
sa'a tace "ok Allah sarki, mu zamu wuce dan daga school muke munason isa gida ne mu huta"
murmushi yayi sai qara qurawa heendu ido yake yace"kunyi gskia kam dan kuwa school daman badai gajiyarwa ba, am nace mlm sa'a kozan number heendu queen qawarki a wajenki dan naga muskila ce queen din ko mgn batason yi kuma hakan yayi matuqar dacewa da zubinta dmn"
sa'a tace "ok khames babu matsala kawo na sanya maka number"
nan ya zaro wayar tasa ya bata sai cigaba da kallon kyakkyawan fuskar heendu yake kamar ya jawota jikinsa yakeji dan ga alama fatarta zatai dadin hugging a cewarsa.

acan 6angaren su doctor khaleepa kuwa tunda ya kallo wajensu heendu sau d'aya yaga wanda suke tare dashi tsaye a wajen bai qara duban wujinba dan baisan miyasa ransa yaji ya 6aci ba daga ganinta dayai da wannan khames din wnda dud garin nan babu wnda baisan mayen mata bane adud cikin abokan
su ba.
dan haka ransa na zafi ya dubi yunus yace "yunus bar rubutun nan haka na sabbin motors din nan na dady anjima ka ida sa masa,
zomu wuce kawai, yayi maganar yana mai durowa saman qafafunsa daga kan motarsa fuskar sa a matuqar daure sosai,
dudda bawai shiri yake da yarinyar ba to amman ai 'yar uwarsa ce bazaiso yaga irinsu khames na tarayya da ita ba gudun hurewar kunne, dudda yasan heendu bata daga
layin mata masu kwad'ai dan wannan tarbiyya ce data samu daga iyayenta amman shidai ya tsargu da tarayyar
su da d'an iskan can mayen mata dan ya iya yaudara qwarai.
suna shiga mota nan doctor ya murza key suka fita anguwar ta wajenda su heenduh ke tsaye ya bi da motar aiko nanma akai sa'a suka qara had'a idanu daya wuce. ga mamakinta sai taga ynda dector Khaleepa din yayi mata wani kallon banza da qyamar wajenda take tsaye, sai kuma taji a take dud ta tsargu da hakan dan haka kawai taja hannun sa'a suka bar wajen bayan sa'a din tagama sa masa number a waya.
cikin jin dadi khames ya juya ya koma motarsa zuciyarsa tayi kace kace ta jiqe jagab da qaunar heendu hakan yakeji matuqa a rayuwar
sa kuwa.
yunus dake gefen doctor khaleepa a cikin motar ashe shima yaga su heendu tareda khames dan haka yace "ah ah doctor wanake gani tareda headache kamar fa khames? mayen matan nan?, mizaisa ta tsaya dashi ko ita,
kobaka lura bane friend?
cikin qunan zuciya doctor khaleepa yace"hmn! miye ruwa na a cikin lamurran headache ne wai yunus? dakabi ka dameni akai ne? kasan bawai wani shiri mike ba dan haka ita ta sani rayuwar tane kowa taga daman tsayawa dashi sai ta yi ay"
yunus yace "qanwar kace fa kuma blood sister dinka dan haka komi ke tsaka ninkun ka jnyesa ka taka mata burki akan khames gskia friend"
shiru doctor Khleepan yayi alamun maganar ma ta ishesa haka, sanin halin mutumin nasa da yunus yai kawai yasa yayi shiru dan yasan koya qara tankawa bawai amsa zai samuba daga doctor khaleepa din
kamar ynda ya zata. heendu kuwa suna isa qofar gudansu ta ce"sa'a kije da wannan kayan gidanku kinsan basu sawuwa nan gida a gaban mama in yaso ranar da zamusa kayan munje gidanku mu shirya sai mu wuce tacan, yanzun inna shiga gida nasan yanda zancewa mama ta barni muje bikin nan kinsan ba barin zuwana fa farty take ba kema kinsan hakan".
sa'a tace "eh hakane Allah yasa kimata dubara sosai dai to komi knn naji nina wuce"
"to qawata sai mun had'u kyaji koya mikayi da maman" cewar heendu.
haka sa'a ta miq'e hnyar gida heenduh kuma ta shiga gidan nasu qirjinta rungume da handouts dinta.
ta hango mama Zainab cikin madafi da sauri heenduh ta ajiye books din tareda isa wajen

maman tace"mama daga samun sauqi sai kifara shiga kicen ki bari na qarasa aikin"
tayi maganar tana karbar robar hannun maman tata, mama tace "barsa heendu ba wani abun ma nikeba mai wahala kinsan tun wancen satin 'yar tiyar shinkafarmu da wake ya qare hakadai muketa manage na rayuwa a gdn, kuma kinga jia babanki bai zauna sana'a ba bare, inda daman dan abunda ya cinikanta ne a ranar yake siyo yar taliya ko gwangwanin shinkafa uku a samu na girkawa, to kinga yanzun haka bai jima da lallabawa ya fita wajen sana'arsan ba baici komi ba sai dan kingin nmn nan najiya, gashi kuma yanzun lokacin sanwa yayi babu abinda zamu dafa a ranar dole na tashi yanzun na nemo wannan tsohon garin rogon dan a kwada akaiwa baba yawale nasa abincin kamar yanda aka saba kai masan, dan haka jeki dakin babanki gefen gadonsa zakiga wani qullun baqar leda wacce aka sa masa nmnsa shima sai kixo ki miqo man langar kwanon da ake zuba masa abincun nasa saiki miqa masa" jiki a sanyaye heendu taje ta d'auko abubuwan ta dawo ta ajiye nan mama ta ida had'a kwadon ta zuba ma baba yawale a langarsa gamida d'an kullin naman nasa wanda suka kasa dashi a daren jiyan.
kwanon heendu ta dauka tareda yafa gyalenta ta fita zuwa gidan baba yawale ta iskesa kwance da carbinsa yanata lazumi, zaunawa tai tareda ajiye masa kwanon a gabansa tace "gashi mai ran qarfe inji mama, baba yawale yatashi zaune yana fadin "madalla zainabu Allah shi albarka bata gajiya da hidima Allah saka da gidan aljanna" "amunn mai ran qarfe,, jiya bakai cigiya taba ko kaga banzo firan dare ba muda sa'a?, baba yawale yace "ai nazata kina gidan giggonki d'ahara ne mai quli quli kinje cinye mata zogale sai gashi khaleepa ma ya shigo dashi ne muka yini dashi anan a tare ba hayaniya kalar taki, tabe lips dinta tai tace "oho kenan ma qwamma da Allah yasa banzo ba, yace "meko sabida mi? kada dai nace har yanzun baku bar wannan halin naku ba? to Allah kawo ranar sasanta wa, zumbur heendu tai ta miqe tace"aa mairan qarfe ba Amin bafa, baba yawale ya kama ha6a yace "ikon Allah, amman kinsan ai yafiki kirki shiyasa kike kishinsa a wajena, yayi maganar cikin tsokana.
"tabb aiko bai fini kirki ba saidai neman suna ni kaja ma nai tafiya na gida bazan zauna ba"ta turo kallabi gaban goshi tai ficewarta gyale a kafada guda d'aya. baba yawale cewa yake "ki gyara mayafin jikinki danke ba kamar kowace budrwa kike ba amman ina ko jinsa batai ba tayi gaba abinta ta fice, girgiza kai kawai yayi zuciyar sa na masa rawa a dud sanda ya tuno dadadden sirrin da suka boye na auran yaran, anya kuwa zasu cigaba da zura ido ga yarinya da aurenta ammn take tareda samari? anya basu so kansu ba? sukaji tsoron abun halitta sa6anin wanda ya halicci halittar shi ba azzalumin kowa bane? shikam yarasa kwanciyar hankali tun sanda yaga heendu takai munzalin cikakkar budurwa gani yake kowane sa6o heendu ta aikata batareda sanin cewa tanada aure ba a kanta tofa tabbas tabbas la shakka sune zasu kwashi zunubin nata inda dai ita harga Allah bata sani ba shima khaleepa din haka kuma, sune dai suka sani gskia dole yasan abunyi kuwa dan bazai dawwama ba a hakan, yanajin shifa koda zai rasa ransa kanya rasu tabbas saiya fadi gskia a dud snda yaji wani ya bujirowa da iyayen heendu maganar aurenta kuwa.
dan babu labarin aure kan aure ko a cikin musulinci kuwa, dan haka ya q'wammace ace sanadiyyar hakan zaibar duniya komi mukhtar zai masa saidai yasa ai masan koda kisa ne kuwa qarewar kaq'e dayace zaisa ai masa kawai shi yanzun dai abu d'aya kawai ya sani bazai taba bari heendu tai aure kan aure ba muddin yana da rai kuwa wannan alqawali ne.
bude abuncin yai ganin nama a sama yasan cewa samosa sukai bayin Allah, qwarai sosai yake

mamakin yanda suke basa kulawa tamfar baffa komi zasu samu a gidan nan koko kuma zasuci tabbas saisun kasa dashi komin rashin dadinsa haka zalika komin dadinsa kuma, yawansa ko kadan dinsa.
bismillah yai tareda jawo abincin ya fara ci bakinsa dauke da adduar dayakewa su baba isma'il fatan gamawa lpia gamida maido hankalin d'an uwansa kusa dashi dan cigaban zumuncinsu.
heenduh kuwa na fita wajen sa'a taje ta karb'o kud'inta d'ari biyar daga nan ta biya shagon da hjy firdauseey keda 'yan haya dayake dud anguwar nan ake siyar da provisions da kayan abinci sbd shagunan nata a jere suke sama da 20 , dan anguwar tasu makekiya ce dan kowace mota zata iya shigowa ta fita kuma lpia.
to nan ta shiga shagon farko ta siyo musu shinkafa da kud'in rabin tiya saurin canjin kuma ta sai musu manja da magi inda tasan sunada sansamin tasshi a gida kuma, koda ace babu saisu haqura suci haka nn inda sun saba.
Koda ta koma gida ta ba mama Zainab kayan tai mata bayanin da kudin makarantar tane ta siyo musu abincin har qwalla mama Zainab ta goge a fakaice tasan heendu dud rawar kanta tana da tausayin iyayenta wannan ke nuna mata cewa ko bayan ransu heendu zataci gaba da alherinta ga mabuqata muddn ta samu damar hakan cikin bud'in Ubangiji, shiyasa kullum cikin zuciyarta tanaiwa 'yar tata add'ua dudda wasu halayen nata datake k'i tasan nan gaba ta q'ara hankali a matsayinta na mace zata daina ne, haka suka kasance a yinun ranar itada mamarta, kuma taji dad'i q'warai da taga khaleepa bai sake waiwayosu ba har dare suka kwanta barci.
khaleepa kuwa sai wajen qarfe 11 saura ya shigo anguwar daga kallon ball shida yunus ajiyesa yai gida sannan shi kuma ya karkata kan motarsa zuwa gidan small dad d'in nasa sai dai kashh!! abinda ya guda ne ya faru, wato har sun rufe gidan su, yasan maybe sunyi tunanin bazai zoba inda ana gama sallar isha'e ne lokuttan shigowar tasa.
juya hancin motar yai zuwa gidan su dai dai wajen gidan su, dayake daga gidan hjy Hadeeza sai nasu to ganin mota wata ja qirar pejo ta tare hnyar yasa shi cigaba da sakin horn amman shuru ransa ya 6aci ya ganin da alamun mai motar na ciki kuma yana 6ata masa lokaci shiyasa a fusace ya fito daga motar tasa ya isa ga motar nan ya leqa knsa ta qofar drive din ciki da nufin masa mgn ya basa waje zai wuce dayake glass din motar an dan zugesa qasa kadan sbd shigowan iska da shaqansa kuma, wacce yagani ne a motar liq'e jikin saurayin nata sai faman tsotsar juna suke kota ina haka kazalika rabin rigar ta a zuge yake har ta dawo saman cikinta ma.
mamaki q'warai ne yakamasa dan bai taba tunanin tsabar tantirancin yarinyar yakai ga ta saida mutuncinta ga mazan iska ba sabida tsabar fand'arewa kalar tata, tsoki yaja da qarfi tareda cewa"excuse mlm bani hnya zan wuce dauke motar nn tk" abinda saurayin knn yaji a saitin tagan motar tasa, aiko da wani sauri ya dube khaleepa ganin yanda fuskarsa take a murtuq babu wani wasa yasa tuni mutumin yasha jinin jikinsa daga rashin mutuncin dayaso kartawa dud wani shege dayazo katse masa jin dadinsa da yayi nisa a ciki,
dan wani mugun qwarjini daya gani ga khaleepa har wani d'an tsoro da shakku yaji ya kamasa dan gani yai guyn yai masa kama da zubin cikakkun soldiers a tunanin sama soja ne yasa personal din kaya yake round a motarsa cikin ward din, shiyasa tsoron sa ya nunku tuni jininsa ya dawo saman akaifar sa. itako cikin rawar murya da borin kunya tai saurin zuge zip d'in rigarta sama kamar ta nutse wajen takeji dan wata kunya data kamata, daqyar tace "am yaya khaleepa ka.. sam bai bari yaji mgnr da tk shirin fad'a ba ya ya qara had'e fuskan nan tasa a qyamace

yabar wajen ya shiga motarsa shi kuma saurayin dayaga alamun b soja bane harya ji dadi ya daina tuno iriyar mugun dukan da zaisha daga belt din jikin khaleepa a tunanin sa.
dan haka ckn saurin gaske ya gyara masa parking yai wucewarsa
ransa cike da mamakin yarinyar harya shiga harabar gidan nasu abun na tuqosa tuni yaji kowace mace ma ta qara sire masa yagodewa Allah daba koyi sanin ynda ake so ba bare yayisa har ya wahalar dashi a banza.
(shifa a tunaninsa so koyansa ake sannan a yisa ma)
a haka ya kashe motar ya shige cikin gida yana sakin tsoki a zuciyar sa still hoton yanayin daya gansu bai baccewa tunanin saba kuma! .

By
Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️📦👁️
🅿️2️⃣6️⃣
Z ara kuwa lokacin da taga khaleepa ya wuce nan take kuwa ta d'aura hannuwa a kanta tace da q'arfin gaske "wayyo Allah na, na shiga uku na hafiz! ya'akai nabari yy khaleepa yaimun wannan wawan kamun?!"
dubanta Hafiz d'in yayi yace "sweet miya faru ne wai?
mizaisa ki shiga uku bacin gamu tare muna jiyarda juna dad'i koko ke bakyajin hakan na qara qaimi akai? ko kuma Innan bai miki ba mu qarasa hotel ne? wani kallon haushi kawai zarah tai masa tace
"iskancin banza da wofi ma knn, ya ina maka mgnr cewa wanda nikeso zan aura ya gammu tareda kai cikin wannan halin ka cemun romance bai isan ba?
zaro idanuwa hafez yy cikin mmki yace wai wannan mai zubin sojojin kike mgn? ta66 gskia ko daga gani bazaiyi wasa ba danni wlh ba qaramin tsorata naiba sweet na danaga zubin halittar sa.

da riga jikinsa kalar kakin soja to wlh nazata sojoji ne masu saka personal din kaya suka fito fateroling a anguwar taku muka tare musu hnya.
kukan takaici ta fashe dashi tace "wlh Allah ya isa Hafiz ka batamun budget danasan yaya khaleepa zai gammu haka daban fito ba banza q'aramin d'an iska"
da gudu tai cikin gida tana cigaba kukan baqinciki shikuma Hafiz dariya ya saki ya shafa gemo yace "oho gaki cikakkyr 'yar iska kuwa, can matsalarki inda dai nasamu nyc ni ai lpia lau bari na fasa wajen wata cikar indai akwai kalarku a gari aimu ba muda matsalar aure rayuwa sai ba'ai"
(niko nace kayya dai Hafiz badai wannan rayuwar ba maras tabbas gskia dan kamataddini tabbas zatai aiki a knku muddun baku cnza ba, wnn fdr AllAh ce.)
daga haka ya tashi motarsa yayi gaba.
zara na shiga falo ta iske uwar tana waya da hjy firdauseey kan wasu sabbun samfur na kayan zannuwan gado da zasu shigo dasu aqasar dayake had'in gwiwan business sukai sunayi tare kuma ba q'aramin riba suke ciba dan a qalla kowa zai tashi da ribar 10 millions dud yan kwanaki.
zubewa tai saman jikin uwar tana burgimar kukanta, a rude hjy Hadeeza ta ajiye wayar ta riq'e 'yar tata tana jijjiga ta dan tayi tunanin ko tayi gamo ne sai cewa take
"a 'uzu billahee mike damunki wai zarah? saida taci kukantah sosai sannan ta dubi uwar tace"wlh mama nidai yaya khaleepa nikeso kawai kuyi mgnr aurenmu kada ciwon zuciya ya kasheni yanzun gashi ya gnmu da hafez cikin motarsa a halin da bai dace ba.
(kuji fa wai har iya fad'a tk ya gnsu a wani hali jama'a)
itako uwar sai tace "Kemadai zara yazaki bari ya gnki aida saiku yi ta inda babu wnda ma zaisan kuna wajen daman har yanzun
mamarsa ta gaza shawo knsa akn mgnr ki gashi kuma kin qara wata illar ya gani da idonsa toyaya knn?
"to mama in bai sona ni wlh ina sonsa a hakan"! ganin ynda ta rud'e ne yasa uwar rarrashinta da cewa komi knn ta bari zuwa gobe zasu qara tattauna mgnr auren nasu itada mamarsa firdauseey din.
sai lokacin ta samu sauqin zarah fa data fad'a mata hakan hartai barci nn kusa da uwar najin dadi.
shiru hjy Hadeeza tayi da tunanin waiya zasuyi da shegen yaron nn ne mai dan banzan taurin kai har gashi yana niyar susutar mata da d'iya?, kuma gashi uwar tasa tasa dokar babu batun kai d'anta wajen boka da niyar jawo ra'ayinsa ga zaran harta ke ce mata wlh koda kuwa ta faki idonta taje tofa tabbas babban tsohon bokanta marakusa suna nan tare kuma zai fad'a mata intaje wani gun kai mata d'a.
ta qara da cewa abatta dashi zata shawo kan d'anta harya amince musu, ita hjy Hadeeza har mmki take ynda hjy firdauseey koda wasa bata bari koda sunan khaleepa yaje wajen mstsafansu bare har akaiga kai musu kokensu aknsa, amman Bakomi babu ynda zatayi dole ta haqura da batun Hjy firdauseey na cewa datai zata shawo musu knsa koda yaushe nema d'in, amman dudda haka gobe dole taje su q'ara tattauna mgnr da ita hjy firdauseey d'in dangane da batun zarah d'in da khaleepa, dan rabon da su qara tattauna batun kusan 2 month knn danta kula sam Hjy firdauseey batason matsawa khaleepa shiyasa take share mgnr lokacin, tsoki hjy Hadeeza ta saki a fili tareda cewa "duttabi ta mutu kn masifar son danta kamar tafi kowa iya haihuwa mtss kayan 6acin rai kawai inbnda shegen naci irin ma na zarah mutumin daya nuna

bai sonka bazaka haqura bane kaima ka barsa, bacin dai kawai kulafanci iriyar na *d'an yau"*.
daga cikin d'aki kuwa mijin Hjy Hadeeza ya qara qwalla mata kira na karo sau babu adadi tun zamnta falon amman bata jeba taji kiran nasa tsabar ta gama dashi, yanzun ma daya qara cewa"haba hjta kefa niketa jira mu kwanta amman kin barni nan sakakai" miqewa tai tace"kaiko ka cika jarababben bawa wlh Alhj, haba dole ne sai ka jini jikinka sannan zakayi barci mtss" haka ta shiga d'akin taita masa mita shiko alhj bala cewa yake"haba keko raba kanki da sabo hajiyata.
rayuwar fararen turawa hjy Hadeeza takeyi a gdnta koda a gbn 'yarta ne abunsu sukeyi babu kunya hakan kuwa da sukeyi da mijin nata ba qaramin bada guduwar 6ata tunanin 'yarsu sukai ba zara, harta fara tunanin jin sha'awar yin ynda taji iyayen nasu na abunsu ne mafarin knn ta tsunduma knta a rayuwar bnza kota kashe q'ishin da iyayenta suka assasa mata a jiki na tsabar sha'awa.
(ana samun hkn iyayenmu dan Allah a kiyaye yin abubuwan da keda kawaici a gaban yara gudun rusa kyakkyawan halinsu zuwa akasin hkn dan sha'awar ba'aimata kawaici musamman ga wanda suka kai matakin balaga, yaran sunsan komi saidai kiga yaran nata kallon iyayen su a kaikaice kuma dud yawanci a cikin gudumuwar iyayen haka ke faruwa).
doctor khaleepa kuwa koda ya isa main palor nasu baiga kowa ba sai mai aikinsu asabe datake dauke colars dake kan dining tai saurin gaishesa ya amsa sannan ya wuce dakinsa yayo wanka ya fito,ya dawo falon qasa ya hau dining coffee yasa asabe ta qara hado masa bayan yaci abunci dan sam bai wasa da cikinsa ko kadan, bayan ya gama ne ya koma samnsa yai brush ya dawo ya kwanta smn gadonsa tareda lumshe ido tunanin abubuwan da suka faru yau tsakanin ba heendu dana zara baqaramin haushi ya qara jiba, sam na zara bai damesa ba a zuciyar sa akan na heendu dan gskia koma ya knn bazai Bari tana tarayya da khames ba zaisan ynda zai bullowa lamarin dan bazai qyaleta ba ta jawo musu surutu ba a family nasu ga jama'ar anguwa dole nema ya sanarwa mama Zainab halinda heendu din take ciki kan kula kalarsu khames bata gari muddin ta nemi masa rashin kunyar tata kuwa wajen mata gargad'i na farko akan khames daya qudurta a ransa zai mata dudda ba son shiga harkarta yakeba amman wannan d'in kamawa tai shiyasa.
da tunanin hakan barci ya d'aukesa batareda ya kashe laptop d'insa ba da yabari kunne tun lokacin fitowarsa daga wanka sakamakon fara duba wasu abubuwan dayai yana turawa doctor hasan gameda kayan aikin da zasu qarowa hospital din nasu.
kuma ya sauka cin abunci sann gashi ya dawon kuma baibi takanta ba har ya kwanta dan yagaji matuqa.
yau takama juma'a bayan an taso masallaci doctor khaleepa yatafi kai dadynsa airport cikin mota bada jimawa ba saiga hjy Hadeeza ta shigo gidan tai sa'a kuwa hjy firdauseey din na zaune ita dai a falo tana kallon tashar blywod, tana ganinta tace cikin farinciki "aminiyar sannunku da zuwa" hjy Hadeeza tace yawwa aminiyar,sosai Hjy firdauseey taga yanayin Hjy Hadeeza a sauye nan take ta matso kusa da ita tace"aminiyar dud ynda akai kina cikin damuwa gskia fad'a mun mike damunki ne haka?
"hmm wlh kedai bari Hjy firdauseey batun yarinyar nan nefa zara gaba daya ta qara rudewa wai itadai khaleepa, khaleepa dai ni gaba daya wlh al'amarinta yafi gaban tunani na, dan jiya fa da qyar nasamu na shawo knta, shine fa nazo tanzun naji Allah sadai kin shawo kan d'an lelen naki aminiyar?

Hjy firdauseey tace "komi yazo qarshe aminiyar da zarar alhaji na ya dawo qasar nan zan samesa mu tattauna mgnr bikin nasu kada ki damu koya amunce ko bai amince ba ai dole ma ya aureta dan kaf garin nn bnda aminiyar qwarai kmr ki"
cikin farinciki Hjy Hadeeza tace
"yawwa aminiyar wlh har naji hankali na ya kwanta kinga yanzun saina fad'a wa Zara ta matsayar zancen, amman naji kince Alhj mukhtar bai nan ina yaje ne?"
Hjy firdauseey tace"yaje Singapore ne maikatarsu ce ta za6esa ta turasa wani aiki har tsawon wata 4 sannan zai dawo"
Hjy Hadeeza tace "ohhh yanzun naji batu, ammam yakamata yasan da mgnr auren kanya dawo fa aminiyar? "
Hjy firdauseey tace"na fara masa mgnr jia ay amman yace in bari yadawo sannan sai ayi komi danna rigaya danace masa khaleepa dinma ya amince da mgnr dan idan yasan khaleepa din baiso bazai ta6a yarda ayi auren ba dan shi sam bai lamunci abinda zai takura khaleepa bafa, koya yisa batareda son sa ba shiyasa nayi masa siyasar cewa ya amince"
shewa sukai tareda tabawa hjy Hadeeza tace "'shiyasa nakejin dadin hulda dake wlh aminiyar sama da kowa kuwa"
nan dai sukaci gaba da tattauna batun.
da misalin q'arfe hud'u na yamma heendu ce zaune qofar dakinta ta baje kayan makeup dinta sai kwallace fuskar nan take saiga sa'a ta shigo nan ta sameta bayan ta zauna gefenta tace"kai qawata wannan kwalliyar fa saikace wacce zata fadar shugabn qasa kokuma ince wacce zata gasar za6en sarauniyar kyawawan dun duniya? hmm qawata bakya gajia da makeup a fuskar ki dud wannan d'anyen kyaun da kike d'auke da shi?"
fari heendu tai da idanun nan nata masu tsananin haske kamar madara ta dubi sa'a tace "hmm kema kin sani yin kwalliyar nan fa qawata a jini na take dan mace daman ai 'yar qwalisa ce bawai wani abu ba,koba haka ba?"
zuba mata idanuwa sa'a tai kawai tana kallon tsabar kyau da Allah ya mallakawa heendu, abinda yafi qara daukar hankalin mutane fuskar heenduh shine yanda takeda zagayayyer face ba doguwa ba, round face cikakka, sai manyan fararen idanun nan nata da sune suka q'ara haskake fuskar tata tareda d'an hancin nan nata mai kyaun gaske wanda ya dace da fuskarta, ga lips dinta jajur dasu masu laushin gske, haqoranta ma farare ne tasss reras dasu. jin da sa'a tai heendu ta tabota tareda cewa" Haba qawata wannan kallon qurillan fa?
dariya sa'a tai tace "hmm kallon kyaunki nake qawata, Wlh qawata kinji dad'inki ki godewa Allah da kyakkyawan sigar dayai miki kota'ina"
kan heendu tace wani abu saiga kira ya shigo wayarta ganin sunan musaddiq ne yasata sakin dan tsoki tareda fadin "hoooo kai na tsani naci wlh haba dan Allah nina mnta ma munyi dashi yaune zaizo"
daukar wayar tai batareda tace komi ba sai shine yace"ranki shidad'e gimbiyar mata gani fa a qofar gida ba iso ke kawai nikeda burin gani"
cikin zuciyar ta tace"hmm jibesa da Allah ance maka inason namiji mai tumbi ne mtss" amman a fili sai tace"ok give me 20 mints i am coming"
daga haka ta kashe wayar ta saida ta qara qara 6ata sama da minti 22 wajen gyaran fuskar nan a qalqale nan a goge nan a kuma shafa can sannan fa suka miqe Itada sa'a bayan ta yane gyalenta a wuya ta shiga d'aki ta iske maman a zaune tana Linkin kayan baba isma'il da heendu

din ta gama wanke masa dazun, tace "mama zan d'an fita ne nn waje musaddiq yazo"
dato mama ta amsa mata amman har a ran mama ba cikin jin dadi take barin heendu tsayawa da samarin taba inda tasan tabbas matar aure ce tun tana jinjirar ta.
heendu tace 'wayyo 'sa'a wlh fitsari nikeji gashi ya isheni da waya mayen jeki dan Allah kudan fara gaisawa kanna gama"
dato sa'a ta amsa sannan ta fita tanawa heendu dariyar fitsari yazo lokacin zance indama Allah yasa ba uban garin bane da kwalliyar ta tashi dan tasan halin heendu tsab zatace saita sake wani sabon wankan da kwalliyar sannan ta fito.
tana fitowa daga bayin ta sawa qafafunta ruwa
tareda tsanesu da wani qaramin towel ta nufi qofar fita knn taga an turo kyauren gidan tareda shigowa kai tsaye kamar ynda ya saba, doctor khaleepa knn, qin matsawa tayi dan ta basa hnya sannan kuma ga mamakinta taga ya tsaya cak gbnta batareda ya wuce ba kamar ynda tai tunani.
saima wanj kallon da yakebin illahiri jikinta dashi bai kuma tnka ba, daga qarshe dai sauke idanunsu sukayi cikin na juna na tsawon daqiqu biyar sannan ya kauda fuskarsa daga tata bayan ya sake tur6une fuskarsa ya matso sosai gabnta har numfashinsa na sauka saman goshinta dan yafita tsawo.
kallon takaici yake qara binta dashi wai shikam yarinyar nan mita dauki knata ne?
dubi yanda doguwar rigar material din ta matse mata mama dud sun bullatso sama dan daqyar ma take numfashi tsabar mataseta da rigar tai sai wani matacin gyalenta wnda yashi y babu dud daya amman a haka take tunanin fita wani waje? , ganin yana shirin bata mata lokaci akan tsareta dayai yasata damuqe fuska tareda 6alla masa harara bayan murgudo baki datai a yatsune tayi nufin bita gefensa dan tai wucewarta,
babu zato kuwa taji yasa wani mugun qarfin damatsan hannuwan sa ya maidota gabnsa ya ajiye kamar wnda ya dauki 'yar tsana dan batada nauyi sam sam, sai aijyar enlargement breast a gaba da kuma qugu nan ne masu qarfin a jikinta. daqyar ya daure ya bude bakinsa cikin kakkausar murya taji yace
"kozan iy sanin miye had'inki da d'an iskan yaron nan khames headache?!..
tunani ta shigayi waye kuma khames?! dan ita kam harga Allah ta ma mnta da zancen wani khames dan haka ta zuba masa idanunta itama tareda cewa "nifa sauri nike zan wuce kabani hnya ana jira na a waje sannan ni kuma bansan wani khames ba dan haka ninka sake ni inda ba 'yar iska bace dazaka kaman hannu ka riqe"
tayi mgnr tareda faman hararar hannuwansa dake damtse da cinyoyin hannuwanta.
cikin fusata ya fuzgota tareda danganta ga bango yace"ok nine dan iskan knn?
yatsine tai tace "nika rabu dani kona kira mama wlh"
jiyayi knsa ta fara sara masa babu shiri sakamakon kwaratsin datake sashi yi batareda ya saba ba shiyasa ya cillar da ita gefe tai saurin dafe qasa ta miqe knn taji muryar mama na cewa "ya ilahi mike faruwa kuma haka tsakanunk da kuma heenduh khaleepa??,,
duqewa yai wajen tareda tamqe knsa dake barazanar fashe masa lokacin dayaga heendu dun ta fice daga gidan bayan gama jifarsa datai da wani kallo wnda yafi kama da kalmar nan ta cewa *na tsaneka fa ni*,,,,,
runtse idanunsa yayi tareda shiga dana sanin na harkar yarinyar daya shiga marar kunya qwarai yayi dana sanin hakan kuwa, dan dabai shiga harkar taba bazai jawa knsa ciwon kaiba

anan... daqyar yasamu ya miqe tsaye tareda fita gidan batareda yacewa mama zainab komi ba. itako ta bisa da kallon mamaki na mike faruwane ga lamarin khaleepa da heendu ne wai da sam *basa ga maciji* tsakani??!!
"Allah shi kyauta" abinda k-wai mama zainab tace knn ta juya ta koma d'aki dn cigaba da linke kayan wankin dan dama hayaniyar maganarsu ce dataji ta fuddo ta daga d'akin dan tasan sune daman inda sun kwana biyu basuyi ba dmn sai yau knn da mai kamawa ta kama....

By
Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🥡🥡
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️🥡👁️
🅿️2️⃣1️⃣
Lokacin da doctor khaleepa din ya fito waje yayi matuqar mamakin ganin heendu tsaye bakin motar musaddiq.
daman musaddiq yasan tane? to inya santa tayaya bai ta6a ganinsu tare ba? , tambayar da yakewa kansa knn, sam jiyayi bai iya shiga gida kamar yanda yai niyya saima samun waje yayi nan cikin barandar gidansu inda suke zama bisa fararen kujerinsu shida friends d'insa dud in sun samu lokacin hkn.
bayan ya zauna bisa kujerar tareda d'ora qafafunsa bisa wata kujerar daya bisa daya yana girgiza su yai setin inda su heendu ke tsaye yana kalla qasa qasa zuciyar sa na masa wani ba dad'i2 yakeji lkcn.
amman bazaka ta6a cewa yadamu dasu ba bare ya kallesu amman kuma dud rabin hankalin sa na wajen dudda knsa naga kllon fuskar wayarsa daya tsurawa ido yana lallatsa ta.
acan 6angaren su heendu kuwa sa'a na tafiya musaddiq ya juyo rareda tsurawa kyakkyawan surar fuskar heendu ido ya saki murmushi yace"mai hasken zuciya ta ina matuqar son fararen idanun nan naki da hancin nn naki gamida baki Allah sa in minyi aure ki bani baby girl mai

kama dake sak din nan haka babyn raina"
a yatsine heendu tace"hmm qwamma da kace mace ma"
cikin 'yar dariya yace bakison ki haifi baby boy ne?
"qwarai fadi kanka tsaye ni mace nikeson haifa dud in nai aure, ko awane haihuwa zanyi zanso naita haifar ta"
kama baki musaddiq yai yace "lallaikam gimbiyar mata a gaisheki gskia kam kina son baby girls naga alama "yayi idashe yin maganar tasa tareda bude murfin gaban motarsa ya fiddo wani dan babban kwalin waya ya miqa mata tareda cewa ga barka da jumaa amman dan girman Allah kada kuce bakiso dan nasan halinki,,,murmushi heendu tai ta saci kallon inda doctor khaleepa yake zaune dan tun wucewarsa take satar kllonsa har inda yake zaune, dan haka wata zuciyar tace mata "ki kar6i kyautar wayar nan man heendu kodan ki q'ara k'onawa dan rainin hankalin nn rai nan take ko ta miqa hannu daya ta karba a yangance tareda furta kalmar "thankzzzz"
haka musaddiq yaita fira itako gimbiyar sai wacce taga dama sannan take zabar mgnrsa daya ta basa amsa har tagaji da tsayuwar ta dubesa tace"zan koma gida musaddiq kasan bn jumurin tsayuwa daiko?
murmushi yayi yace "nasani gimbiyar mata amman sai yaushe za'amun alfarmar sake dawowa dan na kalli wannan iriyar kyakkyawan fuskar taki gimbiyar mata? saida ta dan sake yatsina lips dinta sannan tace "komi knn mayi waya" daga haka ta juya ta shige gidan baba d'ahara mai qoli2 shiko yabi bayanta da kallo dan gaba daya yarinyar tayi kota ina, sauke ajiyar zuciya yai tareda shiga motarsa ya bata wuta tareda nufa hanyar gidansu, dayake can qasan layin gidansu yk.
tun lokacin da doctor khaleepa yaga heendu ta karb'i abu cikin kwalin da musaddiq ya bata dudda baisan komi ba ne a ciki amman saida yaji kamar dai babu dad'i haka a ransa, daga qarshe dai dayaga abun kamar zaisha tunanin sa tabe lips kawai yai tareda korar tunanin hkn a brain dinsa ya gyara zamnsa yaci gaba da touching din wayarsa knn yaji muryar yunus na cewa "yadai friend kai d'aya ne zaune a wajen haka? amman to nayi mamaki dan nasan baka zama kai daya wajen koko kana jiran wani abu ne?"
dubnsa doctor khaleepa yayi yajima sannan yasamu ya bude bakinsa yace"no yunus kawai dai ina dan futawa ne nan din shiyasa"
gyara zama yunus yayi yace "oh koda naji dai mutumina, but ya naga ba baka shirya zuwa buga Ball bane? naga baka sa kayan ba, gashi kuma dud sauran friends namu sun shirya su muhsin da lawal da muazzam fa"
saida doctor khaleepa yad'an mammatsa gefen kansa da yatsunsa guda biyu sannan ya furzar da iska yace"yunus bansan ya akai banjin dad'in zuciya ta bane da jiki na ina tunanin masassara ne keson riqe ni"
yunus yace
"subhanalla friend indai ko haka ne yakamata ka shiga ciki ka d'an sha magani saika kwanta ko? "
girgiza kai doctor khaleepan yayi tareda cewa"zanje buga ball dinnan banson na kwanta ne hot fever dinnan ta saukar mun qwamma inje in excercise na buga ball dinnan kozan samu qarfi qarfi bari na shirya ynxun gani nan fitowa" yayi maganar yana mai miqewa tsaye.
Yunus yace "to inda kace hakan ai lpia lau"
bai jimaba sai gashi ya shiryo cikin wasu fararan kayan q'wallo masu ratsin baq'i wanda sukai

matuqar qara haskaka zatin surarsa,farar safar iya gwiwarsa ta tsaya sakamakon yanda dai kayan qwallo suke kamar ynda kowa yasani.
duqawa yai tareda ida d'aure cambus din igiyoyin takalman sannan suka wuce play ball din tareda sauran friends din nasu.
heendu kuwa tana shiga gidan baba d'ahara ta isketa tana toya q'uli q'uli cikin man gyad'a wanda q'amshin sa dud ya buge wajen da sauri heendu ta ajiye gyalanta da kwalin wayar ta isa wata kujera dake gefen baba d'ahara d'in ta zauna tareda fadin "tsohe ya naga q'ulin yau kad'an ne kuma ba kamar na kullum ba? "
baba d'ahara tace"kedai bari hendo wannan q'ulin na alq'awali ne yau mukai dasu zasu zo karb'ar ragowar masu sarin nasa, dayake jiya suka zo suka d'auki wani, shine nike sauri na ida kona samu naje gidan bikin nan gobe da wurwuri"
heendu tadan lakuto tunkuzar da qaramin yatsanta guda daya ta sa bakinta ta tsotse sannan tace
"biki zakuyi ne tsohe?"
baba d'ahara tace"kaji yarinyar nan kuma dai? kaddai kin mance da bikin zeenatu nane 'yar qanwa ta wanda za'a fara sa gobe?
zaro idanuwa heendu tai tace "Allah kuwa tsohuwa na mnta ashe gobe ne ake fara bikin?
baba d'ahara tace "aikodai gobe ne ga mai yawancin rai"
matsowa heendu tai tareda ruqo d'ayan hannun baba d'ahara tace"yawwa tsohuwar nan wani temako nikeson kimin wajen mama dan Allah kamar yanda kika saba yi muna kinji 'yar baba d'aharar baba yawale?"
da baba d'ahara harta janye baki tana wa heendu kallon hadarin kaji iriyar dai ynda tsoffi ke karkace fuska amman tanajin heendun ta sako mata batun baba yawale a ciki tuni ta saki fuskarta dan baba d'ahara tana matuqar qaunar baba yawale ba kad'an ba kuwa.
duban heendu tai tace"ina saurarinki Allah sadai ba wata qaryar zaki sani naje lankatab'awa uwarki zainabu ba kamar ynda kuka saba sani keda sa'a, nidai dan Allah yaran nan kudaina sani qaryar nan hka dn shekaru na ja fa suke farinciki nane mani inga kun fuddo mazajen aure muyi mu aurar daku koma huta da yawon nan naku na gaira babu sabar"
fari heendu tai wa baba d'ahara da idanun tan nan tace "kai caiiiii Tsohuwar nan baki iya cin ribar zance bafa, yaseen jiya na jewa baba yawale da maganar aurenku fa"
tuni baba d'ahara ta wangalr baki tareda ajiye tunkuzar dake hannunta tasake duban heendu sosai tace"kai 'yar nan hendo fad'a mun to yaya ce miki?
d'an tsinano baki heendu tai tace
"kamin na fad'a miki komi na shirya fatan dai zaki mana yanda muke so ko baba d'aharas ras tamu?
cikin dariya baba d'ahara tace "kaji ja'irar yarinya da wayau wato so kike miyi bani gishiri na baki manda ko?
"yawwa baba d'aharas ras kinje gana dai knn"
kingane so nike koda yaushe ne inkin gama tuya kuli kulin nan kije ki samu mama ki mata bayanin muma zamu jewa zeenatu walima goben nasan inda kece kikai mata mgnr da knki zata yarda kinji ko dan Allah baba d'ahara?! please nida sa'a zaki ce mata zamu je"
kama baki baba d'ahara tai tace
"o'oni yaran zamani, to kenan ina kukai niyyar zuwa inda ba wajen bikin zeena d'in kuka yanki

tikitin nufa ba?
murya qasa qasa heendu tace "kin gane ko baba d'ahara wlh kuwa partyn wata class mate dinmu zamuje gobe ne ake yinsa nasan kuma inna cewa mama partyn wata ne zamuje zata hanani zuwa ne shiyasa nazo na had'a wannan planing din kinji ko baba d'ahara, dan Allah ki taimaka mana kada kisa muji kunyar qawar nan tamu kuma wlh tayi masifar yarda damu a matsayin big friends nata"
baba d'ahara tace "manyan abokai na shegantaka ko na yan bokon zamani?'
heendu tace "Wayyo baba d'ahara kada kice haka man please zakije dai yanzun ko?
walle fa in baki jeba nima bazan fad'a miki plan da zan shirya gameda auranku da baba yawale mairan qarfe na ba inna gama tsarawa ba"
saida baba d'ahara ta hararetа sannan tace "to naji zanje amman saida dare inna gama tuyar nn fa, da sauri heendu tace "inda dai zakije ai babu matsala baba d'aharas ras ta"
nan ma baba d'ahara tace "amman fa akwai matsala hendo,,
cikin zaro idanuwa heendu tace "amman kuma wace iriyar matsala kuma?!
kan baba d'ahara tace wani abu saiga sa'a ta shigo gidan tace "hmn ai daman nasan heendu ki na nan inda kince mun yatafi, naje gida mama tacemun baki shigo ba shiyasa nayo nan"
heendu ta jawo hannun sa'a tace "ke dalla yimana shiru cakwai-kwaiwa bari kiji... nan ta fad'a mata yanda sukai da baba d'ahara yanzun gameda zuwa fatin hapsat.
itama sa'a cikin d'an tsoro2 tace"tofa baba d'ahara wace matsala kuma dai? Baccin muna kuma murna komi ya tafi yanda aka tsara? "
heendu tace"nima dai shi nagani ai"
baba d'ahara saida ta kwashe q'ulinta
tasake zuba wata tunkuzar amai sannan tace "matsalar itace ni ba gobe zan dawo ba sai gata inda dai mu zamuyi hidimar abuncin bikin can gidansu amaryar kunga dawowar mu tare daku zaisha ban ban knn ko?
sauke ajiyar zuciya heendu tai tace"kai ni wlh harkin tsorata ni baba d'ahara, to ai indai haka ne mu munji dad'i kunga bamu ba zullumin ko zaki rigamu dawowa gida a goben bare har mama ta tambayeki mu ina muka tsaya koko sa'a?!"
sa'a tace "wlh kuwa kedai q'awas dan inaga bawai da wuri za'a gama fartyn nan bama"
baba d'ahara ta coge baki tace"ah to wannan kuma ya rage ruwanku, nanta juya taci gaba da tsame qulinta, qarshedai basu baro gidanba saida suka ci zogale da quli wnda baba d'ahara d'in take siyarwar a alakoro kamar ynda suka saba dud in sunzo sunyi Sa'ar tayi san.
daga nan kuma gidan kaka jameela heendu suka nufa wato mamar mama zainab knn, suna wucewa kuwa ta majalissar su haruna mai cemist kuwa nan samarin wajen sukace"mun gaisheda heendu beuty haru na samu miqo miki gaisuwa" ko kulasu bataiba taja tsoki tareda fuzgo hannun sa'a sukai gaba.
isa kabeer ne yace "kai abokina mutuniyar taka fa ta qara cika full wlh, gashi dreesing na matuqar kar6arta koya tasa abu sai ya haskata, face dinta ta qara wani masifar kyau fa billaheel azeem fiye da randa ma tazo nan da bbnta dreesing"
haru yace "hmm kaidai bari abokina na gari ba kmr wannan d'an iskan ba, yayi mgnr yana hararar Hari's
sannan yaci gaba da cewa "yanda kasan hawainiya kullum kyaunta qara rikid'ewa yake, kai insha Allah fa dl babyn nan rabona ce saidai baqinciki ya kashe ka Hari's wlh" cewar haruna.

kecewa da dariya Hari's d'in ya dubi haru daya dinga bin heendu da kallo harta qule daga inda yake hango ta.
Yace"har gobe wlh haru bazan daina baka shawarar ka rabu da heendu beuty ba dan yarinyar klr mnya ce fa masu nera d'ubge a hannu"
matasan suka d'au ihu yayinda haru yace"mugu maq'etaci d'an baqinciki kawai"
kan wannan dramar daine suka maida hankali a majalissar haruna mai chemist.
lokacin dawowar heendu baiba amman kakarta jameela ta hirgad'osu gida sakamakon addabarta da sukai shikuwa mlm zayyanu dariya kawai yake musu yakance "ato bamai jinku jika da kaka nn bada jimawa ba za'a ga kun d'inke kuna qus qus ay"
a hnya ne heendu tace "bazamu je gidn baba yawale ba ynda ake kiran sllr nan nasan yana cen limanci masallaci, sa'a tace aikuwa kema kin sani ai"
da sauri heendu tace"wayyo nayi mantuwa sa'a " sa'a tace mntuwar mi?
heendu tace"dazun musaddiq yamim kyautar waya na mntota gidan baba d'ahara zo muje,,nan kuwa suka isa gidn tana nn kuwa inda ta barta sa'a ana bud'e wayar tayi wani qarar farinciki tace"wawoooo wlh ipone ce kumsa babbar ma kuwa,kai naji dadi fa wlh qawata wayar nn tazo a sa'a zamuyi babu da ita gobe"
shiyasa ma nakarba ai danmu qara bada kala ai a wajen kinsan mu bammason harkar qaranta a waje.
tafawa sukai dariya nn sukaita santin wayar suna faman tattabata har suka baro gidan baba d'ahara bata gama salla ba dayake jam'in su baba yawale take bi anaji sosai ta loud speaker d'in.
suna fotowa kowa ya nufi gidnsu, heendu tana shiga ta iske mama na salla itada maman salis dayake babban tabarmar nn ce tasu shimfide a tsakar gida sai suka daura sallaya akai.
dayake tasan tana fashin salla shiyasa tai wucewarta d'aki ta fad'a bisa babban katifarta dake qasa bayan cillar da gyalenta datai can gefen katifar tata ta shige cikin bargonta tana lallatsa wayar cikin jin dad'i,
acan waje mama zainab bayan sun gama sallar ne maman salis datafara mnyanta tace"ina wuninmu zainabu na shigo na iske anata salla ba'a gaisaba, shine nima nace bari kiga da zaman nan d znyi kn kigama salla gwara nima nayi "
mama zainab tace "lpia lau Alhamdulillah mama, aikam dai qwamma dakikai sllr kinhuta inkinje gida,
nan maman salis tace "dazun naje wajen maman taki Jameela saima take cemun mai gidan naki yasamu rauni mafarin knn nazo na masa ya jiki, to cikin ikon Allah ma sai muka had'u dashi ynzun bada jimawa harma yake cemun daga nan gida ya fito, to shine nai masa ya qafan kuma Alhamdulilla naga qafar ma ta samu lpia mafarin knn nace inda na shigo aibana wuce ba, Shine na shigo danmu gaisa"
cikin fara'a mama zainab tace "amman mungode sosai mama" mamn salis tace "bari to natashi natafi inda mun gaisa kn akira sllr isha'e kuma q'wamma mu koma gida muyita acan"
cikin murmushi mama zainab tace "hakane, amman mama wai ina yaya salis ne rabon dana gnsa tunkan bikin aurenmu fa shekaru da yawa"
maman salis tace "Allah sarki ai tunda q'anena ya d'aukesa aiki inda ya samo masa tofa can yariqesa hannunsa dud yawan shekarun nan kuwa harma ya aura masa yarsa yanzun haka yaransa biyu babban shine musbahu mai shekara 21 sai qaramar mace ce aminatu yar kimanin

shekaru 16 amman dayake aikin nasu kwata kwata ba hutu ba koda yaushe yake zuwa nn ba, dan zuwnsa na farko kwansa biyu lokacin da mukhtar suka tafi mecca to aikin nasu kuma danaga ana samun matsala in zakai tafia shine nace yayi zmnsa ni inna samu lokaci zan dinga zuwa dubasa inda yana mana aiken kayan buqatu na rayuwa kuma yace suna waya da mukhtar kullum, to yanzun dai zancen nan ma da nike miki ana shirin yi masa transper ne zuwa nan garin cikin 'yan watannin nan"
cikin fara'a mama zainab tasake cewa"za'a dawo knn yaya salis Masha AllAh, AllAh shi taimaka kuma mama, "aminn" cewar maman salis sannan ta qara cewa"ina saran insha Allah in salis ya dawo zaiyi qoqarin ganin ya shawo kan alhj mukhtar naku daga baqin qullin da matarsa tai masa, dan abun yai yawa"
cikin sanyin jiki kuma mama zainab tace "'to shiknn mama AllAh shi shi yarda haka akeso ay" maman salis na fita heendu ta fito ta kwantar da kanta a cinyar mama zainab tareda cewa"mama kinga musaddiq ya min kyautar waya d'azun "
mama tace"kingode kam, amman tun d'azun ina kika shige ne tun marece badai kuna tareda shi ba?
mama zainab tai mata tambayar tana mai tsattsareta da idanunta.
da sauri heendu tace "mama a'a wlh bamma tare dashi, baima jimaba ya tafi mu kuma nida sa'a muka shiga gidan baba d'ahara mukai mata yini sannan daga nn kuma mukaje wajen kaka jmcy" sauke ajiyar zuciya mama zainab tai tace "barkanki nazata kuna tare dashi ne har tsawon wnn lokaci ay dasai ranki ya 6aci, sannan kuma ban hanaki cewa mamata jamcy ba? dariya heendu ta qyalqyace da ita sannan tace "afuwan mama na"
ture kanta mama zainab tai daga cinyar ta tana shirin magana saiga baba d'ahara ta shigo gidan da sallama.
mama zainab ta amsa heendu kuwa da gudu taje ta rungume baba d'ahara kamar gaske take cewa "oyoyo baba d'ahara ta Oyoyo oyoyonki"
baba d'ahara tace"nikam 'yar nan sakeni kada ki kada ni q'asa"
cikin murmushi mama zainab tace "Gskiar ki baba d'ahara"
heendu kuwa aka tsinano lips wai tayi fushi an dizga ta mafarin knn tai komawar ta d'aki bayan ta faki idon mama zainab taiwa baba d'ahara signal kan tayi tayi mgnr data kawota.
dan haka bayan sun qara gaisawa nan baba d'ahara taiwa mama zainab bayanin bikin da zataje dasu heenduh gobe, mama zainab tace"baba d'ahara ai basai ma kin zo da knki kin gayamun ba ke mai iko ce akan heendu dan haka babu komi wlh Allah basu zaman lpia amaren" baba d'ahara tace "to to amin amin zainabu ngd da girmamanin nan da kike " mama zainab tace "babu komi ai baba d'ahara zaman taren knn ay"babu jimawa baba d'ahara ta koma gida.
acan d'aki kuwa heendu juye juye kawai take bisa katifarta tana dariya q'asa q'asa tareda cewa"sai yanzun na qara tabbatar da cewa kina masifar qaunar baba yawale na baba d'ahara ta"
lumshe idanu tai jin ynda cikinta ke kuka gashi kuma kwad'on tuwon ruwa taga anyi a gidan nasu, baccin dai batason sake fita gudun kada maman tata ta tambayeta ina zata dataje gidan babanta mukhtar ta samo koda goran yhugurt ne kuwa, dole dai ta haqura taci tuwon ruwan sannan ta kwanta barci wayarta na gefenta a ranta take cewa "yaudai mun rabu da wannan gwaramar wayar tawa munyi new designer ".

ahaka barci ya kwasheta.
washe gari da misalin biyar na marece heenduh ta shirya cikin doguwar rigar ta da hijab dinta taiwa mama sallamar tatafi dan baba d'ahara na jiransu alhalin baba d'ahara tun safe tai tafiyarta gidan bikinsu.
nan mama tai musu adawo lpia Allah tsare.
dan haka kai tsaye heendu tana fitowa daga gidan nasu gidansu sa'a ta nufa ta iske ba kowa sai Sa'ar, dan haka d'akin sa'a suka shige heendu tace "ina mama sa'a tje?"
sa'a tace "taje anguwa anmn lpia lau inda nai mata bayanin zamuje anguwa da baba d'ahara dan haka ta d'auki d'ayan mabud'in gdn tabar mun wannan anan"
heendu tace yana ganki da wannan zumbuleliyar hijab haka sa'a har qasa
cikin gida? badai baki shirya ba kuma dan Allah dai?
saida sa'a ta rufo gdn nasu sannan ta dawo tace "qawata komi saida kula ai yaza'ai nasanya iriyar wannan d'amammun kayan na zauna haka gida ai bazai yuyuba duba fa kiga? tayi maganar tareda cire hijab din jikinta, saiga kwalliyar sa'a ta inglesh wears ta fito dudda kayan basu kamata sosai ba amman kunyarsu takeji, tsoki heendu tai tareda cewa"ke wlh banza ce qawata yanzun wannan kayan da kika sanya miye wani abun qumuniya a ciki, sa'a tace "ke ai kin saba bakkyajin komi niko wlh tsoro gareni"hararta heenduh tai tace "kuma kinyi kyaun gske fa qawata bari nima dai nasa kayan nan naga yaza sumin ne, ina kayan suke ne nawa?
sa'a tace "shiga q'uryan d'aki suna nan bisa gado"
haka ko heendu ta wuce ta sanyo kayan ta fito ta tsaya gaban dogon glass mirrow na maman sa'a tana juye juye yayinda sa'a tayi mutuwar zaune wajen tana kallon yanda kayan sukai masifar mata kyau amman kuma batun d'ameta da sukai babu mgn dan dama roba ne kayan.
gadai wando har qasa pencil amman yabi jikinta lam6as sannan haka ma rigar ta fiddo mata shape din hips dinta da laq'umammen cikinta shafaffe sai daga sama mamanta sunyi masifar cika gidan bra din rigar, sai dai kuma stones din da suketa qyalli gaban rigar inda breast d'inta suke cike fam dam kamar zasu fito waje tsabar matseta da rigar tai baqaramin qawata rigar sukai ba. gabaki daya jikinta babu inda bayya rawa yanda ta kama kitson kanta ta maidoshi gefen wuyanta ba qaramin kyawu ta qara ba,
ga fuskar dama tasha kwalliya sai qyalli take, sa'a sam kasa mgn tai sai daqyar tasamu tace"wlh qawata kamar nai miki kuka dan tsabar kyaun da kikai, ni saina raina ma kaina kinsa na daina jin kunyar kayan ma danasa dan nawa musulmai ne akan naki arna"
ta6e lips dinta taiwa heendu tai tace "aini banjin komi gameda gayu qawata"
sa'a tace "amman ba haka zamu fita ba ko? Heendu kuwa ta zaro fararen idanun ta tace "ke rufa mana asiri mu mutu maza su kaimu tomu kam mahaukatan inane dahar zamu fita anguwar nan haka da take cike da sa'idinawa? After dressing zaki saka ko hijab in yaso ma cire in mun isa wajen"
sa'a tace"aho yanzun naji Batu ay"
nan heendu ta maida baqar doguwar rigar jallabiyarta saman kayan kamar dai yanda ta shigo, itama sa'a ta saka doguwar hijab dinta sannan suka d'auki jukkunansu suka kulle gidan suka tsaida napek suka shiga suka tafi.
sun dan jima sannan suka isa wajen da ake partyn, wani qaton waje ne an qawata sa bnda casu babu abunda kakeji na tashi wajen sannan kuma can gefe motoci ne na alfarma wanda samarin wajen suka zo dasu, heenduh sarkin son rawa harta fara taku a napek kuwa, daman

tun a napek suka cire kayan da suka daura akai tareda cusasu cikin jukkunnan suka zuge.
nan suka daura wani matacin gyalensu wanda 'yan matan kewa laq'abi da *'uryatin*
akai, wnda iyakarsa wuya nan sukai rolling dashi suka tasarwa shiga hall din suna taku d'ai d'ai suka samu waje gefen amarya inda shauran class mates dinsu suke suka zauna tareda sauran qawayen amaryar kowace naji da knta wajen,saidai kuma heendu abinda ta tsana ai mata wato kallo shi samarin wajen kuwa suka tasata dashi harta fara tunanin barin wajen amman da aka saki wani kidan sai tsintar knta tayi a filin rawar tana riqe da sa'a suke takawa cikin yangarsu ta mata isassu. kan kace mi tuni aka fara musu ruwan liqe fiyeda sauran matan dake wajen tuni wajen ya dauki tafi raf raf harda amarya da ango kuwa saida suka tafawa salon heendu,, saida heendu ta gaji sannan dan knta ta koma mazauninta yayinda kowane saurayi keson mata mgn amman ganun basu samu damar yin hkn bane daga fuskarta yasasu kallon nesa nesa da ita dan su azatonsu yar mnya ce ko gidan sarauta yanayin takunta da shan qamshinta,
mamaki ne ko al'ajabi koko idanunsa ne suke masa gizon itace koko mai kama da itace a kalar wannan wajen?? tambayar da doctor khaleepa kewa kansa knn tun lokacin da su heendu suka shigo hall din nan itada sa'a, bai qara tsinkewa da itacen bane saida yaga yanda take juyin rawa in slowly, yayi matuqar mamakin miya kawo ta nan bikin friend dinsa ashir kabeer?
duban inda yake zaune yai can qarshen chairs ya zauna sakamakon alfarmar daya nema daga abokin nasa na cewa nan zai zauna saboda hatsaniyar wurin tabbas yasan zata haifar masa da ciwon kai, shi sam iriyar wannan wuraren ba zuwansu yake ba, danshi baida son ma hayaniya at all a rayuwar sa, sanin halinsa yasa Ango ashir amincewa daya koma bayan ya zauna kamar yanda ya keso dudda yaso ya zauna kusa dashi din kamar yanda aka tsarawa manyan abokan ango da na amarya. wani murmushin takaici ya saki ganin kalar kayan data sa har tazo cikin wannan qattin tana gwatse gwatse, shin mama tasan da hakan kuwa? tambayar dayaiwa zuciyar sa knn, lumshe idanuwa yayi bayan ya cire farin medical glass dinsu na likitoci tareda sake jawo preesing cap dinsa gaba ya rufe rabin fuskarsa, tun zmnsa awajen yayi hakan gudun shawagin 'yan mata a kansa shiyasa ya rufe rabin fuskar tasa daga kishin giden da yake,
kur6ar juice d'inda ke hannunsa yayi bayan ya dubi agogon hannunsa yaga duhu ya fara, dan tsoki yaja tareda qara watsa idanunsa gunda heendu suke zaune, sake d'auke fuskarsa yayi danji yai gaba daya zaman wajen ya ishesa shiyasa kai tsaye ya miqe tsaye tareda komawa cikin motarsa bai tintec glass ya kwanta tareda kunna ac sbd zafin dayaji na ratsa sa,
ganin kiran ashir kabeer ango, saida yad'an motsa sannan ya zaro wayar daga jeans d'insa sannan ya d'aga tunkan yace wani abu ashir yace "haba *likitan mata* yaya ana tsaka da friends event kuma zaka fita ina kallon kafa, snn ga kuma manyan babies cike a wuri please man ka dawo ka bayyana musu kanka nasan dole ladies su girgiza in sunsan da kalar ku wajen nan dan AllAh ka dawo man"saida ya muskuta tareda saka ear pies a kunnen sa yace "no ashir bazan iya zama wajen nan ba amman nai maka alq'awalin ina cikin wajen nan har sai an tashi partyn nan sannan znwuce ok? dole ashir ya haqura badon yaso ba sanin dayai cewa indai khaleepan yai mgn babu canjawa bare qarya a cikinta.
haka waje ya cigaba da, kasancewa har wajen qarfe tara sannnan aka tashi, nn samari suka fara daukar yan matan suna wucewa dasu gidajensu.
qwarai sa'a tai mamakin badai tafiya heendu taifa ta barta ba? dan daman tun dazun take zanzamin su tafi kada mama tai fad'a gashi har goma na shirin idawa.
taji haushi kam ynda har tatafi ta barta gashi kuma tabar mata jikku nansu a hannunta. "badai

haka ta koma gida ba da kayan jikin nata ba? tambayar da sa'a taiwa knta knn a mamakance.
yanzun kam ta tabbas cewa kam heenduh ta wuce abinta kuma ganin saura ita d'ai ya rage tsaye bata shiga motocin da 'yan matan keta shiga ba suna tafiya a wajen yasata shiga itama suka tafi nan kuwa waje ya koma ba kowa kamar ba'a ta6a taron jama'a wajen ba kuwa, gashi hasken gun ma ba wani wadatacce ba ne sosai.
su sa'a basufi minti biyar ba da barin wajen saiga heendu ta 6ullo ta wani d'an lambu hannunta riqe da mango dayake tana matuqar son mangwaro shiyasa tana ganin dj din wajen ya gama bayanin komi angama har an fara shirin daukar mutane ma.
mafarin knn taje tsinkosa ganin ynda yayo qasa qasa alamum basai tasha wahalar curo wa ba, dan ita harga Allah sam tama mnta da an fara tafiya shiyasa ta zauna nan taita shan mangwaro wajen guda uku manya manya,
tana gamawa ne taje wajen famfo ta wanke hannunta tareda qara tsunko d'aya ta ruq'osa a hannunta tareda nufin kaiwa mamanta itama.
wayam taga wajen tuni ko tsoro ya baibayeta ta dora hannunta a knta tareda cewa "wayyoni heenduh na shiga ukku na"!!!
abinka gamai saurin kuka tuni idanunta suka fara kawo ruwa ganin koda nan ma knta isa titi ba qaramin nesa ne da wajen ba.
kife kanta tai a cinyoyin ta tana tsinewa sa'a a ckn zuciyar ta na tafiyar mata da kaya datai a jakkarta, yanzun haka zata doshi hnya har gida da wannan shigar kamar 'yar good evening sai kace wata karuwa? tunanin da take a ranta knn, jin haushin kare ne data jiyo a wani wari nn kurkusa yasata zabura ta miqe taresa barin wajen cikin sauri 2 gudu 2 tana waiwaye gabnta na dakuwa da qarfi na tsabar tsoro.
hango mutum da rayi ya nufi mota hannunsa dauke da wani abu ya saka bayan motar dake kusa dashi ga alama motar tasa ce kuma tafiya zaiyi shima.
dudda bataga fuskarsa ba amnan da gudu ta isa wajen, (doctor khaleepa ne ya samu wani haraban tsaftacaccen guri tun bayan da aka kira sllr magrib bai baro wajen ba saida yai isha'e yana nn zaune saida yaji kidan ya rage sann ya nado abun sallar tasa ya tafo, yayi mamakin ynda yaga har an tashi duba wayarsa yayi da ake kira tun lokcn d yake sllr saiyaga har 12 missed cull daga ashir 3 kuma daga momynsa sai 2 daga yunus, bai maida reply na kiran ba ya nufi motar kawai tareda saka pray mate din a set back), yana qoqarin shiga motar ne yaji murya a bayansa ta mace tana cewa "mlm dan AllAh ka taimaka ka kaini gd wlg bn samu abun haw..... tuni heenduh ta kasa qarasa mgnr tata ganin wnda batai mamaki ba awajen ne, wani dad'i taji ya ziyarceta har tana sauke ajiyar zuciya na ganin komi ya zo mata cikin sauqi,
cikin murna tace "laaa doctor kaine nan daman.... shiru tai ganin wani mugun kallo na qyama da tsana da yake wurgo mata,, ita ba abun tace zata rama ba tai masa rashin kunya ba yaqi daukarta dole ne ta kwantar dakai kota samu ya temaka matan,
jitai yace "Allah ya sawaqa da in d'auki qazanta najasa kamarki a cikin motata, saidai ki kwana anan inhar kuwa saina d'aukeki marar kunyar qarya kawai mai watsi da tarbiyar iyaye"
Qwarai ranta inyai dubu toya baci amman babu ynda zatayi tanaji tana gani ya dinga daddatsa mata munanan magan
ganu masu zafin gaske amman kuma tayi shiru fuskarta na kallonsa tasa idanunta na tsiyayar da qwalla gwanin tausayi, dan tuni bakin masifar nata ya mutu dud tsoro ya baibayeta wajen, tabbas yau tasan khaleepa bai sonta yanzun ganin datai yana shirin shiga motarsa ya barta

wajen aiko da gudu cikin kuka ta aza qirjinta saman bayansa ta had'esu gam gam tareda q'amqamesa tana gunjin kuka tace
"wlh doctor ko zaka kasheni bazan bari ka tafi ka barni wajen nan ba saidai komi zaka mun kamun shi nina d'aukarwa raina shi yanzun nan"!!!
tayi maganar tana qara cuccusa kanta da jikinta a bayansa hannuwanta zagaye saman cikinsa duka, hawaye sun mata kaca kaca a fuska jikinta ko ina rawa yake kamar zata katse takeji a lokacin kuwa,,.....,

By
Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🥡🥡
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️🥡👁️
🅿2️⃣8️⃣
"W Ih doctor kozaka kasheni bazan bari ka tafi ka ka barni wajen nan ba saidai komi zaka mun kamun na d'aukarwa raina shi yanzun nan"!!!.
tayi maganar tareda qara cuccusa kanta da jikinta a bayansa hannuwanta zagaye saman cikinsa duka, hawaye sun mata kaca kaca a fuska jikinta ko'ina rawa take kamar zata tsinke a lokacin take ji kuwa,
cikin 6acin rai da haushinta yasa q'arfi ya wancakalar da ita gefe' wannan karon har sadda heenduh ta fad'i q'asan wajen kuwa.
a zuciye ya nunata da yatsa yace
"nace mini bazan yi dakon najasa ba a cikin motana ba, domin ke najasa CE kinje kin gama gwamatsuwa da maza cikin wajen can kina raye raye da gwatse gwatse sannan Dan kin maisheni kamar me har zaki wani CE na kaiki gida ko no bawanki?,OK daman nine na kawo ki nan d'in ay ko?!"

shiru tai saidai ajiyar zuciya take saki tana tsine masa a cikin zuciyarta dan zugin zafin faduwar datai ba qaramin zafi taji wajen na mata ba,
jitai yace
"ina mai tabbar miki da cewa headache saidai ki shekara a wajen nan inhar saina daukeki kuwa kokuma kikira 'Yan iskan samarin naki su kaiki gida su, sannan kuma ki San da Sanin cewa saina fad'awa su mama inda na ganki da abinda ya kawoki nan Dan inada tabbacin cewa kin yaudareta ne batasan nan kikazo nuna tsiraici ba da wannan q'azan
tattun kayan na jikin kiba wnda yasu ya babu did daya"!!!
yayi maganar ransa a dagule.
kantace wani Abu taji saukar plasher ta photo ya d'auketa foto, har gabanta ya matso tareda rusunowa ya zuqunna saman q'afafunsa yace"kings wannan foton zai zamar mun cikakkar sheda na nunawa wasu mama da small dad Inda na baro ki yanzu hakan, dan daga nan ina mai sake tabbatar miki street can nayi wajensu, dan su tabbatar da yanda kike son 6ata mana family namu kinga sai kisan amsar da zaki basu wacce zata doke q'wararan hujjoji na zan basu OK?"
daga haka ya miq'e yafara takunsa na qasaita ya doshi motarsa da niyar barin wajen aiko da Sauri ta miq'e tsaye da gudu ta sha gabansa batai wata wata ba ta fad'a saman mayalwacin wadataccen q'irjinsa ta rungumesa gam gam tana fidda numfshi mai kama da haki tana cewa cikin rawar murya wacce keson sake sakin kuka "haba doctor kaifa d'an ...d'an u....uwa nane dan Allah ka da katafi ka barni nan wjn wlh bazan q'ara maka rashin kunya ba" tayi maganar hawaye na sulalo mata a saman cck nata.
yaso ya d'anji tausayinta kuma ganin yanda jikinta ke rawa ga alama a matuqar rud'e take muraran, kuka kawai taketa sakar mas@ tana sake fad'in"wlh inka gayama mama haka fushi zatai dani w@nda zan gwammace ma ta dokeni akan fushinta" cikin takaici ya zuba idanunsa a saman gashin kanta da gyalen ya zame yace"OK kinsan da Fushin nata Amman kikai mata zamba cikin aminci kikazo Inda bat@ yarda ba saboda ke tsabar kanki na miki rawa ke gaki a babbar makarantar high
instution ko? kun waye boko na muku ranwa akai kuna yanda kukeso ko musamman make da kika raina mutane ko?!" runtse idanunta tai tareda qara nutsewa jikinsa qanqame dashi daqyar tace"wlh a'a na daina kaji doctor dan Allah ka rufan asiri kada su mama susan inda muka je da sa'a,
Allah amaryar CE classmate dinmu shiyasa kagan mu wajen munzo!"
tsoki yaja yana mai kauda fuskarsa a kan tata, dud duniyar nan babu wacce ke sasa doguwar magana batareda ya ankara ba inba wannan masifaffiyar yarinyar ba mai basa ciwon kai.
jikinsa yaji keson canza masa jin yanda tudun Brest d'in nan nata suka tokare masa a qirjinsa duba da yanda tai mugun qwaqumesa da qyar yasamu qarfin gwiwar janyeta a jikinsa tareda bude back set ya cillata ta gameda rufewa da remot key din motar shima ya Shiga ya tada motar suka bar wajen ko kallonta bai sake yiba ma dan jiyake ta ida cinye masa maganarsa ta daren ranar,,
har a ransa bai iya cewa ga daliiin sa na tausaya matan dayai daga qarshe dai ne zuciyarsa ke cewa"ka taimaka mata ne saboda mutuncin iyayen ta da kuma gudun abunda zai faru ga 'yar tasu inka barota wajen daba amintacce ba.
itako har gwalo ta dunga yi masa ta baya batareda ya kula ba.

gatsine tai tareda cewa a ranta"hmmm dani kake zancen zakasan ka wulaqanta ni Allah kuwa. dai dai qofar gidansu heendun doctor khaleepan ya tsaya batareda ya juyo ba yace "saiki samu damar fitarmin daga mota ko?!
kallon jikinta tai a marairaice ta dubesa tace"'Doctor dan Uwa na bazan iya fita haka ba waje Dan Allah kasa mamin abunda zan rufe kayan nan na jiki na kaji kada mm ta ganni hakan da babana?"
a hasale ya juyo yace "waike dabbar inace dazaki ta matsawa rayuwa tane?,kin nemi temako nai miki kuma bazan qara mini wani ba Dan haka ki ficemun a mota tunkan na fitar dake da kaina Inda bani na saki saka kayan ba bare kiji nauyin fita dasu, OK ai ni sai yauma nasan kinsan wani abu kunya?hmm, gskia nai mamaki kuma fa,mtsss qaryar banza mane kike ashe? nazata zaki iya karad'e garin kaduna da kalar wannan shigar a yanda kika d'uki kan nan naki da mugun girma?".
heenduh dai sai mutsu mutsu take da baki tana son mas tsiwa amman kuma tana tsoron kada ya fitarda ita daga motar,, wata tsawa dataji ya daka mata tareda qara mata nuni data fitar masa a mota dan yagaji da jinta tareda shi magan ganunta na 6ata masa rai, aiko da sauri batasan sand@ ta fice daga mortar ba Inda daman tuni ya bud'e qofofin mortar tun tsayawarsu wajen, yana qoqarin fitowa daga motar shima aiko saiji yayi tayi wata doguwar sukuwa ta dawo zuwa jikinsa tareda fuzgo mirfin motar ta rufe da qarfi jikinta na rawa kab! kab! kab! dan kuwa baba Isma'il ne ta hango yana nufowa nan wajen hannunsa riqe da buhun sa ga alama yataso daga mazauninsu na firan dare, ta tabbata kuwa yanzu qarfe goma na dare yayi dan lokacin ne suke tasowa daga fira shida abokansa.
a hasale ya ingejeta jikinsa zuwa d'ayan set din dake kusa dashi tareda watsa mata kallon banza tareda cewa
"headache wai ke
iskancin miye wannan bazaki tafi bane ki q'yaleni ko saina....jin ana q'yanqyasa masu motar tasa ne ya
sashi yun q'urin bud'ewa aiko tai wuff ta kamo hannuwansa ra riqe qam a qirjinta wnn karan tsoronta muraran ne take cewa"wayyo doctor kada ka bud'e wlh babane inaga Allah shine kada kai mgn mai qarfi zaiji ne"!!
wani banzan kallo yake mata sheqeqe yace "hmmn kinga abu yazo mun a sa'a inda kinq'i barin nan bari nai masa bayanin komi in
yaso saiya shigar dake gidan da kansa inda kinqi shiga ke" ganin da gaske yake danhar ya kama murfun motar zai fita tareda bude muryansa da d'an qarfi yace baba gata....habawa aiko bata bari ya ida maganarsa ba na tona mata asiri tayi wuff ta cimamiyo ta juyo fuskarsa a tata da hannayenta tareda had'e bakinta da nasa waje day'a ta kama lips d'insa ta matse gammm cikin nata tayi hakan ne dan kawai ta tsaidasa daga maganar tasa.
tuni jikinsa yaji ya saki ya kasa koda motsi jin yanda wasu tausasan lips d'inta keta matsar masa nasa a hankali kamar Wanda ake sosawa wasu.
kuma still ba'a daina qwanqwasa motar ba jin datai wayarsa ta dauki qara yana shirin fiddowa a aljihunsa aiko ta qara qaimi wajen matse lips dinsa tareda danne masw hannuwansa dake wajen,,, banda shaqar numfashin juna da jin kalar taushin lips din junansu bassa komi a wajen.
harma sun manta abinda yajaza musu yin hakan kuwa.
sun dauki tsawon lokaci a hakan jin da heendu tai an tsagaita da qwanqwasa qofar motar ne

yasata jin hankalinta ya kwanta ta fara qoqarin zare pink lips dinta daga NASA taji abin yaqi yuyuwa kuwa.
zaro fararen idanuwanta tai waje jin yanda doctor khaleepa ke ma lips dinta wani kalar tsotsa mai masifar dadin gaske da tafiyarda hankalin kowace lafiyayyar mace kuwa.
gashi qamshin nan nasa dud yabi ya cika wajen, yunqurin amsar bakinta ta sakeyi daga wajensa Amman saima jidatai ya ida d'agota cancakat daga Inda take ya d'aurata saman tsakankanin cinyoyinsa yana cigaba da kamo fuskarta yana sucking lips dinta sosan gaske..
sai sakar wa juna numfashi suke mai d'umi har heendu ta fara jin wasu yanayiyyika daga doctor khaleepa din Wanda batasan ynda akai suka fara ratsa ko'ina na jikinta ba.
saida ya tsotse dukkanin wetlips din dake bakinta sannan ya maidata mazauninta suka zubawa juna idanu babu Wanda ya iya marmarin d'auke idanunsa daga kan na d'an uwansa dan kowa akwai abinda yake saqawa a zuciyarsa.
sunkai minti biyar a haka sannan lokaci daya suka harari juna tareda d'auke kai ata gefe gefe, jitai yace"daman haka kike sakarwa samarinki jiki Ashe headache?! Zaro idanunta waje tai turo baki tai tace
"wlh bntabayi bafa, daman Kaine fa kawai daga na rud'e na rufe b@kinmu dakai kuma... kuma shine kaki sakina,,, to..to k@i zancewa dai ko haka k@kewa 'yan matanka"!.
tayi maganar tareda sako wasu qwalla a gefen ido masu zafi Wanda batasan dalilin zubowar tasa ba.
zuba mata ido kawai yayi to kukan na miye? abinda ya tamvayi kansa knn,, kuma saiyaji dadin mgnr datai na cewa bata taba yin hkn da kowa ba yasan kuma sam su mama zainab basu horar da ita magana 2 ba, yasan hkn har iyakar gskiarta ne ta fada masa itan'
dahar zai tanka kuma komi ya tuna sai ya ta6e lips dinsa da suka qara jaaaa yana shirin maganar ne kuma yaji wayarsa ya sake ringing lokaci daya shida ita suka zurawa wayar ido ganin Wanda ke kira.
zarah CE tai kiran kallon juna sukai shida ita sai kawai yaga ta canza fyska tareda dauke kai gefe cikin wani jin haushin da batasan miya saba.
sarai ya kula da sauyawar tata Dan haka wani qasaitaccen
murmushi kawai yayi baice komi ba Dan kawai ya qara qular da heenduh din taji haushi kamar yanda yaga taji ga slama ynxun dudda baisan ma miyasa taji haushun ba shikuma yanada burin sata sakejin ba dad'i k@mar ynda take quntata masa itama lokutta da dama a magan ganunta.
dan haka snda yake qoqarin d'ag'@ kiran saiya katse baiyi wata wata ba ya kira ta tareda saka wayar hands free yace"yadai zarah ina jinki miya faru ne?
Zara dake tsaye gefen motarsa tun d'azun tace "haba Yaya khaleepa tun dazun fa danazo wucewa naga motarka nan nasan kuma kana ciki Inda naga an bud'e motar kuma an rufe lokacn shiyasa na tsaya na danna samu na gnka,wlh dud yau ban gnka ba harna gsji da zaryan zuwa gidan Ku Momy nace mun bakka nan....gskia nayi missing na ganun kyakkyawar fuskar yaya khaleepa na". tayi mgnr a d'an d'are2 dan batasan wacce amsan zata samu ba wataqil ma ya gwasaleta kamar ynda ya saba.
Amman kuma a mamakinta sai taji yace"ok kada ki damu yanzun zaki ganni zarah ganin idonki kuwa give me one mints".
wayyo har cikin ranta taji dadi sosai shiko baiyi wata wata ba ya bud'e motar saiko gata ta

sunkuyo knta tana murmushi.
suna yin arba da juna ko tsakanin heenduh da zarah nan fa kowa ya sakarwa kowa kallon banza dan daman ko school suka had'u babu wnda ke tankawa kowa bare uwa uba nan ckn anguwar tasu.
ita zarah gani take tawuce tankawa kowane talakkan mutum kuma gni tk yawan shigar khaleepa gidansu heendu din yanda taga yarinyar da shegen kyau nan kada yace yana sonta barema tasan 'yan uwa ne su na jini ma, saidai Inda taji dadi kuwa tasan babu ynda za'ayi iyayensu su bari suyi aure duba da yanda ko kadan iyayen khaleepa bason na heendu din suke ba dudda kuwa tasan baban sa wane ga baban heendun.
ita kuma kallon da heendu kewa zarah shine na karuwa ballagaza zahiri duba da ynda take qazamtacciyar tarayya da samarin banza kala kala kawai shiyasa batai mata ba tana tunanin ma bata rasa shaye shaye.
Amman da yake kowa tasan knta sai suka doje kowa ya dauke kansa.
Zarah tace "hala kunje anguwa ne and your sister Yaya khaleepa?
da "em" kawai ya bata amsa tareda cewar INA kikaje ne ke da Daren nan?
tace "momy na ta Aiken can shagon na siyo mata credit, cikin ko'in kula yace "OK kije to ma had'u gobe" yayi mgnr fuskarsa babu alamun wasa dan yasan zata iya taita tsayuwa wajen.
aiko ta juya knn yace"d'an tsaya man' da sauri ko ts dawo tace "to'' saida ya sake duban ta sama da qasa sannan yace "kozaki aramun after-dress din jikinki nanda 12
hours na maido miki?
Cikin mmki ta dubesa da tunanin miye zaida afterdrees shida ke namiji?. Ganin dayai ta tsaya ne yasashi cewa "ok in kuma kina ganin akwai takura jeki abinki barshi"
da sauri race "a'a wlh gashi tayi mgnr tareda cirowa ta miqo masa taqara da cewa dmn dady ne ya matsa mun saina sata samn kayan jikina shiyasa"
amsa yayi tareda cewa"OhK kije kawai zan kawo miki gobe" tafiya tai tana jin dadin yau sunyi mgn mai dadi da khaleepa.
Cillawa heendu rigar yai ya fita daga motar tasa snn ta fito tai masa kallon Sama da qasa a hararance snn tai shigewarta gida.
mama Zainab ta iske tsakar gida takasa zaune sai zirga zirga take yayinda baba Ismail ke cewa "ki kwantar d hnkalinki zainabu inda dai kince sa'a tace sun tafo suma..dai dai nan ta qaraso gidan sai rave rave take cikin Bacin rai mama zainab ta watsa mata kallo tace"kin kyauta mun knn heendu?! zakije ki kashe dare waje?
tun abun marece fa? koko biki hauka ne daga walima?
Tun d'azun fa sa'a tadawo nan gida, shiknn kin kyauta kuma kisani bazaki qara zuwa wani biki ba dan bazaki sa mucigaba da sab'awa Allan ba akan..shiru mama tai jin muryar khaleepa ya shigo gidan tareda cewa "ayi haquri mama tare muke da ita, ce ma nai ta bari mu gama sallaman baq'i abokanmu saina kawota Inda nima ina d'aya daga cikin abokan angon yayi maganar tareda satar kallon heendu data zuba masa idi cikin sauke ajiyar zuciya 6oyayya tareda tunanun rufa mata asirikan dayai tayi yau cikin mamakinsa, kaddai dmn yanada kirki? ta tambayi zuciyarta.
shiko ganin kallon da take masa ne yasashi watsa mata wani kalar kallo Wanda yasa jikinta qara yin sanyi sosai
gani tai ya ta6e baki tareda kauda fuskarsa can gefe...

By
Xexen Fasaha.
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁️📦👁️
🅿20
B aba Ismail' yace "af to shikenan Inda tare kuke babu laifi ay, matsalar dai itace ace an barota ita d'ai acan tana mace mai nauyi a knta kaga hakan bai kyautu ba ay"
khaleepa dai kamar yace wane nauyi ne akan ta? sai kuma dai yayi shiru daga bisani kuma ya miq'e tsaye yace" to shiknn mama natafi saida safenku small dad"
da "Allah tashemu lpia" suka amsa sannan yabi ta gefen inda heenduh ke tsaye har lokacin ya wuce bayan ya d'an matse mata yatsan hannunta guda d'aya da remot keys din sa na mota da gangan kuma"
da harara tabisa tana juyowa kuwa suka had'a ido da mama Zainab, tai saurin sadda kanta q'asa kuwa tana murza yatsan nata daya matse matan tana cije lips d'inta dan kuwa taji zafi.
jitai mama Zainab tace "wannan after drees d'in naga ai bada ita kika fita ba a ina kika samo ta? gaban heenduh yai wata kalar muguwar fad'uwa dan tasan maman tata dasa ido akan dud wani abu daya shafeta na sutura tata koba tata bama, da wasu ma abubuwan muhimmai.
dan haka da Sauri tace "eh..ehm.emm mama acan ne wata Friend d'ina ta ari tawa wai tafison mai kauri shine ni tabani wannan na saka kuma da muka tashi tafowa ban ganta ba amman gobe yaya khaleepa zai kai mata inda qanwar abokin sane ita"!
tayi maganar tana sosa kai gabanta na qara wani tsananta fad'uwa tana kuma roq'on Allah dayasa mama ta yarda da tsarin maganar tata dan tasan maman tata kamar kotu take saida shar'ia filla-filla kuwa ake wanyewa da ita ko.
jitai mama tace
"ahoo shine ke gaki marar ta ido sai kika amshi rigar dud tabi ta kama miki jiki kika Santa ta

hakan ko?
wai yaushe zakiyi hankali ne heenduh dan Allah kuwa?.
baba Ismail yace
"keko zainabu inda dai tabaki uzurinta shikenan ay kuma magana ta wuce ko?"
yayi maganar a d'an fara'ance.
hararta sosai
mama zainab tayi ganin ynda heenduh d'in keta sunne sunne kamar marar gskia hkn yasa tace.
"in kinga dama sai kiyita tsayuwa anan kada kije d'akin naki inda dasaki akai nan wajen da kika kafe ay"
cewar mama Zainab d'in.
tana gama fad'a mata hakan kuwa tai wucewarta d'aki.
wni murmushi baba Ismail yayi yace "zonan wuce d'akin ki heenduh na rabu da maman nan naki mai jiran kiyi laifi ta baibayemun ke, jeki d'akin ki Allah shi miki albarka kinji ko 'yata" cikin jin dad'i tace "ameen baba na mai sona"
ahaka ya wuce yabi bayan mama Zainab' itama ta shige d'akin nata.
tana shiga d'akin
tayi sukuwa saman katifarta cikin jin dad'i ta kwanta tana mai sauke ajiyar zuciya.
da sauri kuma ta miq'e ta turo d'akin nata tareda saka sararaf ta dawo ta cire afterdrees din jikinta da inglesh
wears din nan ta jawo rigar barcinta ta zura tai saurin lunke q'ananun kayan ta 6oyesu cikin kayanta ta koma ta kwanta bisa katifar idanu a rufe sai faman sauke ajiyar zuciya take.
yau kam ta zagi sa'a zagin dama batasan iyakarsa ba, dan a ganinta da bata tafi ta barta wajen ba da dud wannan dabaibayin bai sameta ba yau.
gashi wayarta na cikin jikkarta wacce ke wajen sa'a da saita kirata ta qara zazzageta kotaji sauqin fushinta a kanta.
sosai ta rintse ido dajin jikinta na mata wani iriyar kalar abu yamm! yamm! yem! said kuma jitai jikin nata ya saki hakan kuma dud ya faru ne sakamakon tuno abinda ya faru tsakaninta da wannan d'an girman kan doctor.
a hankali ta saka hannunta tana ta6a le6unan nata tareda miqewa zaune ta dauki madubi ta kalli fuskarta dayake a kwai NEPA aiko nan taga pinks din lips dinta sun koma jawur sabida mugunyar tsotsar dayai musu ta gaba da mugunta ma.
komawa tai ta kwanta tareda jawo filo ta rungume sa tsam cikin qirjinta kamar yanda tasaba, sosai ta lumshe idanunta bazata ce bataji dadin hakan ba dayai matan ba kuma gashi koyaya tai mgn sai qamshin turarensa ya fito cikin bakinta' kazalika dudda ta cire kayan jikinta tofa koyata motsa jikinta qamshinsa ne ke addabar rayuwarta' amman yanda lips dinta taji Sina mata tsu! tsu! na dan zafin matsar da yai musu dole ta dinga furta "Allah kuwa ya isarmun mugu d'an iska yai ta wani tsotsar wa mutane baki kamar maye😒."
tayi maganar kamar zatai kuka.
haka taita juye juye da tunanun abun har barci ya dauketa batareda ta nemi abincin data so ci ba dudda yunwar da takeji tana katsarta kuwa sama sama amman ta kasa ma tashi sam.
haka wanshekare ta tashi cikeda tunanin mafarkan da taitayi gameda doctor' sosai jikinta ya qara mutuwa murus dud inta tuno yanda ya dinga yi mata a mafarkan nata, ta tabbata da'ace ba halin rashin tsarki take ba babu abinda zai hanata yin wnka.

zaune take yanzun hakan a gefen katifarta da handout ahannunta tana son duba wani abu amn taiwan qofa zuru kamar wacce ke tunanin shugowar wasu.
ko kalaci ma batai ba dudda mama ta kawo mata natan kuwa.
muryar sa'a taji a tsakar gida tana gaida mama babu jimawa kuwa saiga shi ta shigo dakin.
zama sa'a tai gefen heenduh riqeda baki cikin mamaki tace "heendu beauty wagga hararar fa da kike mun fa ta miye kuma to?
baccin ma nice ma ya cancanci dana miki ita dan kuturun wulaq'anci har jia zaki tafi ki barni sake da baki saidai shafawa nai naga baki wajen partyn nan tomiye yafi wannan wulaqanci nikega munje tare kin baroni wato ni marar tsoron uwa?, kuma saima niketa mamaki da har kika dawo gida haka rabi tsiraratu wato halp naked ince dai kinci q'aniyarki wajen mama dan naga jikkarki da komi da komi na cikinta na guna?"
heenduh saida ta qara dannawa sa'a wata qatuwar harara sannan tace
"kujimin wannan matar ma, lallaikam sa'a bariki iyawa CE, baccin ma kina 'yar wulaqanci kin tafi kin barni a filin Allah ta'ala ina gararanba amman zakice wai
ma na tafo na qyaleki baccin tare mukaje?
cikin mamaki sa'a tace"tofa, ya ilahee,
ta666 to wlh qawata serious na nemeki bn gnki ba mafarin knn na tafo ko'a tunanina tunda daman kin matsa mun na tafo naq'i shine na zata maybe kina samun left kika gudu kika barni a wajen shiyasa koda na dawo gida nan gidanku ba fara zuwa amman sai mama tace baki dawo ba ganin kamar ranta ya 6aci ne da rashin dawowar taki ne yasa ni mata qaryar cewa kuna hanya mune aka fara d'aukowa, kuma wlh kuwa qawata da gaske nike ki yarda dani man kinsan ba muna muna tsakaninmu fa"
shiru heenduh tai said yanzun ta gano bakin zaren ma ita.
dan haka ta dubi saa tace"wkh qawata in gaya miki wani iccen mangoro ne naga ya fito da 'ya 'ya, kinsanni da son mango kawaifa daga na zagaya na ciro to nad'an jima a wajen wai in gaya miki ina dawowa naga Ashe har an tashi partyn nan"!
a razane sa'a ta dafe qirji tace"mi?!
wai kina nufin nan muka baroki? ca66 d'ijam to Yaya kikayi?
yatsuna fuska heenduh tai tareda ajiye handout din dake hannunta tace
hmmn wannan marar imanin ne ya maidoni gida baccin gama gana mun azaba da yai kuka na gidan duniya sa'a nasha shi jia kan na samu mugun mutumin nan ya maidoni."
sa'a tace "wai wa kike magana wai?"
"doctor man mugu"!
da sauri sa'a ta rufe baki tace"doctor khaleepa fa kikace qawata?
cabbb!! wlh ni namayi mamakin daya daukoki dudda Baku afuwa was junanku"
hmmm kawai heenduh tace amman saita samu kanta da 6oye sirrin su dashi bata fad'awa sa'a matsar data sha ba a baki.
sa'a tace "wai huuu ai doctor akwai nuna aji fa, kumafa wlh dudda fad'in ran nan nasa fa masifar burge mata yake ciki harda ni dan wlh guy din ta ko'ina ya iya murmurza kambun sarautarsa matuqa, waiyama akai ni bngansa ba wajen partyn jia ba saike?,
cikin ko'in kula heendu tace
"inda yana burgeki saiki auresa ay"!
dariya sa'a ta qyalqyace da ita tace "hoo qawata fitina da musifa,

to miye na canza fuska kuma qawata?
kuma nadaiga bawai kula matan yake ba bare musa rai dashi ms"
cikin yatsina fuska heendu tace
"ina matuqar tausayawa dud wacce gigi yasa ta auresa fa ni,
kuda ke sonsa ay wlh ko duka zaku auresa ko 'a jikina fa wnn kuku kaji zaku iya dan nikam bazan iya da halin saba na rashin fuska wlh shima kansa ya sani kuma"
sa'a tace"ni ko aure zaiyi ai nasan bama kalata yake so ba saidai kalarku shuwa"
ta6e lips dinta heendu tai tace
"so bashi a muni fa qawata, sannan kuma kidaina mun ma fatan aurensa can yaje ya samu mai kalar halinsa suyi rayuwarsu nima nasamu daidaini talaka na aura dan auran d'an masu kud'i in akai rashin dace ba qaramar nadama ke samun mace ba, musamman ma in akai dace da surukai marassa *m* iriyan Uwa tasa Hjy firdauseey.
sosai sa'a ke mata dariya tace aike kinsanta ta sanki mamar tasa sai
nikega kamar ma ta daina fad'a in ta kad'o miki kinje musu kwashe kwashen kayan zaqi ko a gidan?
wata 'yar dariyar garari heenduh tai tace "ah tamayi to tagani, kuma bama dole ta daina ja ba ta sakar mun ba,
inda dai nima inada iko da gidan ba ita kad'ai ba?, hmm Allah sa ma d'an nata ya auro mata mai kalar halina tsaitsaye wlh datasan kuwa tagamu da *surukar zamani* dan wlh tsab zan casheta intamun iskaranci dan bawai tsoronta nikeji bafa walla kwata2🤷‍♀️"
sa'a tace "lallaikam naga halama ay, amman plss qawata kibani amsar yaya akai doctor yaje gun partyn nn? dan wlh ban gansa bafa ni, d'age kafad'arta heendub tai tace
"to ohon masa,
nimadai ganinsa nai kawai a gabana zai wuce a lokacin, amman ina tunanin angon nasu nema"
sa'a tace
"aho koda naji dai,
ga jikkarki nan da wayark dan kuwa musaddiq in gaya miki qawata tun jia yake kiranki".
tsoki heendu taja tace
"matsalarsa"
sa'a tai saurin cewa "yawwa qawata na mnta na gaya miki kin kosan jia fa guy dinnan wnda ya siya mana kaya yazo har nan gida nemanki?"
dubanta heenduh tai sosai tace "yakukai dashi?"
sa'a tace "nima dai nace masa dai kuna biki be shine yace zai dawo gobe, snn yace kuma wai koya kira wayarki bakya dauka hakane?
cikin ko'in kula heenduh tace"kinsan bakowace number nike accept ba barea tasa da bnsn taba"
sa'a tace "haka ne, dannayi mamakin ganinsa qofar gidanku lokacin dana fito byn nmnki da naje sai kuma nai tunanin aike bawai 6oyayya bace a anguwar dan da tambaya daya ma za'a iso dashi nan,
ko amsa heenduh bata bata ba saima tashi datai tana dube dube cikin dakin kamar mai neman wani abun.
sa'a tace"qawata wai me kina nema be haka kiketa bincike ko'ina kuma kina yabud'amun kaya a jiki banfa son wulaqanci kin ma maisheni bola ko?

tsoki heendu taja tace"yi haquri qawata wlh narasa Mina ajiye a d'akin nan yake mun wani wari wari can qasa qasa tun jia nikejin hakan mafa"
"toh ko kusu ne ya mutu a dakin naki baki sani ba?
cewar sa'a.
heenduh tace "wama yasani tashi kitayi neman sa dan Allah ma, dan bazan qara ko wuni guda ba cikin dakin nan bare kwana batareda na ganosa bafa, dan na tsani launin d'oyi koya yake Allah kuwa".
nanfa suka ma dakin d'ai d'aya did sun fidda kayan waje suna zuwa can kusurwa inda katifa ke wajen saiga wata leda baq'a da alama dakwai wani abu a cikinta ,had sauri suke wajen sunsunawa bayan sun daukota, saikuwa gashi exactly iriyar warin ne ke tashi a dakin.
suna bud'ewa saiga kaza harts fara tsutsa kad'an.
sa'a tace"kutmelesi ajiyar kaza kikai Ashe qawata?"
mamaki heenduh tai sosai na tuno kazar da khaleepa CE yakawowa su mama wace aka bata bats Ciba harma ta lalace, Dan haka wani dogon tsoki tai tace"nina mnce da itama wlh, takusan sati, doctor be yakawo was mama ita, da akaban nikuma dayake banyi niyyar ciba saina jefata nan, kawo nan na fiddata bola ma Ashe itace dud ta hanamun sukuni ma mtss kayan banza"
"amman qawata dasai kiba mai so yaci ai inda ke bazakici ba, ko almajiri kikaba sa zaki samu lada akan ki ajiyeta tayi d'oyi" cewar sa'a.
a masife heenduh tace "nifa kin isheni malama, dan wanda yama kawo kazar bayya gaba na bare na iya tunawa da wata kazar da ya kawo harna bayar"
saa tace"ke kika sani dai kuma can tsakaninku ne wannan dan kun saba bawai yau kika fara masa rashin kunyarki ba bare abun ya zanemun sabo saidai kuma bansan mizai biyo baya ba dud inya juyo kanki dan kinsan ance mai kurum kurum na nauyin magana zaki ne inya miq'e haiqan, sannan kuma naga zaki iya zuwa gkdansu ki dauko komi kike so kici ko?"
heendu tace "eh idan naje na d'auki daga hannunsa ya fito abun koko?
mtss niya mazo ya rabani da wannan baqar rigar kalar mai ita"
sa'a tace "wacce ba'ai mata gwaninta oho dai ay riga kam dai rayi miki rana kuwa.
taqarashe maganar cikin yiwa heenduh din dariya.
qwace ledar kazar heenduh tai tai waje dan sawa a bola batareda ta sake tankawa sa'ar ba danta q'ulu sosai.
haka ta yaddo kazar ta dawo (niko nace ayya hafsyna kaza ta tafi sai atari ta gaba wataqil an sami fuffuken nan da aketa mgn hhh).
haka suka gyara dakin tareda fesa masa sanyayyar air conditioner mai dadi
dan heendu kam badai gayu ba.
nan bakin qofar dakinta suka shinfid'a carpet itada sa'a suka duq'ufa yin wani game a wayar heendun na wata
'yar mage Angela, dariya kawai suke abinsu.
mama Zainab dake zaune can qofar dakinta tana gyara shinkafa 'yar Hausa wacce baba isma'il ya samo ya auno musu ita kwano d'aya yau da safe dan Allah yasa anyi cinikin kayan miyan nasa jia sosai kam alhamdulilla.
to jin dariyar tasu ta isheta ne wajen hakan ne ya sata d'agowa tace
"haba kuko? kai dan albarkar iyayenku in bazaku daina isata da wannan shirmen dararrakun naku ba to maza maza Ko

kutashi Ku koma d'aki dan kuwa kun hanani jin tafseer a radio d'ina ynda ya kamata."
dole kuwa sukai tsit tareda yin komi a cikin qasa qasa yanda mama Zainab din bazata ji sun ba.
har cikin kanta taji sallamar tasa kafin qamshin turaren sa ya biyo baya.
da sauri ta dago kanta Sam yaqi kallon inda suke itama ganin hakan yasata ta6e baki ganin ynda yaketa daure dauren fuska.
qasa qasa ta cewa sa'a"mtss dubeshi"
sa'a tace "handsome gy. hakan yake, kazalika qarfaffan takunsa gskia yai masifar sake had'uwa yau wlh qawata, dubi yanda fararan kayan nan na aikinsu sukai masa kyau, kazalika medial glass dindake fuskars..
buge mata baki heenduh tai tace"dalla malama surutunki ya isa hk,
ina ruwanmu dashi ma to?mtss kune masu zubdawa mata class wlh"
kan sa'a tace wani abu sai jisukai yana gaisheda mama cikin kalar maganarsa a nutse.
cikin faraa mama Zainab take ansawa sannan tace"likitoci fa koda yaushe babu hutawa khaleepa naga yauma weekend ne lahadi zaku je asibitin knn.
"mama nama dawo at, dayake run qarfe 6na fita sand emergency da aka kawo wata baiwar Allah, shine naje, amman kuma dai alhamdulilla ynxun"
mama Zainab
tace "Allah Sarki Allah sawqqa to"!
"Amunn mama, yana maganar ne yana decline na kiran da zarah ta addabesa dashi tun dazun.
soyake ya cewa heendu ta dauko masa rigar ta jia amman bakinsa yai masa nauyi yaji komi yasa oho.
sosai yayi farinciki lokacin da yaji mama Zainab tace"heenduh dauko masa rigar nn man saiya kaiwa masu ita tad'oro ko zasuyi amfani dashi"
tsam heenduh ta miqe ta shiga daki ta dauko afterdress din a zuciyar ta take cewa"nasan wajen wannan banzar zarah din zaije, saiko gashi ile tana miqa masa rigar kiran zarah na qara shigowa wayar tasa.
dauka yayi wannan karon"gani nan zuwa"
amsar daya bata knn ya kashe wayar.
wani qululu taji ya tasoya tsaya mata a saman qirjinta na jin amsar daya bawa zarah.
komawa tai ta zauna kwata kwata taji ta kasa samun cikakkar nutsuwa, dubn sa'a tai taga hankalinta naga game dinsu yanzun,
tasake dubn sa taga firarsa kawai yake da mama.
tunani take shin wai tawace hanya zatabi tai masa ba daidai ba hartai sanadiyyar hanasa zuwa wajen waccen ballagazar cikin dad'in rai da kuma fanshe haushin klr
wulaqancin dayai mata ne jia?!
tsam kuwa ta miqe cikin qwarin gwiwa da wani murmushin
ta na samun mafita datai.
kai tsaye ta nufi wani qaton bokitin tsarinsu ta daukosa tsagwayam tazo wucewa ta daidai inda yake aiko ta taka wani taklmin ta mai tsini da gangan ta sheqo masa tsarin gaba d'ayansa tun daga saman kansa har zuwa fararen kayan jikinsa sannan ta duqe gefensa tareda cewa"wayyo sannu ban lura bane nazo rage ruwan ne a maguji shine ya kucce mun a han....
babu zato taji mama Zainab ta d'auketa da mari tass Tass abinda maman bata ta6a yi mata ba kuwa wato dukanta.

sa'a daman tunda taga sanda heendu taiwa doctor khlpa wannan aika aikan hannuwa bibbiyu tasata rufe bakinta cikin wani tsantsar mamaki na heendu.
fada kawai mama Zainab take mata tareda cewa"ashe bakida mutunci yarinyar nan?! babu abinda zai hanani zaneki gidan nan kuwa, tayi maganar tana shirin fizgo wani kebel dake jikin wata qusa a bango.
aida wani masifar gudu heendu ta shige cikin daki tana qwalla, taba qofarta garamm ta rufe da qarfi bayan tasa sakata.
har qofar dakin mama ta isa tana cewa"bazaki bud'e mun q'ofar bane koko?
khaleepa datun sanda abun ya faru kansa na duq'e ransa sai tafarfasa yake masa, to sai yanzun ya samu ya dago ya sake duban jikinsa dan ko gaba daya ya 6aci kaca kaca kamar zaiyi amai yakeji a lokacin tsabar qyanqyamin daya shigesa.
miqewa yai tsaye bayan ya zare glass dinsa dasauri yabar gidan anan qofar gida sukai kusan karo yunus daya biyosa gidan dan yaga shigarsa gidan baba Ismail din tun lokcn..
kama baki yunus yai sannan kuma ya fashe da dariya ganin khaleepa dayai dagaje dagaje da tsari mai manja.
daqyar yasamu ya tsaida dariyar tasa yace
"huhhhhhh kaiii!! cancad'i wannan daga gani aikin tijararriyar yarnyar nan headache ne wlh, fadamun man abokina taya hakan ya farune to waima tukun?"
wani takaici ya qara kama doctor khlpan na dariyar qeta da yaga yunus din na masa jiyai kamar ya masa wani kalar mummunan kutafo gamida shaqosa koya sauke hushin
sa a kansa, amman ganin yanda mutane keta kallon jikinsa ne yasashi daure zuciyarsa yabar wajen kamar ya fashe da kuka yakeji tsabar baqin cikin da heenduh ta qunsa masa a safiyar yau d'in nan.....

By
Xexen Fasaha
[1/17, 3:10 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🩻🩻
👁️👁️
DA SAURAN KALLO !!!

Story and writing
by
Xayyneb 💤💤

Fasaha online writers f. o.w.

🌳imparting valuable knowledge and entartaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hawwas~

*Ina miqo gaisuwa ga classic Fedo, gaisuwa taban girma gamida jinjina hajiyata Allah sa kinji

kuma zaki gani*😍

-https://www.facebook.com/Fasaha-Online-Writes-751775151851852/?referrer=whatsapp.

👁🗑👁
P30
heendu ko wuni tai qunshe cikin daki dana sani tayita sau babu adadi na abinda ta akaita, gefe kuma ga mama Zainab na dakon ta Dan tuni ta hirgad'a sa'a gida tace kota had'a da ita inda did kanwar ja ce ita heendun bakinsu a hade yake suke shaq'iyancin su.
har mama ta gama girkin rana wajen qarfe biyu da rabi amman henduh na saq'e a daki yunwa sai qwaqularta take, dole taje ta dauki kununta tun na safen nan ta shanye duka sannan taji fa jikinta ya rage mata rawa rawa na yunwa.
komawa tai gefen katifarta ta zuba tagumi addu'a kawai take Allah kawo babanta kota samu ta fita tayi fitsarin daketa muntsilinta tun d'azun.
cikin ikon Allah kuwa ko minti 5 batai ba taji sllmr baba Ismail ya shigo gidan.
aiko zumbur tai ra miqe ta bude qofar ta fito da gudu ta la6e bayansa ganin yanda maman ta tunkarota aiko ta qadandame baba Ismail tana cewa"dan Allah mama kiyi haquri wlh bada gan gan ba"
baba Ismail kuwa tambayar ba'asi kawai yakewa mama Zainab tareda kare 'yar tasa adud yunqurin da mama Zainab tayo wajen kawo was henduh bulaliya.
dole mama Zainab ta yarda bulalan cikin bacin ran dahar yanzun bai saketa ba tace"ynzu mlm fisabilillahe ace har rawar kan heendu yakai data dakko qazanta ta tsari ta tuleta a jikin khaleepa?
cikin mamaki baba Ismail yace"zainabu kamar Yaya dan ban gane ba, wane kalar tsari kuma a jiki?
quta mama Zainab tai tace "ai gata nan bayanka tai maka cikakken bayani na abinda ta aikata."
kallon heendu baba Ismail yai yace" garin yaya kikai haka keko heenduh na?
tsuraro qwalla tai tace"kuyi haquri baba wlh Nima bada so nabane hkn ya faru tsautsai ne, dan Allan babana ka bawa mama haquri kada tai fushi dani Allah kuwa bazan iya barci ba intai mun fushi"! taqarashe mgnr tareda matso wasu sabbun qwallan.
duban mama Zainab yayi yace"Dan Allah ayi mata haquri zainabu abu na, inda ta ce tsautsayi ne bazata qara ba shiknn ay, kuma
kinga kuskure daman babu wanda bai aikata sa, to du Allah komi ya wuce kinji uwar gida ayafe mata man sarautar gida"
sakin fuska mama Zainab tai tace to shiknn malam amman da sharadi dole taje ta basa haq'uri na rashin ta idon datai masa"!.
baba Ismail yace"indai wannan ne babu matsala nasan d'an nawa da haquri, yanzun abinda yakamata tai wanka taci abinci sannan taje ta basa haqurin ince dai shike nan kuma zainabu na?"
mama Zainab tai murmushi tace
"indai tai mun hakan shiknn mgn ta wuce sai kuma a kiyayi gaba"
har a ran heendu taji dadin sassaucin data samu daga mamar dan haka da sauri ta debi ruwa a rijiya ta Shiga wanka ta jima sannan ta fito ta iske baba Ismail harya gama cin abincin yana

daure kaba.
yana gamawa ya miqe ya koma wajen sana'arsa bayan ya miqawa baba yawale kwanon abincin sa yaita sa albarka kuwa kamar kullum.
Heendu bata jimaba ta gama shafa fowder ta da kwalliyarta yar qa'ida ta sannan ta sanya wata blue din doguwar rigar wani material mai sul6i da gyalen kayan.
kayan sallar tane sud'in.
tana gama cin abincin ta fita tareda cewa mama Zainab "mama naje basa haqurin kamar yanda kika umarce ni, saina dawo"mama Zainab tace ''saura in kinje kiwa mutan gidan rashin kunya dan nasan halinki in bama kiyi sa'a ba suka koroki.
"A'a mama bazanyi ba aina daina nace"
wani murmushi mama Zainab tai tace"hmmn! a baki kenan heendu dadai bansan halinki bane wannan dasai na yarda da mgnr taki ay, sannan kuma ki
tabbatar da cewa saina ganku tare kun dawo gidan nan dashi sannan zan tabbatar da cewa kin yi abunda nace"
wucewa heendu tai tana turo baki a ranta take cewa"wai kamarni da ajina da komi nawa za'a turani bada haquri hmn babu komi yaci darajar iyaye ay"
kai tsaye gidansu sa'a ta wuce ta same ta tana wanki nan ta gaida maman sa'a din sannan suka shiga daki sa'a tace "qawata miyasa zakiyi masa haka ke kuwa?
Allah kuwa bakiji yanda yaban tausayi ba, nazata rufeki fa da duka zaiyi amman saigashi yama bar miki gidan"
harara heendu ta sakar mata tareda cewa"ta666 yazo gidan namu ya doke ni? kema kinsan bazai yiwuba wlh"!
kallon ta sa'a kawai take dan kam halin heenduh sai itan.
amman a fili tace
"hmm Allah shirya mun halinki qawata, amman ina zaki haka kika sha wannan kyau haka?"
heenduh kamar zata fashe da kuka ta dubi sa'a tace"hmn!! zanje bada haquri a umarnin mama ne"
dubanta sa'a tayi sosai tace"ah wane iriyar bada haquri kuma? gawa kuma?
nan heenduh ta fada mata yanda suka qare da mman tata.
sa'a tace "ngd Allah, ai maganinki kenan Inda ko an baki Shawara bakkya d'auka ai ga iriyan ta nan".
tayi maganar tana tsane hannunta mai kunfar wanki da wani tsumman zane.
"saiki tashi ki tafi ay kada kije baya nan, kuma dai kinji abinda maman tace kada kidawo sai dashi."
yamutse fuska heenduh tai ta miqe tsaye tace"Allah kuwa badan ya isa ba zanje basa haquri ba dan sabida mama ne ma kawai, ni qarin haushi na ma nasan majalissar su nacan ta qa'ida inda yau lahadi"
sa'a tace"ban tunanin sun isa futowa yanzun dan sabida sai anyi la'asar suke fitowa kinga yanzun ma uku saura ne" tayi maganar tana mai kallon agogon dake rataye a dakinsu a bango.
miqewa heenduh tai sa'a ma ta miqe tareda kamo hannun heendun na dama tace"qawata ina cikin matsala wlh, in bazaki takura ba in kin dawo kimin waya sai nazo gidan ku mu tattauna matsalar wataqil nasamu mafita akai"
cikin tausayin sa'a daya kama heenduh na ganin ta sauya lokaci daya yasata cewa"to shiknn

qawata insha Allah zan kiraki in na dawo, amman bazaki rakani bayar da haqurin ba knn?
d'an zaro ido sa'a tai tace"rufamin asiri, ke kikai laifinki dan haka ke d'aya zaki gogesa kuma ni koma ba haka ba wankin nan bazai bari naje ko nan da can bane"
heenduh tace
"daman ba kirki kika cika ba ay" qaqalo murmushi sa'a tai tace"koma dai mike nan, kayan nawa ne nikeson wankewa kinga gobe monday school"
ni school d'in nan ma ta soma isana" cewar heenduh.
sa'a tace"haquri zamuyi kinga saura wata biyu mu zana final exam abun ya tafo ay shiyasa kk jin zafinta"
har zaure sa'a ta rako heenduh sannan ta koma taci gaba da wankin ta.
heendu na isa gate din gidan babu shayin komi ta ture qofar ta wajen get ta shige har mai gadin yazo hana wucewa ganin ta dayai ne yasashi sakin fuska tareda cewa"ah heenduh kwana biyu anbar kewayo mu"
cikin girmamawa heenduh tace"munyi hidindimu ne baba sani ga kuma school muna ta test akoda yaushe sbd gabatowar exam shiyasa ban samun fita sosai yanzun"
Mlm sani yace "Allah shi taimaka to 'yata"
"Amimm baba sani"
cikin falon gidan ta shige kai tsaye ta zauna kujera mai facing Hjy firdausey tace
"evening Momy"
wani qasqantaccen kallo Hjy firdauseey ta jefo mata ta dauke kai batareda ta kula heenduh dinba taci gaba da lissafa kayan su na lace kala kala da sukayi odar wanda hjy Hadeeza ta kawo mata su bada jimawa ba, lissafa kayan take tana shigar da last price nasu cikin system din dake gabanta"
heenduh kuwa batai qasa a gwiwa ba tace"nace momy ina wuni fa"
tayi maganar baki a murgud'e.
dubanta Hjy Firdausi tai tace"to marar ta ido marar mutunci kin shigo gidan ko? dole ne akace miki sai na amsa gaisuwar matsiyata ne kamarku koko ne?
nasan yunwa ce ta koroki gidanku saiki je ki cika cikin naki kibar mun gida matsiyata kawai"
wani takaici ne ya tasowa heenduh, lallaima wannan matar, wlh taci arziqin datace wa mamanta tadaina mata rashin kunya wlh da saita mayar mata da raddin mgnr ta kuwa take yanke, amman koba komi ta zamar mata ciwon ido inda har tarasa hnyar dazata daina ganinta a gidan kamar ynda taso tuntuni.
maimakon haka saima miqewa datai ta bude fridge ta dauko holandia yughurt ta dawo ta zauna kan kujerar ta dora kafa daya kan d'aya tana lilasu tareda sha.
tunani take ko khaleepan bai nan ne jin bataji saba, inko haka nan ne tana nan harsai yadawo dan bazata juri kwanciya barci ba mamanta na mata fushi ba tab!, bama zata iya barcin ba sam dan ko tasan halin kanta ita kanta.
sosai Hjy Firdausi tai mamakin yanda yau heenduh batai mata rashin kunyar tata ba, amman ta danganta hakan da tunanin cewa yau qln ko batason 'yan maganar ne danta fuskanci yarinyar muskila ce lokutta da dama kusan halinsu d'aya da khaleepanta intai wani tunanin.
satar kallon heenduh tai babu qarya dan haqiqa yarinyar ba qaramin kyau Allah ya d'asa mata ba ta kowane fanni matsalar dai itace ta tsane ta da iyayenta daba haka ba tasan tabbas da khaleepa ya samu mata har mata ko.

wayarta ta jawo ta kira babu jimawa aka daga tace
"nace Hjy Hadeeza wai nawane kudin qananun lace din ne da manyan su?
Hjy Hadeeza tace "hajiyata ay su q'ananun kudinsu dubu d'ari uku uku da hamsin ne sai manyan kuma biyar da hamsin hamsin"
"to yayi daman ina shigar da list nasu ne"
suna ajiye wayar taci gaba da aikinta tagama knn ta miqe tareda qwallawa asabe kira saigata da sauri ta fito daga cikin kitchen tace "gani Hjy"
cikin tsabar raini dudda a haife asabe ta haife ta amman tsabar tana qasanta babu wulaqancin da batai mata, bama wai ita Kadai ba dud sauran ma'aikatan haka take musu, kuma da zarar ta tsaneka yanzun nn ta koreka tasamo wani shiyasa kowa shakkun mata badai dai yakeba a cikin ma'aikatan gidan
dan sunsan rashin mutuncin ta Kunlun gaba yake ba baya ba indai itace kuwa.
shiyasa asabe jiki na rawa tace"wani abu za'ai miki ne hjy?
tace" bawani abu bane ina fatan keda habiba kun gama girkawa mai tsada na abincin sa komi is ready?
da sauri asabe tace"eh hjy harma an kai masa tun dazun dan yace bazai sauko qasa ba"
shiru Hjy Firdausi tai sannan tace
"in yana wannan zaman dakin tabbas nasan b'ato masa rai akai kuma gashi shi Indai yana fushi baison ganin kowa wajen mts na hanasa shiga cikin talakawa anman yaqi dan babu mamaki sune suka jaza masa wannan q'uncin da yakeyi,, amman bari na barsa zuwa anjima inya saki naji koma miye"
tana gama fadan hakan ta kwashe system dinta tayi gaba zuwa saman
ta,sai kuma ta juyo tace"af na manta asabe biyoni da kayan nan d'aki na dan akwai masu halin 6eraye a wajen kada amun wubb nan da wasu daga ciki"
da sauri asabe tace "to hajiya"
hakan kuwa ta kwashe kayan nan duka Hjy Firdausi na tsaye a saman benenta saida asabe ta gama sannan ta shige dakin nata cikin nuna isa, gwala gwalai sai motsi suke a jikinta kota ina a hakan ta kullo qofan.
asabe ta dubi heenduh tace
"kiyi haquri kinji ko muma haka muke haquri da ita kina gani kuma"
wani murmushin takaici heenduh tai tace"mama asabe babu komi ay abun ba baqona bane a ji bare na damu, kije kici gaba da aikinku kada kiyi laifi kuma"
harta wuce tace
"no momy ki gane dana karbo miki takardar ne na sakota a tsakan kanin wasu files na asibiti to ashe ta sub'uce ta fad'i sa'ilin da na fito daga mota na shigo nan gida to bayan ta kawomun takardar ne nima na tuhumeta a 'inane ta sameta dan nayi matuqar mamakin nima na yaddatan danai momy kinsan kuma wannan takardar in babu ita koda Wanda ya siyarwa da dadyn company din nan ne yai musun bai siyar ba ta zauna Inda shaida d'aya ce kuma mun rasata..." d'an shiru yai da mgnr yana mai sakin numfashi zuciyarsa cikeda mamakin yanda ya iya tsara mgnr bazata haka babu ko tangard'a bare kuma tazgaro a cikinta shidai kawai yasan yana yine danya qwatowa headache k'imarta daga tozarcin da momyn tasa ke shirin yi mata dan jiyake maqoshinsa harya fara masa zafi saboda doguwar maganar dayaketa sakowa
dandai kawai ya ida wankesu daga zargi yasashi daurewa yaci gaba da cewa "kuma momy data kawomin takardar anan take shedamun a kofar gidan baba yawale danai parking din motar dazun alokacin data fito itama daga gidan baba yawalen akai sa'a anan ta hango fadowar takardar kwantiragin lokacin data isa gun ra d'auka nikuma harna shigo gida tofa mafarin knn tun alokacin bata biyoni ba saida tai shirin barci a yanzun take fadawa mamanta mafarin knn

Maman tace tazo takawomun yanzun wataqil ko inada buqatar ta a yanzun lokacin dana neme takardar ban sameta ta..... sannan kuma to abinda yasa da kika shigo dakin nawa baki ganta ba ta d'an b'uya ne toilet gudun kada kiyi zargin wani abu tsakaninmu kuma gashi abinda ta gudan shiya faru kunyi zargin NATA.. yanzun dan Allah Momy ki fadamun bata temake kiba data kawo takardar nan Amman shine hadda samun gudumnuwar munanan maganganu daga gareki har kina kusantata da mazinaciya daga temako Momy??"!!
yayi maganar kamar gaske harda sauya fuskarsa ta koma kalar tausayi.
sosai kuma jikin Hjy firdausey taji yai mata sanyi duban khaleepa tai tace
"toni 'ina nasan hakan bansan wannan bayanin ba ay ko? kuma ai laifinka ne dabaka fadamun da wuri ba har saida hakan ta faru sannan"
sauke ajiyar zuciya yai ganin yanda tsarin maganar dayaiwa momyn tasa ta shigeta sosai sosai kuwa.
duban heenduh yai itama wacce tuni kukanta ya tsaya cak sakamon jin qaryar da khaleepa ke shararawa Hjy firdausey din kuma harta yarda💯.
batai auneba taga ya sakar mata murmushin nuna cewa Shifa *mai nasara* ne akan komi yasa gaba dan haka tama daina mamaki dan nasararsa a jinin sa take tuni batun yau ba.
kauda fuskarta tai ganin yanda ya zubawa hannunta ido daya d'an fasa yana jini jini inda zarah ta ciza din.
Ita kuwa miqewa tsaye tayi lokacin ne taji Hjy firdausey ta dubeta taci gaba da cewa
"ay ke kuma saiki haquri ki kuma kifita kibar man gida angode ba'a godeba".
"Heenduh ta maimaita kalmar
"angode ba'a godeba kuma? mikenan take nufi to?
d'an qaramin tsoki taja cikin ranta tace
""wannan kuma matsalarku ce inda Allah dai yasa nayi free daga sherrinki ahaka tafice daga gidan cikin saurin son ta qarasa gida kozafin dake hannunta bataji sbd qagararta datai ta isa a gida kodan mama Zainab ma kuwa..
zarah kuwa tana ganin heenduh ta fita khaleepa yayi komawarsa saman sa ta kuwa rushe da kukan baqinciki dantaso a 6atawa heenduh suna yau na abinda sukai zargi daga farko ashe abun ba haka bane.. wani kukan ta sakeyi tana kuka tana cewa "toni Momy Yaya zanyi da bakina data fasamun? gashi dutta bi ta wani yayyakushemin jiki ta fasa mun shi kamar wata hatsabibiyar mage,,, shegiyar yarinyar nan sai zugin zafi nikeji kallafa wasu gun harsun fasa ni haqorina kamar yana mun girgid'a inda takaimun duka shegiyar nikeji."
kamota Hjy firdausey tai suka Shiga toilet tasa ta wanke bakin dake yoyon jini da sauran wurare ta baro mata toilet din tabaro zarah din tana gasa jikinta da ruwan zafi sannan da ta gama hhy firdausey ta koma ta kamota suka fito suka dawo daki ta bata magani tasha tace "sannu kiyi kwanciyarki @ nan ki huta sai gobe kya koma gidan naku inda nafadawa momynki nan zaki kwana daman yau."
haka zarah ta kwanta zuciyarta fal tsanar heenduh kam ga ciwukan data jijji mata a jiki sun hanata sukunin rayuwa awahalce barci ya dauketa ko'ina na jikinta na mata zungar ciwo.
shiko khaleepa dasauri yasauko samansa hannunsa daukeda wani dan box aids na dressing din ciwo lokacin dayaga momyn da zarah sunyi daki aiko ya ida fita yabi bayan heenduh dan kareta daga fadan mama Zainab itama inda dai silar sa ne komi keta faruwa yau din kuma daga nan har ma yadan duba mata hannunta daya lura taji ciwon nan.

heenduh kuwa tana ra6e ra6e uwa wata marar gskia ta shiga gidan nasu takuwa iske mama Zainab tsaye tsakar gida tana d'aura musu net itada baba Ismail.
har kusada ita ta isa ta kamo hannun maman nata tace"dan girman Allah mama kiyi haquri mama na ban ankara dare yayi har aka bane wlh" fuzge hannunta mama Zainab tai taqi tanka mata ma taci gaba da qulla gidan sauron saida ta gama tsab sannan ta juyo ta dubi heendu dake tsiyayar qwallan fushin mama Zainab din gareta har haka.
fuska daure mama Zainab tace "kinko san har gidan baba d'ahara d'in naje bisa umarnin babanki akan natafo dake ganin yanda na kasa nutsuwa a Daren nan heenduh yau?
Ina kikaje kenan?,,,
tuni henduh ta fara qyafqyafta idanuwa dan wannan karon kam ta rasa ma ta cewa.
mama Zainab tace"wai badake nike mgn ba bazaki bani amsan daga inda kika fito ba inda yanzun sa'a batanan bare kice mun tare kuke??"
itawai miyasa komi tai sai ace sa'a bata bare....
kuka take shirin saki dan tunaninta uku ya kasu na farko fadan mama Zainab a gareta,,,
na biyu mgnr Hjy firdausey ce kawai ke mata kuwwa a kunne na inda take cewa khaleepa ya auri zarah dazaran dadynsa mukhtar ya dawo ya taimaka yai mata ladabin umarni a hakan ga amince warsa.
na uku kuma zafin marin zarah ne datai mata sai yanzun zafin ke qara shigarta zam zam dan daman hannun zarah kona wani qaton gardin namijin albarka kan tauri.
hannu tasa a kuncin nata tana sosawa zuciyarta na fada mata cewa kema ai kin rama bata shaki a basilla ba ...
zungar da hannunta yasakar mata na cizon zarah din yasata babu shiri sakin kuka a wahale ta durqushe wajen tana matse hannun...daidai nan khaleepa yashigo gidan ganin kukan headache datake yayi zaton ko wani abu mama Zainab tai mata ne dan haka yaqarasa shigowa gidan dad'an sauri sauri byn sallamar dayai.
sosai mama Zainab tai mamakin sake shigowarsa yanzun kuma kan tace wani abu har yayi saurin duqawa kusada heenduh a saman qafafunsa ya dubi mama Zainab bayan sauke idanunsa dayai kan heenduh yaja numfashi yace
"Momy headache nita raka kasuwa zab'an wasu kayan kyautarwa na mata Wanda nikeson bawa abokina gudunmuwa da zaiyi aure, kuma ma to sai banyi zaton zamu jima ba haka shiyasa dana gamu da ita zata shiga gidan matar can tsohuwa lokacin daman nan na nufo danta rakanin shiyasa kanma tashiga gidan nanemi alfarmar ta rakani din to shiyasa mama muka jima din ayi haquri."
sauke ajiyar zuciya mama Zainab tai tace"babu komi to amman aiyaci ace ta qirani a wayar ta inda tafita da ita saita shaidamun kokuma Dana kiratan ga dazun saita fadan din ko? Inda tasan fitarta a dare bana nutsuwa a hakan yanda duniyar nan keta garambawul da mutanen cikinta khaleepa?..
gyaran murya baba Ismail yayi tareda ajiye butar hannunsa daya fito daga ban daki ya qaraso wajen yana cewa "dud naji komi na abinda kuke tattaunawa zainabu kuma inda gashi shi khaleepa yazo yai miki bayani kuma sundawo Ipia ai alhamdulilla ko?"
"hakane Mlm nidama laifinta nagani ba nasa ba data kasa mun bayani tu wuri shiyasa"
baba Ismail yace
"ai komadai mikenan shikenan magana ta wuce"

"To ai shikenan mlm tayi mgnr tanufi daki dauko musu sauran kayan kwanciya shima baba Ismail ya Shiga d'akinsa dan canzo kayan dayake kwanciyar barci dasu shima wato Wanda suka fara danyin taushi cikin kayansa na sawa.
kallon mamaki kawai heenduh kewa khaleepa na qarairayinsa yau din nan kuma wai dud dan ya kareta? batasan sanda da suka had'a ido ba tasakar masa murmushi ba shima taga ya kashe mata ido daya wanda yasa take taji wani iri a jikinta har saida ta lumshe idanunta tana kuwa bud'esu
babu zato kuwah taga khaleepa ya miq'e da sauri cikin shigarsa dayayi ta qananun kayansa dasuka haskasa inda akwai NEPA lokacin ga mamakin ta d'akinta taga yayi shigewarsa.. zaro fararen idanuwanta tayi waje a matuqar mamakan ce da kuma tunanin miyake nufi to??!,
jiyo muryar mama Zainab tayi tace
"saikije ga ruwan wankan kican a boket rufe na hada miki run dazun".
dasauri ta miqe tana kallon hannunta tayi saurin b'oyesa ganin yanda jini ya biyo gefen hannun saurin boyesan da tai gudun kada mama Zainab ta gani ne.
dakin ta shiga ta iskesa ya hard'e q'afafunsa kan daya yana zaune kan kujerar dake dakin ta gaban Mirrow dinta yana latsar wayarsa hankalin sa kwance...batace masa komi ba ta dauki towel dinta ta fita daga dakin bayan ta kunna fankar Sama jin akwai zafi lokacin... kashe qwan dakin tai taja qofar ta saya.
 lokacinda ta fito harta iske su mama Zainab sun kwanta a net dinsu bayan kullo gidan da akai.. jitai gabanta ya wani buga dammm!! Damm! sanin datai khaleepa na gidan basu saniba su kuma sun rufe Yaya kenan to?
 dan haka jikin nata a sanyaye ta dauko kwandon sabulun nasu kawai tadauka takai bayi tadawo ta dauki
bokitin ruwan da hannunta marar ciwo ta Shiga dashi bayin sannan ta fara wankan zuciyarta na tunanin zaman mi wai doctor din kemata ma a daki yaqi tafiya?? !!!
tsoro taji ya shigeta na gudun kaddafa mama Zainab taje cikin dakin in case shiyasa tafara wankan cikin hanzari tana Allah Allah tagama taje ta setasa qofar fita inda tanada tabbacin su mama Zainab sunyi barci zuwa yanzu.....

~I heart you mom Ahmed❤.~

By
Xexen Fasaha.
[2/13, 10:20 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🩻
👁️👁️
DA SAURAN KALLO!!!

Story and writing by Xayyneb💤💤

Fasaha online writers.

🌳Imparting valuable knowledge and intertaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hauwas~.

👁️📦👁️
🅿️4️⃣2️⃣
Y unqurin barin jikinsa tahau yi amman yanda taji ya matse cikinta da hannuwansa a zagayen da suke a saman cikin nata hkn tasa dole ta daina qoqarin tashin daga jikinsa.
saidai cikin mgn qasa qasa bayan ta miqa bakinta setin kunnensa tace
"please rabu dani ka koma makwancinka man kaima"
juyota yayi da hannuwansa ya zuba mata idanunsa, ahankali yasa hannunsa yana gyara mata gashin ta mai sulb'i daya sake sulalowa mata a fuska shima har ya sauka jikinsa.
shima a hankali ya kwantar da kanta bisa qirjinsa yahau shafa gadon bayanta yana mai sunsunar qamshin gashin kan nata yace"em emmmm headache na gaya miki anan zamu kwana waje daya fa, koko dai bakison ki samu baby beautiful kamarki kidinga mata kalar kwalliyar kin nan ta gayu em?"
lumshe idanunta ta hauyi bayan taqara cukwikwiye zanen ta a breast ballons dinta ta qara cusa fuskarta cikin malaywacin qirjnsa a saman gashin dake kwance a qirjin nasa tana shaqar sansanyen qamshin sa mai saka mutum jin barci.
jin yanda yake yamutsa gashin kanta yana mata Susa a cikinsa gamida bata deep kissing a bayan wuyanta yasata sakin ajiyar zuciya jin datai yace tabasa amsa eh ko a'a na son babyn.?
cikin kunya kunya da tsoro still dai kanta na cikin qirjinsa yaji tace cikin wata kalar sabuwar shagwab'abbiyr muryarta mai ratsa dodon kunnuwansa
"to..to..nifa ina tsoron yin ciki ne.,.. kada a gane munyi wani abu tsakaninmu".
"haba headache na ai babu Wanda zai gane mimikeyi kinji?
"em em nidai na haqura da babyn dudda ina sonta" tayi mgnr cikin turo jajayen lips dinta Wanda yaji kamar ya tsotsesu duka ya huta.
"to shikenan zanje hospital namu inkin yarda zan baki maganin hana daukar ciki inna dubo kalar daya dace kisha...kinga daga nan zamu dinga enjoying na junanmu koda yaushe batareda kowa ya sani ba ko headache na kin amince?
jin yanda yake mata mgnr yana dan rurrugata tareda Mirza mata hips dinta cikin Jan hankali hakan baqaramin shocking yasa mata a jiki ba.
narkewa kawai take sakeyi a jikinsa da qyar ta tattaro masa Kalmar cewa"em"
dawani mugun sauri kuwa ya burkitota qasa ya hade bakinsu gam yana gigitata da zafafan kissing dinsa daqyar ta kamo sa ta qanqame tareda ja musu abin rufa tana kwance a cikin jikinsa barci ya kwasheta.
shiko ya jima yana cikin wani kalar tsantsar farinciki na tunanin yanda headache tai saurin amincewa magnrsa dayace zai bata maganin tsarin rashin samun ciki.
murmushi yai a ransa yace"Haba man headache inkin san wata ai bakisan wata ba ai"
haka ya qara matseta cikin faffaden qirjinsa ya manneta tsam tsam a jikinsa yanajin dumin jikinta na ratsa nasa, yana kuma qara shaqar qamshin jikinta tareda qarewa kyakkyawar fuskarta kallo shima babu jimawa barcin ya sacesa cikeda nishad'i.

da asubahi ita ta fara tashi ta zare jikinta a nasa a hankali ta miqe zaune zanenta har lokacin daure ram yake a qirjinta taqi sakinsa koda wasa.
wayarta ta haska masa a fuska tareda zuba masa idanuwanta tana cigabada kallon zatin ktakkyawan surar fuskarsa da ginannen ingarman jikinsa na qarfaffen namijin duniya.
fuskarsa kuwa taga dudda yana barci baqaramin kwarjini taga yayi mata ba sosai.
jitai gabanta yad'an fadi jin yanda tayi kamar ana qara dad'o mata qaunarsa a ranta.
tabbas dud matar data mallaki cikakken namiji haka kamar doctor dinta dole tai kishin abinta saboda hauhawar zalamar kwadayun natattun mata garesa kamar yanda tasan yanata fama dasun kuwa.
sauke ajiyar zuciya tai sannan ta miqe a hankali ta zura hijab dinta tareda fita tsakar gida nan ta fara wanke bakinta dan sotake tasamu doctorn ya fita tukun a gidan nasu.
nanta ga baba Ismail ya fito daga daki hannunsa daukeda carbinsa yana ganinta yayi dan murmushi yace"alhamdulilla heenduh na inda kin tashi daman yanzun nake fad'awa mamanki inta idar da sallar ta tadoki kema dan naga yau kin kusan makara keda muke kusan tashi ma tare a sallar asuba amman yau shiru".
cikin sarqewar murya tace"e..ehh babana naso makara ne yau" wucewa yai yace "zoki rufe gidan to danni zan wuce masallaci kada na rasa jam'e" haka ta fita ta sayo gidan dasauri ta koma dakinta.
ga mamakinta tsaye ta iskesa yana saka rigarsa 'yar saman nan daya cire dan haka dasauri ta qaraso gabansa ta janyo hannunsa cikin mgn qasa qasa tace
"zo..tafo ka fita baba ya tafi masallaci yi sauri ka wuce kada mama ta gama salla ta fito"!
kallonta kawai yakeyi baice komi ba ya fita bayan zura takalman jiqaqqar fatarsa dayai yabar dakin dasauri ta bude masa kofar wajen ya fita nan ta maida qofar ta rufe ta jingina bayanta jikin qofar idanunta lumshe hannuwanta kuma duka biyun dafe a saman qirjinta tana mai sakin ajiyar zuciyan sam barka.
ruwan zafi ta dafa ta shiga tai wanka biyu harda na tsarki dan tasan dole tayisa kuwa sbd abunda tadingaji na fita jikinta sa"ilin dasuke tareda shi.
ahaka ta fito tai sallah ta daura musu kalacin kunun gyada da fanke.
saidai har gari yayi haske sosai baba Ismail bai dawo gida ba..gashi sun saba daya fita masallaci an gama salla yake dawowa gida yaita yin kuma lazeminsa han gari yayi shar amman yau kuma shuru baima dawom ba.
haka mama Zainab ta shifida tabarma waje bayan ta ajiye kofin kunun baba Ismail din ta dubi heenduh dake zaune saman turmi da wayarta a hannunta tana shirin bude wani saqo da musaddiq ya turo mata bayan iyayen missed cull nasa data gani dayake wayar na silent shiyasa bata San yayi kiranba.
To tana cikin qoqarin bude saqon ne kuma taji mama Zainab ba cewa"0h heendu kinga har yanzun babanki shiru bai dawoba ko'ina ya tsaya Kuma Allah a'alamu?!"
heenduh tace
"koyaje wani gun ne to mama a uzurance?
taqarashe mgnr gamida ajiye wayar bata bude text din bama.
sakin ajiyar zuciya mama Zainab tai tace"to Allah sadai lpia"
"Aminn mama"
wasa wasa har wajen azuhur baba Ismail bai dawo ba bare su sasa idanunsu, zuwa lokacin

mama Zainab fa hankalin ta ya soma tashi boyewa kawai take gudun kada heenduh ta lura ta qara Shiga damuwar itama inda tare suke lokacin har yanzun.
suna gama sallar azhur ne suna kuma zaune dai a tsakar gidan har Cikin tsakar kan heenduh taji sallamar sa kamin addababben qamshin turarensa yabiyo baya.
caraff suka hada idanuwa sanda ya zauna kan tabarmar yana gaisarda mama zainab.
bayan sun gaisa take cewa cikin qarfin halinta "ah likitan turai mlm khaleepa har an dawo asibitin ne haka da wurwuri?.
cikin murmushi yana d'an shafa Kansa yace"dayake na zo gida ne d'aukar wasu takardu kuma jia da muka fita naji headache na cewa batajin dadi shiyasa na tafo da mata magani nasan intasha zataji sauqin insha Allah"
mama Zainab tace to angode kuma ni ai bnmaga alamun wata rashin lapia a tareda itaba yanzun hkn ma lanbonta ne data Saba dan heenduh kan batta da raina ciwo komi qanqantarsa a jikinta.
d'an satar kallon ta yayi baidai ce mata komi ba sannan ya bude jikarsa ya fiddo wasu jajayen magunguna saces 2 ya miqa mata yace
"kullum zakisha bibbiyu in daily kuma tundaga yanzun zakisha su dan yanzun zasu fara miki aiki ma a jikinki..."
jiki a sanyaye ta amsa maganin dan tasan kona miye kuwa.
na hans daukar cikin ne dasukai mgn dashi dazyn....
tuni taji tsoro kuma ya shigeta nan take.
bata qara tsinkewa ba saida taga ya miqe da kansa ya debo mata ruwa cikin cup ya miqa mata tareda cewa "shasu ma yanzun na gani kamin natafi."
dole babu yanda ta iya ta ballo maganin ta tura a baki tabi da ruwa idanunta a runtse...
murmushi yasaki yad'an ciji lips dinsa sannan ya miqe yaiwa mama Zainab saida anjima ya fita gidan zuciyarsa fes. saqawa kawai yake a ransa sanda ya shiga motarsa yana tunanin a fili yace "hmn hoooo haba Headache ni din akace miki mashirman cine mai qaramar qwalwa kamar taki har dazan yarda na baki maganin hana daukar ciki ina matsayin likita kuma alhalin nasan babban illar dake jaza hakan shan maganin planing ga matar da bata fara haihuwa ba.....
sarai yasan hakan ba qaramar Matsala take jazawa ba
Mafarin knn dayai mata dubarar dauko mata magungunan qarin jini a zuwan na family planing din ne inda yasan bawai sanin kalar su maganin taiba.
da wannan tunanin ne ya karkata kan motarsa dauki hanyar komawa asibiti dan daman saboda ita dinne har yadawo...
acan kuwa yana fita itama miqewa heenduh tai ta nufi dakinta yayinda mama Zainab ta bita da kallo ranta a cunkushe da rashin ganin dawowar baba Ismail dai. sosai hankalinta yaqara tashi ganin har anyi la'asar kuma duba da duniyar nan yanzun babu tsoron Allah a cikinta mutane Sam babu imani ko kadan.
tunanin hakan datai ne yasa taji hawaye suna shirin zubo mata babu shiri kuwa....

By
Xexen Fasaha
[2/13, 10:20 PM] Xainab Documen: 👁️👁️

🥡🥡
👁️👁️
DA SAURAN KALLO!!!

Story and writing by Xayyneb💤💤💤

Fasaha online writers.

🌳Imparting valuable knowledge and intertaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hauwas~.

👁️🥡👁️
🅿️🔢
T a fito wankan d'aure da towel dinta har gwiwa gashin kanta dud ya manne saman wuyanta zuwa kirjinta Wanda lemar ruwan wanka ce ta jiqasa.
ajiye boket din tai da kwandon a inda suke sannan ta shiga dakin mama zainab nan ta shafa mai a jiknta danma batada da kaya a nan data saka abinta ma.
duban agogon dakin mama Zainab din tayi taga har 11:22 AM.
nan kuwa ta fito
tana shiga dakin nata kuwa wanna Karon ba saman kujera ta iskesa ba, ta iskesa ne tsaye ya zura dukkan 2n hannuwansa cikin aljihun jeans dinsa yana kaikawo cikin tsakar dakin a cikin kalar takunsa.. Yana juyowa 4 eyes sukai kowanensu ya zubawa dan uwansa ido babu qaqqautawa, saurin janye idanunta tayi ta nufi ma'ajiyar kayanta zata dauko sai kawai jin takunsa tayi ya yi mata runfa a bayanta tareda daukota dukanta ya ajiyeta saman gefen katifar ta murya qasa qasa yace
"my headache kiyi zamanki haka you are beutuful cut baby kawo hannunki muga"
zuba masa fararen idanuwanta tai sosai tama kasa miqa masa hannun sai shine ya kamo hannun ya d'an shafa mata dai dai inda taji ciwon da yatsarsa aikuwa tayi saurin janye hannunsa idanunta na shirin zubda ruwa.
girgiza mata kai yayi alamun kada tai kukan, Aid box din ya bude ya gyara mata wajen tareda saka mata wata 'yar farar plistap ya manne wajen.
sakin numfashi tai ta dubi hannun nata sannan ta sake dagowa da idanunta ta dubesa shima din ita yake kallo sosai.
jitai hannunsa ya sauka saman gefen kuncinta inda zarah tasa wajen yayi mata ja sakamakon Marin nan datai mata.
shafa mata wajen yakeyi cikin tsabar tausayinta da kuma wata mugunyar tsanar zarah kan abunda tai matan yaji ya d'arsu a ransa.
cigaba da shafa mata wajen yake kamar zaiyi kuka yakejin kamar ciwukan nata ma dukansu sudawo cikin jikinsa koya samu sauqin bugun zuciyar tasa datake ta famanyi masa.
hannunta ta daura akan nasa a hankali ta janye hannunsa ta miqe staye tana kallon qofa muryarta qasa qasa tace "tasoo muje na bud'e maka q'ofan gida ka fita please dan dare fa nayi.." tayi maganar tana mai saka hijab dinta.

miqewa taga yayi a zatonta fitowar zaiyi saitaga ya zauna saman kujerar gaban mirrow din nan tata dai ya daura qafa daya kan daya yana karkad'awa da takalmansa bayan hannuwansa dayakai bayan wuyansa shima yana wasa da yatsunsa anan.
shima maganarsa qasa qasa yace"ok kije ki gwada bud'e gidan in su small dad suka farka suka ganmu tare Yaya knn?
kinga zaifi kije daki fara budewa inyaso saina biyoki daga baya OK?"
shiru tai tana tunanin kumafa haka ne, bari to taje din ita ta gwada..
cikin sand'a take tafiya harta kai bakin qofar wajen kenan ta d'ora hannunta qarar ta6a kubar ne yasa baba Ismail tashi zaune danshi daman yana d'aya daga cikin mutanen nan marassa nauyin barci motsi Kad'an saiya tadasu koda kuwa na juyin kwanciya ne muddin da mutum kusa dashi saiya ji kuma ya farka to uwa uba kuma kubar gidan Nasu mai d'an q'ara CE.
sai jitai kawai maganarsa yana cewa"ah heenduh ina kuma zaki da dare haka?"!
a mugun razane ta juyo garesa tana wuri wuri da idanu sam takasa motsin kirki saida ga baya dubara ta fado mata tayi saurin cewa"ay..ay nayi zaton ba'a rufe gida bane shiyasa nazo rufewa baba"
tayi maganar gabanta na bugawa dass dass dasssss,
"Aa heendu taya zamu kwanta gida bude ai an rufe dan haka kema kije kiyi kwanciyarki"
haka ta nufi dakin jikinta a sanyaye da'ace dashi din suka fito aidako kwabarsu tai ruwa qwamma ma da Allah yasa yayi dubarar ta fara fitan.
shikuwa daman yana hangen komi akeyi a waje ta labulen tagar tata dan haka tana shigowa yadinga mata dariyar mugunta qasa qasa.
haushi taji ganin yanda yaketa sata tsaka mai wiya yau dan haka harara ta wurga masa tareda murguda baki tace
"akace maka na sare ne? aibawai haqura naiba saika bar gidan nan yau bazaka kwanar mini anan ba qatoto dakai haka kaje ka danne ni wajen kwanciya"
dariya sosai mgnr tata taso basa amman saiya kanne yace "better" ya koma yayi zamansa kan chair din yana latsa wayarsa ma.
sau uku tana son fita tana shakku ana hud'un ne tasakeyin qundun bala ta fita wannan karon yitayi Kamar zata nufi kitchen aikuwa taji muryar baba Ismail again yace"wai miya hanaki barci heenduh na a daren nan sai fitowa kike yawanyi dan Allah kada ki sake fitowa haka nan kiyi kwanciyarki ki huta inda ance dare mahutar bawa ne, danma inason tashi qiyamul laili nima yau...shikenan mgn ta qare kuwa inda har zaiyi sallar dare tasan babu doctor khaleepa babu fita a gidan nan dan inhar baba Ismail yafara sallar dare sai da asuba yake ajiyeta sannan.
dan haka muryarta a sanyaye tace"to baba daman naji qishi ne shiyasa nazo shan ruwa wajen"
tayi mgnr tana mai bude randar ruwan kamar gaske ta debo tai musu shan dole tana cewa inama yanda mama keda nauyin barcin nan haka baba keda shi shima din dabazata wahala haka ba tasani"
tazo wucewa daki knn tace"saida safe baba" yace "to heenduh na Allan bamu alherinsa" "aminn baba"
a haka ta koma dakin ta rufesa yana zaune abinsa yanata gem a phone din nasa kuma yanajin komi da suke fada itada baban.
kayan barci ta dauka tareda shigewa yar kusurwa bayan ta kashe qwan dakin ta saka sannan ta fito ta kunna kwan.

dubanta yake a afakaice ya tabe red lips dinsa yace a ransa"ji abunda yarinyar nan ke boyemun saikace bansan kalarsu ba da zubinsu ba mtss.
ga mamakinsa gani yai ta shimfida tabarma a qasa ta shimfida bargo gamida ajiye filo akai ta dubesa tace"ai sai kazo ka kwanta ga shimfida nan nai maka inda ka qwaqufe sai ka kwanar mana a gida." tayi maganar tanai yatsune fuska tareda zama kan kujerar daya bari ta gaban madubin, ta zauna ta warware parking gashin kanta daya zubo har wajen qugunta nan ta hau linkesa dan taji dadin barci.
zuba mata idanuwa yayi na tsawon lokaci yana kallon ta, ahankali kuma idanunsa suka sauko saman tudun qugunta dake zaune a kujera cikin silikin rigar tata sai wani motsawa suke. hakan ko baqaramin dauke hanlalinsa zuwa gareta yai ba batareda daya zata ba.
baro bakin tagar yayi ya isa bayanta ya tsaya.
tana kallonsa ta madubi ta wani share taci gaba da gyaran gashin ta tana rera 'yar waqarta cikin siririyar muryarta wacce take so sosai sosai fiyeda kowace waqa ta hausa wato waqar *dasauran kallo*.
tayi tayin abinta shiko yana saurarenta saidaga baya ya juya ya dubi shinfid'ar datai masa ya kuma kai dubnsa ga tata ta katifarta,, girgiza kai yayi tareda sakin wani murmushi dan yasan yanzun nan zaiyi maganin ta.
heenduh kuwa tana cikin waqarta babu zato taji hannunwansa saman wuyanta yana shafawa daga bayan nata dayake a tsaye.
yitayi kamar zata tashi aiko yayi saurin ida tusa hannuwan nasa ta saman rigarta zuwa cikin rigar tata ya ruqo balloons niplles dinta yana murzawa.
tuni dud wani qoqarin tashi datakeyi a lokacin taji ta dainasa dan jikinta yayi mata dayi mai tartare da saukar kasalalliyar kasala mai tsananin gaske.
wani dan qarfi ne taji ya saukar mata dan haka tai saurin janye hannunsa ta miqe tsaye batareda ta kallesa ba tace "Kaje dan Allah ga shinfidar kacan katsaya neman mgn."
Tayi mgnr tana mai kashe kwan dakin ta kunna fitilar 'yar qarama mai jonin wayar nan wacce kecin batira uku sbd dakin ya d'anyi musu haske koba yawa tunda babu kyau kwana cikin haske kamar yanda malamin islamiyyar
su ya fada musu in kana kwanciya cikin haske a dare to in akayi sa'a kuma da shed'anun aljannu suka d'auko d'an uwansu marar lafiya zasu iya sakowa bil'adama shi a jiki saikaga mutum yaita shan wuyar ciwo na duniya.
to daman tunda taji wannan maganar gargadin mlm dinnasu daman gata uwar tsoro saita keta kiyaye kwanciyar a haske sosai dan ance zama lpia yafi zama dan sarki muddin kabi mgnr dake cikin tsarkakkun lititttaifan nusulunci zaka wanye lpia.
bayan ta kashe qwan Kai tsaye shimfid'arta ta nufa da niyyar kwanciya bayan ta qara number fankan dakin dan zafi bata rainasa ita koyayane a jikinta.
bata zata ba sai jin takunsa datai ya had'e qirjinsa da bayanta ya rungumo cikinta yasaka mata bakinsa a kunnenta ya d'an lasa sannan yace muryarsa it's very low "tayaya zaki raba mana shimfida headache alhalin muna matsayin halattattun juna?"
janye jikinta tai ta juyo ta kallesa cikin haushinsa tace
"kamanta kanada zarah zabin mamanka?"!
tana fadan hakan ta juya zata tafi yayi saurin rungumo cikinta ya hade bayanta a jikinsa karo na 2 sannan yasake kai bakinsa kunnen ta yace

"kincika kishi headache ga alama anya kuwa nan gaba ba kulleni zaki dingayi a gida ba? yayi mgnr cikin tsokanarta.
hararsa tai ta yamutsa fuska yasake cewa "kuma nina CE miki inason zarah zan aureta? kokinji hakan a bakina headache na?
Sosai taji dadin mgnr tasa amman saita qi gwada masa hakan saima banbare hannuwan sa datai a saman cikinta ta juyo ta dubesa tareda zuba masa idanunta qal qal dasu cikin tabe Yan lips dinta tace
"kama so ta din ni ina ruwana ma"
shima dagowa yayi ya dube cikin idanunta tuni ya gasgasta mgnr tayita ne bawai har zuci ba, nannade hannuwan rigarsa yai yabarsu dai dai Rabin hannuwansa yasha gabanta ya biyota ta dinga ja kuwa da baya baya bata ankara ba saigata ta fada saman katifar tata kanta yunqura ta taso har yayi saurin dora mata nauyin qirjinsa saman shafaffen cikinta da dukiyar breast ballons dinta dasuke tsattsaye bum bun.
harsaida tayi wata yar qara yayi saurin juyota ya koma qasa ita kuma tadawo samansa nan suka sake zubawa juna idanu kowa na saqe saqe a ransa.
tashi tayi zaune ta daure fuska ganin yanda yasha mur shima.
shirin miqewa take daga zaunen dayake saman katifar yasa dogon hannunsa ya fizgota saiko gata tadawo ta zube saman jikinsa qugunta tsakanin laps dinsa cinyoyinsa.
kallonsa tai a marairaice dan tasan indai yai mata kalar wannan ruqon da zaman tofa qyaletan dazaiyi sai Allah.
"Pleases doctor kabarni wlh barci nikeson yi kaji pls?"
zubawa 'yan red lips dinta idanuwa yai ganin yanda take tutturo masa su a cikin shagwabarta nason ya tausaya mata ba qaramin burgesa hakan yai ba kuwa.
matsoda qugunta yayi cikin jikinsa sosai har tanajin yanda yake sake motsa jikinsa da cinyoyinsa tsakanin qugunta.
sosai ta runtse idanunta jin tudun wani abu datai wajen a cikin zaman datai a tsakan kanin cinyar tasa wanda sam ma takasa sanin miye shi abun ne haka.
rungumeta yai ya jawo masu abun rufarta ya lullubesu tana kwance cikin jikinsa dan yahanata ko motsawa sakamakon wani q'aqqarfan ruq'on dayai wa west dinta lokacin.
gaba daya ya matseta cikin jikinsa banda shaqar numfashin juna da sukeyi basu komi.
hannunsa yasaka ya kamo band din gashinta data nunke ya warwaresa saigashi gashin ya sauko a fuskokinsu.
tattara mata shi yai ya maidasa gefen wuyanta yana mai
 shaqar qamshin gashin nata.
hannuwansa ya
d'aura saman hips dinta yana d'an matsa mata su na tsawon lokutta. sosai heenduh takejin dadin hakan shiyasa ma ta qara narke masa a jiki.
hakan kuwa datai najin tausasan breast balloons nata na nutsar qirjinsa ba qaramin kwadaitar ta yaji ta qaru a ransa ba.
cigaba yai da shafa qugun nata yana sakar mata wani deep kissing a lungu da saqo na wuyanta tareda saka yatsunsa guda hudu na kowane hannunwansa yana sosa mata kunnuwanta zuwa qasan ha6arta.
tuni ta fara sakar masa nishi nishi tareda saka hannuwanta biyu ta qanqamesa gamm a jikinta

ta matso da fuskarta a tasa tana goga masa kuncinta saman nasa idanunta a lumshe dan sosai take jin kuma dadin kasancewarsu haka dud inta kallesa taga wannan handsome guy din nan mallakinta ne ba qaramin farinciki ke qara ratsa mata sassan jiki ba.
tsurawa yar baby cut din fuskarta idanu yai ganin ta runtse idanunta hkn yasashi saka mata yatsunsa kan lips dinta yana shafawa a hankali.
abinda ke qara jansa gareta kuwa shine yanda jikinta koda yaushe ke qunshe da daddaden dumi gakuma yanda fatarta keda taushin gaske shiyasa ya qara jawota samansa wannan karon bai tsaya komiba ya saka mata bakinsa cikin nata yana playing sucking lips dinta.
a zatonsa zata hanasa cigaba da abunda yake matan saima yaji ta tallafo fuskarsa sosai da hannuwanta tana masa nata kalar salon daya koyar da ita itama.
tamfar baqin kissing haka suka komawa junansu sosai suke tsotsan bakunan junansu a nishad'ance har bassa fatan abinda ka katsesu ma sukeji a lokacin dan lokacin harya maidata qasa shikuma yayi mata runfa.
saida ya tabbatar daya sakar mata kasala sannan yayi shirin fidda bakinsa cikin nata aiko dasauri yaji ta jawosa ta fuzgo wuyan rigarsa da qarfi saiko gashi ya sake fadowa kanta kanya yi yunqurin wani abun yaji harta qara had'e bakunansu tana shan hot lips nasa.
murnushi yasaki a ransa yana fadin perfect couples munyi matching nidake kenan headache need our between.
saida tasa ya koma ruwa tsundum shima dan daman yaso barinta dan jindayai hucin numfashinsa nason fita waje gudun kada su baba Ismail sujiyosu yasa shi kawai d'aga mata q'afa ba komi ba, amman inda ta nuna masa bata gaji ba aishi daman hakan yakeso ai.
dan haka ya dage yana ta shawo sugar lips dinsa shima babu qaqqautawa.
hannuwansa ya zube saman hannuwan rigarta yayi qasa da ita.
da sauri ta basa baya tayi rubda ciki bayan ta rungume breast dinta jikinta na rawa dan ita bawai haka take nufi ba data jawosa.
dasauri tajawo abin rufar ta rungumesa a qirjinta ta wani qudundunesa sosai sannan ta tashi zaune danshima a zaunen yake dud yakoma kalar tausayi aransa yake cewa wannan headache muguwa CE tasashi a tsaka mai wuya kuma ta zille masa.
"Pleass headache ki bani haqqi na wlh bakiji yanda jikina kemun ba da mara na ciwo zatayi mun",,,
juya fuskarta tai tace"haqqi anan gidan kuma?' tayi mgnr fuskarta a yamutse cikin yanga.
zuba mata idanu yai ganin yanda gashinta ya rufe mata bayanta da qirjinta har gefen fuskarta ma gashi iskan fankar sai kadasa takeyi yana dan nimmiqewa gwanin sha'awa.
"to miye ba adakin matata nike ba"
tabe lips tai tace
"saika bari saika koyi so sannan"
cikin mamaki yace "so? so kuma ? na koya naima wa?
hararsa tai tace"ina mazaunin matarka bantaba jin ka furta Kalmar kana sona ba shine nikuma kk so ka cuceni na baka kaina inka samu abinda kk so daga baya saika barni kaje ka auri zarah za6in momynka ko? nikuma gani wacce aka cusa maka? koda yake ance daman matar cushe batta daraja."
tayi mgnr hawaye na sauko mata.
sosai hankalinsa ya tashi dan haka babu shiri ya gangaro ya kwantar da kansa jikin cinyoyinta

ya zuba mata idanunsa tareda daura hannuwan
sa saman qirjinsa ya rungunesu..yakai minti kusan goma yana kallon kukan nata sannan kuma a hankali ya miqa hannunsa saman fuskarta yana share mata hawayen ganin taqi daina zubosu yasashi miqewa zaune ya jawota kusa dashi tayi saurin qara matse malullubin nata a na shanunta danjidatai zai zame qasa.. shiko ma sam hankalinsa ba'anan yakeba burinsa kawai shine kukan nata ya tsaya cak sakamakon zafin da zuciyarsa ke masa dud a saukar qwalanta guda daya yanaji shima kuma kamar zaiyi kukan ne.
dud yanda yaso ta daina kukan kasawa yayi dole tasa yai maganin abun ta hanyar maida bakinsa cikin natan dayai yarufe gam yahau cigaba da rud'ata harda saka harshensa yana shanye mata hawayen sanna fa yasamu tai tsit da kukan Nata.
idanunsa sunyi jajir ya dubeta yace
"waye ya gaya miki bani sonki headache?
dasauri ta dubesa ya gyada mata Kansa yace"tabbas ada bansan wani ma'anar soba headache saidaga bayan tafiyar danai kwanan nan kan batun fiddo kayan dady a patarcout
lokacin ne nasan kina raina matuqa Headchee dan dud kowane motsi dazanyi saikin shigo rayuwata amman ban dauki abun serious ba dan banyarda da abunda zuciyata Ke nufun
ba a kaknki
..koda nadawo daga tafiyar saina dunga jin kishin ganin kina Huld'a da samarinki zafi nikeji har cikin raina... kamo hannuwanta yai suka zubawa juna idanuwa babu mai kaucewa yaci gaba da cewa"zaki cemun shima wannan ba so bane headache?wlh bn qara amincewa inajinki a raina ba saida Dr mus'ab abokina yaqara fahimtar dani akan dud wannan seems din danikeji gameda ke a so yake zuwa,,
hada hannuwanta yai ya aza bisa fuskarsa idanunsa a rufe yace"zaki soni nima headache a matsayina na abokin rayuwarki?
wani farinciki ne tsantsa taji yana ratsata dan haka a guje ta fada jikinsa tana matsan hawaye na Allah ya karbi adduarta son ta ya bayyana a zuciyar doctor.
tuni farinciki yaji yana shigarsa ganin dayai tayi na'am da mgnrsa dudda bata basa amsaba ai ance alamar tambaya atambayi fuska.
ahankali ya balle botiran rigarsa ya dagota cancakat ya runguneta cikin jikinsa dukkansu suka runtse idanu da qarfi sannan ajiyar zuciya ta biyo bayan hakan Wanda hakan yafaru ne sakamakon yanda shi yaji lumewar Brest balloons dinta cikin faffaden qirjinsa yayinda itakuma taji kwantaccen gashin qirjinsa yana dan tsirar mata dukiyar fulaninta tanfar ana mata Susa a Kansu takeji dan haka sosai tasake shigewa tai luf kwance a jikinsa.
jitai yasaka bakinsa a kunnenta yace a hankali yana lasan gashin lumsassun idanunta "kinason samun baby headache na?na baki baby?
pleass kibani baby mai kamarki kuma ya dauko hasken fararen idanun nan naki masu tsadan samun kalarsu kinji ko sugar lips with Brest na?
gaba daya ta zaro fararen idanuwan nata kuwa tana kallonsa dasu a tsorace wanda hakan kuwa datai baqaramin kyau yaga taqara masa ba dan haka qara matsota cikin jikinsa yayi da qarfi yana kissing dinta kota ina a fuskarta yana cewa
"Please headache kibani baby mai kamarki pleasssssss pleaseee b... because.. of...I love you with all my heaertttt you hear me my headache??.....
turo baki tai gamida turesa tajawo malullubin ta qara rufe jikinta tayi kwanciyarta tana murmushi

a ranta.
shiko cikin bugawar zuciyarsa ya ke dubnta tsoro ya shigesa na tunanin cewa kadafa headache tace zata garasa itama ne tace zata rama abubuwan dayai mata a baya???
tuni kuwa yasha alwashin kar6ar kowane kalar zazzafan horo a gareta matuqar zata soshi shima koda baikai yawan sonda yake mata ba kuwa. dan haka jiki babu qwari yaqara kwanciya bisa bayanta sakamakon rubda cikin dayaga tayi cikin rada yace "ki daina kwanciya rubda ciki headache na kinji ko"
jin tayi masa shiru taqi kuma gyara kwanciyar hkn ne yasanya yasaka hannuwansa ya juyota tareda daura bayanta a jikinsa yazamto suna kallon fankar Sama dake basu dadaddar iska. dudda kuwa khaleepa yasaba da iskan ac Amman sai yaji hakanma yayi masa kodan yana tareda abar son na headache yasa Bayya banbance iskan fankan talakawa data masu shi ta ac ne oho...

~Love you all dears~ ~😻
By
Xexen Fasaha
[2/13, 10:20 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO!!!

Story and writing by Xayyneb💤💤

Fasaha online writers.

🌳Imparting valuable knowledge and intertaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hauwas~.

👁️📦👁️
🅿️🚹
T unda heenduh ta shiga d'aki kwance take rigingine tana kallon silin yayinda wayarta ke aje saman shafaffen cikinta hannunta na akai kuma, tashiga tunani mai zurfi dan sosai itama ta damu da rashin dawowar baban har zuwa wannan lokacin.
gashi kuma bayyada waya bare akirasa aji ko lafia shuru.
jin wayarta na ringing ne yasata
da sauri ta duba ganin kowaye mai kiran...6ata fuska tai ganin musaddiq ne yasata daga wa akaro na biyo da shigowar wanj kiran jiki a sanyaye.
"halo my beautiful lady hope dai kina lpia da kuma wannan ne Nike roqon a yafe mana bamusan miyasa inmun kira ba'a amsa mana ba kuma koda text mukai bawani reply please tell me my beautiful baby miyasa?"
yatsuna bakinta tai sannan tace"no bakamun komi ba bandai jin dadin jikina ne shiyasa kaga

hakan,amman yanzun nasamu lpia"
"Ayya to alhamdulilla dan bansan naga komi na matsa miki 'yar kyakkyawa ta".
dakatar dashi tai da fad'in "naji ngd zan yi wani abu yanzun musaddiq"
"to babu laifi nima ina kan aiki ne na turesa gefe nakiraki da taraddadin kozaki dauka koko? Amman yanzun naji wani qarfi mai tartare da kuzari ya zomin inda naji muryar beautiful na"
"Ok ngd tum"
abinda tace knn yaji tana qoqarin ajiye wayar dasauri yace"ah pls wait beautiful baby na kinko duba message nawa?
a taqaice cikin qosawa tace "zandai duban tukun"
dasauri yasake cewa"no bama saikin duba ma daman namiki text dinne sbd tafiyar gaggawa da tatasomun zuwa wani aiki a Cameron har tsawon 2 month shiyasa nai mk text din, yaci gaba da cewa nayi missing dinki na rashin ganin wannan 'yar kyakkyawa ta kamar na biyo iskar duniya ta nikeji wlh kodan na ganki heenduh sarauniya na Wanda ba'a cika samun mai kalar sunanki ba sai gidajen masarautan mu"
hmn kuma ni gashi banje masarauta ba amman kuma Allah yaban sarauniyar kyawawan duniya" murmushi tai sannan tace
"Sry musaddiq kamar gobe ne ay zaka gama aikin ka dawo inda kwanakin ba suna jimawa bane yanzun ko?"
sauke ajiyar zuciya yai yace"naji dad'i 'yar kyakywa ta shiyasa nike q'ara sonki dan kin iya kwantarwa da mutum hankali"
batace komi ba sakamon tuno khaleepa datai a yanda suka kasance a daren jiyan nan da kalar kuma dramar da akasha kan fitarsa.. bata ankara taji murmushi ya su6uce mata tana mai rufe idanunta taq'ara miqewa sosai kwance a katifar tata tana mai kuma q'ara shaqar q'amshinsa daya had'e dukkan katifar tata da marufin da suka lulluba kuma dashi.. sam shaf ta manta da musadiq nakan layi ma it's, saidai ta tsinkayosa yana cewa"alo alo
'yar kyakkyawa ta kina jina kuwa ko network ne ya riqeki minke banjinki?,
furgigit ta dawo tunanunta tai saurin tashi zaune saman katifar lokacin ne kuma tad'an sausauta murya tace"network ne amman ynxun yy daidai"
"yawwa shikenan to 'yar kyakkyawa ta amman dan girman Allah ki taimaka ki turomun pics din da kikai mun alqawalin zaki turomin kuma shiru?
tana d'aya daga cikin mutane masu cika alqawali saidai ko halin mantuwa yasa ta mantan.
dan haka tace
"ok Sry na mantane afuwan"
cikin wanj jin dadi yace"emhem koda naji dan nasan 'yar kyakkyawa ta batta qaramar mgn intace yes to yes ne haka ma in tace no tofa no d'inne"
hakanan mgnr tasa tasata murmushi dan musaddeq akwai barkwanci lokutta da dama kobatai niyyar masa abuba saikiga tai masa dan tanasan mutum Wanda yasan mutuncin mutane dukiyarsa bata sa yadinga d'agawa ba kamar yanda kawunta keyi.
amman a fili sai tace
"zan turo maka ynxun kayi online you can see it"
"tanxxx somuch 'yar kyakkyawa ta ki gaisar mun dasu mama dan Allah"
"Tom"
abunda tace knn ta latse wayar ta Shiga bincika photos nata nanta tura masa har guda uku

babu Wanda naturally zallar kyaunta da dirinta bai bayyana ba kuwa a cikinsu.
koda yagansu kamar zai rikice mata yabaro garin cameron yakeji yadawo ya ganta a ranar ya juya, saidai da qyar ta shawo kansa ya haqura ta hanyar yimasa voice message mai sakawa mutumin da ake son rarrashinsa cikakkiyar nutsuwa gamsasshiya tofa sai snn ya haquran yaso ta tsaya suyi chating amman ta zulle masa tana mai masa tunin aikin dazata taya mama sannan fane ya haqura badon yaso bane suka rabun.
tana kashe wayar kuwa kamar daga Sama ta jiyo muryar baba Ismail a tsakar gida yana sallama.
Allah sarki heenduh aida gudu ta miq'e kuwa tayo waje ta iske mama Zainab tsaye a gabansa riqeda hannunwan baba Ismail din tana tambayar sa ina ya shige tun asubar yau ne a rud'e.
kan ya bata amsa kuwa har heendu ta ida qarasowa wajen ta rungume baban nata cikin murna harda 'yar guntun qwallan ta tace
"babana munyi kewarka nida mama hankalinmu ya tashi sosai da rashin dawowar ka gida".
murmushi baba Ismail yayi bayan ya shafa kan heenduh sannan ya d'agota ya kamo hannunta da hannun mama Zainab suka qarasa kan tabarmar dake tsakar gidan suka zauna.
mama Zainab tasake miqewa ta d'ebo masa ruwan randa masu sanyi sannan ta dawo ta durqusa a gabansa ya karba tareda cewa"Alhamdulilla zainabu sannunki"
zama mama Zainab tai gefensa tana dubansa cikin tsabar murna koda baikai ga cewa ga abinda ya tsaida sanba tasan tana cikin farinciki ma'ishi kuwa na ganin mijin nata lami lafiya zaune a gabanta itakuwa miyafi wannan farinciki a gareta cikin marecen ranar yau bayaga data cigaba da hamdala wa ubangiji a cikin zuciyarta kamar yanda ta fara tun farkon ganinta dashi a shigowarsa cikin gidan.
"Huuh!! kai masha Allah Alhamdulila Allah mungode maka da kayo ruwa duniya Allah shi qara mana lpia dan darajar ma'aiki saw."
abinda baba Ismail yace knn bayan gama shan ruwan dayai dan kuwa ba qaramar qishirwa ya taraba
da "aminn"
 suka amsa.
sake sauke ajiyar zuciya yai sannan ya dubi mama Zainab yace"kunjini shiru ko? Wlh nima hankalin na nan gida gunkun dan nasan zaku damu daman... kuma bakome ya jaza rashin dawowata gida ba sai rashin lpian baba yawale dan daqyar ya gama mana jam'en salla a masallaci da asubar n@n , tofa koda yagama kasa ma tashi yai daga nan inda ya sallame sallar...mutane nan muka rufesa ganin ko mgn yakasa ne yadafe qirjinsa da hannuwansa yasa yaya salis da shima yazo sallar a masallacin bada umarnin kada a d'aukesa zuwa gida kmr yanda wasu kW cewa yace zaifi kyau street awuce dashi asibiti
to fa kowa saiya aminta da hakan dan sungano cewa ba'a d'au ciwo a kaisa gida a jinginar ba dudda dai lpia ta Allah ce a ko'ina ka zamo to Amman Allah shiyace ka nemi sauqin magani awajen bayinsa da yabaiwa baiwar damar sanin hakan dan samuwar lafiyar sauran bayin nasa marassa lafian.
saida yaya salis ya koma gida ya dauko motarsa sannan muka nufi dala hospital wai Ashe su yajin aiki suke shiyasa muka juyo muka nufi hospital nasu khaleepa inda daman ita asubiti ce mai zaman kanta.
to nan aka karbesa emergency aka Shiga dashi dan checking nasa mune tun abun asuba saifa

yanzun muka samu muka dawo gida nida Yaya salis din danshi baba yawale sun basa kwanciya sakamon hawan jininsa daya taso masa lokaci daya ga kuma massara harda tari babu qaqqautawa.
amman yanzun alhamdulilla inda yasamu barci shiyasa muka dawo gida danni komawa zanyi can wajensa da zama inda mune dai dolen nasa makusantansa a yanzun masu kula dashi" Mama Zainab tace
"kaiii subhanalla ubangiji ma'allahu yabasa lpia"
"aminn" cewar heenduh da baba Ismail dan har a ran heenduh ta tausayawa mai ran qarfenta fa ciwon nan da akace ya taso masa lokaci daya.
sunyi shiru babu Wanda ke cewa komi dan matuqa tausayin baba yawale matuqa yai tasiri a zuciyar su.. babban abinda me tayarwa da baba Ismail hankali shine tunaninsa ina zaisamo kudin dazai biya asibiti da kuma sauran hidimar can?
shiru yasakeyi kawai yana kiran Allah a ransa tareda tazbihi yanawa annabi salati..
suna a hakan ne kuma sukaji
sallamar almajirai iriyar yan matasan samarin nan su wajen goma kuma kowanne Kansa daukeda buhun shinkafa wani kuma taliya ko macroni dasu man turkey da manja suma jarka biyar biyar kamar yanda buhun shinkafa da na su masara da cattons na taliya da kuma macronin suka kasance da yawa suma.
dan wani zaiyi tsammanin cewa inyaga kayan wani dan matashin shagon saida kayan masarufi za'a bude.
dady salis ne ke biye dasu a baya saida ya sallamesu almajiran da suka gama shigowa da kayan duka sannan ya zauna aka gaisa ya dubi baba Ismail yace"qanena kaga KO yanzun nan tafiya ta kamani can garin dana baro yayan mama ne baya lpia shima, kuma tareda Maman zamu tafima da Iyalan nawa dan dubosa"
sosai su baba Ismail suka jajanta masa wa rashin lpian yayan maman salis din kuma surikinsa.
yaci gaba da cewa
"ga abinci nan qanena sannan kuma.... yad'an karkata aljihun rigarsa ya qirgu musu kudi dubu 150 ya miqawa baba Ismail yace"wannan kuma kwayi hidimar data taso a gida sannan ya sake qirgo wata dubu 60 daban ya sake miqawa baba Ismail yace"wannan kuma a siyawa baba yawale komi yakeso yaci inda narigaya danaje na gama biyan kudin gado harna tsawon kwanakun dasuka shard'anta masan zai kai dakuma magungunan dud na siya nan yagwadawa baba Ismail bill din na asibitin dakuma qa'idar yanda baba yawale za'a dunga basa magungunan nasa har jikin nasa yayi daidai.
sosai baba Ismail ke fiddo hawaye bayan gama karanta bill din dayai danshi tunaninsa dabadan Allah ya kawo musu Yaya salis d'unba tayaya zasu iya biyan kudin nan na private hospital dinnan?
dudda suna kulawa da patient dinsu sosai amman asibitin bata kamarsu ce bane masu qaramin qarfi inda su tasun masu qaramin qarfin ma aikata sunyi yajin aiki nan dai.
ahaka yahau godiya da fadin "ngd sosai Yaya salis Allah shi qara arziqi mai amfani haqika ka riqe zumunci kadawo kana mana abinda d'an uwan na ya gaza munshi a rayuwa wato taimakawa rayuwar da Mike ciki a buqatance ngd Allah saka da alheri yajiqan magabata"
dafasa dady salis yai yace"haddasu baffa da inno da sauran musulman Allah amunnn, sannan kuma shima yayan naka zai dawo ya kuma soka kaida iyalinka ya qaunaceku da izinin Allah

wataran saidai labari kaji ko qanen?"
gyada masa kai baba Ismail yayi cikin qirqiro murmushi sannan dady salis yace
"yawwa kuma insha Allah da zarar na dawo zansa a gyara gidan nan yanda ya dace kuma saimu zauna dakai kafadamun kalar sana'ar da kakeson farawa kadaina zama bakin hanyar nan saida cefane dan Sam banson hakan har a raina, kuma ma sainaita ganin kamar cewa mutane zasu zageni kan nakasa tabuka maka komi dud yanda muka taso a zumuncen nan uwa 'yan uwan jini."
Girgiza kai baba Ismail yai yace
"bazasu zageka Yaya salis domin halak d'ina ne na fito nema dan haka dud wani mai kaifin tunani bazai zageka ba koyaga laifinka dubaga d'an uwana na jini ma yana raye bai zamemun dole ba amman kai gashi ka zamemun".
har aran dady salis d'abi'un qanen nasa Ismail kan burgesa na tsagwaron nuna tawakkali da kuma abin duniya da bai rufe masa ido ba.
kan yace wani Abu wayarsa tai ringing ganin matarsa CE wato mmn baby amnat yasashi miqewa da fadin "nina wuce qanena suna can Suna jirana zamu tafi..dasauri heenduh tace"dady salis pleass inkun dawo zaka kawomun baby amnat ta kwanar mun? murmushi dady salis yayi yace"Kunlun saita mun zance ki itada dai Aunty beauty nakaita gunki harmafa ta fadawa mamanta ke? Amman dazarar mun dawo insha Allah zan kawo miki ita heendatuh"
cikin murmushi tace"yawwa thanks dady salis adawo lpia.
saida baba Ismail yarakasa waje sannan yadawo ciki zamansa keda wuya wayar mama Zainab dake can cikin dakinta tahau ringing duban heenduh tai tace"jeki miqomin ita heenduh".
koda taje ganin sunan mama jamila wato mamar mama Zainab din yasata fitowa ta miqawa maman tana cewa qawata CE ke kiranki Ashe mama na"
hararta mama Zainab tai tace"kifa kiyayeni heenduh na fada miki fa"
dariya heenduh tai kawai takoma ta zauna kusada baba Ismail.
mama Zainab bata sake bin ta kanta ba ta d'aga wayar da cewa
"Assalamu alaikum mama barka da marece... shiru tai tana sauraran mgnr mama jamila din dasauri sukaji mama zainab tace
"Innalillahe wa'inna ilaihirraji'un yaushe yarasu mama??..
dutta rud'e cewa takeyi to.. too gani nan zuwa..
dasauri takashe wayar baba Ismail suma sai tanbayar ta waya rasu ne? sukeyi.
cikin hawaye mama Zainab tace"kaka liman malam ne (baban mama jamila dake zaune garin zaria).
Allah yaimasa cikawa yanzun nan.
innalillahe.....tashi zakiyi muje tare"
saida Hjy Hadeeza tad'an gantsara sakamakon wata cakar zugar zafin ciwon jikinta dataji yaja ta soketa,, runtse ido tai tace "kai wash Allah na, daqyar tasamu takoma dai dai lokacin sannan ta dube Hjy firdauseey tace"yafa kamata ki cire tunanin boka marakusa a ranki inda ya rigaya daya mutu, kuma Alhj mukhtar dai kin samesa yanda kikeso to miye yai saura ana damuwan kuma?"
sauke ajiyar zuciya Hjy firdauseey tai snn tace"eh dudda hakan Amman kamar in inason aqara mun wani zazzafan aikin ina kikega zan samu kamarsa? Ai babu"
taqarashe mgnr cikin dafe kanta tana cigaba da sharben kukan baqinciki ga kuma zafin bulalar jikinta dake mata zugi dan abun kam 2 ya hade mata,,wanda tanajin rabonda a bigeta tun tana qarama sai yanzun da girmanta tasha zana daga qaton qauye harma kuwa yana neman zagwanye mata fatar jiki da dukan.
dafata Hjy Hadeeza tai tace wannan ai badamuwa bane inada wani tantirin malami aikinsa yankar wuqa ma yai masa kadan wajen sauri, saidai shi fa dole sai yayi amfani dake sannan zakiga aiki da cikawa, dan shine yaimun aiki kan alhajina dadyn zarah wlh ko kara Alhj bai qetarawa saida umarni na,
saidai kuma shi aikinsa sa'a ne saudayawa zakije kita samyn biyan buqata, sau dayawa kuma zakije kiji shuru, amman biyan buqatar tafi shirun yawa dan haka ki kwatanta kigani"
"yanzun saida kuka watse dashi knn snn buqatarki ta biya?
dudda ciwon dake jikin Hjy Hadeeza saida ta kece da wata kafiran dariya tace"yo miza'a fasa? kuma wlh kijima in gaya miki yafimun Alhj dadin harka, sainaga dama ma nike bawa alhj kaina inbangani ba saidai yahaqura da jarabarsa a ranan nai kwanciya ta, dan haka nan siddan fa in naji kwad'an Mlm har zagawa nike kobadan aiki bama musha budirin mu"

wata dariya suka saka dukkansu snn Hjy firdauseey tace"wani ma yayi rawa balle dan makadi da abinsu,
yanda banda mahaifar nan ma bare naji tsoron ciki ai na amince Qawa indai buqata zata biya qarewar ta gaba yake neman customers dinsa wlh indai zaimyn aiki mai kyau kota baya na yanemi tsab zan basa"
Hjy Hadeeza tace"mikikece na baka na zuba?
ay Indai Mlm kalla ne babu ta inda bai Neman mata, sake darawa Hjy firdauseey tai tace"babu marsala zaki kaini cikin satin nan yamun aikin nan nasu salis dan bawai haqura zanyi b....shiru tai ganin khaleepa ya shigo falon gidan fuskarsa ad'an sake wanda ga alamu yana cikin farinciki Amman dayake muskilin qin qarawa ne saima fuskar tasa bata bayyana ainahin farincikin nasa ba sosai.
gaisheda Hjy Hadeeza yai snn yazauna saman hannun kujerar da Hjy firdauseey take zaune cikin kalar murmushinsa yace "surprise Momy dady yace mun yanzun damukai waya yana nan sauka zuwa Nigeria gobe ko jibi"
wani ihun murnar dadi Hjy firdauseey tasaki tareda kama khaleepan tariqe gam tace
"amman shine bai kira ni yafara myn surprise dinba?"
tayi mgnr tana wage baki.
"Sryy momy yace ai yaita kiranki dazun baki holding ba"
dasauri ta zage jikkarta ta fiddo wayarta ta duba nan take kuwa taga har 8 missed cull na Alhj mukhtar din.
nan tace"aikam dai gashi yakira kuwa Ashe,,shiru tai tana tunanin ina zataji Qarar wata wayarsa tana can tana shan duka ga qaton Allah ta'ala cin tuwon qauye.
Hjy Hadeeza ma cikin zuciyarta sosai tayi farincikin jin Alhj mukhtar zai dawo Nigeria koba komi tafara sunsuno qamshin auren zarah da khaleepa knn kamar yanda Hjy firdauseey ta maganta mata mgnr auren wato inya dawo.
miqewa khaleepa yai zai fita nan tayi saurin cewa "mai tsada ina buqatar magani"
dan dakatawa yai tareda juyowa yace
"Momy na jia fa dana kawo miki?, koba su kike so ba ne?"
kai tsaye ta lauye mgnr da cewa bayan qarasowa har gabansa datai "kagane ko maitsada na wata qawarmu ce jia wani qaton gabjejen mahaukaci ya shiga gidanta ya zaneta ram daqyar jama'a suka kawo mata dauki aka fiddasa a gidan to shinefa fatar jikinta did ta d'addaye ga jini, to kuma saidai jinin ya tsaya yanzun"
sauke ajiyar zuciya yai yace"to Momy zaifi kyau tazo hospital adubata daganan kinga sai abata magun daya dace m...
katsesa tai da cewan "a'a maitsada na munrigaya da munyi mgn da'ita naimata alqawalin zan tambayeka inda wani maganin dazata ringa shafawa ciwukan su warke to saika bani nakai mata kawai,,"
bai son cika doguwar mgn shiyasa yace"ok akwai wani cream lotion zai mata amfani ciwukan suyi saurin qamewa in tana shafasa, inzan dawo gida zan shigo miki dashi sai abata ta dunga gogawa saman ciwukan dan fita zanyi yanzun zamuje wani waje da yunus".
"to shiknn saika dawo amman kada fa kamanta katafo dashi dan Allah dan tanada tsananin buqatarsa a yau ne".
"OK Momy"

abinda yace knn yashige motarsa yabar gidan.
duban Hjy Hadeeza Hjy firdauseey tai ta zauna daqyar sannan tace
"da zarar alhji na yadawo shiknn ai biki yataso a tsakanin zarah da maitsada"
washe baki Hjy Hadeeza tai tace"aikam dai qwamma ayi a ture ay"
"Shidinne ay"
cewar Hjy firdauseey din tana faman sosa bayanta.
miqewa Hjy Hadeeza tai tace
"Zan shiga gida na kwanta nad'an huta hjyta"
"To shiknn saina kawo miki maganin knn" cewar Hjy firdauseey.
"eh ina saurarenki inda tsinannun mutanen nan sun daura mana ciwon dole, dan nikam har abada aibazan manta da mutuwar marakusa ba dud in naga ciwon nn a jikina"
Hjy firdauseey tace"qyale matsiyata Allah Isar mana dai inda bugu ne sun rigaya dasun buga tsinannun"
ahaka har suka rabu suna tsinewa su fillo gambo sanna tafice daga gidan itama Hjy firdauseey din tadawo cikin gidan tareda qara nufar bayi danta qara was
 jikinta wani sabbin gashin ruwan zafin.
misalin qarfe 8:35 pm dady salis ne shida baba Ismail zaune a sitroom din dady salis din Suna total na kudaden ribar masana'antar tasu da yaketa faman qara hauhawa.
bayan sun gama komi ne baba Ismail ya miqe dan shirin tafiya gida anan dady salis ya gyara zama yace
"dawo ka zauna qanena zamuyi mgn"
"to yah salis" cewar baba Ismail din bayan ya dawo ya zauna inda yatashi tareda bismilla.
sake qara zamansa dady salis yai yace "tunda na dawo daga dubiyan kawuna ko
yau kimanin kusan wata 2 kenan cikin ikon Allah kamun natafo daman acan na jejje wajen malaman kirki da nufin su tayamu da addu'a gameda lamarin mukhtar kuma dukkansu sun tabbatar mun da insha Allah zasu tayamu da addua gamida nafilolin dare kmr ynda mukeyi muma, kuma har suka ban shawarar ma dana dinga kai alqur'anai sadaqa makarantun allo dana islamiyya da kuma masallatai dan neman sake dacewa da ba'asan ta inda Allah zai kawo taba, kuma haka akayi dan banma iya cewa ga iya adadin alq'ur anan dana babbayar dakuma sadaqoqi ba masha Allah dai, to kuma koda ma na dawo nan haka naci gaba dabada sadaqa ga malaman addini dan harga Allah banda buri a rayuwa daya wuce naga mukhtar yadawo garemu qanena, to abunda yasa ma kaji na kawo maka wannan mgnr shine yanda wani babban malami wato Mlm Abdul Kareem yace zai bani wani rubutu dud sanda mukhtar yasha rubutun to cikin ikon Allah dud wani qullin sihiri dake jikinsa inma akwaisa to dazarar yasha rubutun nan zai game ko'ina a jikinsa wanda a hankali a hankali sihirin zai narke har yabar jikinsa zai kuma dinga kasayo sa baqiqirin a cikinsa yana kuma d'oyi, kuma zaiyi rashin lafia sbd cutar datake ficcewa daga jikinsa, dud shine ya siffatamun yanda alamomin fitar sihirin zasu fito, sannan kuma yace dud dai acikin rubutun zai hada mun da rubutun maganin kariya daga kowane jifa ko sammu daza'ai masa cikin ikon Allan yagama samunsa saidai yakoma inda aka yosa inma yatafo din.
nima dana buqaci yaimana rubutun sha daga cikin ayoyin qur'ani mai girma na kariyar a dukka iyalan namu yace in Allah ya yarda zaimana namu daban,
to yau da kumai waya da mukhtar yake cemun gobe

ko jibi yana nan dawowa Nigeria, shine kaji sanda kashigo dazun ina waya to dashi Mlm Abdul Kareem din ne nike fada masa dawowar tasa shine yace inzo gobe in amshi rubutukan namu kuma Allah yatema yabamu sa'a.
yanzun gobe insha Allah zanje dasafe can gidansa a rigasa na karb'o, kuma nafada maka hakanne kaima dan kasan lamarin'
qara kallon baba Ismail din yayi yace Kadaure qanena kadinga saka dan uwanka addu'a dan inada tabbacin wannan halayen dayake yi banasa bane d'aura masa akai kuma komi yazo qarshe insha Allah".
sosai baba Ismail yarasa bakin shi dai dazaice ga wacce kalar godia zaiwa dady salis a rayuwa, dan ya gyara musu cikin temakon Allah matuqa, wani sabon kalar son d'an uwansa kuma yayansa mukhtar gamida tsananin kewarsa yaji yana ratsa masa dukkan illahirin jikinsa, cikin goge qwalla yace
"insha Allah Yaya salis zan cigaba dasa sa a addua fiyeda kullum ma,,Allah ubangiji yasaka maka kaima da alheransa Yaya salis, yafaranta maka fiyeda ynda kake faranta mana".
cikin murmushin jin dadin adduar dady salis yadunga cewa "aminn qanena, muje nataka maka inda naga bakazo da motar kaba a qafa ka tako kazo ko?"
"Aa wlh ya salis kaizamanka ngd dan gidan baba yawale zan wuce ma shiyasa"
"to shiknn qanena kagaishe mun dashi
Inkaje"
"to Yaya salis zaiji insha Allah"
ahaka suka rabu cikin jin dadi.
yaukan tun bayan sallar isha'e heenduh keta barci har khaleepa yashigo yazauna suna gaisawa, mama Zainab take CE masa"ni narasa isalin wannan barci na heenduh khaleepa datakeyi kwanan nan au dare au rana bata taba gajiya? Tun ina fadan harna ma haqura"
aran khaleepa murmushi yayi danyasan wannan dud yana daga cikin laulayin heenduh amman a fili kuma saiyace"kotana yawan aiki ne mama?"
mama Zainab tace"Amman khaleepa dan kana aiki kuma sai ace lalacin barci yasameka? kawaidai raggwanci ne yaran zamani aiki kadan dasunyi zasuta raki"
murmushi kadan ya subuce masa kawai yana ayyanawa a ransa inama ace a gidansa ne lollipop take laulayin cikin nasu da shi kansa baisan iya adadin tarairaya da kulawa ba dazata samu, saidai inaaa babu wata damar nuna hakan a yanzun, har ransa yakejin rashin dadin hakan kuwa.
yadan jima sannan yaiwa mama Zainab saida safe yafita gidan zuciyarsa cikeda rashin jin dadin na sugar tasa dabaisata cikin idanunsa ba dud yinin yau kuwa,,
dole yahaqura da qudurin da wuri gobe zai baro asibiti inyagama aiki yazo ya ganta koyaji daidai a ransa, dayake can zai kwana yau sbd ayyukan dazaiyi na dare.
da tunanin hakan ya shige motarsa yanufi hospital din.
tunda hhenduh tagama sallar asuba taji wani amai nason tuqota saifaman maidasa take kuwa cikin yamutsa fuska da danne gefen cikinta dake ciwo yana katsawa mata.
qarfe 9 saura na safe dauriyarta ta qare danda gudu tataso ta fito ta durqushe gaban maguji tana kakarin fiddo kumallo dan babu komi a cikin nata, sosai ta galabaita, can cikin barci mama Zainab tajiyo aman aiko cikin salati tamiqe tayo waje tasamu heenduh did tayi tubus liliss ko hanunta takasa dagawa sosai.

cikin tausayin 'yar tata mama Zainab take mata sannu tareda shafa mata ruwa a fuska.
harta gama tana qoqarin miqewa mama Zainab ta riqeta tace"zauna nan bari na fito, tayi mgnr tareda zaunar da ita kan tabarma.
babu jimawa mama Zainab tafito cikin mayafinta ta fuce waje,, zuwa can sai gata tadawo tasake shiga dakin heenduh ta dauko mata hijab ta iso tasaka mata a jiki sannan tace "taso muje ga napek can natsaida mana" dudda tsananin ciwon kan da heenduh keyi saida ta dubi mama Zainab tace
"inazamu mama?"
"Asubuti kuma karki saki kice zaki misa mum tashi kawai muje dannagaji da ganinki haka heenduh kina ciwon wahala dinn kullum, haba amai badare barana Uwa wata mai yaron Ciki?, kojia cikin dare fama saida naji kina qaqarin aman nan fa a dakinki"
dammm!! heenduh taji gabnta ya yanke ya fadi, jin mama Zainab takamota tamiqe tsaye babu yanda zatayi haka tabita suka tafi asubitin.
sun zauna bin Layin ganin likita ahaka har layi yazo Kansu suka shiga, mama Zainab dakanta tadinga ma likitan bayani gamsasshe nan yayi wani rubutu yabasu yace sukai wajen 'yan awo..
babu bata lokaci sunakai takardar sai kuma aka kaisu wani dan daki nan wata nurse tace heenduh tayo fyyy tabata.
atsorace tayo firsarin tabata zuciyarta sai faman tsinkewa takeyi dan tsoro sanin datai khaleepa ta kalar wnn binciken ne yagano cikin jikinta. sunjima zaune saiga nurse dun tadawo tace
"kutaso muje"
binta sukai nan sukaga sun sake shiga office din likitan nan daya rubuta musu awon.
"Doctor ga result din mun fiddo" cewar nurse din gamida ajiye masa result din a teburin gabansa.
likitan wanda shekarunsa aqalla
zasukai 57 yadauki result din yana dubawa yace
"weldone Sera zaki iya tafiya"
"OK sir" abinda tace knn ta fice.
saida doctor ladan yagama duba result dinn sannan yadago yadubi mama Zainab sannan yamaida dubnsa kacokan a heenduh wacce kamar zata narke dan firgici takeji.
duban mama Zainab doctor ladan ya koma yi sannan yace"munduba komi kuma gameda bayanan da kikai man to wannan bakomi bane yake jazawa yarinyar haka ba face cikin dake jikinta d'an kimanin wata biyu da kwana uku"
gaba daya miyan bakin Mama Zainab taji ya qafe mata a baki tareda jin wata mummunar qishin ruwa dake shigarta sakamakon maqoshinta daya bushe qayau2.
daqyar ta kalato murmushi tace "anya kuwa dai doctor wannan inaga ba result din'yata bane ko kake fad'a?"
murmushi doctor ladan yai yace"kada ki damu munsan aikimmu kuma abunda nagani ne a rubuce shina fada miki kisani kuma awo baya qarya dan haka ga result dunku nan" yayi mgnr tareda fadin"next" saiga wani mutum yashigo ga alama shine mutum na gaba wanda za'a duba.
daqyar mama Zainab tamiqe daga kujerar datake kai tareda daukar result din tafice kotakan heenduh bata biba dan gaba daya kwanyarta ta tushe hatta tafiyar datakeyi jitake kamar ba qafafunta bane ke taka qasar ba Uwa saman iska takejin ta.
dasauri heenduh ta iskota tana gabda fita asibitin daidai inda babu yawan jama'a nan ta zube

gwiwoninta qasa gbn maman tana faman kuka hannuwanta hade👋take cewa "mama dan Allah kiyi haquri"
cikin zafin qunar rai mama Zainab tadubeta hawaye na zubowa a fuskarta itama sannan tace"ni zaki tozarta cikin anguwar nan Hindu? mi iyayenki mu muka rageki dashi daidai azancin qimar iya qarfinmu? dahar zaki je ki bayarda kanki ga wani?!!. yaushe kika zama haka heenduh? yanzun tarbiyyar danai miki kenan kirasa sakamakon da zaki bani saina cikin d'an waje?
wasu zafafan qwalla suke sharewa dukkansu ganin hankalin mutane yafara zuwa Kansu yasa mama Zainab qara share qwallan fuskarta zuciyarta kamar zata fashe dan baqinciki bama sosai take ganin heenduh ba dake zube gabnta, bayan ta share kukan taci gaba da cewa "heenduh kin ganni nan ko? to insha Allah daga nan gidanmu zan koma da zama dan bansan da wanne idon zan fadawa mahaifinki wannan ta'asar dakikai ba kije ke kuma dan kanki ga abinda kikayo" haka mama Zainab tafuce daga asibitin heenduh kuwa saka fuskarta tai cikin jikinta tana kuka wanda muryarta harta dishe, sosai takejin bazata iya taba furta cewa khaleepa ne mai asalin cikin nata ba, hakan ta kudurta a ranta dan tana tunanin in tace shine tofa batasan kallon da iyayensu zasuyi masa ba wanda take tsoron hakan na'iya janyo batawar sa da iyayenta wanda bazatai fatan hakan ba ta qwammace tabar sirrin a ranta tareda daukar dud wani hukunci dazatai *gamdakatar* dashi daga iyayenta na wahala ko kuma tsananin azaba kala kala darashin nuna kulawa kmr yanda mamanta tafara mata yanzun na juya bayan ta gareta lokaci daya datai!!..
hawaye nabin wasu a fuskarta ta dago kai tana hango mman tata bakin titi tsaye goslow ya hanata tsallakawa zuwa anguwar tasu dayake dmn asibitin bayan titin anguwarsun CE sikazo ga dazun din, dan tasan maman tasan bata iya zuwa qasa shiyasa tataro musu abun hawan. kafin kuwa tadauke idanunta ta hango mama Zainab har ta kuwa tsallaka titin hankalinta kamar bai kanta wanda hakan yasa ita mama Zainab din Sam batasan da tafowar motar nan mai tsinannen gudun gaske ba ta 'yan smogal tayo kanta kiyyyyy!!!!!
wata qara heenduh ta qwalla tareda furta"mamahhhhh ta"!!!!!
tuni numfashinta taji yaja ya tsaya mata cak zuciyarta na bugawa da tsananin qarfin gaske fat! fat!! fat!!! kafin ta ida sulalewa wajen qasa ta zube a sume ba'inda ke motsawa a jikin nata kuwa...

zakuji ni shiru sisters kwana biyu, uzuri ne yataso mun sai kuma Allah ya sake sadamu da alherinsa a qarshen sabon satin nan dazai kama insha Allah.

daga maison ganin farincikin ku

Xexen Fasaha. Ce
[3/30, 7:15 AM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO!!!

Story and writing by Xayyneb💤💤

Fasaha online writers.

🌳Imparting valuable knowledge and intertaiment is our concern🌳.

~dedicated to my mom Sadeeq hauwas~.

D wani mugun sauri 'yan smogal din suka take burkin motar amman dudda haka saida suka dan taba jikin mama Zainab din yayinda motar tasu ta d'aga ta baya sannan ta dawo qasa har wasu daga cikin buhunnan shinkafar da suka lallodo suka zube qasan titin.
amman ita dukkan wannan tashin hankalin da mama Zainab ta qara rizqar kanta a ciki bata jishi ba dan kunnenta tsam ya dauko mata qarar da heenduh tai sau daya bata qaraba.
Allah sarki 'ya da uwa sai Allah, sai gashi dud kalar hushin da Maman tai da ita hango ta datai kwance warwas qasa hakan yasa da sauri tayi saurin komawa zuwa wajen da heenduhn take ta durqusa gabanta tana Dan tattaba jikinta, jin datai babu inda ke motsawa ne a jikin heenduhn yasata dan girgiza ta tareda fadin
"heenduh??! ke heenduh ki tashi nace ko?" jin babu wani bayani hakan yasa tai saurin miqewa ta isa wajen wani yaro mai saida pure water nan bakin gate din hospital din ta sayi guda daya tadawo ta sake zuqunnawa gaban heendun ta fasa ruwan tana zubasu a cikin tafin hannunta na dama tana shafawa a fuskar heendun wanda batadau tsawon minti uku ba kuwa heenduh ta farko cikin subbatu tana fadin"a'a dan Allah kada Ku kasheman mamana wayyo mamana,,,"!
sai dud mama Zainab kuma taji ta tsargu da kallon mutanen wajen dasuke giftawa yanzun kuma jefi jefi ciki hadda nurse dinda takaiwa likitan nan result din su suna kallonsu.
cikin takaicin surutan da taji heenduhn na mata yasa ta d'aga hannu ta buge bakin nata dashi, cikin tsananin azabar zafi heenduh tai saurin bude idanunta tareda dawowa cikin nutsuwarta lokaci daya kuma.
wani farinciki heenduh taji ya sauka aranta sa'ilin datai arba da mamanta tsaye lapian Allah a gabanta,ko zafin bakinta ma bataji a Inda jini ya dan futo daga gefen bakin nata ba sam sam ata sanadiyyar bugesan da Maman tayi.
Allah sarki da gudu ta miqe ta rungume mama Zainab din tana cigaba da kuka tama kasa cewa komi.
tureta daga jikinta mama Zainab tai tayi gaba tasake Barin asibitin a karo na biyu, dasauri heendu tabiyo bayanta kuwa, lokacin da mama Zainab ta isa titin har 'Yan smogal din sun gama kwashe buhunnan sun mayar zasu tafi, har kusa dasu mama Zainab ta isa tabasu haquri tareda cewan bata hankalinta ne taratso titi sbd patient dinta da ta baro cikin asibitin.
sun nuna mata babu komi tareda mata fatan samun lpia wa patient din tata sannan suka wuce.
kusan lokaci daya mama Zainab suka isa gidan kaka jameela din kuwa, mama Zainab najin takun sawun heenduh a bayanta aiko a fusace ta juyo tareda nuna heenduh da yatsanta manuni tace"kull kada ki kuskura ki ida qaraso mun da qafarki cikin gidan nan wlh kuwa heenduh, inko bahaka ranki zai sake mummunan 6aci kinjima na fada miki ko? tokiyi maza maza ki koma gidan mahaifinki tunkan dare yai miki"

sulalewa heenduh tai daga jikin bangon zauren datake raku6e, ta durqushe saman gwiwowinta tana sake sakin wani zazzafan kuka danji take gaba daya duniyar tai mata zafi da baqiqqirin battajin dadin komi kuwa a cikinta daidai da qwayar zarra kuwa.
banda hararta babu abinda mama Zainab keyi tana sake jin wani tuququn zafin ciwon abinda heenduh taje ta aikata da aurenta wanda batasan hakan ba ita , wato tanada auren akan NATA.
wasu zafafan hawaye mama Zainab taketa sharewa na baqinciki da takaici da tunanun yaya zatayi kenan ita ne.
daidai nan kaka jamila(Maman mama Zainab)
ta fito daga bayi tana fadin "kai maganganun wa nikeji haka kuma tareda futar sautin kakkarfan wannan kuka.... katse mgnr tai tareda ajiye butar taqaraso gaban heenduh ta kamota zuwa jikinta suka shigo tsakar gidan tareda zama saman tabarma kan tai mgn saiga daya daga cikin almajiran Mlm zayyan ya shigo gidan kansa daukeda buhun gero ya yi sallama mm jamila ta amsa masa sannan ya shigo ya dure buhun a runbun hatsi yagaidasu sannan yace "baba gashi inji Mlm daga gona"
kaka Jameela tace"Mlm din yanzu yana gona kenan?"
ya amsa da fadin
"Eh baba aikin girbi akeyi ne shiyasa yace nafara kawo wannan buhun inyaso saimu qarasa aikin idan na koma, dayake su musa da lurwan da garbate dud tare muke aikin suna can, kuma yace kibada furar da kika dama akai can"
"To shiknn" cewar kaka jameelan tana mai miqewa ta shiga daki, bata dau ko minti daya ba ko sai gashi ta futo daki hannunta riqe da baban qwaryar data dama furan da faifai akai gamida luddai ta miqa masa ya karba ya fita.
dawowa tai ta zauna tana sake kallon heenduh da dud tabi ta rakube jikin bango tana sakin ajiyar zuciya dan tuni kukan yaqiyi mata dadi wajenyi wanda ba arziqi tabarsa jin kanta nawani mummunan sara mata ga kuma wani murd'a ta ciwo da cikin nata keyi.
dafata kaka Jameela tai tace
"jikata heendu mike faruwa ne dan Allah?"
wani sabon kukan kuma taji heendu yazo mata wanda bata shiryaba, mgn take tana girgiza kai tana cewa"dan Allah kema kada kice zaki tsaneni ki juyamun baya akan abinda ban aikata ba bisa son kaina ba face saida tabbas...a fusace mama Zainab tace"tabbas din banzan ki dake gareki, in kuma kinada tabbas kan abunda kika je kika aikata to fad'i tabbas d'in naki...shuru tai kamar zatai wani kukan itama takeji kodan tasamu sauqin zuciyarta..cigaba tai da cewa"wlh heenduh kinban mamaki yanda har kika iya zuwa kika jawo mana fitina muna zaman mu cikin rufin asirin Allah mahalicci"
taqarashe mgnr tareda share kwallan da suka subuto mata.
cikin rashin jin dadi kaka Jameela ta dubi mama Zainab tace"zainabu kul daki daina zubdawa 'yarki hawaye dan wannan zai iya qara zama mata musifa a rayuwa, dan haka kowane laifi tai miki abinda yafi ki dinga mata addu'a kawai kekuma kidinga fadin hasbunallah dan samun sauqin zuciyarki"
cikin duban kaka Jameela din mama Zainab tace"mama wlh kukan nan zuwar min yake dan abunne yafi qarfin zuciyata, wai mama yanzun kamar heenduh duniya zata rudeta har tayi amfani da kyan da Allah ya azurta ta dashi ta dinga bin mutanen wofi har gashi yanzun tana daukeda ciki wata biyu da satitittika,

to dan girman Allah mama ki gayamun wannan tashin hankalin dami yai kama wanda har zaisakamun nutsuwa a cikin zuciyata har abada?"
salati da sallami kaka jameela takeyi gamida qarashewa da fadin"subhanalla innalillahee wa'inna ilaihirraji'u...
gaba daya heenduh taji tsikar jikinta na tashi jin salatin da kaka Jameela keyi, tuni ta qara sautin kukanta gamida girgiza kanta da gaba daya jima takeyi bakinta ya kulle, zufa kam ajikinta sharkaf daga ita har mama Zainab din.
kaka Jameela cikin tsabar mutuwar jiki ta dubi heenduh bakinta na rawa rawa tace
"haba..haba heendatuh baki rasa ci ba baki rasa sha ba a gidan iyayenki kazalika zanen d'aurawa amman miye yakaiki ga aikata wannan mummunan aikin na sabawa mahallicinki da iyayenki dakuma yiwa kanki mummunan tabo a rayuwa wanda zai dawwama har jikokinki zakiji anmusu gorin abinda kakarsu tayi a yarintar ta indai a duniyar nan tamu ce?"
gaba daya jikin heenduh yakatse da kyarma kota'ina, tama gaza dagowa da kanta bare ta dubesu..
kaka jameela cikin karyewar zuciya ta juya ta dubi mama Zainab tace
"yasalamullahe!!!
innalillahe wa'inna'ilaihirraji'iunbabanta yasan da wannnan mgnr ne?"
saida mama Zainab tasake share zufar jikinta sannan tace"bazan iya tunkararsa da wannan zancen ba mama, dan dawowarmu knn ma daga asibiti kingama result din tabbatar da ciki dasuka bamu,
dan haka nina rigaya ma dana yanke Shawara bazan iya komawa gidan ba gskia"
girgiza kai mama Zainab tai tace"dole ko isma'ila yasan da wannan batun gskia, yanzun yana ina?"
"Yana wajen aikin su"
cewar mama Zainab din tanamai jin idanunta na mata zafi kamar ansa mata yaji a cikinsu.
shuru wajen yadauka fiyeda minti biyar sai faman bin heenduh da kallo suke wacce kanta ke saqe cikin cinyoyinta tana kukan bazatacciyar qaddarar data afka mata batareda shirin dasukai da doctor din ya fidda suba tunkan ma aje ko'ina knn.
sai zuwa can kaka Jameela ta bude baki cikin qarfin hali tace
"Dole kuwa yasan a wannan batun dan ba abun boyewa bane,
tashi zakiyi muje gidan gidan naku harmujira dawowarsa zansan yanda zan bullo masa da mgnr indake baki iyawa .."
Badon mama Zainab taso ba haka suka tashi ganin kaka Jameela tadauko mayafinta, nan suka fito.
saida suka iso qofar gidan nasu ne snn mama Zainab tatuna bata dauko key din qyauren wajen gidan nasu ba d'azun dan rud'u sanda zatakai heenduh asibiti, dayake jamlock ne qyauren nasu yanzu, wanda indai aka datsesa saidai abi da makullinsa a sake budesa sanann.
dole mama Zainab tafadawa kaka Jameela hakan,
kai tsaye kaka Jameela tace"kumu shiga gidan baba yawale majirasa anan din"
haka suka shiga gidan da sallama suka iskesa yana zaune da Qur'anic a hannunsa yana karantawa,ganinsu ne yasashi kawo qarshen surar dayake tareda shafa addu'a.
cikin qarfin hali suka gaggaisa dasu mama Zainab tareda masa bayanin matsalar key din da akasamu.

sosai baba yawale ya fahimci su mama Zainab nacikin damuwa musamman ma daya san dud da karadin heenduh Amman yau yajita laqwas dudda mgnr wasan dayai Mata Amman saima gani yai tana matse qwalla.
cikin mamaki ya dubeta sosai yace"to yaufa mikuma ya faru da wannan addababbr baiwar take mana matsen kukan NATA?"
yayi mgnr cikin murmushi..
kasa amsa masa sukayi dukkansu sai daga bisani sannan kaka Jameela ta janye tagumin da tayi bayan sauke wata qaqqarfan ajiyar zuciya datai sannan ta dubi heenduh kuma taqara maida kallonta ga baba yawale daqyar ta bude baki tace"mummunan al'amari ne ya tunkaromu yaukam baba yawale wanda yadagula mana gabaki dayan zuqatanmu da hankulanmu..sosai baba yawale yagyara zama cikin mamaki yace"miye wannan Abu kuwa jameelatu?"
saidaqyar da jibin goshi sannan kaka Jameela ta nuna heenduh da hannu tace"ciki tasamo sannan kuma taqi mana bayanin waye bababansa ma, kaganta nan banda kuka babu abinda takemana tun dazun"
 cikin rawar murya mai gauraye da karayar zucci mama Zainab tace"wlh baba yawale bansan ta yanda babanta zai ji shigar mummunan batun
nan ba inya jisa"
shuru baba yawale yai yana kallonsu fuskarsa daukeda wani kamalallen murmushi dan har ransa yaji farinciki ya mamaya, sosai yasani daman komin daren dadewa gaskia zatayi halinta ta bayyana kamardai ranar yau data fara risqarsu.
sosai su mama Zainab sukai mamakin wannan murmushin dake fitowa daga daga fuskar kamilallen dattijon baba yawale, suda suka zata ma zai shiga tashin hankali shima.
babu zato sukaji yace"Alahamdililla gskia tayi halinta daman najima dajiran zuwan wannan rana ta samun yabanyar da aka jima shekara da shekaru da shuka irinta"
sosai mamakinsu yaqaru suka dinga binsa da kallo zuciyarsu cikeda rashin fahimtar inda zancen baba yawale din ya dosa...

By
Xexen Fasaha
[3/30, 7:15 AM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO!!!

Story and writing by Xayyneb💤💤.

~dedicated to my mom Sadeeq hauwas~.

Allah qara had'a mana kawunanku mutane na qwaran gaske, mafasaha tsabtacacciyar fasaha, Maman abdul jalal da haleema Awwal xexen fasaha takuce muddin rai kada kudamu ana mugun tare har yanzu.

P 58
S aida ya kurb'i furarsa wacce ke gefensa cikin farin kofi sannan yasake duban su mama Zainab still murmushin sa na ga kan fuskarsa yace"dan haka wannan bawai wani abun damuwa bane dazaku tashi hankulan Ku akai"
mama Zainab ta dubi kaka Jameela yayinda itama kaka Jameelan tajuyo dubanta ga mama Zainab sannan kuma lokaci daya atare lokaci dayan dai suka maida kallonsu ga baba yawale din kowacce zuciyarta na tunanin wacce mgn baba yawale ke yi haka na wannan mummunan abun daya samesu amman yake cewa su kwantar da hankali? kodai tsufa ne yake fada masa sabanin abinda suke fada masa yayinda hankalinsa na rudun tsufa yagaza fahimtar ma'anar babban mgnr da suka zo masa dashi ynzu.
jisukai yace"kada kuyimn wata fassara Zainabu da mamanki dan cikin hankali na nike baku wannan amsar kudai kudan dakace ni harshi isma'il din ya dawo saimu ida tattauna mgnr tamu, zanje masallaci jan jam'e yanzun saina dawo" yayi mgnr tareda miqewa yana saka takalmansa roba masu rufi blue.
"To"
abinda sukace knn cikin qarfin hali, binsa sukai da kallo harya fita sannan ne kaka Jameela ta sauke ajiyar zuciya a fili "gskia kam dai din *da sauran kallo* a gabanmu, Allah kawo shi Ismail dindai lpia"
cikin matuqar alhini mama Zainab ta janye tagumin ta itama ta kawo ajiyar zuciya tareda furta "Aminn mama" tana mgnr ne kawai tana kallon heenduh wacce ta miqe tadauki buta tashiga bayi.
tana fitowa tai alwala suma suka miqe sukayi alwalar dan sallar la'asar din.
sunjima dagamawa suka zauna jugum jugum bamai wa wani mgn.
acan waje ko baba yawale koda suka fito masallaci nan ya zauna shida dady salis saman dakalin qofar gidan nasa suna fira. lokacin qarfe 5:22 na yammacin ranar.
hamdala baba yawale yai a zuciyarsa na hango motar baba ismail dayai tana parking can gefen gidansa Inda yasaba ajiyeta.
baba Ismail na futowa motar da jikkarsa a hannu
yakuwa hango su baba yawale din mafarin knn yadoshi wajen yana murmushi faffada a fuskarsa.
da sallama yaqarasa wajen suka amsa masa suma fuskokinsu cikin annushuwa.
yana niyyar zama ne saman dakalin shima anan baba yawale yayi saurin dakatar dashi da fadin"a'a isma'ila kada kakai ma ga zaman nan muje ciki gida zamuyi wata muhimmiyar mgn dakai"
duban baba yawale baba Ismail yayi yace"to baba bari nakai jikkar gida ko?"
girgiza masa kai baba yawale yai yana kallonsa sannan yace
"kada kadamu ay iyalan naka ma suna ciki"
sosai kuma sai baba Ismail yaji jikinsa yayi d'an sanyi kuma yaqara tabbatazwa da eh lallai tabbas mgnr ba qarama bace kam inda har mata da 'yarsa na gidan baba yawale din kan batun.
a sanyaye ya miqe tsaye shima ganin baba yawale din ya fara tashi shima.
shima dady salis miqewa yayi ya dubesu sannan yace"toni zan wuce gida baba...baba yawale yai saurin katsesa da cewa

"a'a salisu ai dakai za'ashiga gidan kaima kaji batun inda dud dai an rigaya an zama daya babu zancen ayi wasa tare ci kuma yazo yazama banban, dan haka kumu shiga gidan dukanmu"
har a ran dady salis yaji dadin rashin bambancin da baba yawale din bai nuna masa ba akan batun nasu na gida.
dan haka binsa sukai suma suka shiga gidan cikin sallama.
su mama Zainab suka amsa yayinda heenduh najin muryan baban nata tayi saurin qara cure jikinta waje daya gabanta na wata kalar azabben yankewa yana faduwa dasss dass.
dukkansu zama sukai kan shimfidar baba yawale, sannan shimà baba yawale ya zauna yana kallon yanda heenduh dud tabi ta takura kanta, sosai ya fahimci bata nutsuwarta, dan haka yace mata cikin kalan wasan da sukeyi" amaryata kifa daina damuwa komi zai bayyana ne yanzun ay insha Allah, dan haka in kika kuma mana wani shesheqar kuka nan sainasa carbi nan nawa na dabaibaye miki baki dashi sainaga ta bud'esa ay kuka" yaqarashe mgnr cikin raha
yayinda baba Ismail da dady salis suka musu dariya, ita kuwa har cikin ranta take furta cewa"shi wai baba yawale miyasa zai na mata hakan a wannan quncin taskun data tsinci kanta cikinsa?
baisan wasa ma lokaci ne dashi ba...
kwatsam taji saukar mgnr baba yawale nacewa"sama'ila da salisu kumu taya junanmu murna dan muna shirin samu qaruwa a cikin dangi ta kyautar d'a da Allah ubangiji buwayin sarki gagara misali yai mana akan 'yarmu heenduh"
cikin baibai na rashin fahimta Su baba Ismail ke faman kallon heenduh da tunanin cikin a ruwa ne ake samunsa yanzun da baba yawale ke musu mgn akai?
abinda sukaji baba yawale din na qara nanatawa shine yasa gaba daya jikinsu yin la'asar sanda kunnensu yasake juyo musu yana cewa"heenduh na dauke da juna biyu na wata biyu da satittika"
amatuqar mugun zabure baba Ismail ya miqe tsaye a gigice yake fadin
"ciccc...ciki kuma fa kace a jikin heenduh na baba?"!
yana mgnr ne idanunsa sun kada sunyi jazur a wajen jikinsa naqara ciri.
kamo hannunsa baba yawale yai na ganin halin dayake ciki uwa zai fadi sbd kyarma"
"Kwantar da hankalinka sai kace bakaine dai ka aurar da 'yar taka ba kuma kasan hakan?
to lokaci ne yazo ya nuna Kansa gashi jaririyar 'yar taka daka auras ta girma harta samu qaruwa tareda jinjirin mijin nan nata da aka aurawa to miye abun tada hankali daga cikin batun em?"
wannan karan dagasu mama Zainab har baba Ismail din gaba daya daskarewa sukai da kallon baba yawale da tunanin kaddai fa ya bayyanawa yaran nan sirrin aurensu na jarinta har cikin nan yakaiga samuwa?,
to in hakan ya kasance gaske kenan matakin da iyayen khaleepa suka furta musu zai hau Kansu muddin suka bayyanawa yaran gskia knn yakusan
Hawa Kansu knn?????!!....katse musu tunani baba yawale ya sakeyi da cewa
"heenduh dube ni nan"
cikin firgita kuwa ta dago tana kallonsa danma ko iyayen nata ta kasa duba.
"kiramun khaleepan ta cikin wayarki"
Abinda yace knn yana mai cigaba da lazuminsa a zuci da carbinsa a hannu.
cikin rawar jiki ta bude jikkarta ta fiddo wayar ta duba number tasa da daman itace a sama sannan ta kira,

tana fara ringing babu jimawa taji an katse wayar, batareda daukar second daya ba saigashi ya kirata..
dasauri tadaga Wayar hannunta na rawa wayar kmr zata qwace mata ma takeji dn ganin wani kallo da mama Zainab da baba Ismail me mata na tsantsagwaron mamaki.
da rawar murya tace"ka...ka..kazo..
gidan baba yawale yanzun injisa" tana gama fadin hakan ta katse wayar batareda tama saurari amsar mi yake bata ba.
dayake daman khaleepa fitowarsa knn daga gida bayan dawowarsa hospital yai wanka yaci abunci yafito knn cikeda azarbabin zuwa gidan baba Ismail din gun sugar din nasa sai kuma ga wannan kiran dole tasa ya cewa yunus yajirasa yana dawowa kaitsaye ya nufo gidan.
cikin muryar sallamarsa ya shiga gidan bayan sun amsa anan ya zauna gefen heenduh qiri qiri ko kunyar iyayen baiji ba sai itace ma tadinga qoqarin janyewa daga garesa cikin basarwa yadunga janyo tafin qafarta alamun ta tsaya a hakan.
saida yagaidasu snn baba yawale yace
"Nasa akiraka ne daman dan nai maka wata tambaya khaleepa"
sai lokacin ya lura da fyskokin su baba Ismail a jugumgumce, hakan yasa ya sake nutsuwa sosai tareda furta
"to"
"To alhamdulilla,,,cewar baba yawale din yana mai ajiye carbinsa gefe daya sannan yaci gaba da cewa
"shin mlm khaleepa daman kasan kuwa matar ka heenduh na dauke da cikinka ko kuwa?
daga farko ya firgita dajin wannan bazatacciyar tambaya daga baba yawale,, sai kuma yayi tunanin to miye? daman shifa jiran zuwan wannan ranar yake fata dan yagaji da boye boyen nan na aurensu gwara abasa matarsa dud wacce za'ayi inyaso sai ayi.
dan haka cikin dakewa gamida Sosa qasan Kansa alamun kunyarsu baba Ismail sannan yace"eh baba najima dasani kamar yanda itama tasani"
murmushin baba yawale ne yasake fadaduwa a saman fuskarsa sannan yace"masha Allah,, kukuma bari kuji yanda lamarin yafaro wanda har yaran Ku sukasan da aurensu da kuke boyewa wanda bakowa ne yafara fallasa hakan ba face kanwa mamar khalepan inkun fahimceni...nan take baba yawale yafada musu tun asalin farkon yanda su khaleepa suka ji mgnr daga bakin Hjy furdauseey sanda take fadawa qawarta harkawo zuwan da su khaleepan sukai wajensa da mgnr shi kuma ya sake tabbatar musu da haka batun shike har kuma zuwa damar dayabasu ta kasantuwa mata da miji adud sanda suka so hakan domin halalin juna suke sud'in tuni..
yaqarashe mgnr da cewa"to miye abin tashin hankali anan inda cikin nan da ubansa gashi kusa?" yayi mgnr yana mai sake sakin murmushi.
daga mama Zainab har baba Ismail har kawo kaka Jameela wata sanyayyen ajiyar zuciya suka saki dan koba komi hankulansu ya kwanta dajin matsayin sahihancin Inda cikin jikin heenduh yasamu usuli kuma zarginsu yasauka a kanta na tunanunsu ko cikin waje ne dan basu taba tunanun cewa baba yawale din zai fadawa su heenduh matsayin junansu a garesu ba,
hatta dady salis shima saida yai mamakin wannan auren jarinta haka da'akai musu dan baita saniba shima inba yanzun ba, kuma sosai yaji dadin hakan a ransa.
cikin sake sauke ajiyar baba Ismail yadubi baba yawale yace"amman baba baka gudun abinda

iyayen shi khaleepa zasuyi kmr ynda sukace muddin muka bayyana gskian lamarin nan?"
"abinda Nike tunani nima knn wlh a zuciyata dan nasan halin Yaya fursauseey sosai ta dauki zafi kan haka,
dady salis yace
"zafi kamar yaya?"
atsanake baba Ismail da baba yawale suka bayyana musu abinda mukhtar yace shida maidakinsa kan batun Indai suka furta sa.
tsoki dady salis yayi tareda cewa
"wannan kuma ba hujja bane...nan baba yawale shima ya katsesa da cewa"abunda nagani knn nima haryasa nakaiga bayyanawa yaran gskia dan lokacin dazasu santa kuma yayi, kuma wlh ko d'ar bazanji tsoron hukuncin da mukhtar zai yi Kn hkn ba"
shiru baba Ismail yai zuwa can kuma wurin yai tsit sai muryar khaleepa dasuka tsinkayo yana cewa"insha Allah dady bazaice komi akaiba dan daman nayanke shawarar daya dawo zan fada masa komi da kaina.
"Hakan yayi khaleepa gwarzon namiji haka akeso yazama ay ba tsoro"
cewar baba yawale da dady salis.
saida suka qara tattaunawa sosai kan batun sannan sukaiwa baba yawale sallama sika fito.
kaka Jameela tawuce gida hakanan taji farinciki samuwan cikin heenduh dantanaji kamar cikin shine silan gyaruwan zumuncin 'Yan uwan,
suma kuma su mama Zainab da baba Ismail iriyar tuanin kk jameela hakan ne aransu kuma suke fata.
shima daddy salis gida ya wuce.
su mama Zainab ne suka shiga gida heendun naqoqarin binsu ciki a d'arare babu zato taji an ruqo mata qasan hijab..dasauri tajuyo ganin doctor ne keta marairaicewa akan tatsaya su gaisa da baby nayler cikin inkiya dayake mata ata cikin nagartattun idanunsa zuwa nata,aiko cikin kunya ta fuzge hijab dinta dan ganin mama Zainab tajuyo takamasu ahakan, aiko da gudu tayi cikn gida shi murmushi abinma yabasa, ahaka yatafi yanajin zuciyarsa wasai yau na tunanin su mama Zainab sunsan yasan wacece heenduh garesa inda harda babban sheda ma ajikinta.
heendu kuwa tana shiga gidan nasu tasamu su mama Zainab zaune nn tsakar gida aiko cikin kunya ta rab'asu tabi ta jikin bango tana qoqarin shigewa cikin dakinta knn taji baba Ismail yace
"yaki zonan ki zauna heenduh na"
wata sanyayan ajiyar zuciya ta sauke jin mgnr tasa cikin kulawa bakamar d'azun ba daya tashi hankalin ta, kazalika koda tajuyo taga fuskar mama Zainab asake itama hakan baqaramin dadi da nutsuwa ya kamata ba lokaci daya.
danhaka cikin qarfin gwiwa ta dawo tazauna kusada baba Ismail din kanta qasa dan kunyar cikin jikinta take jiwa kanta dan tasan izuwa yanzun iyayen nata sunsan tayanda tasamu cikin dud saitaji kunyar m@ had'a idanu takeji dasu ita kam yanzu.
sosai su mama Zainab suka lura da hakan dan haka suka dubi juna shida mama Zainab sukai murmushi.
baba Ismail yai gyaran murya yace
"daga farko mun fahimci zancen baibai heenduh dudda damn muna tantaman tarbiyyar da mukai miki bazaki iya watsi da'ita ba saidai zuwan qaddara wacce ta rigayi fata kuma, muna miki addu'an Allah saukeki lpia, snn kuma mamanki zata dinga baki kulawa insha Allah, yanzun

kije d'akin ki huta ko Inda ansha kuka dagake har Maman naki"
yayi mgnr cikin myrmushin son mgn.
afakaice mama Zainab ta wulqa masa harara tadubi heenduh tace
"jeki daki heenduh inkinason wani abun kimim mgn"
haka heenduh tawuni daki komi takeson ci kuwa mama Zainab sai tai mata shi kankace mi...
farinciki yadawo cikin rayuwar heenduh sabanin dazun dayai mata balaguro a jiki.
abin Allah kuma daga mama Zainab har baba Ismail sai sukaji son cikin jikim heenduhn tasu har cikin ransu dazuciya daya kuma.
washe garin ranar da misalin qarfe tara na safe dady salis zaune cikin motarsa yana driving dan tafia airport dauko babban aminin nasa wanda jirginsu zai sauka nanda hour guda, kuma daga khaleepa har Hjy furdauseey babu wanda mukhtar din yafadawa zaidawo yaudin dan sosai yakeson musu surprise.
dady salis din na'isa airport din tunkan yafito ya miqa hannunsa ya dauko sanyayen laksera mai duhu yad'an sha kad'an ya rage iya adadin yanda rubutun nan daya karbo zai ida cikashe robar, bismilla yai tareda fasa qullin rubutun ya zurara sa ata bakin robar duka sannan ya karkad'e ya mayarda murfin a kai ya rufe tareda ajiye robar lemon gaban motarsa. sannan yafito ya qarasa wajen zaman tarbar baqin na airport din wanda keda jama'a da dama dasukazo daukar 'yan uwansu da abokan arzuqan su suma.
ba'a dau rabin awa ba jirgin su yasauka matafiyan suka fara saukowa one by one yayinda dady mukhtar shine mutum na uku a sahun fitowa,
sosai yanisa tareda shaqar iskar Nigeria dinsa ahankali yakejin kewa ta babban shaqiqinsa qanensa kuma dan uwansa wanda baisan miyasa ba akwanan nan yake matuqar jin hakan ajikinsa musamman ma yawan mafarkan baffansa da inno dayakeyi dazarar ya runtsa kuwa, babban ma abunda ke tada masa hankali yanda muraran cikin mafarkin nasa dazarar yaga iyayen nasa saiyai yunqurun binsu amman saiyaga sun juya masa baya alamun kamar suna fushi dashi ma,,
qwalwarsa kuma tatushe yanason tunano wane laifi yaimusu amman sam yakasa saima yaji wani abun daban yataso yatokare wannan tunanin nasa.
mafarkin dayai Daren jia da baffansa shine yana zaune saiga baffansa yazo har inda yake babu abunda yake cewa face"kariqe addo'e mukhtar domun addua da azkar muddin takobin mumune ce kaikuma kajima da daina yunsu dudda kanada ilimin sanunsu, salla akan lokacinta tana yawan kucce maka mukhtar sbd zafin neman duniya shin tayaya in kanaqin yin hakan salla Kn lokacinta da addu'oen Neman kariyar ta ubangijinmu kowanne abu bazaiyi tasiri akanba ba in aka maka?"
daidai nan ne kuma mukhtar din ya farka, haka yawuni sukuku tun lokacin dan daqyar ma yaqarasa shirya komi nasa sannan yabaro qasar.
sauke ajiyar zuciya yai tareda ida saukowa saman matakalan jirgin yatunkaro inda yahango daddy salis suna
tsattsaye.
sosai dady salis yaga abokin nasa yaqara haske da stayi da kakkauran jiki, kyau da annuri alamun hankalinsa kwance,saidai alamun manyanta data fara rizqarsu.
cikin tsantsar farinciki suka rungume juna suna dariya saidaga busani suka kwashi trolleys dinsa sukasa a motor suka shiga suma suka fara tafia.

cikin murmushi dady salis yadubi dady mukhtar
yace"welcome back to our nation my big friend fatan komi lpia ko?"
cikin murmushi dady mukhtar yace"oh thanks so my big friend All is fine alhamdulilla ya qasar tamu Yakuma yarana su meenat"
"Komi lpia abokina,yayi mgnr tareda dauko laksera dinnan mai rubutun Mlm aciki yadubesa yace
"gashi kadan taba abu mai sanyi natanadar maka shine domin nasan zai amfaneka tareda zama garkuwa a cikin jikinka"
sosai dady mukhtar ya fadada murmushinsa ya miqa hannunsa ya karba tareda furta
"Kasanko daman ina buqatar Abu mai sanyi kasan whether tacan data nan Nigeria tasha mana bambam shiyasa dud bayan lokaci nikejin qishi gakuma zafi,but nasan zandaina daga yau Inda nadawo qasata abar alfaharina ko friend" murmushi sukai daganan ya bude murfin robar zaifarasha dasauri dady salis yace "my friend zaifi maka kyau kafin kafarasha don't forget bismilla kafara bismilla zaifi ma'ana"
"hakane abokina nasha'afa ne
kuma na gode datunatarwa amini na qwarai" yayi mgnr cikin murmushi tareda yin bismillsn yakafa bakinsa arobar yafara sha wanda bashine ya janye robar ba saidaya shanye lemon tas sannan.
cikin murmushin jin dadi dady salis yace"gskia abokina kaji qishin ruwa fa inaga"
dady mukhtar yace"wlh kuwa kuma bakaji yanda hadin lemon nan yaimyn ba babu qarfin gass dinnan nasa sosai kmr ammasa surki ne"
wani murmushi dady salis yasakeyi ataqaice yace"inaga haka yazo maka kai"
shiru dady mukhtar yai jin yanda zufa keta ketowa a jikinsa saifaman share goshinsa yake da hankicerf.
sosai dady salis yalura da hakan shiyasa yaishiru harsuka qaraso anguwar tasu akuma gate dun gidan dady mukhtar din.
yunus ne yaga fitowarsu motan danhaka yayi saurin isowa wajen yafasa shiga motarsa zuwa inda zaijen ga lokacin.
gaishesu yai cikin farincikin dawowan dady mukhtar din snn dakansa yadunga daukar jikkunan yana shigar dasu ciki.
nan dady salis yadubesa yace"zan wuce friend saimun hadu anjima"
cikin rashin jin dadi dady mukhtar yace"haba mana friend bazamu shiga tare cikin gidan ba knn?"
girgiza kai dady salis yai cikin fara'a yace"inaso kahuta sosai inkai wanka kaci abinci abokina zamu hadu tonight insha Allah danzanje office ne yanzun"
"To shiknn my friend ngd saimun hadun" musabuha sukaqarayi snn suka rabun.
lokacin ne yunus yafito daga gidan yasake yiwa dady salis barka da dawowa cikin jin dadi dady mukhtar ya amsa sannan yunus yashiga motarsa cikin sauri domin yaqagara ya isa hospital dinsu khaleepa danya fado masa zuwan bazatan dadyn nasa.
dady mukhtar kuwa afalo yaci karo da Hjy furdauseey tana qoqarin fitowa taga mijin NATA.
aiko qanqamesa tai tana ihun murna jikinta sai b'ari yake batasan dalilin faruwan hakan ba.
ruwan wanka ta hada masa yashiga yayo yafito yazura jallabiya sukahau dining saifaman nan danan takeyi dashi hatta abuncin ita tabasa ma.

saidaya gama cin abuncin sannan suka dawo nan qasan falon suka zauna cikin washe baki hjy furdauseey tadubesa tace"oni auran maitsada na da zarah yatafo knn Inda kadawo...
dakatar da ita yai yace"haba Hjy ta kibari Mayi mgnr daga baya yanzun ina buqatar hutawa ne"sororo tai tana kallonsa aranta take furta"ni furdauseey yau mi kunnena ke jiye mun ne? Mukhtar keman musun yagaji fa akan mgn dazan masa sabanin da dajikinsa har rawa yk wajen sauraran uzurina?
amman dayake muguwar yar bariki ce ata kowane fanni shiyasa tai saurin saita nutsuwarta tareda cewa"afuwan to alhajina ahuta lpia... tana qoqarin miqewa saiga khaleepa asukwane yashigo falon.
hakanne yasa takoma ta zauna.
a hanzarce yaqarasa jikin dadyn ya kwanta yace"barka da dawowa my dad imiss you a lot" cikin sabon murnushi dady mukhtar yace"miss you too my don, my gental man yanaga kaqara girma haka kama zarce handsome mi momynka take girka maka kakusan taddoni agirma?" dariya Hjy furdsuseey tai tace"wlh kuwa alhajina nima ina mamakin budewar da maitsada na yake qarayi Uwa mai sabon aure, amman inaga hakan yasamo asali ne daga dokin auransa dayake da zarah ko maitsada na?"
nanda nan khaleepa yaji ransa yabaci Da mgnr zarah data sako.
tsam ya miqe yana yamutsa fuska yace"Momy dady zankoma hospital daman ina cikin ayyuka ne natafo ganin Dad na"
yana gama fadin HK yaisaurin ficewa yashige motarsa yabar anguwar.
Acan falo kuwa dady mukhtar yaturawa Hjy furdausey jikkunan tsarabovinsu sannan yadauki sauran yanufi dakunsa dasu bacin yace mata zai kwanta yadan huta.
dole tahaqura ta kwashi kayan tashige dakunta badan taso So ba.
khaleepa sai ana gama sallar isha'e ya shigo cikin anguwar.
Har qofan gidan baba Ismail yaje ya tsaya da motarsa yana son Shiga gidan amman wata masifaffiyan kunyarsu yakeji, sosai yamatsu dason ganin baby pace cut sugar n tasa yarasa yadda zaiyi.
saiya fito kamar zai nufi gidan snn ya koma motar tasa kuma, wayarsa yajawo yadanna number heenduhn amman katsam yaji ana cewa it's switch off.
runtse idanunsa yai gam sosai yaji kansa nason yafara ciwo ransa namasa babu dadi zuciyarsa nabasa kalar d'aci2 wata zuciyar tace"kai maganin matsalar nan khaleepa koka samu sauqin zyciyarka gamida dawowar matarka hannunka kadaina zagaye zagayen nan dan abun yayi yawa gskia.
yana gama tunanin hakan da sauri kuwa ya juya kan motarsa zuwa gida.
dawani sabon saurin yakashe motar yashigo falon gidan inda ya iske momynsa da dadynsa zaune a falon suna kallon tashar BBC London.
ganin yanda yafado musu falon a sukwane yasasu saurun miqewa tsaye dan azatonsu ba lpia ba musamman ganin yanda sukai idanunsa sunyi jazur jijiyoyin kansa suntaso rad'a rad'a.
agigice kuwa Hjy furdauseey ta matsa gabansa tana kamo hannuwansa take cewa"mai tsadana lapiyanka Lau kuwa kashigo mana haka a hautsune dud kabi katada mana hankula?..
janye hannunsa yai daga nata sannan yataka takunsa qarfaffa cikin combus din shoes dinsa budaddu masu qara yaja yatsaya gaban dadynsa mukhtar murya cikin dakewa yace"dady ayau zan sanar muku da cewa inada buqatar matata heenduh tadawo hannuna namatsayin dindun

din.
Cikin wata razananniyar qarar mgn yaji Hjy furdausey tace
"Kai khaleepa?!!!!!
abinda bata tabayi ba knn ambaton sunansa muraran.
kankace mi harta iso gabansa tashaqo kwalar rigarsa tahau dauke sa da zafafan maruka kota ina, amman yana tsaye qyam agabanta shiko cikin dakakkar zyciyarsa.
ahaukace takoma dukan kafadunsa tana cewa"wayyo nashiga uku matsiyatan mutanen sun tona mun asiri kaicona qarya suke maka khaleepa kada kayarda dasu dukiyar Ku sukeso, wayyo mukhtar kaje kasa akamasu a daure muddin rayuwa tsinanun munafukan..."
tayi mgnr tanajin numfashinta na fuzga..janyewa doctorn yai daga gabanta yana kallonta sannan yajuya yadubi dadynsa da kamar an sassaqa awajen komotsi yakasa bare yai mgn.
juyo da kallonsa yasakeyi ga Hjy furdauseey kaitsaye yace"tabbas Momy matatace heenduh nasani wanda yanzun haka mgnr nan danike tana dauke da cikina natsawon kusan wata uku a jikinta"
aitanajin haka tayo wani muguwar ashar tareda yo kukan kura zata nufo khaleepa saikawai jiri yakwasheta kamanninta suka sauya nan take sakamakon murgud'ewa da bakinta ya farayi idanunta suka jujjuye take takife a wajen hannunta a maqale kamar wanda inna takama ta gabakin ta izuwa yanzun yakusan zuwa ga kunnenta tsabar yanda aka janyesa tareda futowar dalalowar miyau a cikinsa tana kakari...
dawani mugun sauri khaleepa da dady mukhtar suka nufota hankali tashe....!

By
Xexen Fasaha
[3/30, 7:15 AM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO!!!

Story and writing by Xayyneb💤💤

~dedicated to my mom Sadeeq hauwas~.

👁️📦👁️
🅿5️⃣
G anin da khaleepa yai momyn tasa sai faman kakkafewa take qarayi hakan ya sashi saurin duban dadyn nasa cikin wani sabon tashin hankali yake furta"dady...dadyyy mumu... mukaita asibitin mu kawai...yana mgnr ne tareda kinkimota cikin hannuwansa yai mata daukar jinjirai ya tallafota yafito dasauri yayinda dady mukhtar yafito cikin sauri yashiga motar yajasu zuwa asubitin, salati kawai ke fitowa a bakinsa dan hankalinsa yayi mugun tashi gskia, dandai yasan matar tasa batada jinnu amman dayace sune suka taso a jikinta yanda take wannan kanannad'a haka.

suna isa aaibitin dasauri nurse ta turo gado wanda khaleepan yakirata tun suna hnya data zama ready daman.
dan haka dakansa ya daura momyn nasa a gadon daukar marassa lpian yanufi emergency room din da ita yayinda dady mukhtar ya zauna saman wata kujera yama rasa abinda ke masa dadi kawai saiya tura tafukan hannuwansa cikin fuskarsa.
yana nan zaune sama da awa 2 wato wuzin sha biyu saura na dare knn sannan khaleepa ya fito daga dakin daya shigar da momyn tasa jikinsa sai gumi yake faman tsattsafowa dan hatta farar rigar lolikitocin dake jikinsa saman kafadarsa ya ratayota.
zama yai kusada da dadyn nasa tareda jingina bayansa a kujerar sannan ya saki wata qaqqarfan ajiyan zuciya tareda zare medical glass din idanunsa yasa hankicerf yashare gumin fuskarsa.
dafa kafadan dadyn nasa dayai ne tareda furta"dady" hakan ne yasa dady mukhtar saurin janye taguminsa yajuyo yadubi khaleepan danshi kam kwata kwata ma baisan ya fito ba.
cikin muryar karaya yace"yajikin maman naka danna soma fidda rai ma ganin shurun tayi yawa dan masallacin kun can naje har na dawo kuma najima banji motsinka ba"
ya qarashe mgnr tareda shafe zufar goshinsa da bayan hannunsa dudda easi dun dake wajen kuwa.
saida khaleepa yayi dan shuru na tsawon minti 3 sannan ya jinginar da kansa a kafadan dadyn nasa murya a kasalance yace
"dady mummunan hawan jini ne ya shige Momy lokaci daya wanda yakusan zuwa qarshe sosai, badan Allah yataimaka ba dady zuwan namu asibitin nan kan lokaci dababu abunda zai hana momy kamuwa da cutar faralize, ciwon baren mutuwar jiki ya sameta,,dan da alama mgnr da mukai ne a gida ya bugeta sosai,
amman yanzun Alhamdulilla dady komi ya dawo mata lpia lau tama samu sauqi zuwa gobe da safe zata iya komi da kanta dan barci take yanzun sakamakon injections danai mata dasauran abubuwan daya dace"
sauke ajiyar zuciya dadyn yai tareda hamdalla na sauqin da ubabgiji Allah ya saukar musu dashi.
cikin karewar zuci khaleepa yasake duban dadyn yanajin babu dadin abun da zai sake fitowa daga bakinsa dangane da wani ciwon na daban dake jikin momyn, dandai kawai babu yanda suka iya da qaddarar ubangiji ne.
daqyar yabude baki yace
"dady Momy na daukeda cutar ciwon sugar a jikinta a binciken danai, dan har ma yafara nisa sosai a jikinta,, dady..dady ina tsoron Momy taji wani ciwo a jikinta gudun matsala ta rashin warkewa ga cuta....
dakatar dashi dady mukhtar yai yace
"komi kaga Allah ubangiji ya daurawa bawansa hakan yana nufin qaddarar sa ce ta rayuwa wanda daman a rubuce yake watom cikakken musulmi shine mai iya jure haqurin zaman qaddarar da mahallincinsa ya nufesa da ita domin gwada imaninsa, dan haka kada kasa damuwan hakan aranka Allah zaiyi maganin abun da iyakarsa tazo"
wani sanyayyen numfashi khaleepa ya sauke yace"to dady kuma zan duba magungunan daya kamata tadinga sha dan raguwar ciwon a jikinta cikin ikon Allah ma zai iya barinta in akai dace"
"Allah sa to haka ake fata ay"

"Ameeen dady muje nakaika gida inyaso saina dawo dan daman zan kwana wani aikin kuma anan asibitin zan dinga kewaya momyn kozata farka ta buqaci wani abun"
girgiza kai dady mukhtar yai yace "hakanma yayi to,
amman kabar motar a hannunka danko munyi waya da dadynka salis yana hanya ma yanzun zaka gansa inyazo kaga saimu wucen kaiba saika fito b...katsewa mgnr dady mukhtar tai sakamon kiran dady salis din dayagani yashigo Wayar tasa, nan danan Kuwa yai saurin dagawa da fadin"assalamu alaikum ka'iso ne hospital din salis?"
daga can dady salis yace"eh mukhtar bansan bangaren da kuke bane ka fito gani nn moto park na asibitin"
dady mukhtar yace"OK gani nn fitowa to ynzun"
"OK saika fito" Cewar dady salis din suka ajiye wayar atare.
tareda khaleepan suka fito anan dady salis yai musu yamai jiki dady mukhtar ya amsa da fadin"ay mai jiki kam alhamdulilla dasauqi dan tama samu barci zuwa gobe da safe zan dawo insha Allah, zamu tafine yanzun dan khaleepan shi yanada duty ne na dare.
"To shiknn saimu wucen goben dasafe madawo tare"
cewar dady salis.
haka khaleepa yajuya yakoma asibitin bayan sunyi sallama da su dadyn sun wuce suma.
office dinsa yanufa yana tafiya yana sake trying number heenduh still tana rufe ake ce masa, tsokin haushi kawai yai tareda jefa Wayar aljihunsa ya'ida nufa office din nasa dan fara shirin ayyukan dazaiyi.
tun da dady mukhtar yayo sallar asuba ya dawo yazo nan falo saman kujera ya had'a tagumi danjinsa yake yau tun tashinsa uwa wani sabon mutum dabn wanda aka daukewa kaya masu tsananin nauyi saman kansa,
sosai yake jinsa kamar wanda ya farka daga wani dad'ad'd'en nannauyen shekararren mafarki marar dadi.
dan sosai hotunan abubuwan dayaita yiwa iyayensa musamman ma dan uwansa qaninsa Ismail yanda yabanzatar dasu yazamana ma babu wata kyakkyawan alaqa atsakaninsu face ta zallar rashin mutunci dayaita danqara musu...
babu zato yaji hawaye na zuraro masa a fuska wanda rabon da hawaye su sauka fuskarsa zai iya cewa tun na yarinta danko su baffa dasuka rasu bazai iya tunawa yayi kuka koko baiba.
afili yake cewa da qarfi
"miya faru dakai ne mukhtar ka zamowa dan uwanka gurnanin zaki? miyasa kagaza cigaba da qaunarsa da tarairayarsa gamida basa dukkan jin dadi na dukkan rayuwa kamar yanda ka faro masa daga farko miyasa?! Miyasa?! Miyasa?!
akan mi hakan yaita faruwa waye silar faruwan hakan kuma tsakaninku mukhtar?" tambayar dayaita yiwa kansa knn yagaza samo amsar Kuma,, sosai yaqara runtse idanunsa sanda ya tuna mummunan fad'an bata kashin dasikai da qanen nasa akan mallakin gidansu su dukansu na iyayensu amman ya qwace?? dakuma sanda yasa aka koresa a makarantar dayake teaching bacin yasan teaching shine burin qanen nasa a rayuwa? yanaji yana gani kuma qanensa yake kwana da yunwa dudda dumbin dukiyarsa kuma? saidai ya 6uge da seda cefane a bakin hanya yana samu yana cigar da iyalensa wanda ahakan ma baqinciki yake masa kuma dai? kuka sosai dady mukhtar yakeyi har ya sauko nn qasan carpert din yanayi sakamakon sauran kalar mummunan wulaqancin da kwanyarsa

taita tunowa yaiwa qanen nasa naqin qari miyasa hkn?
gakuma babban tashin hankalinsa yanda iyayensa har suka rasu da baqincikin sa arai batareda ya nemi gafararsu ba? kuka sosai yaitayi babu qaqqautawa kamar yaron goye wanda hakan yasa masa jin saukar masasara mai kyarma ta kamasa gawani ciwon kai,,,daqyar yatashi yaje yasha magani ya dawo ya kwanta nan qasan tiles dudda sanyinsa kuwa dake damun jikinsa sakamakon masassarar daya saukar masa amman shi sam hakan bai damesa ba danji yake to miye amfanin kwanciyarsa waje mai laushi alhalin qanensa gudan jininsa nacan yana saka haqarqarinsa cikin gurarun daki dababu ko arziqin suminti a cikinsa sakamom zaizayewa dayai. (dan shi a tunaninsa har yanzun isma'il na cikin zafin talaucin daya sanshi dashi a baya shiyasa yake tunanin hakan)
haka yaita sambatu yana cewa"wayyo Allah na nacuci kaina da kaina ni mukhtar.... haka yaita yi gwanin tausayi kamin yasamu barci ya daukesa, wanda baisamu maganin yasakesa ba saida misalin qarfe tara na safia.
tashi yai zaune yai zuru, saigashi cikin ikon Allah ciwon kuma yasauka saidai kuma har lokacin babu tunanin komi aransa daya wuce yaga yasaka qanen nasa a idanunsa yanemi gafararsa ko Allah yasa nutsuwar kwanciyar hankalinsa datai qaura daga jikinsa tadawo masa.
tunanowa yai da asuba daya fito daga masallaci har sau wajen uku yana zuwa qofar gidan Ismail din amman saiyaga baiga gidan ba saima wani tsantsararren gida mai dutsi daga waje sabon gini a gidan dayasan na Ismail dinne kuma a da, sosai yaita mamaki a ransa lokacin na tunanin kodai Ismail siyarda gidan yai yabar anguwan? tunanin hakan dayai kuwa baqaramin fad'ar masa da gaba yaiba na tsoron cewa Allah sadai ba garin suka bari ba inda baisan Inda zasu koma ba bare yasaka komar nemansa shi da iyalin nasa.
ahaka yamiqe cikin kasalar jiki yayo wanka ya shirya ya fito cikin shigarsa ta kamala kaida ganinsa kaga babban mutum wanda tsaban hutu da nera suka gama bin jikinsa suka shanye, anan ya dauki makullin motarsa ya fita gidan cikin motarsa kai tsaye qofan gate din gidan dady salis yatsaya inbai mantaba kamar yanda yashiga gidan a daren jia byn sunje sun dawo daga gaido maman salis din dan haka yakega kmr nan ne qofar gate din gidan salis din.
amman dan kawar da taraddadin sa yasa ya fuddo wayarsa yakira number dady salis din yashaida masa gashi qofar gidansa yazo.
babu jimawa saiga dady salis din kuwa ya fito cikin fara'a yaqaraso inda dady mukhtar din yafito yake jinginr a jikin mortar tasa, suka kama hannun juna sukai musabuha sannan cikin murmushi dady salis yace"ay saika shigo ciki kayi breakfast ko dan nasan tunanin madam bazai barka cin wani abun ba sosai danni nazata ma sammakon fitowa zakai ay muje asubitin dantun dazun nashirya ma ni"
wani dan guntun murmushi dady mukhtar yai yace"kamin nan inason kagayan ina qanena yakoma ne dannata zuwa gidan banganin gidan saima wani sabon gini awajen"
wani sanyayyen ruwan farinciki ne dady salis din yaji a ransa na murnar jin abunda mukhtar ke fada yau da bakinsa, nason ganin qanen nasa abin mamaki, lallai kam mai roqon Allah baitaba tabewa a rayuwarsa komin tsawon lokaci kuwa haka batun shike.
amman afili saiyai shirin waina mukhtar din dan haka ya tsuke fuska kadan sannan yace "ni sanda ma na dawo garin nan nima ban iskesu ba dan jinai jama'a na cewa anwayi gari ne aka nemesu aka rasa har zamn yanzun kuwa babu labarinsu da'aka sakeji....habawa ay tunkan dady salis ya'ida zancen nasa dady mukhtar ya cimamiyo kwalarsa a gigice jiki na rawa

idanunsa na yoyon ruwan hawaye murya na rawa yace"kaddai kacemun qanena yayi duniyarsa yabarni salis? kaddai kana nufin kace yatafi da fushin yayansa akan munanan laifukan daya dinga aikata masa da iyayensu? kaddai kacemun yatsani ganin yayansa ne salis shiyasa yabar garin dan girman mahaliccunmu Allah?!!,,,,,
sakinsa yai yaduqe jikinsa qasa yana kuka yake cewa
"billahel azeem salis a dud inda qanena yashige arayuwa koda kuwa ace zan rasa dukiyata, lpia ta, raina,saina gano gudan jinina na nemi yafiyarsa najiyar dashi jin dadin rayuwa sannan zan samu salama a cikin zuciyata..can yatsaida kukan tareda miqewa tsaye yana share hawayen sa cikin murmushi dole yake cewa murya narawa
"kaicona salis nabar iyayena da dan uwana da baqincina aransu wanda narantse da girman Allah mahallicina salis bansan sanda hankali ya gurgurshe mun daga jikina ba harta kaini ga aikata musu wannan mummunan laifukan dani kaina bazan iya yafewa kaina shiba face qanena yaya femun...kakarewa mgne tai nadan lokaci sannan yasamu mgnr ta dawo masa yaci gaba da cewa"zan nemosa a rayuwa, salis zan Shiga duniya nemo qanena jinina mudawo muyi rayuwarmu cikin farinciki kamar yanda muka farota kamun wannan mumunan qaddarar data afko mani..
yaqarashe mgnr tareda rungume salis yana sake fiddo hawaye masu tsananin zafi da quna a zuciya.
sosai zuciyar salis yaji takaraya shima yafara hawayen tausayin mukhtar danzuwa yanzun kam ya yarda cewa💯wato d'ari bisa d'ari hankalin mukhtar din sa yadawo jikinsa inda har yake fadin wannan maganganun masu ciwo dubaga ma yanda yakeyi kamar zai shide wajen mgnr sbd qona masa rai da abinda ya aikatawa ahalin nasa kuma yake fad'a da bakinsa kunnensa nasake jiye masa hakan, kuma dud sanda kuwa mummunan furuci daya yafito daga bakinsa dangane da abinda yaiwa qanen nasa a rayuwa kukansa dad'a qaruwa yakeyi danya lura da hakan sosai shi dady salis din.
hannunsa dady salis ya kamo suka shiga cikin motar mukhtar din shida Kansa dady salis din ke tuqi batareda yasake cewa dady mukhtar din komi ba, baitsaya ko'ina ba sai qofar gidan baba Ismail din dankuwa yanada tabbacin baije office ba yau yana gida yau weekend.
dady salis yace"muje qanenka nacikin gidannan bar yanzun dan wasa nike maka baibar gari ba"dagudu dady mukhtar yayi cikin gidan kuwa.
hakan kuwa akayi dan nan saman qaton shimfidadden carpert suka samesu shida mama Zainab suna fira yayinda heendun ke kwance saman qafafun mama Zainab tana mata parking din tulin gashin kan nan nata data gama mata shartarsa.
ai suna ganin mukhtar din yashigo gidan yana tunkarosu babu wanda baiji d'ar aransa ba dan atunaninsu koyaji mgnr cikin heenduh ne yashigo wulaqantasu kamar yanda yasaba.
dan haka kallonsa kawai suke suna jiran jin damai yazo kuma yau.
tuni heenduh tadauki mayafinta ta rufe kanta bayan ta miqe zaune tanawa dady salis sannu da zuwa danko kallon inda dadyn mukhtar yake tsaye ba taiba sam.
sosai mukhtar yaji zafin hakan a karo na farko a rayuwarsa ace wacce take matsayin 'yarsa take nuna masa halin ko'inkula haka? amman kominene yama faru shine sila ay.
tuni hawaye suka sake cicciko masa a idanunsa dawani mugun hanzari ya ida isa gaban qanen nasa baijira komi ba ya rungumesa yana cigaba da zubda hawaye na tsantsar nadama cewa yake "qanena ga yayanka yadawo gareka yana mai neman yafiyarka akan munanan abubuwan

daya akaita gareku da iyalinka,, qanena kawa girman Allah da iyayenmu kadubeni cikin salama batareda ka tuno abinda na'aikata gareka ba kayafen qanena nayi nadama a rayiwa ta, wlh qanena nikaina ban cewa ga dalilin dayasa Nike maka haka a lokacin, dan sainayi nakoma na zauna kuma nadingajin zafin hakan mai ciwo a cikin qasan zuciyata dan billaheel azeem nagaza sanin miya sameni a lokacin jina nake kamar baniba ne wani mutum ne daban ke rayuwa a jikina..amman a yau najini a jikina nine, nine mukhtar din Ismail na inno da baffa..!!! kayafemun qanena gani na durqushe a gabanka yau ina yafeyanka kayafen dan darajar iyayenmu qanena" yayi mgnr tareda durqushewa saman gwiwowinsa hannuwansa hade waje daya ya fuskanci Ismail alamun Neman tuban sa qarara a fuskarsa dahar lokacin bata daina zubda hawaye ba.
gaba dayan wajen saida jikinsu yai sanyi dajin kalaman mukhtar dan mama Zainab da heenduh suma basusan sanda suka dinga share hawaye facey facey a fuskarsu na tsananun tausayin nadamarsa daya nuna qarara yana kuka kuma.
Allah sarki dagudu baba Ismail yashige jikin yayan nasa shima yana kuka, amman shi kukan farinciki yake na dawowar yayansa garesa, d'an uwansa talli daya a rayuwa hankalinsa yadawo garesa tomi yafi wannan dadi da farinciki bayaga yadinga godia ga Allah mabuwayi gagara misali.
saida sukai kuka sosai dan tunowa da rayuwarsu ta baya dasukai da iyayensu mai dadi saidaga bisani baba Ismail yadinga cewa"wlh nina nayafe maka Yaya na, daman ban riqekaba a raina Sanin yanda muka shaqu da juna nasan cewa komin Daren dadewa muddan darai a jikinmu zaka dawo ga gudan qanenka,zamu cigaba da yin daddadan rayuwar mu cikin salama da qaunar juna kamar yanda muka saba tun yarinta". yaqarashe mgnr tareda qara riqe yayan nasa yana hamdala gamida yiwa annabi salati.
jikin kowa zuwa lokacin ya mutu mururus a wajen kuwa sbd kukan babba tashin hankali ne dashi.
daqyar suka saita hankulansu suka zauna nan kan carpet din sosai gaba dayansu sann mukhtar yace"ngd sosai qanena daka yafemun ngd ngd"! mgnr yake yana goge hawayen fuskarsa dasuka gaza yanke masa har lokacin, yana murmushi kuma. kamo hannuwansa baba Ismail yai yace"yayana kadaina damuwa dan qanenka komi yawuce garesa tamfar ba'aiba dan haka kadaina *tuna baya* kan wannan lamarin daya wuce ma dan Allah"
yayi mgnr cikin murmushi"
shima dady mukhtar din yayi wani qaqararren murmushi baice komiba dan ko haryanzun abunda yaiwa qanen nasa dud inya tunosa baqaramin bugun zuciyarsa yake qara yiba.
d'an bata fuska baba Ismail yai sbd lura da hakan dayai dan haka yayi nufin furta masa abinda suka saba cewa juna shi sa'ilin yarinta dadud in daya yaga dayan a halin damuwa, sake duban yayan nasa yai yace *"zanyi fushi dakai na tsawon minti daya yayana,* inhar baka daina damuwa haka bafa"yaqarashe mgnr cikin d'an murmushi.,Allah sarki nan take mukhtar yasaki dariyan dabai shirya ba sbd tuno wannan ta'adar tasun dayai.
nantake sika ida yin d'ayar ta'adar tasu wato suka had'a hannu🤜🤛a dun qule suka sake sakin dariya cikin farinciki kmr su cinye juna dan murnar farincikin shiryawar tasu yau a rayuwa cikin hukuncin Allah.
cikin murmushi dady mukhtar yadubi mama Zainab datake qara goge qwallar farinciki tana mai fatan Allah sa wannan shiryuwar harda yayar tata furdauseey.

jitai dady mukhtar din yace"Zainab kema kiyafemun laifukan danai miki dankema kinada haqqi akan furta yafiyarki a kaina danna matsa muku number haqiqa a rayuwa" dasauri mama Zainab ta girgiza kai cikin kakalo murmushi tace"bakomi Yaya mukhtar nayafe maka ubabgiji Allah yayafe mana baki daya" aminn suka amsa harda dady salis dake gefensu yanata faman zuba murmushi.
" 'Yata kema zaki yafewa baban naki ko?" cewar dady mukhtar din daya dubi heenduh cikin fara'a.
akunyace tace"sosaima nayafe maka komi duka dady" taqarashe mgnr cikin miqewa tsaye dasauri tabar wajen tashige dakinta ranta fal qal murnar hadin kawunan iyayen NATA.
dariya sukai mata nan take dady salis yasasu kowannen yai salatin annabi Muhammad s.a.w. dan qara jadada farincikinsu kan hakan.
bayan sunyi harda add'ou harga iyayensu sun shafa ne sannan dady mukhtar yaita kallon gidan qanen nasa cikin mamaki danyasan da gidan aiba haka shike ba dandud yamace sa'ilin daya sansu cikinsa.
baba Ismail ne yalura da hakan dan nhaka yace"yayana wannan gidan namu Yaya salis nema yagyara mana shi sannan yabani manager a ma'aikatarsa(dayake shima dady salis yashaidawa mukhtar din ma'sanaantar tasa daya bude)
danhaka kaga komi na rayuwarmu yacanza cikin ikon Allah"cikin tsantsar farinciki dady mukhtar ya rungume dady salis yana masa godiyar alherin dayaiwa qanen nasa, shiko dady salis nunawa yai babu komi ai dud yiwa Kaine an rigaya da zama daya.
sunjima suna zaman farinciki da mgnr cikin heenduh da dady mukhtar yaimusu cikin tsananin jindadin zai samu jika a jinin dan uwansa.
sai wajen qarfe sha biyu na safiyan ranar sannan dady mukhtar ya dubi qanen nasa yace "kozaka biyomu ne asibiti qanena?" cikin mamaki baba Ismail yace"waye babu lpia yayana?" dady salis ya amshe dacewa"Hjy furdauseey CE amman jikin yayi sauqi" dady mukhtar yace "dan khaleepa ma yace zata iya dawowa gidan yau"
Allah sarki
Nan take baba Ismail yamiqe, mutum mai sanyi hali dan Sam baituno rashin mutuncin Hjy furdauseey ba amman yadubi mama Zainab yace jeki maman heenduh ki dauko mayafinki mutafi ganota tare..dady mukhtar yace"dama kabarta qanena" girgiza kai baba Ismail yai yace"ai dubiya CE yayana bakomi"hakan kuwa mama Zainab tahado kayan abinci tasaka a basket sannan sukatafi harda heenduh ma.
Suna isa dakin da Hjy furdauseey din take nan suka iske Hjy Hadeeza harda zarah sai khaleepa dake zaune gefe momyn tasa yana bata ruwan tea a tea spoon zuwa cikin bakinta da Allah ya temaketa yadawo daidai daga gurmud'ewar dayai hakama kuma hannunta yadawo daidai shima.
Hjy fuedauseey naganin yanda dady mukhtar yariqo hannun baba Ismail tuni zuciyarta ta tsinke babu shiri ta qware da tea din bakinta dan ganin abun take Uwa a mafarki.
"sannu Hjy" suka hau mata yayinda dud rabin hankalin doctor kega heenduh dayaga sai faman kumburi take tana cika tana batsewa wanda shi yakasa gane dalilin hakan, yayinda a bangaren heenduh ba komi ne yajaza mata hakanba face ganin zarah datai kusada shi.
nanko suka hau bankawa junansu harara a boye itada zaran kowace kishi na cinta dankuwa Hjy furdauseey tafada musu komi yafaru dangane da mgnr cikin heenduh tun kamin shigowan

khaleepa ma dakin tana fada musu tana kuka , lokacin cikin dabara Hjy Hadeeza tadinga kwatanta mata da tabar tada hankalinta inyaso in sun koma gida sasan abinyi .
shiyasa koda su baba Ismail sukai mata yajiki kadaran kadahan ta amsa musu wato a daqile babu yabo babu fallasa.
danzuwa yanzun kam tashaida haduwan kawunansu da junansu yadawo.
jitake uwa tai hauka ko lokacin.
sosai khaleepa yakeson kebawa da sugarn tasa sai alama yake mata da 'ido amman sai faman sake daure masa fuska take tanashan qamshi, yayinda Hjy furdauseey taqurawa cikin heenduh ido tanaji Uwa ta tausheta taita bugun cikin harsaita mutu snn zata barta.
dan dai kawai rashin imani kalar na hjy firdauseey.
dole khaleepa yahaqura kuwa badon yasoba ganin dayai lollipop din tasa Asama take yau mulkin ya motsa.
saida suka jima sannan suka rankaya harda Hjy furdauseey suka nufo gida cikin motocinsu dandama khaleepan ne yace kada su tafo abari dadyn yazo amman dabadan haka ba datuni Hjy furdauseey ra tsufa gida yanda takejin ciwon mgnr nan ta cikin heenduh mafita kawai takeson samu wajen qawarta ko'amutu ka'ai komi wannan ba damuwarta bane, damuwarta shine Indai za'a kashe d'an cikin heenduh da'ita kanta heendun kokuma ahaukatata to yanzun ko zataji daidai.
danko tuni tasha alwashin komi zai faru bazatabar bibiyan heenduh ba saitaga bayanta da iyayenta.
itada Hjy Hadeeza da zarah na cikin mortar ita Hjy hadeezan, yayinda baba Ismail da dady salis da dady mukhtar suke cikin mortar dady mukhtar din.
saikuma mortar khaleepa da heenduh CE kawai a cikinta saikuma kwandon kayan abincin dake bayan mortar wanda mama Zainab takai wanda qiri qiri su haj Hadeeza sukaqi karba,
har lokacin kumburin fushi heenduh kawai takeyi yayinda tuqin sa yi shima baice mata uffan ba har suka isa cikin anguwarsu.
kaitsaye su Hjy Hadeeza gate din gidan dady mukhtar dinsuka shiga da motarsu, yayinda shi kuma dady mukhtar yakarkata motarsa domin zuwa masallaci sallar azhur bayan ajiye mama Zainab dasukai kodar gidan nanma yabar motar shima sukai alwala suka shiga masallaci sakamon sallar azhur da suka jiyo baba yawale nashirin had'a jam'e. khaleepa kuwa ganin dayai heenduh na qoqarin bude motar sanda yai parking qofar gidan baba Ismail din aiko yayi saurin danna remote ya rufe dukkan qofofin motar baitsaya wani bata lokaci ba yayi saurin kwantar da fuskarsa saman laps dinta.
cikin wata sabuwan hararsa da turo red lips dinta take cewa"nika dagani natafi gida."
tsurawa fuskarta idanunsa yai a marairaice yace
"waikin daina sona ne? haba lollipop na kiketa mun bore yau dudda daukin ganinki danakeyi amman ke ko a jikinkiki kin barni a damuwa da naita Kiran wayanki kashe lollpop na why? Kuma gashi nazo anata hararena konayi laifine nadaba haquri sugar lips na" yayi mgnr murya a sanyaye shagwabe.
hararsa tasakeyi sannan tahau ture kansa a cinyoyinta amman yaqi bata damar hakan saima zagayo da dogayen arms dinsa dayai ta qugunta yasake kwanciya laps dinta sosai.
cikin tsiwa tace
"nika rabu dani natafi inyaso saikaje waccen Mayyar zarah din taita cigaba da shisshige maka

kai kuma kana qyaleta"
dariya sosai mgnr tabasa saidai yakanne yadubeta yace"Sry sugar na i swear bansama tana shisshuge munba ni bare nadamu da ita awajen,, qasa qasa da Maurya yai yace
"Kinsan ke d'ai CE a zuciyar nan dukkanta lollpop na kidaina damuwa"
wani farinciki kalaman suka sanyata, jin yana mata susar qadangare a tafin hannunta daya riqo hakan yasata qyalqyacewa da dariya.
sosai yaji dadin hakan miqewa yai zaune yamatso jikinta a cikin kunnenta yace "I miss you lollipop na"!
lumshe fararen idanunta tai murya qasa 2 itama tamayar masa"miss you too my doctor"
saida ya janye rigarta ta qasa yahau shafa cikinta shafaffe kmr babu baby a cikinsa yana fadin"baby neyler na kema nayi missing naki fa sosai yayi mgnr tareda daura kunnensa a cikin wai nufinsa baby tabasa amsa yayinda heenduh keta qara sakar masa siririyar dariyarta itama tana shafa cikin da hannunta cikin jin dadi.
dasauri yadago yace"lollipop na kinjime baby neyler tace kuwa" cikin zaro idanuwa heenduh tace"a'a"
saida ya murmusa tareda kashe mata ido daya snn yace"tace atemakawa dadynta muje otel danmu gaisa sosai da ita dan nkwana biyu batajini ba kusa"
turo baki heenduh tai zata kamar masa kukan nata na shagawaba nanko yayi saurin kamo bakinta cikin nasa yana gigitata tunaninta.
abunka da'an kwana biyu ba'a had'u ba hakan yasa heenduh sake ruqo fuskarsa da hannuwanta tana taimaka masa yayinda take qara tura masa sugar lips din nata abakinsa..sosai jikinsu yamutu babu shiri ya kwantar da kujerar motar ya kwantar da heenduh akai ahankali yasake bin jikinta ya lafe bayan yadaura hannunwansa bisa nashanunta dayaji sun qara masa wani mugun cika da laushi ,
snn yamaida bakinsa kan nata yana qoqarin zage zep din gaban rigarta ne sukaji ringing....
dasauri heenduh ta bude idanunta tai azamar miqewa Zaune tafiddo wayarta a jikka taga mama Zainab CE kekiran..gabanta na faduwa tadaga Wayar taji mama Zainab tace"wai ina kika tsaya ne heenduh tun dazun kuma?"
cikin rawar murya tace"gag...gani nan mama tafe na biya ta wajen baba d'ahara ne"
"to kitafo ynzun kinajidai anata sallah ay"
"To mama"
tana ajuye wyr tayi saurin dubnsa tace"please doctor budemun qofar nan natafi"
Har aransa baiso hakan ba amman Yaya'iya, cikin kasala yace "zamuyi vidio chat ko sugar na?"
sosai ta tausaya masa ganin halinda yake ciki amman Yaya ta iya babu damar tai helping nasa koyayane dan mama Zainab najiranta tadawo.
ahankali tace"eh"
kamar zaiyi kuka yasake jawota ya sake tsotsan d'an zagayayyen bakintan sosai sannan yabude Mata kofan ta dauki kayansu dake back set tawuce ciki,
sai dayaga shigarta hartana sake waiwayonsa snn tashige gidan duka daganan yawuce shima sakamon wayar da yunus keta masa lokacin.
Hjy furdausey kuwa sun nutse daki itada zarah da Hjy Hadeeza kan batun heendun.
Hjy Hadeeza taja numfashi sannan tace"kinga tun rannan nace miki kizo muje gidan mlmin nan nawa kikace abari alhj yadawo togashi yadawon shikuma mlm wlh yau kwanansa biyu yaje

lekoja wani aikin"
Dafe qirji Hjy furdauseey tai tace"kibari dan girman Allah? Knn haka zamu bar wadannan tsinannun mutanen nan ne sakaka muyita jiran harsai mlm dawo?,yanda nalura hankalin Alhj Yakoma garesu yau muraran? Kai ina wlh bazata sabuba ehe"caraf zarah tace"wlh gaskian ki momy kidau mataki Kansu barema tsinnanniyar nan heenduh data dauki cikin danki"
runtse udanuwa Hjy furdauseey tai tace"daina tunamin HK zarah dan zuciyata tarai bindiga ne wlh"
Hjy Hadeeza tace "haba kwantar da hankalinki inada malamai kala kala Gobe maje, ai mumeda garin mun san ko'ina, gidan Mlm da gidan boka" dariya sukai ta mugunta haka suka wuni saqa mugun nufinsu ga heenduh kuwa da iyayenta.
washe gari kuwa sukaiwa gidan wani dan tsubbo tsinke sukakai masa kokensu nantake yashafa qasa yashare yai wasu surutai zuwacan yadago yadubesu yace"Hjy saidai fa kuyi haqyri domun yarinyar nan da iyayenta sunci sunsha maganin tsari a jikinsu daga dukkan mugun Abu Daza'ai musu,
dan haka ina baku shawaran ku haqura dan ko'ina kuksje haka za'ace muku saidai aqi fada muku gskia".
haka suka baro wajen dan tsumbun jiki a sanyaye basu daddara suka qara zuwa wajen wani shima haka yace musu kmr yanda nafarkon yace musu.
Basu qara daddaraba dai saida sukaje wajen bokaye da malamai samada a qirga a ranar amman dud babu sa'a haka suka dawo gida sika baje falo cikin takaici matuqa.
Dafe kai Hjy furdauseey tai tace"dama nasani tunda marakusa na ya mutu bazan sake samun hatsabibi kamarsaba, gskia nayi mummunan rashi" tayi mgnr tana matse kwalla tareda fyace majina da habar zanenta.
dafata Hjy Hadeeza tai tace"in haggu taqiya saimu koma dama, ma'ana mubar komi har zaqwaqurin mlmin nan nawa yadawo ayita taqare dan zazzafan aiki yke wlh kota ina yasan makaman mutum, amman kafunnan zamu canja taku, wato ina nufin mukoma kissa tamu ta mata wato cikin laf laf da ladabi da biyya zaki shawo mana kan ahljnki tahanyar nuna masa sonda zarah ke wa khaleepa wanda yasata kwanciya asibiti, to kinsan mukhtar da tausayi nasan zai amunce...
tafawa sukai Hjy fyrdauseey cikin qatuwan dariya tace kinkawo Shawara, mufara da itan to Kan Mlm yadawo ayi mai gava dayan ga matsiyatan mayun."
hakanko akai dadare Hjy furdauseey taciwo kwalliya tanufo dakin dady mukhtar tanawani rangwada kotsari babu abun.
har India yake kwance taje tazauna.
Kankacemi saita fashe dakukan qissa,, dasauri yatashi zaune yana fadin"subhanalla furdauseey lpianki kuwa? Miyafaru?"
cikin kukan munafunci taci gaba da cewa"kataima mun yallabaina kafuddani kunyar qawata Hjy Hadeeza, wlhl azeem yallabai na karkaso kaga yanda zarah ke matuqan son khaleepa,harfa a sanaddiyan son
sa nefa harta kamu da ciwon zuciya dansai ma jia aka sallamota daga asubiti".
dasauri dady yaqara gyara zamansa yace"innalillahe..
yanzun abun haryakai gasu wannan ciwon haka a jikin yarinyar daman?
saida ta fyace majina da hankicerf sannan faki idonsa taimasa gwalo tace"wlh kuwa yallabai

yamafi haka indai kan sonda zarah kewa mai tsada ne,, shiyasa na tausaya mata, dan so musifa ne zai iya kar mutum kataimaka dan Allah ayi auran nan"
shiru dady mukhtar yai dan sosai yaji tausayin halinda akace zaran take,, kuma ganinsa in akai auran da zarah dud qara ma hada danqon zumunci ne inda mamanta aminiyace ga Hjy din babu wata matsala.
dagowa yai tadubeta cikin tausayawa matuqa yace"shiknn daina kukan za'ai auran insha Allah,, kuma ki fadawa zaran tadaina damuwa ta kwantar da hankalinta , gobe in Allah yakaimu zanje nashaidawa qanena samuje neman auran nata harda salis kinga sai akaisu gidan nasa rana daya, heenduh a zuwan uwargida zarah amarya kuma Ince shuknn zance ya qare?"
sosai taji wani kutu kutun baqinci a ranta na ambato Ismail da heenduh dayai amman yata iya dole tabi komi sannu kmr yanda suka tsara.
danhaka a fili taqaqaro murmushin dole snn tace"eh shiknn yallabai na ngd"
daga haka suka kwanta dan dare yafara kam lokacin.
Kamar yanda yafurta kuwa washe gari yaja yaja salis sukaje gidan Ismail mama Zainab taimusu shimfida tabasu wake.
 anan suka zauna dady mukhtar yafada musu buqatarsu tazuwa neman auren zarah byn ya shaida musu ciwon nata kan binin khaleepa cikin tausayi..
Sam baba Ismail baiji haushin hakanba saima tausayawa zarah dayai shima sosai.
sabanin salis dayaji wa heenduh kishin za'ai mata kishiya tunkan tare, knn ranar tariyarta gidan mijinta ranar zuwan kishiyarta knn? baitaba jin hknba shikam.
qara duban baba Ismail yai yaga ransa fess ba damuwa saima murmushi dayake yana cewa"Allah kaimu goven saimuje gidansu zarah dun asa lokacin daurin auren Inda kace babu lokacin saka wani biki inda tariyar tasu duka yanda nike zato bazata wuce nanda sati biyu ba, Allah sa alheri kuma yayana yabashi ikon riqesu dukkansu"
sosai dady mukhtar yaji farincikin goyon bayansa da d'an uwan nasa dayai masa batareda damuwa ba da hukuncin nasa "
danhaka yace "aminn qanena ngd da kyakkyawan fahimta dakamun" daga nn suka fita dukkansu a gidan a tare su 3 zuwa gidan baba yawale dan shaida masa shima zancen a matsayinsa na uba garesu.
heenduh dake cikin d'akinta tanajin komi suka gama tattaunawa dan tuni fuskarta tai kace kace da hawaye, da gudu tafada gadonta tana kuka wiwi banda radadin zafi babu abinda zuciyarta ke mata.
cikin muryan kuka ta tashi zaune a fili tace"wlh narantse da Allah bazan taba zama a cuceni ba tafiyata zanyi sai abasa itan da hujja" da sauri ta miqe tasaka hijab da takalmanta zata fuce daga d'akin knn taji cikinta yayi mata wani mugun juyawa babu shiri tadafe cikin tareda durqushewa qasa tana cije lebe tareda faman sakin nishi kan kukan azaban zafin ciwon murd'awan cikin nata dayake yakece mata...

~Indai kasan/kinsan tanzz kawai zaki/CE ko kyautar emoji babu add'ua bare comment dud innai posting, to gskia kai/ ki shiru da bakinka/ bakinki dan harga Allah na yafe miki/maka akan zaman type din danai ka karanta /kika karanta, dan wnn abubuwan 2 basu marubuci keso wajenku ba inkunyi tunani fisabillila har in dai kana karantawa kanajin dad'i kuma yadace kai

coment kan labarin daya qunshi novel din koda kuwa comment s din ba yawa ne maimakon heart ko tanzz, sharhinku ga labarin shine zaifi bamu qwarin gwiwar qara muku hob'basa ay muma kan lavarin da kuke bibiya~.

```daga taku Maison ganin farin cikinku```...

Xexen Fasaha.
[3/30, 7:15 AM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO!!!

Story and writing by Xayyneb💤💤

kuyi haquri masoyan heenduh kan complain naku da kuketayi kan auran zarah da khaleepa, dan saida zuwan wata cutar ake kauda wata cutar kamar dai yanda zai faru nan gaba in kuna biye da alqalamin xexen fasaha da yardar Allah....

Kuma comments naku ya burgeni ya qayatar dani sosai😍👏🏻👍💯

~dedicated to my mom Sadeeq hauwas~.

I heart you mom Ahmed.
👁️📦👁️
🅿️🆓
R untse idanunta tayi katamau hannunta dafe da cikinta tahau cije baki wanda har lokacin cikin bai lafa ba, babu shiri ta fara kamo sunayen Allah kala daban daban dan neman rangwame.
tadauki kusan munti 15 a hakan tana hadawa da addu'oe sannan taji kamar d'aukewan ruwan sama ciwon ya tafi lokaci daya kamar ba'ita bace take murqususu ba.
wani sanyayyen numfashi ta saki bayan tayi wani tunani sai kawai ma ta yakice hijab din bayan cire takalmn nata datai takoma bakin gado ta zuba tagumi still hawayen zafin kishi basu tsagaita daga tsattsafowa ta cikin idanunta suna sauka saman fuskar taba tareda radadin zafin da zuciyar ta ke mata.
muryan mama Zainab taji bakin qofan kamin ta'ida shigowa d'akin ta zauna tana kallon fuskan heenduh dahar lokacin ta gagari share hawayen nata.
har aran mama Zainab taji tausayin 'yar tata wanda tasan dole kowace mace akaiwa hakan tadamu amman duniyar dole sai ana runtse mata idanu koda bakason abun kuwa to girman mutumin da matsayinsa gareka daya nemi afuwan hakan daga gareku dole ka saduda kayi mubaya'a bare wannan raya sunna ne ba wani aibu ba.
bareshi mukhtar dinda keda babban matsayi garesu ai yafi gaban yanemi alfarma garesu su gagara masa.
dafa heenduh tai bayan ta goge mata hawayen fuskarta cikin dauriya tace"kiyi haquri heenduh
```

nasan kishi akwai ciwo to amman haquri zaki, inma kinyi tunani ai abokiyar zama nada dad'i ta fannoni da dama in Allah yasa kikai dace data gari, mutane basu gane bane,kinga a misali koda baki lpia miji bainan zata iya temaka miki harma da dawainiyan yaranku dasauran hidiman gida, dan haka kiyi haquri Inda bawai saman ki zata zauna ba kuma ba kanki aka farawa mace qarin abokiyan zama ba bare ki damu kanki, dan Allah kiyi haquri ki kwantar da hankali dan kishiya 'yar Uwa ce zakiga in kuka hada kanku mijinku shima ba qaramin jin dadi da alfaharin hakan zaiba"
shiru heenduh tai tana sauraron maman aranta take cewa"kayya dai mama dud abubuwan nan da kika lissafo na tabbata zarah ko daya bazata iya ba bare aji dadin zama da'ita, amman dayake batason musawa Maman yasata cewa cikin muryan kuka"to..to mama bakomi"
murmushi mama Zainab tai tana shafa kan heenduh tace"yawwa 'yata 'yar albarka naji dadin yanda kikemun biyayya akan komi na baki haquri a Kansa dama sauran wasu
Abubuwan wanda da'ace haka 'ya'yan zamanin nan kewa iyayensu daba hakaba, da duniya tazauna lpia, amman ynzu lokaci yazo da iyaye zasu umarci d'a da abunda sukega sunfi qarfin samunsa garesa amman kai tsaye zai nuna bazai iya ba..amman Allah kyauta dai yakuma shurya mana zuri'a
"Ameeen mama" "heenduh Kema kuma Allah baki masu miki biyayya sauda qafa kamar yanda kike mana a rayuwa"
cewar baba Ismail daya shugo dakin yazauna shima.
mama Zainab ta amsa da "amunn baban heenduh, Allah kuma sauketa lpia dai"
"Aminn" inji baban.
har aran heenduh taji dadin addu'an iyayen nata amman yanda zuciyarta ke mata quna akan dud wai matan kirki na garin nan arasa ma wacce za'a bata a matsayin kishiya sai wannan muguwar ballagazan,, ??!sosai ta qudura a ranta dud ranar da kuwa khaleepa igiyoyin auran zarah ya yarda ya riqesu a hannunsa to wlh saiya gane wacece heenduh a ranar Inda shida bakinsa ya furta mata baison zarah, todanmi kuma zataji haka daga Sama nawai auransu katsam? to knn ma da saninsa da amincewarsa hakan zai faru itace zai maida shashasha ma? wani mugun haushinsa daqin son ganin koda fuskarsa ne sbd kishi daya rufe mata ido taji ya kamata.
daurewa kawai tai taci gaba da sauraran nasihohin da iyayen nata ke qara mata Wanda gaba daya bama cikin nutsuwarta take ba lokacin dan tunanunta yai nisa na qudurinta dake ranta.
bayan fitar baba Ismail da bama tasan ya fita ba taji mama Zainab tace"wai nikam heenduh wanne kayane can kiketa faman rufewa da bargo tunsanda nadawo daga Zaria fa na lura dasu a dakin nan?"
dasauri heenduh takai dubanta ga manyan jikkunan nan dasuka amso kayan d'inkin da khaleepa na kayan daya siya matan ne wanda har yanzun ko daya tagaza fuddowa tasa sbd gudun tambayar Maman a lokacin shiyasa taketa faman rufesu.
amman yanzun datasan cewa maman tasan da mgnr su ta auren da khaleepa fili yasata sauke ajiyan zuciya tareda miqewa tsaye batace komiba takamo hannun mama Zainab suka isa ga jikkan ta yaye bargon saiga d'ika d'ikan ghana mst go dinnan cikeda kayan.
daqyar tasake duban mama Zainab tace"doctor ne ya kawon su sanda kina Zaria , ni ko daya banma gwada sawa a jikina ba, tayi mgnr tana hararan jikkunan kamar khaleepa ne akan nasu sbd haushinsa dake qara nanuqar mata zuciyarta saitakeji Uwa ta qona kayan ma kotai sadaqa

dasu tadaina ganinsu kwata kwata.
cikin fadada murmushi mama Zainab tace"ina ruwan khaleepa baigajiya ay"
tana mgnr ne tana duba kayan bayan zuge zip din jikkunan datai,, sosai mama Zainab tayi mamakin dumbin kayan nan da khaleepa ya kashi kudi haka Kansu, duban heenduh tai tace"kuma heenduh bakice yarage siyan kayan ba sainikega kmr anyi barnar kudi da yawa, wannan kaya haka da yawan gaske na kanti dana dinkawa uwa dai lefen mace guda goma kokuma ince na 'yar shugaban qasa?"
cikin duban Maman heenduh tace"nace masa yarage daukan kayan mama amman saiya nuna a'a.
shiru mama Zainab tai tace"dudda kike matarsa komi Allah yabasa iko zai miki ammn kayan nan da yawa fa heenduh gwanin tsoro, ga tsadan gske kuma dan dud supopi ne atamfofin hakama lace da material da kayan kantin nan akwai kudi sosai, gskia kam qwamma da baki fara saka kayan nan ba zaifi kyau inkin tare gidansa kmr yanda aka tsara nanda sati2 kyasa kayan acan karki jawomana mgn aga kinasaka wannan manyan kayan kinsan mutane da zargi zasuyi zaton babanki na kwasan kudin inda yasamu aiki yana kashe mamu, dan haka barima kigani kamamun jikkunan mukai d'akuna can qarqashin gado na ajiye su...dole kuwa takamawa Maman sukakai kayan can duka sannan fa tadawo dakinta ta kwanta tana ganin kiran wayan khaleepa Amman saidai tai tsoki ta latse koren kiran ya katse..dataga bai daina kiran ba saima ta kashe wayar gaba daya tai kwanciyarta tana tunanukan takaici hardaga qarshe tasamu barci ya dauketa.
a marecen ranar ne dady mukhtar sukai mgn da baban zarah akan mgnr zuwa Neman auren zarah wa yaronsa khaleepa saigashi nan danan baban ya amunce da cewa yabasa auren zarah ga khaleepa, dan har aran baban zarah yayi matuqar farinciki da hakan kamar ya zuba ruwa a qasa yasha yakeji dankoba komi rufin asirinsa ne in zarah tai aure koya samu tadaina ja masa mgn da zund'ensa ga mutane idan yafita da surutunsu nacewa gidansa yafi qarfinsa matarsa da 'yarsa _ke mulkasa.
 wanda da haka ne suka rabu da daddy mukhtar bayan sunyi musabuha kowa yawuce gidansa.
washe gari ko kamar yanda aka
Zanta da baba Ismail da dady salis da dady mukhtar din suka shirya sukaje gidansu zarah anan sitroom baban zarah da yayansa suka amshesu da karamci bayan anyi abinda yadace aka tsaida ranar daurin aure nanda sati 2 masu zuwa.
dazasu tafuko har waje baban Zara yabiyosu yana fadin yafa gode yafa gode Allah saka da alheri yabar zumunci.
sosai a zuqatan su dady mukhtar suka rasa godiiyar mi baban zarah yakeyi musu haka inda sunsan indai dan arziqi ne shima yanada nasa a aljuhu kuma susukaje nema aka basu...dole dai suka fudda zaton komi a ransu suka tafi.
da misalun qarfe hudu na yamna zarah da mamanta Hjy Hadeeza suka fad'o falon gidan kuwa Uwa an jefosu dan sallama ma kam a janye batunta gefe dan batta cikin tsarinsu na rayuwa ga wuri in sunje bare suyi ta.
anan falo suka samu Hjy furdauseey ta daura kafa daya kan daya tana kallon tibi.
Aida sauri babu ko kunya zarah ta fad'a jikin Hjy furdauseey tana tsallen murna take cewa"wayyo dad'i ni zarah nanda sati 2 zanzamo mata a gidan Yaya khaleepa na kyakkyawa na,

ai dole nema naware kudaden gyaran jiki dana kayan mata danya jini zamzam kota ina, ammanfa Hjy kin gyaramun zako kikiga yanda zan dunga tattalin d'anki kosau nawa ya buqaceni a rana zan basa wlh dan niko banda rowan kaina kaman yanda naji wasu matan nawa mazajensu wlh, tofa wannan shine albishir dazan miki momyna suruka ta sakamakon namijin qoqarin dakikai mun wajen sawa dady mgnr auran nan ta tabbata da shirinki na qasa ...buge mata baki Hjy Hadeeza tai tace
"to marar kunyan banza uwarmi takawo mgnr raya sunna kuma anan?, bakida setin bakin iya mgn ko zarah? Ynxunfa Hjy ta zama surukanki ki daina yin abu haka sakaka na gallaqanci" tayi mgnr tana qyaftawa zaran ido a fakaice..aiko cikin fahintar mgnr da uwar tai mata da ido dayake 'yan bariki ne itada uwar harta gane nufinta, shiyasa nan danan zaran ta boye fuska Uwa gaske wai ita nan kunya takoma tazauna ta nutsu tace"sorry in law na momy tsabar d'okin murna ne wlh yasani fadan hakan ban shirya ba" tayi mgnr tareda yiwa uwarta signal da uban tayani muninta a fuska.
murmushi Hjy furdayseey tai tace"tomiye na damuwa danki CE hakan? ba mijinki bane zarah 'yata?, ni fa damuwa ta shine ynx Mlm yadawo wlh kona rabasa da auran wanna n
 Mayyar yarinyar kokyaji dadin waqatawa ke daya a gidansa"
fashewa da dariya zarah tai tace"wlh kuwa dakin kyauta"
Hjy Hadeeza tace"ay dayake ma munyi waya dashi d'azun yace saura Kadan yagama aikin NASA nacan yadawo nan"
Hjy furauseey na shirin mgn saiga dady mukhtar ya shigo cikin falon da sallama ga alama dawowarsa knn daga waje.
dasauri zarah da Hjy Hadeeza suka gaishesa cikin girmamawan qarya, shiko ya ansa cikin fara'a sannan yawuce samansa.
nan Hjy Hadeeza taiwa hjy frdauseey rad'a da cewa"sun wuce zasu dawo anjima" sannan suka fita ita kuma ta koma tazauna tana cigaba da kallon tv dan tasan wanka Alhj mukhtar zaiyi shiyasa bata bisan ba ta tsaya zamn jiran yagama ya sauko.
azahari TV take kallo amman aranta wassafawa take na kalar mummunan ta'adin dazatasa mlm yaiwa heenduh muddun yadawo kuwa.
wani murmushin mugunta tasaki taredata girgiza kafa a fili tace
"hmnn dani kuke zance matsiyatan nan wato ma har kun mance wace Firdausyn meron tsimbe knn ko?
wacce bata mantuwa da yafiwa bare kuma daukan fansa? Hmnn muje zuwa tayaro kyau take bata qarko ay yayinda yaro baisan wuta ba inba takata yaiba yajita a jikinsa ba.
wata mugunyar dariya tasaki ita d'ai a wajen uwa wata mahaukaciya sabuwan kamu, aranta tace "hmm auran nagani kuma banga zaman saba ay, tsinannu mayu kawai" haka taita tuqawa tana qarawa harsanda taji motsin saukowar dady mukhtar daga saman benen zuwa falo.
yana qarasowa kuwa kuwa yana zama saiga khaleepa yashigo falon d sallama hannunsa riqeda jikkar laptop dinsa idanunsa sayeda medical farin glass dinsa gwanin fin kyau yama qarayi yau.
sosai yake a gajiye dan aikin dayai yau asubiti ya wahalshe sa sosai ga tentions dinda heenduh ta aza masa na rasa gane kashe masa waya datai yau,
burinsa kawai yai wanka yaje gidan danshi gudunsa ma kada kobata lpia bata dai fada masa bane ko batason takura danyasan halin 'yar kayansa shiyasa takashe Wayar tatan may be ma.

saida yaje jikin momyn da dadyn nasa sukai kalar gaisuwarsu sanan yamiqe yana yamutsa fuska yace"wlh dady Momy nagaji sosai yau a hospital, wanka kawai nike sonyi konaji Strong nawa yadawo ..cikin murmushu dady mukhtar yace
"sannu my son jeka kayo wankan daman akwai mgnr dazumiyi dakai"
"to dady"
Momyn tace
"yawwa maitsada na afito lpia to"
dasauri yahaura Sama kuwa zuwa side nasa.
duban ta dady mukhtar yaice
"kinsan dud bidurin mgnr auran nan da ake baida labari amman yanzun zaijisa nasan zaiji dad'i".
Cikin murmushi tace"qwamma yasani kam kozai fara shirye shuryen daya kamata shima a matsayinsa na ango kam"
tayi mgnr cikin girgiza qafa.
minti 20 tsakani saigashi ya sauko falon cikin shigarsa ta jar t-shet da farin jeans sosai sukai masa kyau kayan musamman dasuka kama jikinsa saiyai gwanin kyau da burgewa sosai,ga damtsensa cike hakama gashin hannunsa har zuwa wajen yatsunsa kwankwance suke baqaqe yas yas, sajen fuskarsa da girarsa gamida cikakkun gassan idanunsa madaidaita shiya qara bayyana sirrin kyan fuskar tasa dan kallo d'aya zakai masa kai zaton baqon balarabe ne ingarma fari Sol a gabanka.
tundaga nesa iyayen suke kallonsa dayaba tsarin kyan halitta ta d'an nasu.
harkusa da dady mukhtar ya zauna ya kallesa yace "iam ready dady na wace mgn zamuyi?"
Yayi mgnr tareda kallon momynsa Uwa gareta zaisamu amsar.
saida dady mukhtar yai gyaran murya tareda gyara zamansa sannan yace"mgnr dai nasan daman dai kasan da zamanta tuni tunknma Nina sanda ita"
duban dadyn yai yace"mgnr CE ta 6acemun amman tunamun dad dan gskia I forget it"
dady mukhtar yace"OK ba wata mgn bace illa ta auran Ku da zarah wacce kuka gama tsarawa kaida momynka yun asa'ilin da bannan, sannan kaida bakinka inbaka mantaba mukai waya Kn mgnr kuma ka jaddadamun amincewarka ga zarah, inban mntaba lokacin harna roqi ku dagan qafa kaida momynka kamin na dawo dannaga kamar momyn taka taso ayi bikin tun lokacin, saida na alqawanta mata dazarar na dawo za'akai mgnr gaban manya to shine yanzun cikin ikon Allah da yardarsa da kuma cika alqawalin danaiwa momynka yau munje nema maka auran zarah nida babanka Ismail da d'ayan baban naka salis kuma Alhamdulilla mahaifanta sun amshemu hannu bibbiyu dan haka nan take muka tsaida ranar daurin auren naku nanda sati biyu masu isuwa wato jumaa' ta sama kamar yanda aka tsara ranar za'akai itama heendun tokaga saisu tare ranar gaba daya, shiyasa nasanar maka da zancen kokaima Kanada wani shiri karan kanka da abokanka na hidiman bikin dazakuyi, tokaji dalilin Kiran naka danai nace zamuyi mgn"
tunda khaleepa yagama jin saukar wannan hargitsattsan mgnr gaba daya tunaninsa yabar kansa yayinda jikinsa gumi yadinga tsattsafowa kota'ina banda heenduh babu wacce ke karakaina a tunaninsa, dawane duba zai kalli heenduh ne? bacin yagama fallasa mata qin zarah da rashin damuwa dayakeyi kanta bare yaji koda burbushin sonta ne a ransa? Knn zatai masa kallon maqaryaci mayaudari mai fuska biyu knn? alhalin har aransa ba haka bane??

abinda mashi yafi d'aga masa hankali yasan heenduh da tsananin kishi musamman yanda basu shiri da zaran shiya san hakan,
zai iya rantsewa kan wannan mgnr tsab heenduh zata iya masa bore tareda juya masa baya dudda sonda sukewa junansu kuwa, inda gashi cikin mgnr dady ga alama su heenduh sunsan da mgnr auran sboda gashi harda babanta a zuwan nema masa auren zarah ma, to tayaya zata fahimta babu wata mace a dukkan rayiwarsa harga Allah bayan ita? Ita ya fara so ita kuma zaici gaba da so har qarshen rayuwarsa.
dafe kansa yai sakamon bugasa dayaji ana masa Uwa ana doka masa guduma akan kuwa tsaban yanda kwanyarsa taketa hango masa yanda zasu kwashe da heenduh dan jikinsa na basa za'a samu babban matsala kuwa ta sanadiyyan auran zarah kuwa da aka qaqaba masa ta qarfi dayaji, Sam bazai iya musawa iyayensa ba bare gardama danbai sababa dan haka samuyai ya miqe yana qoqarin barin falon knn yaji
dady mukhtar yace
"yaka tashi bakace komiba kuma?" Hjy furdausey tace"a to Nima dai da abunda zance knn ay" baijin zai iya juyowa dan ba shakka da zarar sun kallesa zasu harbo tsananin tashin hankalin daya mamaye zuciyarsa dan haka daqyar ya hada kalman "to dady Allah kaimu lkcn lpia" yana gama fadin hakan kuwa ya fice dawani mugun sauri daga falon.
kaitsaye gidansu yunus yanufa yawuce dakinsa aiko ya iske yunus din yana waya ga alama shidama yarinyar sane..wani wawan ball khaleepa yayida wani qaton jug na glass cikeda ruwa Wanda ke ajiye tsakan dakin saiga cup dinkuwa yatashi yabugi bangon dakin yadawo qasa yayi tatsa tatsa dashi wanda ruwan da suka faso sune har jikin yunus suka fallatsa amman khaleepa ko'a jikinsa saima zaman sa da yayi can gefe yahada kaida gwiwa yayi shiru sai zufa yake.
babu arziqi yunus sukai sallama da budurwar tasa ganin yanda abokin nasa ya shigo gigice dasauri ya'isa garesa ya zuqunna tareda tabosa da cewa"friend doctor lpia kuwa?" d'agowa khaleepa yayi wanda hakan kuwa baqaramin qara tadawa Yunus hankali yaiba sakamakon ganin yanda idanun khaleepan sukai jaaaaazur dan tsabar tention daya bawa kansa.
"haba dan Allah nace kafadan mike faruwa newai kabi ka tashi hankalinka haka?"
cikin mgn wacce murya tagama sanyi babu qarfi a cikinta khaleepa yakalli yunus yace"bansan taya zamu qareba yunus da ita, yunus inaji a jikina wannan mgnr bawai qarama bace gareta dan tanada kishi a kaina yunus,, yunus sonta yamun kamun bazata batareda na shiryawa hakanba, munso junanmu muna kan son junanmu yunus, sanda mike farincikin daman mallakan juna batareda wani shakku ba ko boye boye na tarayyarmu gudun fallasuwan sirrin ga iyayenmu, amman lokaci d'aya yunus wani baqon al'amari ya ratso mana wanda narasa ta yanda zan bullo mata da batun tagane babu niyyata acikin lamarin face *biyayyan iyaye*" yaqarshe mgnr tareda sakin wani zazzafan numfashi.
gaba daya yunus yagaza gane inda zancen abokin nasa ya dosa kwata kwata..dan haka yasake dubnsa yace"kafahimtar dani danni bangane kan zancen ba, kuma atarayya tadakai bansan ma kafara soyayya da mace ba ayanda nasan halinka kan rashin maida hankali gasu matan ma gaba daya, dan hana rantsuwa zan iya cewa headche dinka CE kawai ma kake kulawa inkaso shima tab'a 'yar tsaman tsakaninku da'ita"
shiru yunus yai yana kallon khaleepan kawai tareda sauraran amsarsa kmr ynda ya buqata yawarware masa manufar sanin inda zancen sa yasa gaba saida khaleepa yasake sakin wani numfashin sannan yafara korowa yunus tarihin aurensu shida heenduh ta hangar baba yawale

dayai musu qarun haske kan batun dakuma rayuwar dasukai harta kaisu ga
samun cikin dasuke raino da tattali har kawo mgnr auran Zara kuma yanzun.
yana kawowa nan yasauke ajiyan zuciya yace"to yunus gashi su dady sunkarbo auran zarah kuma kasan bazan taba iya musawa ba tayaya knn zan kalli lollipop ?"
sakin baki kawai yunus yai yana kallonsa cikeda mamakin auransa dawai heenduh headache? danhaka yace"amman wlh abokina kai masifan maidani garwa ko? Wato Ashe kasan heenduh takace kaki fadan in san madam dunmu CE saima kabi kadinga lalube yarinya har ka samu kyautar sadaqi(ciki),ammandanka maidani baho saiyanzun da matsala ta kawoka ka fada munko kai dan iska? Sabanin da dakaje kakejin dadunka kama manta dani wajenmun wannan bayanin ko?"
tsoki khaleepa yai yace"toba gashi yanzun kaji ba? nidai kagayamun mafita kawai Kan ynda zanjewa lollipop dan wlh nasan zaiyi matuqar wuya mukwashe ta dad'i da ita"
shiru yunus yai danhar a ransa shima baiso kmr khaleepa kamili zai auri ballagaza kamar zarah ba, yarinyar data gama tsiyayar da mutuncinta a titi gaba d'aya,
to amman Yaya zasuyi sai haquri dan dukkan d'a nagari bazai taba jayayya da iyayensa ba dan gamawa da duniya lpia kan buqatarsu garesu muddun bata kaucewa hanya ba, wataqil ma kota sanadiyyan auran nasa ne zarah zata shiriya daga shashancin qazantacciyar rayuwar barikin cikin gida datakeyi.
danhaka yunus yadafa kafadan khaleepa yace"naji kuma nafahimceka kuma kada ka damu da mgnr auran zarah kabi umarnin iyayen dan Neman rabauta dan kuwa aljannar namiji naga iyayensa sabanin ta mace dake qasan qafafun mijinta, dan haka komi Nada iyakarsa zakaga wataran kmr ba'aiba abokina"sosai khaleepa yaji dadin tunasarwan nan ta yunus madalla da aboki na Gari shiyasa akeson tarayya dasu dan baka kyakkyawan Shawara dud inka shiga cikin taskun matsala kuwa, sa6anin wasu abokan da zasu ida dulmiyaka ta hnyar baka gurbataccuyar shawara a rayuwa wanda wataqil kazo kana nadama ta hakan daga baya.
katse masa tunani yunus yai dacewa"batun heenduh kuma babu matsala insha Allah, kaidai bari na shiga cikin gida na amso mana abinci inmun gama saimuje wajenta ninasan ta yanda zan bullowa headache dun tamu mai yawan bamu ciwon kai"
mgnr yake yana dariya harya shige cikin gidan nasu, khaleepa saman katifa ya kishingid'a tareda sakin sanyayyen numfashi snn ya lumshe idanunsa yana murmushi kawai abinsa na mgnr yunus dayai kan heenduh ynxu dazai fitan.
a kuma daidai wannan lokacin ne heenduh ta fito daga gidan baba yawale sakamakon abincinsa data miqa masa still ranta a matuqar jagule yake, tana gabda shiga gidansu ne taji yo murya daga bayanta ance"heey 'yar kyakkyawata naji dad'in ganinki kuwa, Kice yau nazo anguwar a sa'a"
dasauri heenduh tajuyo tana kallon fuskar saurayin da kmr tasansa wani GU saidai ta manta.
lura dayai bATA ganesa bane yasashi cewa"I'm khames hasan gwanda Wanda muka taba haduwa keda qawarki a boutique na madam lera siyan kaya??"
you remember ?!Yy tmbyr yana kallonta Uwa ya lasheta ykji .sosai ta tunosa kuwa, wato shine mutumin dayasai musu kaya a bikin Nafeesa qawarsu,
rabonta dajin lbrinsa tun sanda sa'a tace mata yazo nemnta a kwanan bayan nan.
jitai yaci gaba da cewa"to Yaya kike ranar danazo sister naki da'ita muka hadu takemin baki nan to daga washe garin ranar ne dadyna yaturani wani course a garin faris najima a can sai cikin

satin nan na dawo, kina raina beuty dud tsawon lokacun nan 'yar kykkayawa,, shiru yai snn jin taqi mgn saima yawan kallon cikin gidansu datake Uwa mai gudun wani ya isketa, azahiri hakane a ranta dan gskia saurayin mutumun yafiya surutun tsiya gashi yanda warin taba keta fitowa ta bakinsa dawani tsami data rasa game kalarsa abakin nasa kmr lemo kmr wani Abu, wanda azahirin gskia barasa CE tasa masa tsamin bakin nan dan yanzun haka fitowarsa knn daga hotel inda suka rabu da yarinyarsa darabon zaiga heenduh ne yasashi shugowa cikin anguwar tasu wajen abokansa nura isa.
jitai katsam yace
"akwai zafin rana baby ko zamu d'an qarasa cikin motata maqarasa firar tamu acan?"
kinsan wannan kyakkyawan jikin naki bazaiso jin zafin rana ba ga alama.
dasauri ta kallesa karo na farko data dubesa ta watsar snn tace"kai haquri Mlm danda aurena ynzun haka" daga haka tai gaba dudda kiranda yabiyota da dan gudunsa yanai mata amman kuwa taqi tsayawa hartai nasarar samun ida shiga gida tana tsoki a ranta dan ita maza sun koyar da'ita tsoronsu gani take dud mayaudara ne mgnr qarya kmr ynda khaleepa ya nuna mata.
Khamees kuwa lashe bakinsa yai byn yashiga Mota cikin takaicin rashin kulasa datai danhar yafara wassafa ynda zaiji babyn inda ace tabasa hadin kai, tsoki yaja kawai yaja snn yaja motarsa a zuciyarsa yana fadin"tsiyan wasu matan cikin anguwan knn, ga abun neman kudi a jikinsu amman kauyanci da rashin wayewa ke d'awainiya dasu..
ahaka yabar anguwar zuciyarsa cikeda haushin rashin samun had'in kan wannan zuqeqiyar babyn da sha'awarta ta tsurga masa tunn farkon ganinsa da ita kuwa, amman ganin dayai babu sa'an komi kanta ala dole yahaqura danya lura babyn miskilace bakalar tasu bace wnn, haka yabar anguwar gaba d'aya yana cizon leb'e..
heenduh kuwa tana shiga gida kusada mama Zainab tazauna suna d'an fira jifa jifa ko mnti 10 batai da shigowa ba wani matashin saurayi Umar Yashigo gidan da sallama yagaida mama Zainab snn yace"ana sallama da heenduh waje inji musaddiq"
kallon heenduh mama Zainab tayi yayinda itama heenduh dIn ta dubeta zuciyarta cikeda tunanin musaddiq kuma? Yadawo Gari knn shima?
sosai abinda yabata mamaki Neman number sa datai Tarasa a cikin wayarta, gashi Sam bata riqe number sa aka ba sa6anin ta mamanta data sa'a data riqe tun da jimawa ma.
Kasa ma yunqurin tashi tai dantasan mama Zainab da qyar zata barta cigaba da tsayuwa dashi sabanin da kamin fallasiwan auransu.
Amman kuma ga tarin amamakin ta saitaji mama Zainab tace"to Umar jeka kace masa gata nan"
Umar na fita suka sake kallon juna mama Zainab tace
"yazuwa yanzun heenduh yakamata kisanarwa musaddiq matsayinki na matar aure inkin fita yanzun, dan baya halatta cigaba da tarayyarku kina matar wani da d'inma dakukai akwai dalili shiyasa harmuka bakku dudda bada son muba,Allah yafe mana kuma, dan haka yanzun kije kimasa bayani ta yanda zai fahimta"
haka heebduh ta miqe jikinta a sanyaye dan bata masan ta inda zata farowa musaddiq wannan mgnr ba.
haka ta iskesa zauran gidansu jingine jikin bango zuciyarsa cikeda mamakin yanda aka gyara gidansu heenduh haka har aka fiddo qaton foundation haka a zaure danshi bayan abokinsa

daya fada masa nan ne gidan dabazai gane saba sa ma sam sam.
ganin ta'iso Inda take cikin sallama yasashi sakin fara'an nan tasa ya amsata tareda gyara tsayuwarsa. Yace "Gimbiya ta Heenduh barka da warhaka fatan mundawo mun sameku lpia?"
wani murmushi ta qaqalo tace
"alhamdulilla musaddiq ya hanya?"
"Hanya alhamdulilla gimbiya dan banma jima dasauka ba gida kawai naje na'ajiye jikkata nai wanka nayo nan dannaji wani laifi nai haka ba'a daukan wayana innai text ma babu responding?,
shiru heenduh tai dan ita kam halinta ne hakan tama saba indai batasan number ba toka a text koga kira bata dagawa bare dubawa iyaka intaga text da baquwan number sunma taru a Wayan to batch operation takeyi dutta marking tasharesu..jitai yaci gaba da cewa"queen beauty na inlaifi nayi akemun wannan horon ayi haquri, dan Allah mani ki amunce mun na turo magabata na gidanku ayi mgnr aur....wata gigitacciyar tsawa sukaji an sakar musu tareda cewa "kada ka kuskura kaqarasa wannan banzan furucin naka akan matata wawan mutum kawai"
abinda khaleepa yace knn lokacinda yaqaraso wajen yana jefawa
musaddiq din mugun duba.
cikin kalar dubansa shima musaddiq din yace
"Kaikuma asuwa dazaka dakatar dani daga qudurina akan matar dazan aura? Inkana cikun masu sonta ne saika gwada sa'anka kaima har Allah yabawa mai rabo sa'a ,kadaina ganin kana brother nata sa'a bata anan ay"
cikin zafin rai khaleepa yashaqo kwalan rigan musaddiq yace
"kaika isa? nafi qarfin natsaya takara dakai wlh banza abanza ma dakai mai matowa mace...tuni rigima taso kaurewa daqyar yunus yashiga tsakani yarabasu yana basu haquri kowa yaja yatsaya sai haki yake tsakanin khaleepa da musaddiq din,,
cikin fushi heenduh tadubi khaleepa yayinda ta'isa garesa tasa hannuwanta tana dukan qirjinsa cikin muryan kuka take cewa"wlh natsaneka! natsaneka! kafitarmun arayuwa doctor bazan iya zaman auranka ba danda auran maqaryaci kmrka gwaramun auran ingantattun mutane masu mgn daya ta gaskia da gskia kamar su musaddiq din wlh..."tsabar takaici da zafin furucin nata datake masa ne yakeji Uwa tana watsa masa garwashin wuta a jikinsa hakanne yasa baisan sanda yafidda hannunsa yasakar mata wasu zafafan maruka ba jikake Tass tass...jikinsa na ciri.
durqushewa tasaki qaran kuka tace"kamin komi daidai da Kaine amman kasani nagama yin sonka a rayuwa mugu kawai...muryan baba Ismail takatse mgnr khaleepan dayake shirinyi zuciyar cikeda nadamar marukan dayai matan wanda yasan zafin kishi da ambatar jin haushin tsanarsa datace tayi ne yajaza hakan dayai matan batareda ya saniba.
ji sukai baba Ismail din yace"subhanalla
heenduh, khaleepa, yunusa musaddiq mike faruwa ne kuketa sa'insa haka tundaga fa waje na jiyoku kuna hakan ?.,,,.

Hmmn dasauran kallon nan fadai Fans, kudai kumuje zuwa dai da yardar Allah.

~Allah qara miki lpia mom Sadeeq hauwas d'ina~.👏🏻

By
Xexen Fasaha.
[4/18, 11:06 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO.

story and writing
by
Xayyneb 💤💤

~dedicated to my mom sadeeq hauwas~°

👁️📦👁️
🅿️6️⃣1️⃣
K owanen su kasa magana yai awajen dan banda kukan heenduh babu abinda ke tashi a wajen.
"kunmin shiru ku fadamun mana dan hankalina yasoma d'aguwa nima"cewan baba isma'il d'in yana mai sake binsu da kallo.
daqyar yunus ya samu yafad'a masa komi ya haddasa faruwan hakan.
duban Khaleepa baba isma'il d'in yai da yaketa faman sakin hucin zafin zuciya yanaji uwa baba isma'il yabasa dama daya koyawa mutumin nan hankali.
janye fuskarsa baba isma'il yayi daga ta khaleepa sannan yamaida dubansa ga musaddeq daya mayarda kansa qasa bakka iya gane yanayin da yake ciki Sam.
girgiza kansa baba isma'il yai sannan kuma ya sauke ajiyan zuciya yace "dud ku biyoni cikin gida zamuyi magana daku"
babu musu heenduh ta samu ta miq'e tsaye tabi bayan baban nata mararta na katsawa yayinda suma su khaleepa d'in suka biyo bayanta har zuwa sitroom d'in baba isma'il d'in kamar yanda suka samesa ciki.
zama sukai sannan baba isma'il yayi 'yar gyaran murya yace "Alhamdillah na fahimci dud Inda zancen naku yandoma, kuma kai khaleepa a wannan lamarin kada kaga laifin bawan Allah yaron nan musaddeq danba laifinsa bane tun Fargo laifinmu ne dabamu fad'a masa gaskiyar lamari ba gameda tsakaninku da heenduh, daga nan kuma baba isma'il ya juya ya dubi heenduh da fuskarta ke kallon qasa yace "heenduh kin fadawa musaddeq ne abunda ke tsakaninku da yayanki khaleepa tun sa'ilin da gskian zancen auranku ya'ida fitowa ne?"
bata d'ago fuskarta ba dan tasan dole yau musaddeq yaji ainahin ko'ita wacece.
daqyar tasamu kalmar "a'a" ta fito daga cikin bakinta.
saddar da kansa baba isma'il yayi qasa yana kallon hannunsa sannan ya d'ago ya dubi musaddeq yace"kai haquri da abinda kunnen ka zai jiya Maka daga garemu musaddeq, dan gskian mgn cigaba da boyewa baida wani amfani agaremu baki daya, sirrintawar damukai abaya muka sa6awa ubangiji to muna cigaba da roqon ubangiji Allah daya yafe mana kan tsawon tarayyar damuka barku ku kayi da heenduh alhalin tana mallakin wani, shiru yai sannan yaci gaba da cewa "musaddeq heenduh da kuke zaman saurayi da budurwa da ita kamar

yanda kuka zata daga kai har ita to ahaqiqanin gskia heenduh matar aure ce musaddeq tun tana jinjirarta a cikin zane ranar rad' in sunanta aka d'aura mata aure da d'an uwanta gashi nan khaleepa"
ay azabure musaddeq yad'ago da fuskarsa yana kallon baba isma'il bakinsa na kyarma yace "auurrr... aure kuma heenduh a jarinta baba?"
baba isma'il yace"qwarai kuwa musaddeq suma basu San da hakan ba har tsawon shekaru sama da 25 sai wannan lokacin a kuma cikin wannan 'yan watannin suka sani musaddeq, bakomai neyasa kuwa muka boye musu gskian auran nasu ba musaddeq sai dan saboda wata gaggaruman matsala ta cikin gida wacce take sirri ne saikuma yanzu da Allah ya kawo mana maslaha a lamarin daidaituwar zumun cin namu har suma suka san da auran awattni uku da suka wuce, to wannan shine gskian zance, saboda haka kayi haquri musaddeq munsan babu dadi dan nasan ko wataqil zuciyarka zata iya zarga maka ko akanmi dud wannan jumawan da kukai da ita heendun bamu hanata tsayuwa dakai ba, to babu yanda zamuyi ne wlh musaddeq dan munsan a lokacin muddin wani bangare daga cikin mu da basu San da auran ba suka san an sani to a lokacin gskia zan iya cewa gaba dayanmu daga mu har ita heebduhn rayuwarmu zata fuskanci wata barazanar ta daban akanma wacce muke ciki wato barazanar rasa rayuwarmu a lokacin, shiyasa muka haqura muka cigaba da roqon Allah Akan yai mana maganin abun daya gagari qarfin mu a lokacin, to sai gashi da Allah ya kawo iyakar komi yazamo tarihi anyi setling nakomi ya
daidaita,kayi haquri musaddeq muna roqa Maka ubangiji Allah kaima ya musanya Maka da mace mafi dacewan alheri a gareka kaima,da fatan zakaiwa mgn ta kyakkyawan fahimta musaddeq dan wannan shine babban dalilin dayasa nace kazo muyi mgn dakai kai haquri dan Allah musaddeq dan bazan taba iya gajiya da baka haquri ba sakamakon barinka cikin duhu da mu kayi maka kuma ba'a San ranmu ba kai haquri dan Allah"
Sosai musaddeq yayi mamaki wannan babban magana dayakeji daga bakin baba isma'il din wanda ya tabbata da'ace ba'a bakinsa yafarajin wannan zance ba lashakka kuwa bazai ta6a yadda ba da magnr, saidai harga Allah son heenduh ya shigesa sosai har yana mamaki yanda yamatowa heenduh haka, lallai so bawasa bane, yazaiyi dole yahaqura komi sonda yake mata kuwa lazeem ne rabuwa da'ita dan cigaba da girmama tsarin dokokin musulnci na rashin halatta yin tarayya da matar aure batareda izinin mijin taba, koba komi yaji dadin yanda baba isma'il yayi masa zancen cikin tsantsar kyautatawan lafazi da nuna san mutumin da ake fahintarwar yasan inda aka dosa gamida haqura da abun , yatabbata da'ace wasu iyayen ne daban kai tsaye kota yaya takama haka zasuyi masa mgnr kotai masa dad'i ko kuma akasin hakan sukam dai basu damu ba, kuma yatabbatar dacewa su baba isma'il abin duniya bai rufe musu ido ba bare yayi tunanin kodan kud'i ne suka auras ga heenduh GA khaleepa toba hakaba ne kuman dan tun jarinta kam yafi qarfin ace son abin duniya saidai dan qulla zumunta kmr yanda baban yace marigayi baffan nasu yayi, dan haka a hankali kuma sai musaddeq d'in kuma yaji ransa yarage damuwa sakamakon ambatan Allah dayakeyi can qasan ransa cikin 'yan muntunan nan kuwa, dan haka cikin murmushi yad' ago yadubi baba isma'il yace"to shiknn baba na fahimci mgnr ka bakomai ina kuma roqon Allah daya basu zama lpia a tsakani ", cikin farin ciki baba isma'il yace" masha Allah ngd sosai musaddeq da fahinta ta dakai Allah saka maka da alheri" cikin wani murmushin dole musaddeq yace"aminn baba insha Allah nima zanyi amanna nayi biyayya ga auran wacce mahaifiyata taso bani na aura wato 'yar qanen baba na hafsat,

todayake su iyayen nawa sunso nayi auran kuma da suka fahimci muna tarayya da' ita heenduh to sai suka janye mun mgnr hafsat d'in da tunanin in Allah yaqaddara matatace ko bayan auran namu da heenduh ne saina auretan inda rabon, todayake Allah yasa ita heenduh ba rabona bacen Allah sa hakan yafi alheri"
da amin suka amsa inka dauke heenduh da khaleepa, har gaban khaleepa musaddeq yaje yabasa hannu sukai musanya cikin yiwa juna murmushin dan zuwa lokacin hankalin khaleepa ya d'an kwanta tunda yafuskanci musdq ya haqura da binbinin heenduhn tasa kuwa.
dan haka musaddeq yace "ayi haquri abinda yafaru tsakanin mu ynx likita akan rashin sanine" cikin wani kwantaccen murmushin khaleepa yace "komi ya wuce musaddeq kuma insha Allah zamuna tare har yanzu kada kadamu" yunus ya amshe da fadin "hakane kuma dayardar Allah in bikin naka ma yaqaraso muma zamu shigo cikin hidimar ayi damu insha Allah"
haka musaddeq yaiwa heenduh Satan kallon bankwana yafuta baba isma'il yabisa shima dan heenduh kam batasan sunma fatan ba sbd kanta na qasa har lokacin, to Jin shiru yayi yawa ne a wajen yasata daguwa aiko caraff takama idanun khaleepa yana faman qare mata kallo, yayinda yunus ke kusa dashi nandanan ta b'ata fuskarta ta daureta tam tareda kauda kai gefe.
jitai yunus yace, "afuwan amaryamu muna qara dai bada haquri na tsautsayin daya gitta a tsakaninku da mutumin tsantsar kishine yasa shi yin hakan ayi haquri muna tuba" wani takaici ne yasake taso mata wato itama zasu rainawa hankali knn dawasu maganganun su na bacin ran?, alhalin yana ganin sanda abokin nasan ke faffaska mata marika a lokacin bai basa haquri ba sai yanzu da'aka rabata damai sonta na gaskia ko?, jitai kamar tarufesu da duka dan haka cikin fushi ta yunqura zata miqe knn saiga baba isma'il d'in yasake dawowa sitroom d'in yazauna a inda ya tashi . hakanne yasata komawa ta zauna dole. baba ismail dinne yadubi khaleepa sannan ya maido da dubansa wajen heenduh yace" heenduh na kema zakiyi haquri da abinda nasan kinji wataqil kodaga ma bakin mahaifiyarki Inda munyi magnr da'ita wato mgnr auran zarah da khaleepa nanda sati na sama,munsan kishi halitta ne acikin zuciyar kowace mace, da hakane niqe qara tausar heenduh na data qara haquri da dauriya gamida jajircewa fiye da yadda na sanki dasu kinji ko heenduh na?"
cikin dubara heenduh tayi saurin maida hawayen idanunta ta shanyesu dan kwata kwata battason baban nata yafuskanci damuwarta ko kadan kan wannan batun, dan haka cikin sanyin murya ta dago ta dubi baban tace"mama ta fadamun babana bakomai kuma,,, taqarashe mgnr muryarta nason fara seizing dasauri kuma ta datse mgnr tareda mayar da fuskarta qasa tana wasa da yatsun hannunta kamar ta fashe takeji tsabar yanda can qasan zuciyar ta yake qara 6aci da d'acin mgnr zarah.
sosai fara'ar dake fuskar baba isma'il ta q'ara fad'ad'a yace "naji dad'i kuwa heenduh na Allah shiyi muku albalrka dukkanku kuma ina roqon Allah kuma Allah Baku masu muku d'a'a kamar yanda kuke mana"da aminn suka amsa"sannan ne baba ismail din ya miqe tsaye yace" nashiga cikin gida ni zand'an watsa ruwa dan dama daga office nake na dawo na iske wannan lamarin amman alhamdillah ay Inda komi ya wuce an fahimci juna Allah kuma qara hade Kanunku" yunus ne yace " amin baba sai anjima to"
"to shikenan mujima da yawa yunus"cewa baba ismail din yana mai ida fucewa daga sitroom din.
har gaban heenduh doctor yataso tsam daga mazaununsa ya durqusa gabanta sam baiji kunyar yunus ba yakamo hannunta yana murzawa cikin nasa a hankali, wanda haka kuwa ba qaramin

tadawa heenduh tsigan jiki yaiba lokacin, ahankali ya kwantar da kansa saman qafafunta muryarsa cikin son lallashi yake cewa"please lollipop na kiyi haquri da marin da kikaga nai miki d'azun dan zan iya rantse miki da Allah bansan ma sanda hakan ya faru ba, kawaidai tsananin zafin maganganun dakikai munne suka samu gurbi araina harna kaiga yin wannan gangancin..... bai ida qarasa fadin mgnr tasa ba azabure ta miqe da qarfi bayan ta ture kansa daga jikinta cikin tsiwa sosai takama qugunta na dama da hannunta ta riqe tace"ok nicema naja harka maran ko? wato kai bakaga kalar cin amanar daka munba ko na qaramin kishiya ko? wani murmushin takaici tasaki tace "uhmm yaya khaleepa to albishirin ka ni heenduh isma'il inamai farin cikin shaida maka cewa Kagama samun Jin wani d' and'anon farin ciki daga gareni ko misqala zarratun adai wannan lokacin wannan alqawali ne, sannan kuma Abu na 2 shine bazan taba yarda akaini gidan kaba kamar yanda ake fada Allah kuwa saidai akai maka zarah din ita kad'ai kaga saima kufi sakewa a gidan ku babuni 'yar had'in aure na iyaye bare natakura muku"tana gama fadin hakan tajuya zata bar wajen aiko taq'i daya khaleepa ya yariqo cinyar hannunta tareda juyo da ita zuwa gabansa, har wata 'yar qara tasaki sanda taji zafin riqon nasa uwa zai ballata kuwa taji lokacin, harara tasakar masa tace"miye haka ne? sakarmun hannu fa mlm kaje can kariqe matarka zabun ka" kallon ta kawai yake shi dud wannan shirmen maganganun nata bai daukesu wasu Ababa face kawai na zallar kishi dan yasan data huce zata daina masa wannan borin sudawo daidai, dubanta yai yana sakin wani dafaffen murmushi idanunsa nakan baby face dinta kallon jajayen yan hyalan hyalan lebunanta yayi uwa tashafa musu janbaki amman babu komi data shafa musu akai natural haka suke daman,ji yake uwa ya jawota jikinsa yatsotse mata su tass koyasamu nutsuwa.
yana qoqarin mgn ne yaji yunus yace"haba headache namu atemaka arage zafin nan da aka dauka damu haka man a ajiye kishin nan gefe muzauna muyi mgnr yanda zaku gudanar danaku hidiman bikin keda qawayenki kinga babu lokaci sauran mana sati 2 fa,,, afusace tajuya tadubi yunus tace "ina ganin girmanka yunus dan haka kaimum shiru da bakin ka kaima kannadawo kanka" tayi mgnr tana banka masa harara shima.
dariya takusan qwacewa yunus yy saurin saitata saiyai saurin maye gurbin faffaden murmushi a madadin dariyar, dan yasan dayayi dariyar nan tsab headache zata qara qufuluwa ne dasu , dan haka cikin murmushin yace
"a'a to Inda abun hakane kam Allah huci zuciyar ki rankishidad'e, nadaina cewa komi din kamar yanda kika buqata gani aside nazama dan kallo"
tsoki tai tareda tabe baki tace"karufawa kanka asiri knn"juyowa tai tadubi khaleepa dayaketa kallon ta yana sakar Mata wani kwantaccen murmushi sam tama lura babu damuwan komi a tareda shi, dasauri ko tajanye fuskarta danji datai gabanta na faduwa sbd kallon da yake matan ne tarigaya datasan ma'anarsa tuni kuwa, dan kallo ne nanuna tsananin buqatuwa yake Mata dud sanda taga yana matashi kuwa tasan miye aransa, amman saita basar tadinga kallon wani wajen daban tasake daure fuskarta tareda furta cewa"kada ka ciremun hannu karabu dani mlm zan wuce"tayi mgnr tana murguda masa d'an bakinta najin masifa.
Cikin kalar muryasa yace"yanzun bazaki daina tsiwace tsiwacen nan ba da fushin ba lollipop na?, kai tsaye tabasa amsa da fadin
"eh danka ji ma kuma ka sani yanzu ma nafara maka hakan ehe" matsota yayi kurkusa da jikinsa yazageye hannuwansa ta bayan qugunta yariqo to gam Jin tana kicikicin zillewa yasashi cewa"nanda kwana qalilan zan mallakeki cikin gidana fa to miye nawani yimani kakkafi da

yanga damage? please calm down man sugar na yayi mgnr tareda ida rungumota tsam a jikinsa enlargement ballons nata kuwa cike saman qirjinsa yajisu lausasa.
cikin takaici da tsakanin kunyar abinda yai matan gaban yunus din aiko daqarfi ta turesa daga jikinta ganin jikinsa har ya soma saki.
nan takoma baya tana sauke numfashi tace
"ko mafarki kayi naganin cewa zan tare cikin gidanga to Allah kuwa inka tashi kayi sadaqa dan abinda bazai taba yuyuwa bane"tana gama fadin hakan tafuce dasauri ganin datai khaleepa din yana qoqarin isowa wajen nata da nufin sake kawo mata caffa kuma ita bata shiryawa hakan ba.
murmushi sukai suda yunus sannan suka fuce suma suna dariyar mgnr shirmen mgnr tata dansu a shirme suke jin komi nadaga bakin nata kam.
wasa wasa har sauran sati daya biki amman khaleepa yaqi yarda WA yunus sufara tsarin fatittika na bikin dan har yanzu heenduh taqi kwantar da hankalinta itama shiyasa yakejin komi bai masa dad'i shiga, danta rantse masa bazata halarci party ko daya ba suje suyi da zarah mafarin knn abubuwan suka qara dame masa.
gefe guda zarah sai faman shiri akeyi na gyaran amarci dan tunda satin bikin yashigo take tara qawayenta maza da mata kullum sai sunje anyi party na innaniha ayita shaye shaye da sauran abubuwan ko kyan gani babu kuwa, zarah ta yanke shawarar yin wannan fatittika ne tun sanda tajewa da khaleepa da mgnr shagulgulan bikin kai tsaye yace bazaiyi ko daya ba in ita zatayi taje tayi yabata change.
mafarin knn take bushasharta na fatittika fitsararru da friends nata maza da Mata haryau gashi gobe daurin aure.
mama zainab ma tayi qoqari sosai wajen gyara d'iyar tata ciki da waje harna tsawon sati kuwa, shiyasa nn danan fatan heenduh taqara kyau ko'ina ta gitta tashin qamshi ne kawai ke maye gurbin wajen, kallo daya kamata bazakace tana d'aukeda ciki bama sam tsaban bin jikinta dayai.
hausawa na cewa komi akasawa lokaci zanzo, yaukam dandazon mutanen a bababan masallacin juma'an dake anguwar tasu baba isma'il bayan sllr jumaan daaka gama suka shaida daurun auran zarah da khaleepa ananne kuma take mai shaila awajen yasaka amsa kuwa ta masallacin yana qara jaddadawa mutanen wajen da cewa kamar
dai yanda dady mukhtar yabasa izini, nan yafara dacewa "Aassalamu alaikum jama'a gawata sanarwa daga bakin iyaye ango since a shaida muku cewa yau ango khaleepa da qanwarsa 'yar uwa tasa heendatu auransu ya jima da d' auruwa tun azamanin jarintarsu aka daurasa, wannan jaddadawa ne ga jama'a domin wanda baisani ba yasani yau,, aureeeee daikam ya jima da dauruwa tsakanin heenduh da khaleepa, dan haka yanzu heendatu na mazaunin uwargida ta khaleepa zarah nazaman Amarya ubangiji yasaka albalrka ga auran gamida zuria dayyaba,..... "
Ana gama daurun auran kuwa aynan take wajen kuwa yakaure da hayaniya mutanen nata mamaki auran heendatu da khaleepa kowa nata fad'in albarkacin bakinsa kuwa, cikin mutanen dasuka halarci daurun auran kuwa harda haruna mai khemist da abokansa wanda mamaki suma nawai jin jimammen auran heenduh da khaleepa jiki a sanyawa haruna yaja tawagarsa suka tafi, dan harga Allah yaso heenduh amman yazaiyi Inda da auranta ba batun so yaqare kam yana fatan Allah masanya masa dawacce yake so kamar heenduh shima.

ango khaleepa kuma yaci adonsa cikin dakakkiyar shaddarsa dark blue sai maq'in nera take, yasha yar ciki da babban riga kansa hular nan ta zauna sosai gwanin kyau haka kwantacciyar sumar sa ta kwanta bayan gashinsa nakan nasa baki Kirin sai sheqi yakeyi kuwa, qafafunsa sanye da takalman sawu ciki, hannunsa d'aure da agogonsa q'irar diamond light blue, kowa kuwa yaggansa yasan yana cikin farin ciki lokacin na ganin yau lollipop nasa zata zama mallakinsa suyi rayuwa gida daya na har Abadan abidina,
danshi harga Allah mantawa ma yake dawata zarah cikin rayuwarsu, lollipop ce kawai tsaye cikin rayuwarsa.
hakanne yasa yasamu yazulle daga cikin abokansa su yunus kai tsaye gidan baba isma'il yashiga dudda iyayen mutanen yan biki dake cike da gidan kuwa sai tsiya ake masa amman haka yashiga kutsawa ciki burunsa kawai yaga heenduh a lokacin saiko yaci karo da mama zainab tafi to daga daki, babban sanda yace Mata bak'in abokansa ne sukazo zasu gaisa da heenduh shiyasa yashugo da knsa, take kuwa mama zainab tace"ayya khaleepa ay tun safe heenduh na gidan kawunka salis,, Sosa kansa yai cikin yar kunya sannan yace"to mama shikenan bari saina kaisu can din"
yana fita kuma nan waje yasamu su yunus yakoma cikin su yana shirin ma yunus zancen zuwa gidan dady salis din knn nan yaga maroqa da mawaqa goge na gargajiya sun tunkarosa suna qarasowa kuma suka qara bude muryan su suka hau masa kirani da fadin " *🥁🎸kaga jajirtaccen tsayyen namijin Mata 2 gimbiya heenduh uwargida sarautar mataye ta kyawawa da fatima zarah, gimbiya heenduh mai babban suna wanda sunan sai a gidan masu masarautar musulman nuggeria shikan dada bayyana sarauniya heenduh uwargida ga khaleepa Allah ja kwana yabar masoyi da masoyiyarsa injini Usain mai goge jiqan audun malam*..
sosai khaleepa yaji dadin wannan waqar dayaji mawaqin yafiya saka lollipop din nasa aciki ,nan kuma yabude bakin aljihunsa yaita musu ruwa dubu dubu karshen kudin Nigeria suko suna kwashewa suna sawa aljihu bashine yabar musu ruwan kudinba har saida su yunus suka janyesa sannan.
sosai yunus yaji dadin hkn danshine dmn dakansa yasanar da maroqan yanda zasu tunkari khaleepa da waqar tasu sanda yashiga gidan baba ismail din.
daman abokan angon sun hada reception nasu na abokai da aminan arziqa da zarar an gama d'aurin auren shiyasa dud yawancin abokan suka fara nufan garden din gidan so khaleepan inda nan suke fatin nasu.
yarage daga yunus sai khaleepan tsaye wajen mota wanda ganin wajen yayi sauqin jama'a yasa khaleepan ya dubi yunus bayan yakalli watch din hannunsa sannan yace "yunus kashiga ciki kufara event din nan please zanje wani waje ne yanzun nan zan dawo"
cikin mamaki yunus yace " dadai kahaqura an gama event dinnan sann kaga ynzu friends namu zasuta tambsyar ina
ango fa"
6ata fuska khaleepa yayi yace"no,, no bazan iyaba yunus dud yau ban saka lollipop na a idanuwa naba ,wlh ba kaji yanda nikejin jikina ba uwa nayi rashin wani abu daga jikina please yunus kaje kaji da friends din namu kaban 15 mnt naje gidan dady sales naga lollipop na ko naji qarfin jikin gudanar da event din nan yau cikin dadin rai., "
sosai yunus yaji tausayin khaleepan,, lallai so maisaka abu laushi komun taurinsa kuwa, bayaga haka dubi yanda so yakejan abokin nasa dud miskilancin nan ya'ajesa gefe yana nan nan da

abokiyar fadan nasa ada ayanzun kuma abokiyar rayuwa ta aure tahar abada, dan haka cikin murmushin sauke ajiyan zuciya yunus yace"jeka abokin adawo lpia tareda gaishe man da mutuniyar tamu ,
murmushin Jin dadi khaleepan yasaki yace"yawwa friend tnxx yanzun nn zndawo"
yy mgnr cikin saurin shiga motorsa ya wuce, shima yunus ya wuce wajen abokan nasu, daidai qofar gidan dady sales yy parking yarasa tayaya zai shiga gidan, aqalla yajima zaune a cikin motor harya fara yanke shawarar yafito ya aiki yaro sakamakon wayar tata dayaita bugawa taqi shiga, yana shirin kirawo wani yaro saiko ya hango baby amnat tafi to daga gidan nasu.
da sauri ya bude motor yafito itama tana hangosa tayi murmushi tareda nufosa tana fadin "oyoyo uncle khaleepan "
sanyayyen murmushi yai yace" oyoyo babyna amnat aunty ki heenduh na ciki ko?
"eh uncle doctor tana tareda momy na, zomuje narakaka inyaso sainaje gidan su grandpa damn momy ceta aikin can"
sosai yaji dadin hkn kuwa dan haka har falon gidan suka shiga nan suke iske momeyn amnat din zaune yayinda heendub ke gefenta tana kwance saman doguwar kujera idanunta lumshe kamar mai barci amman tsabar damuwa ne cunkushe kawai cikin zuciyarta, dan kuwa qiri qiri taqi gayyato abokanta wani biki danko sa'a ma bata fada Mata ba balle.
jitake tomimane abin gayya a wannan aure da'a ka kuntata mata a cikinsa, dan ita Batama ganin laifin kowa daya wuce doctor din dan Inda bai amine da auran zarah d'inba bazasuyi masa dole ba iyayen nasa.
dan haka kuwa tanajin muryarsa falon tareda qamshinsa haka baqaramin fadar Mata da gaba yaiba sakeyin lamo tai tanajin yana gaida momyn amnat ta amsa cikin took arsa dacewa "ango na amarya sannunku da hidima fa, allah sanya alheri yabaka ikon riqesu lpia kuma" tanajin sanda yake amsawa cikin muryarsa da " aminn aunty."
wani kulukulun sabon jin haushi yataso mata tareda tokare mata zuciyarta, wato zarginta nasan zarah da yake yazama gaskiya knn Inda gashi yana amsawa da aminn da'aka musu addu'a.
jitai momyn amnat nad'an ta6ata tana cewa "heenduh..?heenduh tashi ga doctor nn yaxow"tana gama fadin haka tamiqe tabar falon danufin hadowa khaleepan koda kayan motsa baki ne.
shiko ganin tabar falon yasa shi qarasowa har kusada heenduh ya zauna , yazuba Mata fararen idanunsa yana kallon yanda atamfar jikinta lemon green riga da Zane suka masifar karba ta, fuskarta simple make up ne amman baqaramin kyau taiba, sosai yashagala da kallon to saiko gashi caraff ta Bude idanunta sukai four eyes, ganin shigarsa shine ya tabbatar mata da aure yashiga tsakanin sa da zarah knn ?babu zato taji ko mararta tayi wani mummunan murdawa gamida katsawa amman dudda abin datakeji saida tayi qoqarin matsawa daga garesa tamiqe tsaye tana aiko mass da wani kalar mummunan kallo, shiko kokarin ruqota yake kodan yararrasheta danya hangi kishin nata kuwa qarara a cikin idanunta ya motsa, saura kadan yariqota kuwa tayi saurin ture hannuwansa hawaye suka fara zubo Mata murya narawa cikin tsawa tsawa tace
"macuci mayaudari kawai ni kafutar mun daga nan mizai kawoka wajena alhalin kadai na sona nima kuma nadaina sonka kawai ka futa kakoma wajen zarah nabar mata kai duka.... taqarashe mgnr tareda ida fashewa dawani kakkarfan kuka, har cikin ransa yakejin zafin kukan nata kuwa matuqa, danhaka murya a sanyaye yace"wai dan Allah lollipop wanne kalar kishi ne haka ne

dake sai kace kank...katsesa tai ta hanyar d'aga masa hannu datai zatai mgn knn taji lokaci daya cikin ta yasake wani mugun juyawa sbd tsananin azaban zafi wata qara tasaki tareda dafe cikinta da hannuwa biyu ta zube awajen tana murqususun azaba danko kukan ma tagazayi nai, ta runtse idanunta tana sakin salati domin azatonta mako mutuwa zatayi yanda takejin wannan azaban a cikin nata, ba su Ankara ba dukkansu kuwa sai ganin jini sukai yana malalowa a qasa daga jikin qasan ta.
aida gudu yaqaraso wajen yazube hankali tashe idanunsa 'sukai jawur nan take, cikin tashin hankali yake cewa "shikenan?! ,,, shikenan! hankalinki ya kwanta kin zubda zubda min cikin neylar" yy mgnr jikinsa na rawa.
damqo hannuwanta yai idanunsa jujjuye da tashin hankali yake cigaba da cewa " me yasa???!!! miyasa ??miyasa akan wannan banzan kishin naki heenduh zaki zubar min da gudan janina minai miki haka kikai hateing dina haka why! why minai miki kifadamun nace!!!! yayi mgnr cikin wata matsanciyar gigitacciyar tsawa gamida girgiza kafadunta, yayinda itakuwa batasan Inda kanta yaiba tun sanda taji yafurta zubewar cikin nata kuwa tune ta shid'e a wajen tareda sumewa gaba daya, lura dayai bata numfashi ne yasa shi qara gigicewa tuni yazame babban rigar jikinsa da hularsa cikin jinin ya sunkuyo ya sungumeta a jikinsa zaifita saiga momyn amnat sunshugo falon hannunta daukeda plate na snack sai baby amnat nariq'e da jug na lemo a plate itama. dukkansu rudewa sukai ganin yanda jini ya bata musu kaya musamman heenduh ma dasuka lura bata numfashi sakamakon ko'ina na jikinta daya saki ,, momyn amnat cewa take "wayyo allah Mike faruwa khaleepan miyasame ta,, kasa mgn yai yawuce kawai dawani mugun sauri ya fito ya bud'e motarsa yasakata abaya dasauri momyn amnat ma ta'iso ta shige motor yaja dagudu suka bar gidan yayinda cikin kuka baby amnat ta nufi gidan su heenduh.
Suna isa asubitin dakansa ya dauko ta a saman kafad'a ya shigar da ita emergency room na masu miscrage yafara dubata,, yadau tsawon lokaci a kanta Amman dud yanda yaso ya tsaida zubewar cikin amman ina Allah bai yarda ba saida ya zube tsab ,,, daqyar yana share hawaye yayi mata wankin ciki tareda wasu allurai yasaqala mata qarin jini ta hanyar jininsa daya deba da kansa nan take yasa mata danta zubar da jinin sosai,, zama yai gaban gadon yana kallon yanda take sauke numfashi jiyai idanunsa suncika da qwalla nn yad'ora kansa ajikin gadon nata wasu zafafan hawayen d'acin baqinciki na fita cikin idanun nasa.
yajima haka harya samu yatsaida zubar hawayen nasa lokacin har ledar jinin daya samata taqare nanya zareta yasake mayar mata da qarin ruwa danta samu qarfin jiki,, saida yayi tsawuwan minti 10 yana kallon to saidaga bisani yabar dakin yana fitowa waje kuwa nn ya iske dady sales da dady mukhtar gamida baba ismail sai momyn menat da mama zainab dukkansu sunyi jugun jugun musamman masu mama zainab da baby amnat ta kai musu wnn labarin maitada hankali na cewa datai musu GA aunty heenduh can cikin jini.
suna ganin fitowar khaleepan kuwa sukayo kansa da tambayar yaya jikin nata? ""
jikin babansa yashige yana hawaye dan xuciyarsa sosai take sake raunana kan fitar cikin nn dud inya tuno kuwa.. a haka yashaida musu zubewar cikin heenduh dudda yaboye musu ainihin dalilin fitar cikin kuwa.
har dakin suka shiga ganinta sunji babu dadi suma amman ya suka iya da abinda Allah yaqaddara saihaquri ay,,nan su dady sales sukai ta rarrashinsa dan kmr yaro yakoma musu kuwa, saidaqyar yayi settling xuciyarsa da kansa sannan yayi saurin barin room din dukansa.
burinsa ya'isa office d'insa koya samu wata nutsuwar acan, danshi kota b'acin kayan da jikinsa

sukai bai damuba daya chanza su, haka yawuce yana goge hawaye xuciyarsa na cigaba da rawa dud inya tuno cikin sa na baby neylar yafita da gske kuwa, haka ya'ida
wucewa yashige office dinsa ko ganin gabnsa baiyi sosai, gefe guda GA kiran wayarsa da momynsa da yunus gamida amarya zarah dasuketa famanyi amman kwata kwata yama rasa ta'inda ake daukan wayar ma a rayuwa bare yayi qoqarin yin hakan. haka suka zauna asibitin harzuwa
lokacin da'aka kira sallar la'asar su dady mukhtar suka nufi masallacin asibitin danyin salla yayinda mama zainab taje gida itada baby amnat daukewa heenduh kayan dazata sake,nan akabar maman menat wajenta, basu jimaba suka dawo akai sa'a ko minti uku su mama zainab ba suyi da dawowa ba heenduh ta farfad'o tareda bude idanunta.
ahankali ta d'aga
hannun ta na dama ta d'aurasa saman cikin nata jin wayam babu alamun wannan d'an tudun cikin nata data keji inta taba a wajen nan take ta fashe da wani gigitaccen kuka naqin qari harda turje turje banda baby neylar babu abinda taken tunawa . dasauri _su_mama zainab suka yo kanta suna faman rarrashi, momyn meenat kecewa "kiyi haquri heenduh insha Allah ubangiji zai canza miki wani kiyi haquri da wannan daya fuce kinji ko?, kihaqura ba'a fushi da ikon Allah kuma Inda rayuwa bata qareba bazaka yanke qauna ba ay daga samun haihuwan kudama zaku fara rayuwa yanzu,, kiyi haquri ki kwantar da hankalinki muma knmu bamuji dadin zubewarsa ba, amman babu yadda muka iya sai haquri, tashi muje toilet ki gyara jikinki kiyi wanka ga part nan dasauran kaya an dauko miki daga gida saiki cire wadannan na jikin naki dasuka baci, ganin qarin ruwa yaqare heenduh bata tsaya wata wata tasa hannu ta fusgesa harsu mama zainab namata fadan mimakon tabari akirawo khaleepan, shiru tai a haka momyn meenat takamata suka shiga toilet din tadan taimaka Mata da hada ruwan dumi sannan tabaro toilet din bayan ta'ajiye Mata kayan da zata saka,
bata jimaba tafi to bayin sanye da doguwar rigar material green colour da gyalenta data yafosa aka, taqara wani haske sosai saidai kai daka ganta kasan tana cikin tashi hankali kala daban daban, dasauri momyn amnat takamota tazaunar da ita sannan tamiqe tana cewa"bari naje toilet nawanko kayan dakika cire,, da kallo kawai heenduh tabita batace komiba hartaga shigewarta toilet din kuwa, kallon ta tamaida can gefe tahango mama, zainab na salla Dan haka cikin murmushin qarfin Hali ta juyo ta dubi baby amnat data sata gaba tana kallo kamar mai tsaron lafiyanta tace "baby amnat kinsan office din yaya khaleepan ko?
dasauri cikin jin dadi na ganin aunty tata na mgn tace " eh aunty nasani dazun munje , yawwa tojeki ki kiramin shi, aiko dasauri baby amnat ta fuce, nan danan heenduh tamiqe ta zuge jikkar momyn amnat ta dauko wayarta data sakata ciki tun zuwanta gidan nasu, tareds wasu kudi data gani cikin jikkar ta dauko dubu uku dasauri tazuge jikkar tagyara mayafin kanta ta rufe fuskarta dashi tabi tawata kofar ta fuce daga asibitin tahau napep babu Inda ta sauketa sai tashar mota kuwa tabarin garin kaduna.....
tarasa wanne gari zatace akaita gashi sai tambayrta Inda zata direbobin tashar keyi, batasan ko'ina ba batta zuwa ko'ina to ina zatace akaita kenan yanzu??,,,,

kuyi haquri kunjuni shiru uzurirrikane wlh..

By
Xexen Fasaha.
[4/18, 11:06 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO.

story and writing
by
Xayyneb 💤💤

~dedicated to my mom sadeeq hauwas~°

👁️📦👁️
🅿️52
K awai gidan sa'a dake garin bauci taji shiya fad'o mata arai a cikin lokacin, dan haka Inda motan baucin take kai tsaye nan ta nufa kamar yanda aka gwada mata kuwa.
tayi sa'a kuwa babu jimawa motor tasu ta d'aga suka bar tashar tareda miqar hanyan bauci, tanajin sanda ake cewa a harhad'o kudin mota nata ne first din badawa suna manne cikin hannunta daman, dankuwa jitake
gaba daya jikinta yasaki tasan muddin iyayen nata suka ankara da bata nan tofa tasan ba qaramin tashi hankalinsu zaiyi ba naqin qarawa ma.
sotakeyi ta samu tayi kuka kota samu relief a cikin zuciyar ta amman ina babu damar hakan domin babu yanda zatai kuka da iyayen mutanen nan cikeda mota tasan dole zasu d'iga mata ayar tambaya mafarin knn ta haq'ura ta daure tareda shanye kukan nata saima duq'ar da fuskarta datai saman qafafunta ta lumshe idanuwa uwa mai bacci a haka sukaci gaba da tafiya sune basu sauka cikin garin bauchi ba harsai da ana kiran sallar isha'e, wai nan danma direban yayi sauri ne kamar yanda taji wasu na fada a cikin motor lokacin da suka ison,
tana fitowa itama daga cikin motor ta tari napek tahau babu Inda ta sauketa sai a anguwar G. R. A. a qofan gidan sa'a.
jin da mai gadin yayi ana qwanqwasawa ne yasashi ajiye 'yar radio din tasa tajin waqoqin zamani da yake gyara
yaje ya bud' e qofan,, wani murmushin qarfin hali heenduh ta qaqalo taiwa yahuza mai gadin, dan kuwa mutumin tane shi d'in tun lokacin da sukazo bikin sa'a suka saba dashi da yake d'an ban dariya ne haryake cewa heenduh matarsa ita kuma tana cemasa ango na, dan koda zata tafi kuwa har kyautar tsarabar baban dudu yakawo mata mai masifan dad'i da yake shi matarsa yuhanasu take yi na siyarwa .
dan haka yana arba da'ita ya washe baki yana fad'in "ah matana shaukan dale ankayeh ne? to malaba malaba isuwa shiki koh?"
(da yake jinin fillo ne shiyasa hausan be fita sosai a cikin bakinsa).
shigowa tai tana fad'in"ango na mun sameku lpia yaya matanka yuhanah?

cikin mgnr sa ta dariya yace' 'laffiyyallau mukke''
"to yayi nina shiga daga ciki saimun hadu gobe ko?' '
"to matana ahuta lahiey, abinda yace knn yakoma yaci gaba da gyaransa yana maijin dadin abokiyan dramar sa tazo.
tana shiga falon kuwa taci Karo da sa'a tana ajuye jug a center table tareda qoqarin zama a kujera..... jin muryar heenduh datai ne tana sallama cikin siririyan muryan nan tata data santa da'ita kamar daga sama yasata saurin miqewa tajuyo tana kallon qofan shigowa falon,, arba sukai da juna kuwa, dagudu suka tarbi juna sa'a na tsallen murna heenduh kuwa kamar an bude mata fanfon kuka haka ta farasa wiwi kamar jira take tashi go falon daman ta farasa, nan kuma sai jikin sa'a yayi sanyi takamo hannuwan heenduh suka zauna saman kujera tana fad'in "ya subhanillah ya ilahu ,, wlh qawata kinsaka gabana sai faduwa yakeyi na tunanun ko mutuwa akai mana ne? jin heenduh taqi mgn saici gaba da kukan take harda sakin shessheqa yasa sa'a qara rudewa ta rungumota jikinta tana cewa "kiwa girman Allah da darajar iyayenmu ki fadamun mike faruwa haka?, wlh nima shingin qiris na fara nawa kukan dan kin kadar mun da zuciya sai bugawa take"!
daqyar heenduh ta samu daman bude bakinta dan muryarta zuwa lokacin harta shaqe nan tadubi sa'a hawaye na cigaba da sulalo mata a fuskarta tace "baby na sa'a baby na nayler danike muddin qauna tunkan naganta tazo hannuna yaya khaleepa yayi sanadiyar dahar tatafi ta barmu,, wayyo sa'a ki fadamun yaya zanyi wlh ina cikin matsala ta matsanancin tashin hankali shiyasa na gudo zuwa nan batareda sanin kowa ba harsu mama kuwa dan daga saman gadon asibiti nake yanzu haka kingama shaidan hakan anan, tayi mgnr tareda nunawa sa'a Inda 'yar plsta ta qarin ruwa take a hannunta.
sosai hankalin sa'a yaqara tashi tace " innalillahee qawata dan Allah mike faruwa haka harda zafi harki iya gudowa gida su mama basu sani ba? wacece kuma baby nayler ne? "
girgiza kai kawai heenduh keyi cikin soyuwar zuciya tace" wlh babu dadin ji ne abunne sa'a wlh gaduk mai sona zai tausayamun a halin da'aka sanya zuciyata a ciki dan dukan yayi mun yawa,,,,,, nan heenduh ta shedawa sa'a tun usulin shirinsu da khaleepa zuwa samun cikin nata da kuma shiryawar su iyayen nata hardai kawo mgnr auran zarah dayau da aka d'aurasa dakuma abinda yafaru da'ita da doctor din harya jaza zubewan cikin dakuma gudowarta anan d'in yanzun,,,,,,,, taqarashe mgnr da cewa sa'a "Allah kuwa zama da zarah masifa ne kinsan tuni munsan halinta haka kawai ina zaman zamana akawomun tashin hankali, wlh kuwa sa'a nida'ace ba zarah bace Allah kuwa zan haqura da mgnr babana nazauna amman nakasa dan bansan miyasa naji na tsani zarah ba haka da yawa"
tayi maganar tareda dafe kanta dake faman sara mata, sauke ajiyan zuciya sa'a tayi tareda janye tagumin fuskarta datai ta kalli heenduh cikin tausayawa, dan sosai zaka fahimci kalar fad'awan datayi sbd tsaban tashin hankalin da take ciki kuwa, takuma tausaya mata matuqa gaya.
jitai sa'a d'in tace"gskia an cucemu kam qawata, wlh doctor bai mana adalci ba daya had'a class d'inmu dana waccen karyar mazan kuma kinmin daidai wlh da kikai tafowanki inyaso yaji yaji Inda dad'i k'untatawa masoyi shima"
d'agowa heenduh tai tana kallon sa'a d'in idanunta suka sake kawo ruwa muryarta nad'an kyarma tace"ni abinda yafi damuna halin da su mama zasu shiga insun duba sunga bani nan inajin tsoron abinda zai faru gaskiya "

sa'a tace" hakane amman ga shawara mai zai hana ki rubuta musu text koda zuwa gobe ne inkin hutu, ki rubuta musu text cikin hikima da dubara wanda zaisa hankulansu ya kwanta ko? dan gaskiya bazanso ki komawa doctor da zarah yanzu ba dan inada tabbacin zuwa yanzu an kaita gidansa mayyar mazan"
wannan maganar da sa'a tayi kuwa na cewan ankai zarah gidan ba qaramin girgiza xuciyar heenduh yaiba dan haka kwantar da fuskarta tayi saman hannun kujeran da take tayi tareda lumshe idanunta wanda Allah kad'ai kalar yasan zafin da zuciyar ta ke mata matuqa.
jitai sa'a ta dafata taci gaba da cewan " ynzun qawata da'ace hakan bai faru ba da bazan tab'a sanin ana mayin bikin tarewar kiba kin kyauta mun knn haka amunci da qawance yace ayi daman?"
d'agowa da fuskarta tayi tadubi sa'a cikin sanyin murya tace"kiyi haquri qawata wlh dud abokaina babu wanda na gayyata daman fa, dan tunda aka fara mgnr ma ta tariyan nan wlh bnda wani cikakken qoshin lpia ma a jikina bakiga dud nama rame ba?"
kamo hannuwanta sa'a tai ta riqe tareda dubnta tace"to shikenan qawata babu damuwa dan daman nima cikin satin nan mukayi mgn da my na jia dazai yi tafiya logos akan zanje gida nayi kwana 7 na gaishesu sannan,amman Inda gaki kinzo to insha Allah Bama zankai satin ba kwana uku zanyi na dawo ai zaki iya zama ke daya a gidan ko qawa?"
lumshe idanunta heenduh tai sanda taji batareda ta ankara ba tunanun khaleepa ya fada mata arai na zaton cewa yanzu hakama qilan yana can shida amaryar sa zarah yana mata kalar abinda yake matan nan insuna tare.
wasu 'siraran qwalla ta goge tadubi sa'a tana nurmyshin qarfin hali sannan tace"zan iya zama qawata kada kidamu Allah maidoki lpia kuma dan Allah kada kifa fad'awa kowa cewan ina nan bauchi gidanki kinji?, gyada mata kai sa'a tayi alamun babu wanda zata fad'awa, snn heenduh tace"amman inkinje gidanmu dan Allah ki qara kwantarwa dasu baba da mama na hankali dan Allah qawata"
" to insha Allah zansan yanda zan qara kwantar musu da hankali innaje karki damu, yanzu taso muje kiyi wanka kamin kifito saina dafa miki mutumin naki cus cus kici ki qoshi, daman d'azun nayi miyan kifi nasan kina sonta da cus cost, taso taso muje..... haka taja hannun heenduh data ida zare layikan cikin wayarta dan gudun kiran wani ma, daga nan suka wuce bedroom din sa'a d'in tayo wanka tafi to tasaka kayan barcin da sa'a ta ajiye matan sannan tafi to falon ta d'anci abincin ba sosai ba shima dan sa'a tayi magiyan taci abunci gudun kada yunwa tai mata wani abun.
tana gamawa suka koma daki suka kwanta dud yanda sa'a taso suyi fira amman sai heenduh tai lamo ta rufe idanunta uwa mai bacci dole tasa sa'a tahaqura da firan ta kwanta itama.
yayinda wannan dare gaba dayan sa a baibai ya zowa heenduh dan takasa runtsuwa dai dai da second one banda daukan chaji na fitunannun tunanuka babu abunda kwanyar ta ke addabarta dasu.
dole ta miqe tashiga toilet tayo alwala ta fito ta shimfida pray mate tafara salla domin kai kukanta ga rabbul samawati dayai mata maganin abinda ya addabi zuciyarta kuwa.
saida tayi sallar asuba gari yayi sha sannan fa ta samu barci ya sureta anan kan sallayar da take.
acan kuwa asubiti koda mama zainab ta gama sallarta ta isha'e wuzin 8:24, tayi mamaki qwarai yanda bataga heenduh saman gadon ba alhalin yanzu datana salla tadinga jin mgnrsu da baby

meenat kuma.
komawa tayi gefe gadon ta zauna dan a tunanin ta ko heenduh na toilet 🚽 ne jin motsin futowa ne daga toilet d'in yasa mama zainab ta maida kallon ta ga wajen, sosai tayi mamakin ganin momyn meenat ce kawai ta fito daga toilet d'in harta iso ta zauna cikin murmushi ta dubi mama zainab tace"a'a to ina kuma ita heenduh tayi kuma itada bata jin qarfin jikinta? Allah sa daito ba baby amnat ta biyewa ba suka shige cikin asibitin yawo kmr yanda naji tana matsa mata a dazun dasu fitan"
tayi mgnr tana kallon gadon da heenduh ke akai,
mama zainab tace" to kam saidai hakan gaskiya, dannima yanzu na gamajin maganar su da'ina salla itada
ameentun.... katsewa mgnr mama zainab tayi ganin khaleepa ya shago room d'in hannunsa riqeda hannun baby amnat d'in
[4/18, 11:06 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🧃🧃
👁️👁️
DA SAURAN KALLO.

story and writing
by
Xayyneb 💤💤

~dedicated to my mom sadeeq hauwas~°

Assalamu alaikum dears sisters nayita jin qorafe qorafen ku da dama na cewa ta yaya heenduh dake cikin jini zatai salla?
to inaso ku d'an fahimta dears, sufa mata kowacce da kuke gani da yanayin da Allah yake halittarsa akanta, zaku iya ganin wata macen ma wacce ta haihu ma a ranar jini zai iya *d'auke mata kuma kunga knn dole taci gaba da ibadarta Inda mai hanawan yakau , wata kuma zaina iya mata wasa ma, wato yanzu zata gansa yanzun kuma zataga ya d'auke (ga wa'yanda jinin ke musu wasa knn inkun fahimta).*
*to shin sisters bazakuyi tunanin ko'itama heenduh na d'aya daga cikin jinsin matannan guda 2 dana lissafo muku ba yanzun?, Dan haka ku daina mamaki da nace tai salla, ko da yake *koma dai a wanne jinsin ta kasance inkuna biye da xexen fasahan taku zaku fahimta.....*
sannan kuma danace mama zainab ta gama sallar isha'e to kuyi haquri akasi aka samu na sanin cewa fa d'an Adam da yawan mantuwa yake kuma nasan kun san da hakan, to ina nufin data gama sallar la'asar wai saina mnta nace muku isha'en ta idar.
dafatan kun fahimci bayanan nawa 😊🤝,,,, Allahu ta'ala a'alamu...

👁️🧃👁️
🅿️🚻
S osai doctor khaleepa ya maida hankalinsa kan gadon da heenduh take ganin dayai gadon wayam babu kowa akai sai mama zainab dake gefen gadon still yayinda momyn amnat ke tsaye gefen ta, tunani yai kotana cikin toilet ne shiyasa yadan saki fuskarsa yaqaraso wajen su

mama zainab d'in ya gaidasu suka amsa, momyn amnat tace "a'a kinga kuma maman heenduh ashe amnat na tareda doctor to ina ita heenduh tayi?"
hakanan mama zainab taji gabanta ya fadi tadago tana shirin mgn knn baby amnat tai saurin cewa"momy ina aunty beauty ne? yanzun fa ta aikeni nakirawo mata doctor ina tatafi ta barni bacin munyi tareda ni zatai round a asubiti shan iska? taqarashe mgnr tana bata baki uwa zatai kuka kuwa, kamo hannunta khaleepa yai snn ya dubi su mama zainab yace "momy bari mu duba koda nan waje ne wataqil tana wajen.... a haka yaja hannun baby amnat suka fuce ... tun daga barandar dakin Fargo yafara dubawa amman sam babu ita babu dalilunta wasa wasa haka yaita dube dube amman ina komai kama da heenduh bai gani ba, sosai hankalinsa ya tashi danhar cikin dakunan da sake maqautaka dasu dud ya shiga ya duba amman bai ganta ba, dan haka dasauri ya koma wajen su mama zainab din baby meenat na biye dashi a baya. hankalinsa tashe yashiga dakin suna ganunsa kuwa dud suka miqe tsaye suna tambayar yaya tana ina,, cikin dan rawar murya yace"mo.... momy babu Inda ban dubata ba amman ban ganta ba,,, innalillahee to ina taje kuma tana ma fama da lalura a jikinta? cewar momyn amnat dan hankalina ya dagu itama,,, kwata kwata mama zainab kuwa kasa mgn tayi ita saima duqar dakai datayi kawai.
sallamar su baba isma'il ne yasata dagowa da kanta tareda amsa sallamar.
daga tsaye doctor ya sulale ya zuqunna kasa sakamakon kansa dayaji yana sarawa, wai wannan wanne kamar qaddara ce Allah ya jarabcesu da ita? danshi kam yanaji a jikinsa cewa heenduh na cikin asibitin ba nisa taiba, damuwarsa mizaisa ta fita waje tana jinyar kanta kuma. anan ya tsinkayi momyn amnat na shedawa su baba isma'il d'in baasan Inda heenduh ta shige ba cikin asibitin.... dady mukhtar yace"adai qara dubawa sosai amman banda abin heendatu ma ina zata batajin wani kuzari sosai, dady sales yace, "nalura yarinyar nada qarfin Hali kuma" baba isma'il yace " ikon Allah kuma kaga tun da muku futo masallaci muke zaune can wajen masallacin amman ko gilmawarta bamu gani ba..... katsewa mgnr baba isma'il tai ganin yanda khaleepa yayi azaman miqewa da sauri yabar dakin nan danan suma baba isma'il d'in suka rufa masa baya, daki bayan daki haka khaleepa yaita shiga suma suna biye dashi, saida yakwashi sama da awa daya wato wuzin qarfe shidda na yamma yana bin dakunan patients yana dubawa amman saidai yaita ganin majinyata damasu jinyarsu, daki na qarshe dasuka shiga suka duba nanma babu ita hakan ba qaramin mummunan faduwan gaba ya dinga haddasawa a zuciyar khaleepa ba, aida sauri ya nufi office din doctor musab ya banka da qafarsa amman yana shiga yaga babu kowa cikin office d'in, haka yafito da wani mugun saurin ya nufi office dinsa dan yayi tunanin baya batada kadan kosanda yafito ita kuma zata iya zuwa office d'in nasa tunda baisan neman da take masan ba kmr yanda baby amnat ta je ta shaida masan ba a dazun d'in da yake tsaka da ayyukan daya jijjibowa kansa danyasamu ya kore koda rabin damuwar da heenduh tasa masa ne, haka yazage yana duba patient a lokacin uwa ba ango ba, to koda kuwa yayi saqon kiran nasa datakeyi dole kuma yabaro patients d'in yatafo dan tana ransa kuwa dud da bata masan datai kuwa.
to ganin dayai office d'in nasa ba kowa yasashi durqushewa wajen jikinsa ka wani mummunan ciri hankalinsa yatashi sosai zuwa lokacin dud zufa tayi masa wanka kuwa ta jiqe shaddar nan tasa dahar lokacin bai cire ba, daman ga bacin data farayi tun Sanda yadauko heenduh a dazun.
a haka su baba isma'il suka shigo office d'in dasauri ganinsa a hakan yasa suma hankulansu

qara tashi matuqa, cikin mgnr dady sales yace"yailahu babu shakka wani abu ya faru da heenduh dan dud yanda akai lashakka daukar ta za'ayi a bar asibitin nan da ita"yayi mgnr yana share zufan goshinsa, yayinda dady mukhtar yace " tabbas hakane sales dan yarinyar da adazun bata sanma Inda kanta yake ba taina zata iya barin asibutin nan ma? kai gaskiya da yanda akayi.
Allah sarki baba isma'il dudda dumbin damuwar da yake aciki na rashin taqamai mai Inda yar tasa tayi a wannan duniya da tazama abin tsoro amman ganin yanda gaba ya lura jikin khaleepa na karkarwa tsikan jikinsa na mimmimeqa yasashi dafasa da fadin "kayi haquri khaleepa komi zaizo da sauqi insha Allah heenduh babu abinda zai faru daita insha Allah kaji,? ya haquri ka dawo cikin nutsuwarka.... ai khaleepa bai ida bari yayi abinda baba isma'il ke fada masan ba da wani mugun taqi na gudu yabar office din uwa marar hankali wanda babu shiri kuwa iyayen nasu suka buyosa suna kira amman kojinsu baiyi ma kwata kwata wanda babu Inda yayi tsinke sai gaban man police security dinda ke tsaron bakin room d'in da heenduh ke ciki.
yana zuwa kuwa ya samesa zaune bisa kejera bai tsaya wata wata ba yacakumosa jikinsa uwa zaikatse dan rawar da yake qarayi fadi yake cikin gigitacciyar murya da man "ina kake harda zaka bari a fitar mun da matata bakada hankali? bakasan aikin kaba ko to kaje daga yau wannan uniform d'in sunzama haramiya a jikinka yayi mgnr tareda sakarwa maigadin duka kota ina shiko saifaman cewa yake sorry sir I swear I don't see her out..... daukesa da mari khaleepa yayi wanda babu arziqi ya'ida hadiye mgnr dai dai nan su dady mukhtar suka qara so daqyar suka cire security d'in daga hannun khaleepa d'in aiko khaleepa babu zato yaji wasu zafafan hawaye masu tsakanin quna suna sululo masa a fuskarsa wanda dasauri yashige jikin baba isma'il d'in yana kuka mai girgiza jiki na tsakanin ban tausayi, fadi yake "please dady ina heenduh na take kumedomun da'ita wlh zucuyana bugawa yake sosai dan Allah tana ina dady kufadamun kufadum,, yayi mgnr tareda rirriqe baba isma'il wanda dukknsu suma basu Ankara ba sukaji hawaye babiyowa ta fuskokinsu suna sharewa...

kuyi haquri da wnn wlh sbd ma mgnr Saman 👆can ne tasa nayi type din dankuga amsan ku, sbd busy nk kwananan Amma insha Allah komi zaiyi daidai.
kuyi haquri in kinga type errors bn samu nayi editing ba.

Xexen Fasaha
[4/18, 11:06 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO.

story and writing
by
Xayyneb 💤💤

~dedicated to my mom sadeeq hauwas~°

D ady salis ne yayi qoqarin jawo hannun khaleepa d'in suka koma can dakin dasu mama zainab suke dukkansu,
su mama zainab na ganin shigowarsu sukai saurin tarbarsu, momyn amnat ce tai saurin furta cewar"yaya anganta kuwa? Allah yasa, dan ubangijin mu na roqeku kada kuce muna sace heenduh azayi?!,,, tayi mgnr hawaye na zuraro mata daga fuska yayinda mama zainab zaiyi wuya kace ita ga yanayin halin da take ciki dan kuwa, dan kwata kwata ma kasa mgn ma tayi saidai binsu kawai da takeyi da idanunta...
su dady mukhtar kasa amsa musu sukai kowa yai jigum jigum sai khaleepa kawai ne yafara mgn yana mai cigaba dajin wani dandanon maqaqin daci a idanunsa banda azaban zafi da harbawa babu abinda zuciyarsa tafiye yimasa lokacin, daqyar yadago jajayen idanunsa yadubi su mama zainab hawaye na tsiyaya gefe kuncinsa na dama, sosai mama zainab tai mamakin abinda yasaka khaleepa kuka haka, dan iya sanin ta dashi mutum ne shi mai taurin rai farin cikinsa da baqincikinsa ma ba fiye gane masa su zakai ba in yana cikinsu amman yau kam da alama babban abu ya girgiza zuciyarsa rawanin buzu yayo qasa warwas, abinda kaga khaleepa ya zubarwa hawaye kansa lallaikam abun azeemun ne kuma yanada matuqar mahimmanci garesa, babu zato taji yana fadi cikin muryarsa da cewa, "mama heenduh mun duba a gaba kidayan hospital din nan bamu sameta ciki ba, mama waye zai daukemun mata? mama ki fadamun waye shi bazan taba yafe masa wannan mummunan sa6on zunubin daya aikata gareni har abada kuwa na rantse!!!!"
mgnr yake cikin wani sabon tashin hankalin dayake Jin yana sake shigarsa lokacin.
gaba daya suma su mama zainab sai suka ida rudewa tareda rawar jiki daya kwashe su nan take, suna faman cigaba da tsattsafo hawaye na tunanun ina heenduh tayi a cikin wannan rayuwa haka mai ban tsoro??
daqyar dady mukhtar yashawo kansu suka zauna kowa yai shiru bakkajin motsin komi face na shessheqan kukan momyn amnat da amnat d'in yayinda mama zainab tunda ta sadda kanta qasan wajen bayan ta zauna to bata sake marmarin sake dagowa ba saidai tanajin komi ke faruwa a wajen, sosai mama zainab takeda tsananin nuna alkunya akan dud wani lamari daya shafi heenduh.
dady mukhtar ya dubesu dukknsu shima yasake sauke wata ajiyan zuciyar sannan ya hada hannunwansa waje guda ya dunqule su ya daura saman qafafunsa sannan yace"ya ilahi ya rahman innalillahee wa'inna ilaihirr ajiun,Allah ka kawo mana dauki, haqiqa daga ubangiji Allah muka fito kuma daga garesa ne zamu koma, tabbas tashin hankali yasamemu ba kadan ba, dan 6acewan d'a ba qaramun tashin hankali bane ga iyayensa wanda kuwa har gwada ace yau ga gawarsa a gabanka kasan wannan Allahn daya bakannan shine ya karbi abinsa tareda sanin daka qarayi na cewa kaima adud sanda Allah ya buqaceka tabbas ko second bazaka qara ba,, shiru yai nadan wasu daqiqa sannan yasake duban fuskokinsu kowa yayi jigum jigum jiki a matuqar sanyaye,,, cigaba yai da cewa " to bare kuma wannan b'ata ce bawai mutuwa ba, saidai kuma ni'inaji a jikina adud Inda heenduh take bata mummunan waje cikin hukuncun Allah, dudda dai dukknmu nan bamu da tabbaccin cewan shin ya'ilahi d'auketa akayi ne?
ya'ilahi ita d'in da kanta tabar nan d'in to allahu ta'ala dai a'alamu, yanzu ina roqonku da girman Allah ku kwantar da hankulanku kada kubawa jama'a damar sanin halin da muke ciki ta hanyar

ganin damuwan a fuskokinsu, dan Allah inaso ku dauka cewa tanfar heenduh na gida ne dan yanzu daga nan Inmun tashi zamusa afara mana roqon Allah ubangiji daya bayyana mana ita ko jin wani Ibr daga gareta,, insha Allah zamu dauki tsawon sati Ana wannan roqon Allah daga bangarenmu mudaku dakuma sauran malamai na Allah, dan tabbas dud wanda ya maida lamarinsa ga Allah bazai taba tabewa ba da fatan kun fahimci ni, kaima kuma khaleepa ka fahimci zancen nawa kuyi haquri zata dawo nan bada jumawa ba da yardar Allah dan dukknmu nan dama sauran musulman Allah munsan adud kan lamari in akasa ubangiji Allah a cikinsa to zakuga abun yazo cikin sauqi da yankewan wahala insha Allah, zamu cigaba da addu'a bazamu taba gajiyawa ba har Allah ya bayyanata garemu"

daga dady salis har baba isma'il dasu mama zainab sunji hankulansu kashi 50 cikin dari daya bar kansu to jin wannan sanyayen hikayan fasihan bayanai da dady mukhtar yayi ba qaramun sanyaya musu zuqata sukai ba, nan take sukai na'am da shawarar da ya kawo musun Inda babu yanda suka'iya da tsarin Allah wanda sunsan daman Allah ne ya hukunta heenduh zata barsu a wannan lokaci to yaya zasuyi da ikon Allah Inda babu damar yin shisshgi a lamarin ubangiji, dan kuwa dud inka cika musulmi na qwarai kuwa tofa jarabi na qaddarori da dama zakaita cin Karo dasu a rayuwarka dan auna imaninka, kuma daukan qaddara ma ga musulmi na abunda Allah ya nufesa dashi to wannan ma lada ce mai zaman kanta.

baba isma'il ne ya sauke ajiyar zuciya ya dubi yayan nasa cikin qarfin zuciya yake " hakane yaya munkuma ji dadi sosai da wannan tunasarwa taka ubangiji Allah kuma yasa tana hannu na gari" da aminn aka amsa yayinda shima dady salis yace "amman kuma mutane 'yan biki yaya za'ayi dasu knn dan kaga dole zasu tuhumi Inda ita heenduh take dan kaita gidan mijinta kamar yanda a'lada ta sabar"

momyn amnat cikin sanyayen murya tace " hakane kam dady amnat dan wlh kaga wayana nan tun dazun mama(maman salis d'in knn take nufi) taketa mamu waya nida momyn heenduh kan mutane 'yan biki sun fara jaje na babu ita heenduh babu mamanta kuma kasan mutanen yan biki basusan ita heenduh d'in nama asibitin ba"

dady mukhtar yace

"yanzun abunda za'ayi ke maman meenat kikira maman kice ta sallami kowane abokin arziqi da fadin cewan an d'aga tariyar heenduh gidan nata sai nanda wani dan lokaci, sannan kuma dan Allah ina roqon kada kowa a cikinmu ya sanarwa da wani batan heenduh inkun dauke mama daya zama dole ta sani daman ita, dan muddin mutane sukaji b'atan nata to Allah kadai yasan surutun da mutane zasuyi tayi, dan wasu zasuce ma gaban kanta tai tatafi dadai sauran su,,, kunsan mutane da maida qaramun magana ya zama babba, musamman ma in mgnr ta dura cikin taron mata to insha Allah in ba'ai sa'a ba yanzu kaji an murd'e mgnr lokaci daya ta bada ma'anar wani batun na daban kuma,, koni kaina bazan fadawa hjy furdausey wannan batun ba dan bansan mgnr ta fita, mucigaba da roqon Allah har Allah ya kawo mana mafita a lamarin, saidai batun ita zarah d'in babu matsala zata iya tarewa a gidan dan gudun zargi na cewa itama d'in adaga tarewar ta gidan kunga knn za'a sakawa mutane wasu wasi a zuqatansu ace mata biyu babu wacce aka kai a ranar da aka tabbas daza'a kaisu gidan mijin nasu rana daya kuma ko ba haka ba?"

baba isma'il da dady salis suka amsa da hakama shawarar ce yayi, dan haka nan take momyn amnat takira mmn salis ta shaida mata dud abunda akace itama ta buqaci Jin dalilin sallaman mutanen amman sai momyn amnat din ta nusar da'ita data bari insun dawo daga asibitin sayi

mgnr.
a haka suka baro asibitin amman dudda wannan kalamen da dady mukhtar yayi zuciyar khaleepa batabar masa zafi ba, shiyasa koda ya had'u da abokansa su yunus suna shirin masa complain na yaje wajen amarensa ya sharesu dakatar dasu yayi tareda basu haquri ya nuna baijin dadin jikinsa mashi yanzun haka, dole suka tausaya masa kuwa
dan sun kula da rashin nutsuwa kuwa muraran daga doctor d'in nasu musamman da kalolin idanunsa suka sauya daga na'uin asalin fararensu zuwa na'uin jaaa....daga nan ya karb'i key d'in dakin yunus ya wuce danyafi son ya kwanta Inda zaisamu yayi jinyar zuciyarsa shi daya batareda an takura masa ba, asali ma shi koyaye ne baison yaji kowa ya rab'esa bare yasa shi mgn, mafarin knn ya kashe dukkan wayoyinsa bayan kiran number heenduh daya tayi tafi shurun masaqi amman taqi shiga, kwanciya yai a katifan yunus idanunsa na kallon sama yayinda wasu zafafan tafasassun ruwan hawaye suke qara baquntar fuskarsa batareda ya ankara ba,dankuwa jiyakeyi in bai bawa hawayen damar futowa ba tofa bazai taba samu sukunun sauqin zugugin zafin da zuciyarsa ke masa ba a lokacin.
acan kuwa gidan su heenduh bayan 'yan biki dud kowa ta tatafi su dady mukhtar suka iso gidan suka iskesa rufe dole suka nufi gidan mmn salis d'in anan suka sameta itada baba d'ahara ananne kuma mmn salis d'in tashaida musu dalilin rufo gidan datai wato sbd yan biki basu katsewa shugowa gidan, wato wasu na tafiya wanda sukaji lamarin d'aga tariyar wasu kuma na shigowa wadanda basusan da mgnr d'agawan tariyar ba.
mafarin knn ta kallo gidan sbd kowa yazo dole dai yaja daga knn.
mama zainab ta nuna hakanma yayi, babu b'ata lokaci kuwa nanma dady mukhtar ganin baba dahara dayai kuma yasan itama tanfar jinin suce yasa yafada musu batan heenduh, sosai hankulansu kuwa ya d'agu dan baba dahara hannuwa ta daura aka tana kuka daqyar dady mukhtar ya shawo kansu suma suka dan haqura ta hanyar bayanan dayaiwa su mama zainab d'in a dazun suma.
haka sukai jigum jigum har aka kirayi sallar magrib sannan su mama zainab suka fara shirin salla dan qara had'awa cikin adduo'en'insu na salla da roqon Allah ya maido heenduh gida lpia ko hankulansu ya kwanta.
suma su baba isma'il koda suka fito daga masallaci byn sungama sallar isha'e bin baba yawale sukai har gida shima suka shaida masa batan heenduhn kuwa.
Allah sarki har rikicewa baba yawale yasoyi saida salati da fadin Allah sannan ya dawo dadai gamida tausarsa dasu baba isma'il d'in suka dinga yi.. baba yawale bawan Allah dakansa yayi musu alqawalin farayin qiyamullailai tundaga yanzu kan batan heenduhn har sai Allah ya bayyanata lpia tukun, sosai sukaji dadi daga nan bayan sun fito wajen mlm zayyanu baban mama zainab suka nufa basu fito fili sun shaida masa 6atan ba amman sunbuqaci yatayasu da addu'a kan wata 'yarsu data b'ace,, babu b'ata lokaci kuwa tun anan wajen mlm zayyan yafara addu'a kuma sunji dadi sosai daga nan suka qara nausawa wasu wuraren mlm kuwa dan barar addu' oe dud dai kan Allah ya taimaka ya kawo qarshen lamarin lpia.
yayinda kuwa acan bangarensu amarya zarah tun bayan sallar juma'a wato ana gama daurin aure knn, nanfa ta azalzala su momynta da a kaita gidan mijinta dan tasha alwashin saita riga heenduh taka gidan.. haka kuwa babu kunya hjy furdausey uwar ango da hjy hadeeza aminiyarta kuma uwar amarya suka saka zarah a mota batareda sunja mace ko daya daga yan biki ba ko qawayenta suda kansu suka nufi kaita wai kada aje a bata gidan a cewarsu da

kwamacala ta mutanen daba saban ba.
wanda hakan da suka aikata kuwa ba qaramun surutu yaja musu ba daga mutane yan biki suna cewa tunda uwa tasu ta haifesu sukazo duniya basu taba ganin wannan abun kunyar ba kojin labarinsa, acewai uwar ango da uwar amarya kuma sune kadai zasukai amarya wannan zamani damai yai kama kuma wai har suna cewa suzasu siyawa amarya baki idan ango da abokansa sunzo dan suna nan har suzo bazasu tafo ba, wai sune iyayen biki kota ina sun fanshi abokan amarya da yan rakiyarta... haka jama'a sukaita gulma kuwa har a hankali gida ya dawo ba kowa inka dauke baba musa mai gadin gidan dady mukhtar d'in, dan yan biki kowa ta kama gabanta cikeda takaicin abun kunyar dasu hjy furdausey suka watsattsaka yau.
su hjy hadeeza kuwa da hjy furdausey har an kawo zarah amarya cikin tamfacecen gidan khaleepa wanda babu kawai ke babu a cikinsa, komi najin dadin rayuwa akwaisa cikinsa kuwa, har saman benen dakin zarah suka shige daman zarah bawani lullub'i datai saima gwala idanuwa datai tayi babu kunya takewa iyayyen santun gidan da kod'asa.
har saman gadon amarya kuwa su hjy furdausey suka haye sukai baje baje kowacce ta miqe qafafunta kuwa suna shewa da gud'a ayyuriiri nanaye.
yayinda zarah ta mimmiqe saman gadon ta dubi hjy furdausey tace "momy oh nice yau a gidan yaya khaleepa a matsayin mayarda???? wohoho inama ace ni d'ai ce batareda an jonamun da wannan mai siffan aljannun ba sai shegen kyaun tsiya wlh har baqin cikin ganunta nike yanda kikasan na b'ata mata fuska da acid matsiyciyar yarinyar nan haka Nike ji wlh dan wlh ko kyaun ta kadai na fuska ya'isa yasa ta daukewa yaya khaleepa hankali dashi bare na jiki shegiyan ga tsinannen kugu da nonuwa kota ina zata iya janye masa hankali billaheel axeem baqinciki na knn... hjy hadeza ta kstseta da buge mata baki snn tace "ke ar shasha sai wani lissafin banza kk saikace ke ba mace ba? ko'ance miki kyau shine so? "
turo lebunan nan nata tayi yayinda hjy furdausey tace "kibar damun knki zarah kawai kedai kiyi shurunki gidan nn dake d'aya ya dace dan haka kada kisaka tunanun cewa kinama dawata kishiya kisa kawai a ranki ke d'ai ce lokacin hakan zaizo"
hjy hadeeza tace"fad'a mata dai nibari ma nakira mlm lamma (da yake sunansa ya bace a bakin mutane *mlm lamma* ake kiransa dashi)
naji yayane batun dawowarsa..." yawwa tambayar mana shi aminiyas" cewar hjy furdausey d'in tana mai saurin gyara zama.
babu jimawa kuwa mlm lamma d'in ya d'aga wayan "hello... hello.. abinda hjy hadeeza ke cewa knn,, jin datai kamar network yana hanata jiyo mgnr da mlm lamma d'in ke cewa yasata yimusu alama dabari taje waje qilan network d'in ya dawo.
saiko gasa tana fita akayi sa'a network d'in ya dawo normal nan ta maqe murya a hankali tace "hmnn barkanka da aiki mlm lamma na zakin mazaje nayi missing zakanyar ka fa kwana biyu dan Allah kayi kayi ka dawo dud na matsu wlh naganmu tareda kai, gakuma aikin nan fa na zarah kasan yaune aka daura auran kuma kaqi ka dawo kayi mana aikin nan, babu zato taji mlm lamma d'in nata d'an tsubbu yace"bangane ba hjy hadeeza? wai kina nufin 'yata zarah kika auras ban gari? wannan wai wanne kalar mummunan wulaqanci ne kk min hjy hadeeza? nafa lura qiriqiri kinason ki mantar dani cewa ninai miki cikin zarah kika haifeta sa' ilin da kike neman cikin idanuwa rufe sakamakon sanin da kika mijinki mai kudi ne kinason kici kudi ko? nikuma matsiyaci talakka ko? to wlh in kika wasa zan tona asiri ga mijinki alhj Bala dan yasan 'yata Zara ba 'yar sa bace sanholon mutum kawai dashi"!!! yaqarashe mgnr da qarfun gske

cikin tsawa.
SOSAI gaban hjy hadeeza ya buga dammm dan kwata kwata kam batai zaton mlm lamma zai dauki zafi haka ba, itako inya tona mata asiri aiya kasheta kam da ranta,sirri ne tsakanin su dud duniya babu wanda yasan hakan kuma saisu biyu wato itada mlm d'in danko aminiyarta hjy furdauseey bata yarda ta fada mata ba dan shegen wayau ne da'ita hjy hadeezan, dan haka ta qara rage murya tafara rarrashinsa da cewa "haba zakina miyayi zafi haka? to shikenan naji kayi haquri na karbi lefina ina kuma mai tabbatar maka da cewa baza'a kuma hakan ba, kasan ay bazakai fushi daniba nasamu nutsuwa wlh kaima kasan banda abin jin dadi kamarka a duniyar nan"
jitai mlm lamma yasaki ransa harda yar dariya snn yace"to to naji shiknn amman naji kince tanada kishiya kuma kinga zai zamo abin kunya ne a gareni ace ina cikakken bokan zaure tantirin dan tsubbu ace 'yata na da ki shiya to knn inama amfanin aikin nawa?, hjy hadeeza tace' "shi dinne ay nima na gani fa, shiyasa naqagara ka dawo ayita ta qare... shiru mlm yy yana dan tunani snn zuwa can yace "zanyi aiki dole kishiyar tabi duniya ta shigeta ta haukace kuma, amman kada ki bari shi angon ya kusanci zarah dan inya kusanceta to aikin bazai tafi yanda akeso ba, dan bama zaiyi ba kwata kwata, dan haka kuce mata kada ta yarda ya kusanceta nima zan dawo cikin watannan dazarar nadawo saikuzo nafada muku yanda za'ayi aikin dan tundaga nan zan fara had'osa ma."
sosai hjy hadeeza taji dadin hakan kuwa shiyasa suna gama wayar dasauri takoma daki ta sheda musu sunyi waya da mlm lamma da kuma sharadun daya gindaya, nan take hjy furdausey tai na'am da hkn dan batta da buri daman saina son taga bayan heenduh a rayuwa, yayinda kuwa ita zarah sam wannan hukuncun bai mata dadi ba dan taso jin kalar zumar khaleepa a tareda ita yau din nan, amman yazatayi babu yanda ta'iya dole ta haqura saidai tasan dole ta dinga samun hanya suna cigaba da sheqe ayarsu da saurayinta hafiz dantasan bazata iya rayuwan sati daya batareda namiji ya wainata ba(x)knn.
haka sukaita zama gidan har dare sannan suka tafi dan mgnr mlm lamma tasa ma sun fasa jiran zuwan angon da abokansa kamar yanda sukai tunanin zasu zon , dansunsan babu wani amarci da za'ayi dan yanzu dan ance abi doka a zauna lpia wato dokar mlm lamma.
haka sukabar zarah tanata faman kiran wayan ango khaleepa kashe dole takira hafez ta kwatanta masa gidan da yazo ynxn dan wata sha'awa datakeji na tsirga mata lokacin tasan hakan harda magungunan da taita d'irka ne na mata a yau shine ya jaza mata hakan, babu jimawa kuwa saiga hafez yazo, da kanta tafito ta shigo dashi har dakinta kan gadonta ta kulle dakin, nanta nuna masa buqatarta ta maitarta a fili ,shiko sai mmki yake yanda ranar amarci ace zarah bazata bar shegantakarta ba dai yau d'aya? amman kam zarah tacika tantiriyar gaske shikan bazai damuba dan gaba ta kaisa gobarar titi a jos.. haka ya biye mata sukaita sharholiyarsu a gadon ta na sunna anan gidan yayi kwana saida asubahi sannan yasaka kayansa tarakosa ya fuce yashige motarsa yana tafe yana dariya dadin daya kwashe yabar ango da fankon hq ba kwabonsa bare sisinsa. (zarah baki biyo kyawawan halayen mai asalin sunan ba, fadimatul zarah. Allah shirya dai ya kyauta kuma amin).
yau kwana 2 kenan khaleepa na gidan su yunus a dakin yunus d'in rashin lpia sosai yakeyi kuma yaqi bari yunus d'in ya shaidawa su dady mukhtar d'in dancema su dadyn ma yayi yaje Abuja wani aiki kwana 2 tafiyar gaggawa ce ta samesa, ya fadi hakanne kuma kawai danya samu yayi jinyar kansa kawai, yayinda yunus idanuwa kawai ya zuba masa danya kasa gane

kan doctor khaleepa d'in kwata kwata kam.
da misalin qarfe goma saura na dare heenduh na kwance bisa gado yayinda tuni sa'a tayi barci daman ta kwanta ne da wuri sbd sammakon dazatayi gobe zuwa kd ganin gida gobe Monday.
idanuwan heenduh na bisa screen d'in wayarta tana qara karanto text dinda ta rubuta tun jiya wato wanda zata turawa baba isma'il amman takasa sending dinsa banda azababben fad'uwa babu abinda gabanta keyi mata a yanzu. wata zuciyar ke cewa anya kuwa heenduh ga abunda kikayi kin kyauta knn? lashakka iyayenki nacan dud in hankalinsu yayi dubu to tasasshe ne.
runtse idanuwan ta tayi tareda danna sending saqon ya tafiya snn tayi saurin kashe wayar ta tullar da'ita gefe can, aiko tasaki wani dan marayan kuka kawai ta cusa fuskarta cikin filo tanayin sa qasa qasa gudun farkawar sa'a, sotake ta tashi tayi koda nafila ne ta roqi Allah daya yaye mata damuwar da take ciki saidai babu daman salla sakamakon jinin data gani yana d'an d'iso mata a qasanta tun safiyan yau kuwa.
haka taita kama sunayen Allah kala daban daban har barci yayi nasarar surarta a haka cikeda mafarkan gida.
akayi sa'a kuma a daidai sanda heenduh ta tura message d'in a wayar baba isma'il lokacin suna tare da dady mukhtar da dady salees anan cikin sitroom d'in baba isma'il suna qara tattaunawa kan batun ita heenduh danyau kwana biyu knn da faruwan hakan.
mama zainab ce ta shigo wajen da sallama ta ajiye musu ruwa a cups dake saman plate d'in qarfen data dauko ruwan bayan ta gaishesu wanda kaidai ganinta kasan dauriya kawai take a lamurranta, sosai suke tausaya mata musamman baba isma'il ma da kullum saiya rarrasheta dud dare dan muddin dare yayi tofa babu batun barci kuma a idanunta yakau kwana suke yin salla, yanzu dinma qaqalo fara'a tai tace"ga ruwa nan bari na hado muku abincin (da yake kwanan nan dud dare gidan baba isma'il d'in su dady mukhtar suke cin abincin dare)
sannu da aiki sukai mata bata jima ba da fita kuwa baba isma'il yaji qarar shigowan saqo a wayarsa, sam bai duba ba har saida yasha ruwa sannan ya dauki wayar dake gefe hannun kujerar da yake zaune yafara dubawa.
dasauri ya miqe tsaye yana mai qara kallon number heendun tasa da kuma text d'in data turo masa kamar haka.
~"Assalamu alaikum iyayena, dan Allah ina roqonku daku kwantar da hankalinku kan rashin ganina da kukai,ina mai tabbatar muku da cewa a'inda nike ban cikin matsi na takura ina cikin qoshin lpia kuma insha Allah zan dawo gareku nan bada jimawa ba bissalam na barku lpia saqo daga 'yarku heenduh"~°
wani farinciki baba isma'il yajisa a ciki uwa kuwa ance masa yau ga heenduh ta dawo gida an ganta lokacin.
nan take yabawa su dady mukhtar wayar jikinsa na rawa, suka karanta suma sunyi farin ciki matuqa sai godiya sukewa Allah, ana cikin haka kuwa saiga mama zainab ta dawo hannunta daukeda colors da plates ta ajiye tana shirin fita baba isma'il ya miqa mata saqon batace komi ba ta karba ta karanta itama, Allah sarki saiga hawaye na biyo mata a fuskarta, cikin mamaki suke kallon ta atunaninsu saima tafisu murna daganin wannan saqon amman shine take kuka kuma? baba isma'il ya amshi wayar yadubeta cikin tausayawa yake "haba zainab miyasa kuka kuma? keda zakiyi farin ciki na ganin alamun da mukayi ubangijnmu Allah ya karbi adduanmu mun fara samun bayanai a kanta" share hawaye fuskarta mama zainab tayi taqaqaro murmushi tace"haqiqa farin ciki ne yasa ni kuka amman damuwa ta shine shin baban heenduh ita

heenduh wai da kanta tagujemu tabarmu ne tareda sakawa hankalinmu ya tashi haka kan wani tunani nata can na daban? shiru tai sannan taci gaba da cewa " inko tunani na yazamo hakan wato yazamana gaskiya ne tokuwa dud sanda heenduh ta dawo zata fuskanci fushina wanda bata taba sanin ina dashi ba, shiru baba isma'il d'in yayi zuwa can yadubi mama zainab d'in shima ransa babu dad'i yace"gskia ne amman maman heenduh ban tunanin tarbiyar da mukaiwa heenduh zata sakata tayi kuma wannan gangancin, saidai kuma d'an yau baka gane masa ka haifesa ne baka haifi halin saba kuma nima banjin zan goyi bayan heenduh a wannan karon in har tunaninki yazamana gaskiya ne..... katsesa dady mukhtar yayi yace"nasan heenduh bama zata aikata mana hakan ba mudai fatanmu Allah bayyana mana inda take, dady salis yace "aminn zata dawo lpia insha Allah kudai kumuci gaba da addu'a Allah tsareta adud inda yazamana ta zamo yamaidota gida lpia kuma"
da aminn suka amsa su dukknsu, fita mama zainab tayi jikinta ya mutu sosai da ganin wannan text message na heenduh gaskiya, dan ta fara tantama akan wai saceta akai ko kuma 6ata tayi sosai tasan halin heenduh da taurin kai a kusan dukkan lamari nata wanda saidaga baya tazo tanawa abun kuka kuma.
qarfe 2 na washe garin ranar sa'a ta dura gida murna wajen iyayenta da 'yan uwa babu mgn kuwa, saida ta hutu knn awanshekare da safe wajen 11 sannan tayi wanka tatafi gidan su heenduh.
Allah sarki sosai mama zainab taita hidima ga sa'a tun zuwanta kuwa, sa'a cikin tausayi taita satar kallon mama zainab ganin dud tayi rama wanda kallo daya zakai mata ka fuskanci tana cikin matsananciyar damuwa, haka ta daure tafara cin soyayyen plantain da mama zainab d'in ta ajiye mata.
sallamar khaleepa ne yasata saurin kallo wajen, sosai ya d'an rame shima, sanye yake da baqar riga mai zanen *don't hurt me*, a gaban ta da farin rubutu , sai farin jeans d'in wando, babu fara'a kwata kwata a fuskarsa danhar yau baijin dad'i a jikin sa ko qarfin sa ma baiji sosai abinci kuwa rabon da yacisa full tun juma'a banda ruwan tea babu abinda yafiso kuwa.
wasu hawayen tausayin wannan ahalin ne yatararwa sa'a a cikin idanunta, nan tayi dubarar gogesu.
Karo na farko knn dataji tabar goyon bayan heenduh kan abinda tayi na barin gida.
tanaji suna gaisawa shida mama zainab d'in a lokacin, itama sa'a d'in ta gaishesa ya amsa batareda ya kallo Inda take bama.
jitai mama zainab tace "khaleepa bari a kawo abinci ko? gani tai ya girgiza kai a hankali ya bude baki yace" a'a mama azumi nake yi abarsa ngd yanzu ma nashigo na gaishe ki ne dan mun hadu baban dazun. "
mama zainab tace"Allah sarki, Allah bada lada kuma"
"amin mama"
agogon hannunsa ya kalla snn ya miqe tsaye yace"zanje wani wuri mama saina dawo" mama zainab tabisa da adawo lpia harya fice idanunta na kansa banda tausayin kansu bata komi,, dasauri sa'a ta miqe tsaye tace wa mama zainab tana zuwa, a haka tafice dasauri daidai lokacin data hango khaleepa na qoqarin barin zauren gidan ta qwala masa kira da fadin "yaya khaleepa dan tsaya zan fada Maka wata mgn.....
dakatawa yayi harta iso wajen, nan kuwa ya juyo fuskarsa ba walwala ko miskala zarratin amman hakan saima kyau dayaqara sawa fuskarsa tayi,jin ta tsaidasa kuma tayi shiru tana Inda

indar mgn yasa yaqara watso mata dubansa tareda zuba mata idanunsa kaifafa wanda babu shiri sa'a ta dauke idanunta a nasa sakamakon wani qwarjini dataga idanun nasa suka qarayi mata yau fiyeda ko yaushe matuqa,, daqyar ta samu ta bude baki tafara da cewa"amm... immm.. yaya khaleepa daman zan shaida maka cewa ne heenduh fa tana can gida na a garin bauchi can ne taje ta 6uya.....!!!

~hmnnan..... niko nace sa'a mai tonon silili knn, koko kunga laifin sa'a dears fans anan~???

by
Xexen Fasaha.
[4/18, 11:06 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO.

story and writing
by
Xayyneb 💤💤

~dedicated to my mom sadeeq hauwas~°

👁️📦👁️
🅿️5️⃣1️⃣
G a baki daya khaleepa yaji mgnr tazo masa uwa a durar mikiya yanajin kamar mafarki yake da hakan, wato sa'a na fada masa hakan kuma.
fiddo idanuwa yayi cikin mamaki yasake duban sa'a yace " kin tabbatar maganarki gaskiya ne sa'a datu?kinsan kuma ba wasa Nike daku ba bare kimun qarya fa" yy mgnr yana mai sake tsareta da idanunsa.
cikin rantsuwar mgn sa'a tace"wlh Allah kuwa yaya khaleepa heenduh nacan gida na yau kwananta uku"lumshe idanuwa khaleepa yayi zuciyar sa na wani bugawa fat fat fat saboda tsabar farin ciki uwa ya zubda ruwa qasa yasha yakeji,godia kawai yayinda miqawa ga ubangiji acan qasan ransa,daka kalli fuskarsa kuwa zakasan ransa a matuqar farance yake sosai wanda ko sa'a dake gabansa saida ta fahimci hakan.
amman saiya kanne dudda wani shashi na zuciyar sa na tuhumar to akanmi heenduh zata gudu ne kuma? juyowa yai ya kalli sa'a kai tsaye yace"kota fada miki dalilin tafowarta ta ne zuwa wajenki?"
sauke ajiyar zuciya sa'a tai batareda boye masa komi ba ta fada masa dukkan dalilan da'ita heenduh ta fada mata na gameda zubewar cikinta da take tuhumar sa da shine sila gamida auran zarah dayayi na ganin zaici amanarta ne kawai" wani kalar dan guntun murmushi khaleepa yayi sanda yagama jin bayanan sa'a d'in sosai yayi mamakin kan hakanne kawai zaisa ta gudu tabar mutane cikin tashin hankali? shin miyasa tunanin headache yafiya qaranta ne? dan intai wani shiriritan tofa insha Allah ko yaro qarami bazai yi hakan ba, sake duban sa'a

yayi tareda katsewar tunanunsa yace "OK ngd sa'a kiban full address d'in gidan naki a bauchi d'in to sainaje na tafo da ita... nan take sa'a ta basa full address d'in gidanta kuwa tana shirin komawa cikin gida ne yace" amman please sa'a kada ki fadawa kowa wannan mgnr kinji ko?"
gyada kai tayi tareda cewa "insha Allah bazan fadawa kowa ba hakan yaya khaleepa"
daga haka ta wuce cikin gida shima yafuce da sauri yaje dakin yunus ya samu yunus d'in yana bayi yana wanka nanfa cikin sauri ya dauki dud wani abunda yake buqata sannan ya dauko key d'in motorsa ya futo waje yashige motorsa tareda bata wuta kan kece mi har ya dauki hanyar garin bauchi kuwa, gudu yake shararawa na mutunci a kan titi uwa mai gasan tsere na wasan motocin dud duniya kuwa, wanda hakanne yasa sharp sharp ya iso cikin garin bauci yaita bin address har ya iso anguwar dai dai gate d'in gidan sa'a ya kashe motor ya futo, watch d'in hannunsa ya kalla yaga har d'aya ta kusa, nan yayi takun sa ya tafo tareda isa qofan gidan yasa key d'in hannunsa yayi nocking d'in qofan wanda babu jumawa saiga maigadi yahuza fillon nan yazo ya bude masa qofan,, ganin khaleepa dayai bai kuma sansa ba yasashi cewa"asshalamu alaikoum mlm mashu gidan basha nan sunje ganin jida"
wani dan taqaitaccen murmushi khaleepa yai yasake duban mutumin heenduhn yace"eh nasani ay heenduh na ciki ita ko? "gyara tsayuwa yahuza yayi yace" eh Itakam ay tana shiki batama juma da barin nan haraban ba"
"OK mijinta ne to ni, fatan zaka bani hanya na wuce?"aiko khaleepa na fadan hakan yahuza fillon yaita kallon sa yana hango kuma tsantsar tsabar kamarsu da heenduh d'in wanda shi sam bai lura dama hakan ba sai yanzun da khaleepa yabasa haske.
dan haka cikin sauri yace "ah to yalla6ai shannunka da juwa ka shigo tana ciki dai kmr yanda dai na maganta makan yanju to"
shigowa khaleepa yayi yanata kallon kowa ne side d'in gidan da tunanin yanzun fa lollipop d'in sa na ciki fa? a haka harya doshi shiga falon gidan yanajin yahuza fillon na cewa "afito lpia yalla6ai".
har tsakiyan falon ya shiga ganin babu kowa a cikinsa sai qarar TV ma dake tashi yasa shi sake bin falon da kallo haryayi nasarar hango wata qofan daki dake bude wanda ga alama nan ne hanyar shiga dakin.
zama yayi saman kujera tareda daukan qafarsa daya ya aza saman gudar dayar qafar tasa yana karkadawa yayinda fuskarsa ke bisa fuskan TV plasma d'in yana kallon tashar da suke hasko wani film na Indian wanda hakan yaja hankalinsa yana kallon soyayyar da film d'in ke nunawa tsantsa tsakanin miji da matar harda yaransu guda biyu da gani ahalin gidan na cikin kwanciyar hankali sosai, lumshe idanunsa yayi tareda dan kishingidawa saman 3sthear d'in da yake akai zaune, wato yadan kwanta knn yana tunanin wani abu a ransa bai ankara ba saijin motsi yayi wanda tabbas kuwa yasan kobai juya ba itace ta fito daga daki dan yanada tabbacin ita d'ai ce a cikin falon da kuma dakunan gidan,
sake gyara kwanciyarsa yayi ya zuba mata kaifafan idanunsa ransa wasai da wani mummunan jin dadi daya mamayeta , kallon ta kawai yake kogaza yunqurin tashi ya qiyi dan kam yafison ta gansa da kanta batareda yayi mata inshara da kansa ba kodan ta ma mamakantu da ganin nasa, mafarin knn daya cigaba da jifanta da kallon sa, sosai shigarta taso dilmiyar da tunanun sa kuwa.
yayinda ata bangaren heenduh kuwa tun tana toilet tana wanka tadingajin wani gizon qamshi wanda tuni tashaida mamallakin sa saidai tasan kawai gizo ne na hasashen zuciya dan tasan

ko kusa babu abinda zai kawosa gidan nan Inda babu wanda yasan tana nan kuwa, a haka harta gama wannan wankan da tunanin hakan a ranta, sosai gabanta taji yayi mata wani azababban bugawa dammmmmm!! dam!!!!! a sa'ilin data fito daga toilet d'in zuwa room d'in dakin nan taji kamshin yamafi yawwa anan uwa yana cikin dakin,,, sosai jikinta ya mutu daqyar ta samu ta shafa mai ko fowder bata murza ba ma amman kyaun ta natural baiban shaining ba akota ina kuwa a jikinta.
zafin da akeyi dudda akwai fankoki sama da uku a dakin amman batabar jin dishi dishin zafin ba koyaye ne a jikinta kuwa, mafarin knn yasata saka wata yar riga iya cinya dud tabi mata jiki kwata kwata battada nauyi rigar, gata kuma shara shara mai qananun kofofi wanda ko bra bata saka ba dan tafi son tajita a haka Inda tasan babu mai shigowa cikin gidan.
shiyasa komi na jikinta bata boyewa hatta cikakkun tsaye young manya maman ninta koyaya ta motsa jikinta suma samsun yi nasu motsin na daban.
parking gashinta tayi tareda saka turare a jiknta dan ita ma'abociyar son qamshi ce matuqa.
jin cikinta na mata alamun jin yunwa tasan kuwa dole taji hakan dan kuwa tun safiyan yau babu abinda tasakawa cikinta mafarin knn ta dauko wayarta ta nufo falon,,, dasss dasss wannan karon kam haka gabanta yayi wani azababban bugawa sakamon tabbatarwa datai da koma yayane tabbas mai kalan turaren doctor ya shigo gidan nan, to da yaushe knn? harbata ga kowa ba? koko tana ciki ne aka shigo aka tafin bata sani ba!? tambayar datakewa zuciyarta knn.
kallon falon kawai take cigaba dayi jiki a sanyaye wanda sai daqyar ta samu dai ta daurewa tanufi hanyar kitchen d'in dan samawa cikinta haqinanin haqqinsa.
ta gabansa tazo tabi ta wuce amman da yake hausawa sunce hankali ke gani ido kam gululu ne shiyasa hankalin ta baibi ta wajen ba ta shige kitchen shiko yabi bayan ta da kallo babu shiri ya lumshe idanunsa danjin yanda wani abu ke masa xirrrr xirrrr yana tsurga masa a jiki, qara lafewa yayi cikin kujerar wanda babu jumawa saigata ta fito daukeda cup na ☕ a hannunta da soyayyen dankali daqwai wanda tun data gama hadasu tun dazun harta kaima yahuza nasa amman ita bata waiwaye natan ba sai yanzu.
zama tai tai seting TV tana kallo yayinda take cin komi dake gabanta a hankali wanda a haka taci babu laifi dudda har yau batajin dadin zuciyar ta kuwa komi cikin sanyin jiki take yinsa uwa marar lpia, sosai jiknta yaqara sanyi akan dud abinda takeyi wanda shi kansa saida ya fahimci hakan harya fara tunanun to kodai bata lpia ne dan sanyin jikinta datake da ya qaru sosai akan ma wanda ya Santa dashi naturally d'inta.
saida taji cikinta yayi dan nauyi ne yasata zuwa ta wanke kayan datai amfani dasu ta dawo falon knn zata wuce daki nan tsakan falon taja ta tsaya tanason dai sake tantance sanin Inda wannan futinannen qamshin ke qara bujiro mata, kamar ance ta kai dubnta kuwa Inda yake nan ta ga ya tsareta da idanunsan nan yana bin ko'ina nata da kallo daga kishingiden sa da yake dai hankali kwance .
matuqa ta girgiza gamida gigita wanda babu arziqi ta kwalla wani uban ihun dan a zaton ko aljanine yayi mata siffar shi.
dudta bi ta rude tana shirin shigewa tsakankanin kujeru ta buya saiko taga ya taso ya nufota, aida gudu tayi cikin daki tana haki ta turo qofa zata datse shiko yasa hannuwansa da qarfi ya turo qofan daki ya shigo nan kuwa ta duqe a rude kasa tana kuka tana fadin "a'uzubillahe minal shaidanin rajeem bismillahirra'manirra'hemwa'innahu sulaimanu wa'innahu bismillahir rahem"

haka taita salati ta kama idanuwa kuwa ta rintse su gam jiknta naci gaba da rawa zufa dud ta rufe ta a jiki.
shi abunma dariya yaso basa ganin lura dayai tamaishesa aljani,amman sai ya gimtse baiyi hakan ba, ahankali ya tako ya iso gabanta yaja ya tsaya hannuwansa zube suke cikin aljuhun wandonsa duka biyun ya zuba mata idanuwa kawai yana bunta da kallo.
zuqunnawa yayi gabanta saman qafafunsa yasake zubo mata idanunsa kawai kallon ta yana sakin wani murmushi wanda rabon da yayisa tun tana nan
[4/18, 11:06 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO.

story and writing
by
Xayyneb 💤💤

~dedicated to my mom sadeeq hauwas~°

👁️📦👁️
🅿️6️⃣6️⃣
A hankali ya miqa hannuwan sa ya aza saman kafadun ta ya riqosu tareda dan jijjigata yace "ki nutsu fa, nine nan bawani ba, look at me baby, kalleni sosai bawai sprit bane, aljani kamar yanda kika dauka ba matsoraciya kawai banda rigima babu abinda ke dawainiya dake sai kuma tsoro" yaqarshe mgnr tareda kamata suka miqe tsaya tare jikinsu na gogan juna.
sai a lokacin ne nutsuwa taji ta saukar mata harda sauke wata sanyayyen ajiyan zuciya tayi,data bude idanunta kallon sa kawai takeyi da fararen idanun nata fuskarta cikeda tsantsar tsabar mamakin yanda akayi yazo nan Inda babu wanda yasan da hakan kuwa, to waye ya fada masa?"
sa'a, amsar da taji zuciyar ta knn ta bata, tuni ranta taji kam ya baci banda bankawa sa'a kwandunan zage zage babu abinda takeyi a cikin zuciyar ta, qasa tayi da idanunta ganin hannunsa na riqe da nata yasata fusge hannun ta a fusace taja tunga tana qare masa kallo tareda yatsuna fuskarta snn tace "wlh nasan babu munafukan da zata fada maka cewa ina nan face sa'a, mtsss wlh kuwa da nasan zaka zo da tuni na qara mai nabar gidan nan"
jin wannan kalaman nata dayayi ransa kuwa ya baci dasu dan haka cikin fushi ya daka mata tsawa da cewa "ke kifa shiga taitayinki wlh, wannan ba komi ne kikeyi ba kuwa face borin kunya kike neman nad'esa da hauka,har kan wani banza kishi naki zaki iya guduwa kibar gida? kinsan kuwa iya girman tashin hankalin da kika jefa iyayenmu ciki kuwa? wanda har yanzu suna cigaba da jinyar zuqatansu kan rashinki? kin dauki akhakina kin zubar mun da ciki sannan kuma kin dauki alhakinmu na d'aga mana hankali da kikai da tunanun ko sace ki akayi, heenduh shin yaya zakiyi da wannan alhakin mutanen da kika dauka na hanasu bacci da samun cikakkiyar nutsuwa a garesu dud dan a cewarki an miki laifi ko ?to mu knn wannan abin da kikai mana miye sunnsa musamman mani da kika zubar min da ciki sbd tsaban kishin ki can, dakikai mun hakan kinga na dauki wani qwaqqwaran mataki a kanki ne em?! girgiza kai yayi tareda yin

murmushin takaici snn yaci gaba da cewa "ki dauka kinada 'ya kuma tai miki wannan abin da kikaiwa iyayenki wato na bujerewa umarnunsu harta kaiga guduwa ta barki shin wane kalar zafi da radadi zakiji zuciyar ki tayi a lokacin? , amman ke baki damu ba kinbar iyayenki a halin qunci da damuwa wanda in ba roqonsu gafara kikai ba Allah ba bazai yafe miki ba dan sabawa iyaye ba qaramin zunubi bane babba, wanda ke har gara ke dan hanyar samun aljannarki tana wajena amman ni kuma hanyar samun tawa aljannar tana wajen mahaifana to ki gayamun saina qi bin umarnunsu kan sun zabamin mata ke kuma nabi naki ra'ayin innai hakan kin kyautawa rayuwa ta knn? hakan na nufin nayi fatali da mgnr iyayena knn fa? kiyi tunani akai, amman ynxun dud laifin da kikai mana baki gansa ba harma kina batun qarawa gaba saboda shed'an nata kad'a miki gangarsa ta kururuwa akai lollipop"
shiru tai dan jikinta ba qaramin sanyi taji yayi ba, dan ko harga Allah tasan tun Sanda tabar gida bata qara samun wata nutsuwa ba itama, koda yaushe iyayenta na cikin ranta, to miyasa zata aikata hakan wa iyayenta ta daga musu hankali ma kan wata kishiya can wacce ba'akanta zata zauna ba intazo,, zuqunnawa tayi qasa dan gaba daya zuciyar ta a dagule take jitake banda ganin iyayen nata batta buqatar komi a lokacin kota roqesu gafarar abinda ta aikata kuwa, wani kukan ne taji ya zo mata nan taita yinsa sosai hadda shessheqa, bai hanata ba yasan tadauro intai kukan ya rage mata wani damuwan kamar yanda yasan hakan kuwa shima Inda ya shiga damuwan shima,,
saida ta jima sosai tana kuka sannan taji dan relief a ranta, miqewa tai batareda ta kallesa ba ta futo nan falon dan wani haushin sama ta ke qaraji dud Akan zarah kuwa daya aura dan abin ne yafi ma tsone mata 👁️👁️.
zama tai saman kujera tana sauke ajiyan zuciya, ganinsa tayi shima ya futo ya qaraso kusa da'ita ya zauna tareda ruqo hannunta yana murza mata tafukan ta.
sosai taji dumin gumin hannunsa na ratsa mata dukkan illahirin jikinta, so take ta janye hannunta amman a maimakon hakan saima saya idanunta datai wato ta lumshe su.
jitai yasaki ajiyan zuciya shima sannan taji yaci gaba da cewa "kada ki damu dan indai ta nine lollipop na yafe miki komi kikai mun gaba daya,danni komi nawa naki ne, da farin cikin ki nike rayuwa kema kinsan hakan lollipop na"
hakanan taji kalaman nasa sun mata dadi amman bata nuna hakan ba a fuskarta ba saima amshe hannunta datai daga nasa ta miqe tsaye batareda ta kallesa ba tajuya fuskarta can wani waje, cikin mgnr yanga tace"mizakaci ne a kawo maka?"murmushi yasaki ya kwanta saman kujerar ya mimmiqe yace "rabon danaci abincin kirki tun ranar da lollipop na ta gudu ta barni inata walagigi cikin kuncin rayuwa" ganiyai ta hararesa ta gefen idanunta tareda tabe lips batace komi ba, murmushi kawai yayi ya miqe tsaye yatako gabanta tareda tsayawa a bayanta baice mata uffan bama anan sai ma jitai kawai ya rungumota ta baya ya manna bayanta cikin faffadan qirjinsa hannuwan sa na saman shafafen cikinta ya zagaye ta dasu.
dukkan su saida suka saki wata qaqqarfan ajiyan zuciya dan ankwana biyu basuji dumin junan suba shiyasa da hakan ta faru yanzun sai sukaji uwa sun kwana 1000 ne basuji dumin junan su ba.
ahankali taji yana murza mata qugunta mai sharp sosai qirar kalangu, babu bata lokaci taji yayi sama da hannunwansa zuwa wuyanta yana shafa ta tareda matsa mata kafadunta a hankali gamida yi mata busar sanyayyen iska a dogon wuyanta.
jikinta rawa kawai taji yana mata a sanda taji ya juyo da'ita zuwa gabansa bai tsaya wata wata

ba ya tallafo fuskarta da hannyensa murya qasa qasa taji yace "wannan nike son ci,yayi mgnr gamida shafa mata yan jajayen red lips d'in nan nata da babban yatsan sa na hannun dama,aiko zaro idanuwa tayi tana kallon sa so take tai masa tsiwar tata aikam lura da hakan dayayi nan da nan ko yayi saurin rufe bakin tsiwar ta hanyar daura bakinsa saman tausasan sweet lips dinta da yayi yana mata shan alewa a kansu..... da sauri taji ya ida jawota suka zube saman 3sthear d'in nan ya kwantar da ita jikinsa fuskarta na kallon rufin dakin kamar yanda ya saba mata kwanciyar hakan knn a jikinsa dan yanda zai taba abinda yake so San ransa a jikinta, nan ya rungumota tsam a jikinsa yana cigaba da bata wasu azabatattun deep kissing wanda yasan suna girgiza ta, banda sauke ajiyan zuciya batta komi a lokacin kuwa, qirjinta sai sama da qasa sukeyi idanunta a rufe gam gam, a hankali taji yayi qasa da hannuwan sa yana mata tafiyan tsutsa tun daga saman laps, cinyoyinta har kawo ramin cibiyarta yayinda ya'ida yin sama da hannuwan sa yana qoqarin daura hannuwan sa saman burinsa nashanunta, aiko ta shammacesa tayi wuff tabar jikinsa da gudu ta shige daki ta turo ta fada saman gado tana sauke numfashi.
murmushi kawai yayi ya miqe ya nufi wata hanya da yasan toilet ne a wajen daga kallon wajen kuwa, shiga yayi yayo wanka tareda alwala yafi to ya isa bakin qofar dakin da dan qarfi yace "you ready, ki zama cikin shiri kamun nayo salla na dawo mu wuce."
yasan bazai samu amsarta ba dan haka bai wani tsaya ba yafuce daga falon ya samu yahuza mai gadi ya tambayesa inane masallacin anguwar, babu bata lokaci yahuza ya masa kwantance sannan shikuma ya fita.
acan ko daki haushin kanta dud ya qumeta na tunanin cewa mima yasa zata sakar masa jiki da fuska harya samu damar mata hakan ma? gashi yana niyyar daga mata hankali kawai,, tsoki taja ta miqe ta nufi toilet tacire kayanta ta fara wanka, koda ta fito wata atanfa riga da siket ta saka dinki zamani daga kayan sa'a, dinki yayi sharp d'in jikinta tsab.. tana jinsa daya dawo yana mata mgn Akan tafi to su tafi kada suyi dare a hanya,, amman banza tai masa sadda ta mila tasha iska sannan ta fito da wani dan qaramin gyale a saman kafada, tayine dan yaji haushi sanin datai yayi hating ta sanya gyale ta fito kuwa, kuma shima sarai ya lura da hakan amman daya fahimci neman ba'asi takeyi yasa shi sharewa kawai baibi ta kanta ba harsuka shiga mota yahuza yabude musu gate suka wuce ita dashi wato yahuzan sai daguwa juna hannu suke.
koda suka dauki hanya babu wanda ya cewa d'an uwansa uffan gudu kawai yake tsalawa dudda yasan tana tsoron gudunsa na mota amman saiya share yaqara speed sosai.
ta tsorata matuqa amman kuma girman kai yama hanata data roqesa yarage gudu saima saka fuskarta datai ta cusa ta cikin qafafunta tana kiran Allah a ranta.
sarai ya lura da hakan murmushi kawai yayi abunsa yaci gaba da tuqinsa zuciyar sa wasai cikin tunanin cewa yagano lollipop dinsa cikin yardar ubangiji Allah hargata kusa dashi miyafiye masa farin ciki a wannan rana babba a garesa bayan yaita godewa ubangiji sarki Allah.
sune sai ana kiran sallar isha'e snn suka iso cikin garin kaduna a cikin anguwar su.
dai dai qofan gidan su heenduh ya tsaya tareda kashe motor ya juyo yana kallon yanda ta saddar da kanta qasa ko motsin kirki ta gazayi wanda a zahirin gskia kam banda tsabar tsoro na tunanin hukuncin dasu mama zainab zasu ya mata babu abinda ke damunta,, hannuwanta dukknsu na zube saman cinyoyinta tana kallon su, jin yayi parking ne yasa ta dago da kanta.
reassess! rass! rassss! taji gabanta ya yanke yana bugawa,, cikin halin tsoron da take ciki ne taji saukar hanuwansa cikin nata yana qoqarin riqo mata hannuwan da sigar kwantar mata da

hankali dayake son yi gamida bada confidence sakamakon lura dayai da furgicin datai, aiko babu bata lokaci nan tayi saurin ture hannunsa tareda buge hannun daga jikinta ta juyo tana dandanda masa manya harararraki cikeda tsiwa tace "kada ka kuma, dan jikina haramiya ne gareka nafada maka hakan kuma ynxun ma na qara maimaita maka, Inda ban sonka sai kaje wajen wacce kakeso itama kuma take sonka amaryar taka, sai kaje wajen ta tabaka dukkan jin dadi" taqarashe mgnr tareda yamutsa fuska.
tabe lips yayi ya dubeta cikin son ya qara quleta danya fuskanci kishin ne nata ya kuma bujirowa, nan ko ya kanne mata ido daya tareda dage gira ya tabe baki yace "kinyi gskia dan amarya kam akwai nuna qwazo abin cwai cwai dad'i muah"
wani qululun takaici ne yasake taso mata a fusace kuwa ta Bude motor ta fice zuwa cikin gidan nasu gabanta na cigaba da bugawa kuwa sosai, shima Bude motor yayi ya fito tareda rufeta ya biyo bayan heenduh zuwa cikin gidan yana mata dariyar kishin nan nata a ransa.
tana shiga ta samu mama zainab ita da baba isma'il zaune saman carpet nan tsakar gida tana yanka masa kankana sallamar datai ne cikin d'ari d'ari tareda bin bango hakan ne yasa daga mama zainab har baba isma'il suka dago fuskokinsu da sauri suna kallon to cikin mamaki wanda lokaci daya suka miqe cikin tsakanin farin ciki kuwa, dasauri mama zainab ta'iso gabanta tana fadin"henduh kece kuwa? inn..... ii.... ina kika shiga ne Allah yabaki ikon futowa yau...? kai alhamdillah mun gode Allah, Allah qarawa annabinsa daraja aminn, tana mgnr ne cikin zubar hawaye farin ciki dasauri suka rungume juna suna hawaye daidai nan khaleepa ya qara so wajen cikin murmushi ya isa kusada baba isma'il daketa faman godiya ga Allah hannuwansa na'a sama,shima banda fara'a baya komi,, baba isma'il ya dubi khaleepa cikin mamaki yace"ah khaleepa yana ganku tare? badai kai ka nemo mana ita ba?, khaleepa yace "eh taje gidan sa'a ne qawar ta a bauci dan ta samu sauqin zuciyarta kamar yanda nasamu labarin hakan daga ita sa'a d'in, to shine sa'a d'in taban address d'in naje na daukota,,, jin hakan da mama zainab tayi taji ranta yabaci nan take ta ture heenduh daga jikinta da sauri, nan ta matsa daga gabanta sosai tana mata kallon mamaki,,, da gudu kuwa heenduh ta
qara so gaban mama zainab ta duqa qasa tareda rirriqe qafafun mama zainab d'in cikin kukan nadama na abinda ta aikata musu take cewa "dan Allah mama kuyi haquri, baba ku yafeman wlh bada sona na tafi batareda sanun ku ba,, tunkudeta mama zainab tai bayan ta watsa mata marurruka qarawa biyu saiga heenduh a qasa, da sauri khaleepa ya'iso wajen ya tayar da ita ya dubi mama zainab ransa babu dadi shima yace "dan Allah mama kuyi haquri ku yafe mata damuwar data saku wlh nina yafe mata har a raina,, cikin wani sabon bacin ran mama zainab tace" rabu dani khaleepa na fuskanci taurin kan heenduh ya shallake tunanin mu, yanzu fisabilllahe bacin tana 'yar banzar yarinya dud tausarta da mukayi kan batun auran nan tai mana lub lub uwa ta dauki maganar mu da muhimmanci amman ashe ba haka bane ita a ranta ba? harta iya daukan satan hanya ta tafi gari ya garara har bauci ba tareda sanin muba tana halin ciwo kuma amman ko kanta bata tausayawa bare mu da mukayi tunanin sace ta akayi ta tada mana hankula a banza a wofi!?amman shine yanzu da Allah yasa ita sa'a d'in ta fada Inda take har aka ganota dafa knn Bama tayi niyyar dawowa gidan ba dan yanzun dan ubanta, kuma shine dan batada kunya tazo tana mana kukan qarya Alan? "
taqarashe mgnr tareda qoqarin wani marin heenduh wanda dasauri khaleepa ya shiga tsakani saiga saukar marin tasss saman fuskarsa amman bai damu ba saima mama zainab d'in data dinga basa haquri dan bashi tazo mari ba, amman shi fadi ma kawai yake "kuyi dai haquri

mama ku yafe mata bazata qara ba insha Allah... shiru mama zainab tai amman badan tawai haqura da hukunta heenduhn ba.
heenduh daketa a cigaba da rusgar kuka ganin datai babu sa'a ta samun sauqi a wajen mama zainab hakan yasata rarrafawa gaban baba isma'il dake tsaya yana kallon ta kawai tun dazun yana mamakin abinda tayi shima wanda ko kwata kwata bai tsaye hakan daga gare taba.
dasauri mama zainab tabar wajen tareda shigewa daki,
heenduh kuwa tana isa wajen baba isma'il d'in shima ta dafa qafafunsa cikin hawaye tace "babana nasan kai bazaka iya taba yin fushi da heenduhn kaba, dan girman Allah ka yafe mun kuma kasa mama ta yafemun itama wlh bazan taba samun nutsuwa ba in kuna fushi dani a rayuwa ta gwaramun kuyita mun huro mai tsanani wanda koda hakanne zaiyi sanadiyyar rayuwa ta na amunce da hak... kanta ida mgnr baba isma'il ya qwace qafarsa daga gareta yana kallon ta cikin tsananin d'acin zuciya ta bacin rai yana cewa "wlh kinban mamaki heenduh matuqa gaya kuwa, da hankalinki da tunanin ki kikai wannan abin? girgiza kai yace lallaikam kin mana d'an baka zata ba, kin batamun rai sosai heenduhn wanda baki taba 6atan rai ba kamar wannan lokacin, kiyi haquri heenduh bazan iya fara kallonki da fuskar afuwa ba kamar yanda kike buqatan hakan daga gareni... kuka heenduh ta qara fasawa tadaura hannuwanta aka ta zube qasa tana burgima da mad'od'owa tana fadin "wayyoni Allah ni heenduh rayuwa kinmin zafi iyayena sun tsananta fushi dani, ubangiji Allah na roqeka ka dauki raina na hutu...adaidai nan mama zainab ta fito daga daki hannunta boye a bayanta tana isowa kuwa wajen da heenduh take, heenduh nata billayin kuka a qasa kuwa, bata ankara ba saijin zazzafan saukar wayar wuta tadunga ji a jikinta, ai wani uban ihun ta kurma tareda miqewa tsaye a guje ta fada jikin khaleepa tana ihun tsalle tsalle tareda sakin wani kukan tareda sake qamqamesa a jiknta dake rawa kota'ina.
wanda shima khaleepa tsakanin tausayin hukuncin dayaga tana kar6a daga iyayenta ne yasashi fitar hankalinsa a jikinsa sbd zugin zafin da zuciyarsa ke masa, sosai yaqara qanqameta jikinsa yana sakin ajiyar zuciya mai zafi, dasauri baba isma'il yajuya yabar gidan yayinda mama zainab tai shigewarta daki bayan ta jefar da bulalan qasa..suna qanqame da juna a haka saiga baba isma'il ya dawo shida baba dahara tareda dady mukhtar da dady salis sun biyo baya suma sun shigo gidan.....

by
Xexen Fasaha
[4/18, 11:06 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
📦📦
👁️👁️
DA SAURAN KALLO.

story and writing
by
Xayyneb 💤💤

~dedicated to my mom sadeeq hauwas~°

*

A hankali cikin dubara khaleepa ya zame heenduh daga jikinsa suka zauna nan saman carpet d'in, suma su dady mukhtar d'in suka qaraso suna shirin zama saiga baba yawale shima yashigo gidan da sallama hannun sa riqe da carbunsa, kusan tare mmn sales da momyn amnat suka shigo gidan suma anan suma suka zauna dukkansu suna sake gaishe da baba yawale d'in.
sake futowa mama zainab tasakeyi jin mgnr baba dahara tana rarrashin heenduh dacewa tabar kukan haka nan komi yazo qarshe ay insha Allah Inda tadawo gida lpia.
zama mama zainab tayi dud aka nutsu wajen, saida baba yawale y bude taron wajen da addua gamida salatin annabi sannan fa baba isma'il yakoro musu bayanin komi ya faru har kawo futarsa dayai yanzu yakirawo su.
shiru kowa yayi a wajen banda sallallamin baba dahara da tashin shessheqar kukan heenduh bakajin komi a wajen.
cikin d'ashewar murya wacce taci kuka ta qoshi heenduh ta bude bakinta da qyar tace"kuyafemun dan girman Allah wlh na tuba bazan qara ba, kuma wlh ni gidan sa'a kawai naje bawani waje ba, ko sa'a din ma aka kirawo aka tambayeta zata shaida muku hakan ne....
kwab'e mata baki mama zainab tayi tace "sakarar banza da wofi yimana shuru mikuma zaki fada mana wanda zamu yarda dake yanzu ay babu shi,, kuka ta qara saki tanayi tana dafe kai gwanin tausayi wanda khaleepa baisan sanda ya fara zubda mata hawaye ba na tsakanin tausayin ta dake bin ko ina a cikin saqon jikinsa. sosai su dady mukhtar suka tausayawa heenduh matuqa, sunsan komi ya faru da mutum qaddarar sane dudda itama heenduh d'in nada laifi amman Inda ta gane kuranta tazo tana neman ahi na tuba ai sai a haqura komi ya wuce Inda ubangiji Allah ma ana masa laifi ya yafe bare mutum abin halittarsa.
baba yawale yadubi heenduh sannan ya dubi su baba isma'il kawai ya girgiza kai yace " komi dai ya rigaya daya faru, sai ayi haquri kuma, ya dubi heenduh yace" kinfi kowa laifi hendatu miyasa zakije wani waje ba tareda sanin kowa ba? kinbi kin tadawa kowa hankali sannan kuma kinqi bugowa a waya ki fadi inda kika je har saida Allah ya kawo wannan yarinya sa'a datu ta fada gskia a hakan da kikayi kin kyauta knn? " girgiza kai tayi cikin share hawaye tace" ban kyauta ba amman kuyafemun narantse da Allah mairan qarfe bazan sake maimaita hakan ba"
baba yawale ya maida dubansa ga mama zainab da baba isma'il yace "zainabu da isma'il indai kun daukeni da gske a matsayin mahaifi to ku yafewa heenduh dan qaddara nakan kowa kuma kun hukuntata yanzu iya hukuntawa wanda nasan koda wasa bazata qara fara gigin sake aikata hakan ba,
dagowa baba isma'il d'in yayi fuskarsa a sake dan shima runtse idanuwa kawai yayi ya kauda ido akan heendun tasa yayi mata hukunci da daidai abinda ta aikata kuwa, dan haka yace "nina yafe mata komi ya wuce baba, daman munyi mata hakane danta gane iyaye ba abin wasa bane, bakomai ynxun komi ya wuce Allah baku zama lpia kuma, Allah shi muku albarka" cikin murmushi dady mukhtar da dady sales sukai tareda cewa "aminn qanenmu,, dady mukhtar yasake cewa " naji dadin sake fahimtar juna da akayi haka a sauqaqe komi ya wuce ai insha Allah,, dady sales ya karbe da fadin cewa
"hakane, aci gaba da haquri dai dan haquri shine ka isa gaci Allah iyakar qarshen taqaddamar

knn Allah kiyaye gaba kuma"
da aminn suka amsa, cikin fara'a baba dahara tace "uwargida ta gudu tabar ango a rude to ina kaga a gaishesu? dud tasa yabi ya rame ko? hmnn kinci arziqi ban aure miki shi bama ay na tausaya miki shi Inda kin gaji kin bada kai kin sare" duka wajen akayi dariya harda mama zainab da baba isma'il kuwa, dankuwa hatta gogan naku doctor saida ya dan murmusa dan shima yaji dadin yanda su mama zainab suka sauko daga fushun nasu kan heenduh.
yayinda heenduh kuwa wani farin ciki ne taji ya mamaye mata zuciyar ta najin baban ta ya haqura ya yafe mata gashi harda ma sa mata albarka,, jitai mama itama mama zainab tace "baba yawale bakomai ka'isa garemu ai fiye da komi ma na duniyar nan, dan haka nima d'in nayafe mata saboda kai, amman da sharadin karan kaina ban amunce mata ba dako kwana daya ne wannan shashashan yarinyar ta qara mun a gida ba, ta tashi tabi mijinta can gidan sa, kuma ki bude wadannan kunnuwan naki marassa ji kijini, to fa muddin naji kinyi wani abun wanda zai batawa abokiyan zaman ki rai ko kuma shi khaleepa d'in to Allah kuwa zamu sake gauraya dake ne dan ranki sai yafi nayau 6aci sakaryar yarinya kawai wacce batasan annabi ya faku ba"
murmushi mamn meenat tai tace "ah adaiyi haquri komuda mama ne da baba dahara mu rakata dakin nata, mama zainab tace" wlh kuwa mmn menatu kinji na rantse babu wanda zai rakata,kuma ko wannan dukan danai mata ita tajawa kanta, banso ma na tsaya mata iya haka ba Inda naga alaman rawar kanta bai buyuyuwa da nasiha kad'ai, Inda ko an mata nasihar bata dauka dole sai an had'a da tab'a mata lpian jikanta snn za'a daidaita da'ita yarinyar kawai"
baba yawale yace "kinada iko sosai akan heenduh zainabu dan haka komi kika yanke yayi Allah sa shine mafi a'ala akan tafiyar ta dakin nata yanzun kuma hakan amin,, kama hab'a baba dahara tayi tace "o'oni heenduh kinjawa kanki kinga mamanki ta hana mu rakaki bare na koya miki kwalliyan zamani kina cancarewa,, dariya mgnr baba dahara ta basu dan kuwa sunsan wasa ne kawai baba dahara d'in ke mata dan haka nan take su baba yawale suka dungayiwa heenduh da khaleepa nasiha kan sabuwar rayuwa da zasu fara, sosai nasihan ta dinga ratsa heenduh har batasan wani kukan ya sake kutto mata ba kuwa ta cigaba da yinsa.. daga qarshe suka umarcesa
daya dauki matarsa su tafi Allah basu zaman lpia..... haka su mmn meenat da mmn sales da baba dahara suka rakosu har mota babu wasu kaya dauka dauka wanda ya danganci heenduh Inda daman tun ran safiyan juma'an data gabata aka rigaya aka kai mata kayan nata... dazasu tafi nanma saida baba yawale ya rufe taro da addue dan cika sunnar manzo kan hadusin dayazo yayi mgn da cewa turr da majalisin da'aka zaunasa tundaga farkonsa har qarshensa sannan aka tashi ba'a ambaci Allah ko manzon saba ciki, tofa anyi alla wadai da zaman nan.
suna shafa addua'n ko
a haka heenduh tana kuka su mmn meenat suka fito da'ita daga cikin gidan suka saka ta mota khaleepa yashiga motar shima yaja suka tafi sai bye bye su mmn sales suke musu har suka qule sannan kuma su mmn sales suka dawo suka samu mama zainab nan zaune Inda suka barta,nan suka ci gaba da qara tattaunawa kan batun, yayinda tuni daman baba yawale yawuce shi gida abinsa ransa qar farin ciki naganin cewan yau Allah ya cika masa burinsa da ransa yaga tarewar zaman auran heenduh da khaleepa koba komi ya cika alqawalin daya daukarwa kansa na bayyanuwar gskia kan auran jariran yaran, manya kuma a yanzun, duniya knn komi lokacin sa yake ci, a haka yashiga gidan nasa ya kullo.

su kuma su dady mukhtar suna can zaune cikin sit room d'in baba isma'il suna cin abuncinsu kamar yanda suka saba, zuqatansu fall farin ciki fira kawai suke hankali kwance, sai bayan sun gama ne suka fito itama baba dahara harta yi musu bankwana ta wuce gida zuciyarta cikeda tunano baba yawale kuwa dan zaman da sukai yau tareda shi baqaramin tsaya mata yayi a rai ba, dan haka tana murmushi itama harta shige gidanta ta rufo sa da yake jikokin nan nata sun gama hutunsu sun koma.
dady sales suka shiga motarsa shida mmnsa da mmn meenat suka wuce gida saida suka fara ajiye mmn sannan sukai bankwana suka wuce gida suma can bayan layin su maman knn.. baba isma'il kuwa har qofar gida yaraka yayan nasa snn sukai bankwana shi ya dawo ciki shi kuma dady mukhtar din ya wuce kowa zuqatansu fall farin ciki a wannan dare tunbuna ma mama zainab din da baba isma'il kwanan farin ciki sukai a daren.
khaleepa kuwa tunda aka kawo zarah gidan bai tako qafarsa ba cikinsa ba dan ya fada Mata itama a waya tafiyar tasa Abuja kmr yanda ya fadawa su dady mukhtar da momynsa kuwa sa'ilun da yake cikin tasku kwana biyu da suka wuce, to sai fa yau a rana ta uku da tarewar zarah a gidan yaduro a cikinsa. dakansa yakai heenduh har dakinta tanata kuka kuwa wanda shi harya sare wa rarrashinta kuwa, a haka ya qyaleta snn yasake saukowa qasan falon yasake ganin babu dai kowa dai a cikinsa kamar yanda suka wutosa yanzun, banda qarar esi kota'ina a falon bakkajin motsin komi, dakinsa shima ya wuce yashiga wanka ya fito ya saka jallabiya ya shinfuda sallaya yafara salla.
zarah kuwa tun shugowarsu cikin harabar gidan take tsaye ta saman window d'in tana kallon su,kallon ta ta maida ga heenduh ganin yadda ta qara mata haske da kyau gamida cika tamfar ta manyan yan mata yasata jin wani sabon tsanarta maras algus ya lunku cikin zuciyarta, ranta ya bata babu shakka kuwa tare da ita yayi tafiyar a Abuja Inda gashi sun dawo gida tare.
amman a fili murmushi tai sanda ta tuno kalar tarkon d zasu datsa mata muddin mlm lamma ya dawo kuwa to tabbas tata ta qare saitaga qaryar feleqe da iskanci gamida mannewa miji uwa gum.
ganin sun yo cikin falon gidan wato ta daina ganin su hakan ne yasata komawa bakin gado tana zama kuwa saiga kiran hjy furdausey ya shigo wayar tata, tsoki tai tareda furta "mtssss tsohuwar banza nifa yanzun bakida wani amfani da zaki mun a rayuwa Inda har kin sake kin mallaka min danki dai, tsoki ta qara ja tareda katse wayar kai tsaye ta kirawo mamanta hjy hadeeza, kamar jira take uwar ta dauka nan ko ta fara cewa" momy nifa iskancin nacin da kiran wannan tsohuwar guzumar qawarki da take isana dashi kulluyaumum walailatun yafa fara isana, haba mace sai nacin son da na masifa kullum fa saita tambayeni ya dawo daga tafiyar sa koko? to dan kambu..... cinyesa nace zanyi inya dawo ne? inda abinda take tunani bazai faru tsakanina dashi ba dan yanzun, ni wannan ba damuwa ta bane dan inada madadinsa sama da nawa innaso, haba haka kawai mata ta koma karya uwar d'a"
hjy hadeeza tace "nima naga take taken matsiyaciyar tunda akai auran nan take yawan saka mun ido adud Inda taji nace zanje, to ban sanar mata ba ko tana zargin zamuyiwa danta wani surqullen ne bayan idonta oho" zarah tace bar tsinanniya Allah kuwa in tazo gidan nan ko fuska ta ta gama samu hartagaji tabar zuwa..... hjy hadeeza tace "a'a kada kiyi hakan, ke yarinya ce kinda qarancin tunani, ay bari zamuyi mlm lemma ya dawo mu samu muje tare da ita a gama da matsalar kishiyar nan taki in yaso itama hjy furdauseey d'in sai muje daga baya musa aimata zama daya a tura mata baqin aljani a jikinta yazamana ta ma nakasa takoma battada sauran

wani amfani a rayuwarta wanda a haka zata ita ganin muna juya danta babu abinda zata iya Inda tana zaune waje daya ciwo ya cinyeta, kinga shikenan sai kiyi sabuwar duniyar ki keda mijinki hnkali kwance babu mai sa muku ido"
dariya zarah tasaki harda wani dan ihun murna tace "ihuhu wlh kin kawo shawara momy na dan wlh ga dukkan alama irinnsu hjy furdauseey ne ke da shegen sakawa matayen 'y' yansu idanu a gidansu su rasa saqat inaaaaaaa wlh nikam bazan iyaba momy gwara da zaki mun maganin jarababba wanda har bacin ciki yasa ta hadiye zuciya ta mutu a nakastanta"
"kedai kawai mu'ida jira mlm lamma ya dawo musan abinyi, amman yanxu kada fa ki nuna mata wani abu daya danganci raini mubi a sannu har muyi aikin nan dan in ki kace zaki gwada mata rashin mutuncinki harya fusatata zata iya qin zuwa wajen mlm din damu kuma zatama iya sakawa dan nata ya danqara miki saki kuma kinsan bazai musu ba Inda daman bawai sonki yake ba kin sani kema dan baida yanda zaiyi da iyayen nasa ne yasa ya yardan da auran, dan haka kisan yanda zakiyi mata mgn da fatan dai kin fahimceni ko? "
" inaaa ay kada kiji komi kawai momy na fahimci dukkan ki ay"
hjy hadeeza tace " yawwa kidai kiyaye kamar yanda nace mikin" daga haka ne suka ajiye wayar.
zarah tana ajiye wayar kuwa saiga kiran hjy furdauseey d'in ya sake shugowa wayar tata, figar wayar tai ta daga taqi cewa komi sai hararar wayar take.
hjy furdauseey tace "lpia dai zarah nike ta kiran wayar ki kinqi dagawa qarshema sainaji an katse ta?"
cikin mgnr gadara zarah tace "eh, nayi baquwa ne wayar na hannun 'yarta kuma shiyasa kikaji hakan" Sam hjy furdauseey bataji dadin amsar da zarah ta mayar mata ba amman saita daure tace "daman ba wani abu bane yasa na kira ba nakirawo wayar maitsada ne najita kashe kuma ynxun dadynsa daya shigo gida yake cemun yadawo daga tafiyar dayai to shine nace in yadawo nan gida kice masa inason nagansa dan kwana uku knn rabona dana sakasa cikin idanuna".
tabe baki zarah tayi tareda juyasa tawani hura qofofin hancinan nan nata sama abin ko kyau bai mata ba, snn kai tsaye tace "ban gansa ba, bai shigo ba inya shigo inban manta ba na fada masa dankin sanni da yawan mantuwa,tana gama fadan hakan kuwa bata jira komi ba ta kashe wayar tabar hjy furdauseey dake zaune cikin falon ta dayin sakatoto da baki cikin mmkin zarah wanda tama Gaza gane Inda yarinyar ta dosa,,
a haka tamiqe jiki babu lakka ta koma dakin alhj mukhtar tana masa complain na har yanzu khaleepa bai shigo ya ganta ba anan alhj mukhtar ya nuna mata wataqil koya gaji ne amman yasan zaiyi wuya gobe bai shigo ba, a haka ta kwanta dai zuciyar ta babu dadi ga damuwar son ganin khaleepa ga kuma takaicin zarah.
heenduh kuwa tana ganin futar khaleepa daga dakin nata nan ta wancakalar da gyalenta ta miqe tashiga toilet ta watsa ruwa sbd dud jikanta babu dadi kukan data sha ne har takejin uwa tana masassara ma, nan tayo alwala ta fito tayi sallar ta, tana gamawa ta bude Inda taga kayan ta suke nanta zaqulo wasu riga da wanda na barci tasaka, ta qaro qarfin iskan dakin tareda kashe fitilar dake bed side dinta, tahau gado knn tajawo blanket tana shurin rufe rabin jikanta taji ya turo qofar dakin ya shigo, saurin kwanciya tai tareda lumshe idanunta uwa mai barci kuwa, tsaye yayi yana kallon ta, ahankali ya miqe hannunsa ya kunna hasken dakin wanda nan da nan haske ya gauraya dakin dukkansa.

kusa da gadon ya qarasa yasa hannu ya janye abin rufar tareda dan girgiza kafadunta kadan yana fadin "lollipop ki taso man muje falo inaso na hada kune keda zarah muyi mgn gudun shiga haqqin wata ko?" aiko tanajin hakan wani takaici ya qumeta dan haka tuni ta wartsake daga barcin qaryar tata da takeyi ta miqe zaune ta wasa masa harara tace "na huttassheka basai kasha wahalan mgn ba dan I think bai wuce na rabon girki bako? to kaje na yafe mata kai aje ayita shan amarci lpia" tana gama fadan hakan kuwa tai kwanciyar ta,, wani mummunan 6acin rai mgnr tata ta haddasawa khaleepa, tunda yake da'ita bata ta6a bata masa rai kamar haka ba, wai ita wanne kalar hali ne da'ita? an doketa an mata nasiha da addua amman abin nata ya shallake tunanun mai tunani, dan haka tuni idanunsa suka fara bada kalar ja,,,, daman muddin ransa ya baci haka ne alama atattare dashi, cikin zafin zuciya da fushi ya daka mata wata uwar tsawa da fadin

"keeeeeee??!! nan yasa hannu daya ya ida funcikota daga kwancen da take wanda adai dai nan zarah ta saurin tasowa daga kujerar da take zaune a nan falo sakamakon tsawar da tajiyo daga dakin heenduh d'in,aiko nan take ta'iso saman kofan dakin na heenduh ta lafe ta musu la6e, jitai khaleepa yace "ki shiga hankalinki dani nonsense girl,,, kuma kibar ganin cewa ina shanye dud wani abu da kike mun banson daine kawai ki taso mun da asalin fushi nane b'oyayye , but I can't now,,, kin kaini mature, abinda kika furtan yanzu ya dugunzuma mun zuciya gaba dayaketa,! zakisan kuma kinyiwa d'an halak hakan, kuma abinda kike taqama dashi a jikinki kije ki jiqasu duka ki shanye an haqura dasu dan inada wajen samunsu it's available inaso,,

 mtwww "

yana gama fadan hakan ya turata saman gado ta fad'a akai tanata zazzare idanuwa kuwa, qafarsa ya daura a qarfen gadon ya dan sunkuyo fuskarsa wacce babu annuri ko kadan yanzun a kanta, wanda hakan ba qaramun fad'ar mata da gaba yayi ba kuwa, dan khaleepa kuwa na ainahin taga ya rikid'e ya koma mata sak, wato. marar wasa da fara'a din nan ko kadan, "nidake aga mafashi dan yanzu aka fara wasan!" abinda yace knn ya nufi barin dakin wanda da gudu zarah ta sauko ta koma wajen zaman ta zuciyarta cikeda tunanun tomi heenduh ta guma masa haka da zafi dud yabi ya haukace haka da masifa lokaci daya?." yana barin dakin kuwa heenduh ta fashe da kuka gamida jin haushin kanta na abunda tace masa yanzun kuma gashi yayi fushi ya tafi, wai ita mike damun tane? tambayar da taita yiwa kanta knn kuwa.

khaleepa kuwa yana fitowa falo dudda yaga zarah kuwa amman kuma ko Inda take ma bai sake kallo ba ya fuce da ga gidan yashige motarsa ya kunna, wanda heenduh najin qarar tashin motor tasa kuwa hakan yasa da gudu ta tashi ta bude qofar window tana hangensa harya fuce daga gidan, zubewa tai saman gado tareda dafe kanta tana adduan Allah kare mata shi,,, hawaye suka ci gaba da mata ambaliya a fuska sanda taita kiransa a wayarta amman sam yaqi d'agawa.

shiko koda fitarsa kai tsaye gidansu yaje har hjy furdausey kuwa ta fara bacci ya mata waya sai gata kuwa ta sauko qasan falon ta zauna cikeda farin cikin ganinsa nan tahau cewa "dadynka yake cemun ka dawo kuma naga baka shigo kaga momyn taka ba itama kuma ta ganka ba, shiyasa nakira wayan ka kuma taqi shiga inche dai lpia mai tsada na?" wani dan murmushi yayi kadan wanda baikai har zucci ba sannan yace

"phone d'in ne na barta a motor ne momy shiyasa kuma tana rufe, saurin kauda zancen yayi gamida shafa cikinsa yana motsa fuskarsa yace "momy yunwa nikeji kun rage abinci ne a

gidan?"
dasauri hjy furdausey ta miqe tana fadin"mai tsada na ai ko babu abuncin nan saina dafa Maka kowanne kake da buqatar ci kuwa bare ma akwai, ta so muje kaci gashi can a dining area "a haka yaje ya zauna yafara cin abinci, wanda yaci sa ko sosai ya qoshi wanda ba shine yabar gidan ba sai wajen sha biyu na dare snn yayi bankwana da momyn ya shiga dakinsa ya debo wasu kaya ya saka a but din motarsa ya shiga motor ya kunna tareda barin anguwar,
koda ya dawo gidan dakinsa ya shuge yayi kwanciyar sa baibi ta kan kuwa ba cikinsu.
washe gari da misalin qarfe 11pm ya fito dakinsa sanye cikin qananun kaya wanda suka qara haskasa sosai, kai tsaye kitchen ya nufa, babu zato ya iske heenduh tsaye cikin kitchen d'in tana hada breakfast, tana sanye cikin wata qaramar riga da wando jeans na mata jajaye da surkin fari wanda kayan suka matseta gam gam sunmata kyau matuqar gske kuwa, Snn tayi gammo da gashin ta tuni ta koma uwa yar baby kuwa, tana ganinsa taji gabanta ya wani mummunan bugawa dasauri ta sunne kanta tareda furta "ina kwana doctor?" acan qasan ma qoshi tayi mgnr, sarai ya jita kuma tasan yaji d'in amman saiyayi burus da'ita ya nufi Inda yaga ctl yayi sa'a akwai ruwan zafi kuwa a cikinsa, nan ya dauko cup yana qoqarin hadawa da kansa knn tayi saurin qarasowa gabansa taja ta tsaya tana kallon sa tace "gafa breakfast nan ina shirya maka..... wani kallo taga ya jefeta dashi fuskarsa a tamqe ya watsa mata harara gamida tabe lips yace
"nop, bani buqatar hakan daga gareki kibari wacce kika barwani tai mun hakan OK? "zuba masa idanuwa kawai tayi tana kallo jikinta a sanyaye,,, tsulum saiga zarah ta shigo cikin kitchen d'in cikin kayan barci ga alama tashin ta knn ko wanka batai ba gashin dokin nan dake kanta dud ya gargitse kuwa, tana ganin khaleepa tasaki wani murmushi danta qunsawa heenduh takaici kawai ta nufi khaleepa ta wani shige qirjinsa ta rungumesa tana kwarkwasa gamida shafa sajen fuskarsa tace "Haney na naga kana qoqarin hada cooffe ka bari na hada maka man, dudda khaleepa yanajin tsamin bakin zarah a hancinsa sanda take masa wannan mgnr amman dan kawai ya quntatawa heenduh taji itama Inda dadi kawai saiya ida zagaya hannuwansa ya rungumota jikinsa ya hada goshinsu waje daya yana kallon ta yana qaqaro murmushi,
wanda zarah kuwa jinta datai a cikin jikin wanda take mafarkin samu ne yasata jin wani mugun dadi a ranta tuni ta manta a Inda take kuwa sakamakon qanshin nan nasa daya baibaiyeta.
runtse idanunta heenduh tai da qarfi tareda runtse wuqar dake hannunta a cikin tafin hannunta wanda hakan yasa tasaki wata 'yar qara sakamakon yankewa da tayi da wuqar kad'an... dasauri suka kallo ta kuwa, tsoki yaja ya janye daga jikin zarah yace cikin murnushin mugunta wa heenduh "swt zarah soya mun indomie da qwai ki hadomin da tea ina falo please quick zan fita ne ynxun"
dasauri zarah ta amsa da "to honey an gama"
daga haka ya fuce abinsa.
yana fita kuwa zarah ta kama yin wata miqa tana fadin" hmnn ina ruwan Haney na, dud yabi ya gajiyar dani a daren jia da zaqinsa marar qosarwa,, hmmn gskia nayi dace da samun gwarzon mazaje namiji tamfar da dubu maqi gani kam saidai su kauda ido,, ahayye nanaye garin dad'i ashe dai yana nesa inji 6arawon zuma,, tana mgnr tana hada kayan girkin, dagowa zarah tai ta dubi heenduh datake nad'e hannunta da tissue nan ta tabe baki tafara aikinta.
kukan zucci kawai heenduh takeyi tana cigaba da dana sani a ranta yanzu gashi wannan

figaggiyar zarah ta gano basu shiri itakam ta shiga ukunta, haka ta daure taci gaba da aikin wanke kayan datai amfani dasu ba tareda tabawa zarah damar fahimtar damuwarta taba gudun kada taga wallenta ta raina mata class... gani tai zarah ta kwashi kayan girkin nata data gama hadawa tabar kitchen d'in tana tuntsura mata dariya gamida rera waqar"ahayye wata tafi wata,,, ahayye koni nafi..... tana fita kuwa hawaye suka dinga zubowa heenduh wanda daqyar ta samu ta tsaidasu, nan taji kwata kwata breakfast d'in data hada ma yafita ranta nanta barsa ta futo falo nan ma tasake cin Karo da wani kayan takaicin, dan zarah ce tagani zaune gandan gandan saman cinyar doctor tana basa breakfast d'in a baki,, dauke fuskarta tayi sanda suka hada ido dashi tayi saurin hayewa dakinta ta zube saman gado tana sharar qwalla.
wasa wasa yau kwana uku knn babu abinda zarah da doctor suke qunsa mata bayan kayan takaici muddin yana gida to zataita ganinsu a falo tare jikin juna, dan ta lura zarah dinma tafi rawar jikin shige masa akanshi muskilin naku.
wanda a 6angaren zarah kuwa tayi mamakin yanda khaleepa ke riritata a falo in suna tare musamman ma inya lura heenduh na wajen, dud girman tannan da qibarta har goyata yake suna wasa da dariya amman da zarar tashiga dakinsa zataga babu fuska kwata kwata uwa bashi ba, ko jikinta bai marmarin tabawa bare ma, itako takan tabe baki tace "haka nakeso ay daman kayi komi guy lokacin ka ne, nima nawa tym d'in zaizo very soon, takan bar masa dakin nasa kuwa tunbuna intaga yana harare harare gamida daure rai har tsorata takeyi.
yauma kamar kullum da qarfe 6:11pm na marece zarah ta ciwo wata kwalliya da wasu qananun kaya, mini skirt da riga uryatan, pimples d'in bleaching dud sun cike mata fuska, breast sunbi sun kwanta talauu wanda rufun asirinta bra d'in da take sawa mai soso itake taso mata da kwantaccen gaban nata, cikin taku ta iso nan falo Inda khaleepa ke zaune saman carpet ya tasa laptop dinsa gaba yana aika wani saqo a ciki...
zama tayi gefen a kafafunsa tana shirin mgn knn saiga heenduh tana saukowa daga samanta cikin shigarta ta dogon wando pencil roba da kuma wata 'yar half best wacce hatta rabin dukiyar fulaninta ana ganinsu waje,
dud yanda tayi takunta saisun girgiza kuwa suna rawa sakamakon bra d'in da bata saka musu ba,
daga khaleepa har zarah qarar hl-shoes dinta da turaren jikinta sune suka ja hankulansu gareta, kasa janye idanunsa khaleepa yayi daga kanta gaba daya, dan jiyai tana shirin burkita masa brain har yana shirin manta abunda yakeyi kuwa cikin laptop d'in nasan,
a hankali ya dauke idanunsa ya maida a laptop d'in ya ida tura saqon amman kuma yaqi sake duban Inda heenduhn take saima wata foledr daya bude ta pictures d'in gidaje yana dubawa one by one ta hanyar using dayakeyi da hannunsa Saman tamfurin d'in laptop d'in. tsoki zarah tayi tawani bata fuska dan taji haushin shigar da heenduhn tayi shegiyar yarinya sai masifafen kyau uwa ita ta zabawa kanta sura dubi yanda take neman janye masa hankali dudda tasan ba shiri suke ba da junansu,abinda zarah ke cewa knn a ranta. yayinda sarai heenduh ta lura da kallon da khaleepa yai mata, hakama ta lura da bacin ran zarah dan haka murmushi ta saki a ranta take furta cewa " hmnn zarah knn kin dauka ke daya ne kika iya salon duniyanci wajen janye hankalin miji? to kuwa kinyi kadan, dan nima macece, nagama jurar dud wani iskancinki a gidan nan na salon bariki, ni dake aga wanda zaiyi nasara a garesa,,, ahaka ta qaro so gabansu cikin tafiyar yanga babu bata lokaci tayi masauki saman kafafunsa dake mimmiqe a carpet d'in, dasauri zarah ta kalleta sannan ta juya ta kalli khaleepa d'in daya dago shima ya sake zubawa

heenduhn idanunsa kawai yana kallon yanda take sakar masa wani tattausan murmushin ta... daure fuskarsa yayi tamau yana qoqarin tureta nanko tayi saurin riqesa ta marairaice murya kai a langabe tana turo masa qirjinta datasan sune burinsa, nan ta fara cewa "please and please doctor I want to talk with you, inason yin magana dakai please" sake hade girar sama data qasa yayi kan ya ce wani abu zarah tai zuruf tace "kamarya kina son mgn dashi kuma? saiki bari in rigaki fadin tawa buqatar dan nima ina da'ita.... kallon ta kawai heenduh tai a banzance batace mata komi ba tadai qara kallon khaleepa dake kallon fuskarta, a marairaice" Please doctor na mgnr tanada girma.. nanma zarah ta dubesa cikin murya a sama dan bata iya tsaranta mgn ba lab lab ba, tace "honey ka manta ne yau ne zamuje gidan mu..." ya isa zarah bari na fara jin uzurinta snn, Inda tarigaki fad'an hakan,, abinda khaleepa yace knn bayan janye idanunsa dayai daga heenduh ya maidasu ga ita zaran, turo baki tayi tace "haba hany yaufa ne nace mak... zarah stop it, isay gate out from here pleases,, in yaso kya fadi naki uzurin inta gama fadan nata because I hate argument in between OK? jeki kawai,, haka zarah ta miqe jiki ba qwari ta hau samanta tana waiwayensu zuciyarta cikeda takaicin kunyar daya bata yau kam, koda ta shiga dakin labewa tai tana hangosu,,, saidai kashh!! batajin abinda suke fada amman ahaka ta tsaya ta zura musu 👁️👁️.
zarah na barin wajen ya juyo yana kallon ta da wannan d'aurarriyar fuskar tasa yayi mata alama da 'ido data fad'i uzurin nata yaji,,,
heenduh ko dud saitabi ta dabarce takasa nutsuwa banda fadin "ammmmmman.... ,,,,innnnnnn,,,,, bata iya furta komi,, zamewa tayi ta koma gefe jikinsa ta shige ta daura hannunta saman laptop dinsa itama tana kallon fictures d'in,,hakanne yasa zara barin inda take da sauri dan takaici.
" bakida abinda zaki ce ne dan inada abinyi OK? "
shiru tai kawai tama miqe zaune tana kallon sa idanunta sunyi narai narai zuciyarta cikeda nadamar abunda tayi masa, so take ta basa haquri amman ta rasa ta'inda zata fara mgnr ma,,, babu zato taga ya miqe tsaye ya kwashe laptop d'insa zaibar wajen aiko da sauri tasha gabansa cikin rawar murya tace "yayana dan Allah kayi haquri da abinda na maka ka yafemun natuba nabi Allah da manzonsa nabika ka ya haquri ka yafemun please.... tayi mgnr hawaye sun cicciko mata,,,
gani tayi yayi mata wani wulaqantaccen kallo ya tabe baki gamida yamutsa fuskarsa tareda jan wani dogon tsoki yayi wucewarsa yahaye samansa,, Allah sarki da gudu ta bisa tana zubda hawaye,,,,, sai dai inaaa kan takai Inda yake harya shige dakinsa ya ida datse qofar sa ya rufe harda murza mata key a jiki.
nanko ta sulale wajen ta zauna tareda had'a kai da gwiwa tana cigaba da sakin wani sabon kukan marar yankewa,,,,,,,,...

by
Xexen Fasaha
[4/18, 11:06 PM] Xainab Documen: 👁️👁️

DA SAURAN KALLO.

story and writing
by
Xayyneb 💤💤

~dedicated to my mom sadeeq hauwas~°

"RANAR KUKE JIRA YAU GATA TAZO.....!!!
(inji wani mawaq'i)"

J a khaleepa yayi ya tsaya adai dai bakin qofar shiga falon gidan sakamon tunowa dayai ya manto da gift d'in da yunus ya siyo ya basa yace yabawa madam heenduh kyautar bikinsu, kuma gashi ya barosa a cikin motorsa, jiyai yunus yace "yadai mlm naga kaja ka tsaya mana a hanya uwa an d'aureka a wajen? in bazaka wuce ba ni kaban hanyar na wuce, dan wannan qamshin girkin yamun kama dana headac..... dafe baki yai ganin khaleepa ya juyo yana watsa masa harara, cikin dariya yunus yace "au sorry na manta ne oga, ina son nace queen heenduh neh fa wai, wannan qamshin girkin nasan kalar nata ne dan kuwa na san qamshin girkinta tun tana gida,,, wlh kuwa friend miyau na harya fara tsinkewa ma in gaya maka mafa, please let's go man" hararsa khaleepa yayi sannan ya d'an saki murmushi tareda fadin "kaidai ka sani da tarin kayan kwad'anka,
ni kaida lollipop d'in ma ta fannin kwad'ai da maqulashe bansan gwani ba"
yayi mgnr yana mai niyyar komawa da baya.
dariya yunus yayi yace
"eh munji dai bakomai mlm, bin khaleepa yayi da kallo ganin ya juya yana tafiya hakan yasa shi cewa "a'a yaya zaka fita ne ka barni kuma anan?"
cikin nisa daga wajen da khaleepa ya farayi dan kuwa har yayi kusa ma da isa bakin motor, to jin abinda yunus yacen ne yasashi d'an waiwayowa yace "shiga ciki ka jirani a falo, gift d'in nan naka zan dauko danna baiwa maishi abinsa"
yunus yace "OK shikenan to"
kai tsaye kuwa yunus ya d'aga qafarsa ta dama ya kutsa kansa @ cikin falon gidan tareda sallamarsa da fadin cewa"Assalamu alaikum masu gida gamu mun qara so cikin yardar Allah" yana gama fadan hakan yasa qafarsa ya ida tsallakowa ya shigo falon gidan.....!!!!! (faqat) wanda adaidai wannan lokacin ne hjy hadeeza dake zaune kusada hjy furdauseey anan gidan alhj mukhtar d'in, dan daman tana gidan tunda suka dawo, dan cewa tayi bazata bar gidan ba har sai sunji waya daga zarah in khaleepa ya dawo ya tsallako domin shigowa gidan snn hankalinsu zai kwantan.
aiko dai dai sanda yunus ya shigo falon ai anan take daga hjy furdauseey har hjy hadeeza suka kwarwatsa wani uba uban ihun suka mimmiqe tsaye suna billayi tareda qanqame jikunnansu wanda sukeji uwa ana galgala musu zazzafan garwashin wuta a kota 'ina a cikin jikinsu kuwa, gwara kawunansu suka dinga yi a bango suna ihu gamida cizgar gashi kansu suna kuka dan hankalinsu kuwa qoqarin gushewa yakeyi kwata kwata daga cikin jikinsu,,, da gudu dady mukhtar yasauko qasa jin wannan ihun, da yake yana cikin bedroom dinsa gama wankansa knn

da shiryawarsa yana qoqarin futowa zuwa gidan qanen nasa cin girkin dare kmr yanda suka saba kuwa dayin hkn tun shiryawarsu,,,yana saukowa qasa kuwa abinda yagani ne na faruwa dasu hjy hadeeza ba qaramin tayar masa da hankali yayiba, musamman dayaga yanda suka cumamiyi junansu suna dukan fusakokinsu jini na futowa ta baki ta hanci gamida turawa junansu mummunan zagi na batsa na wulaqanci gamida aibata juna,,,
a rud'e yake cewa "kai subhanillah hjy Mike damunku haka da girmanku kuna abu na qananun yara marassa hankali?? babu wanda ya kulasa a cikin su dan basu sanma yanayi ba, kasa rabasu yayi dan haka jiki na rawa ya fito ya shedawa baba musa mai gadi yaje da marmaza ya kirawo masa baba isma'il da baba yawale gamida dady sales yanzu nan, dasauri kuwa baba musa ya fita shima a rud'e dan halin dayaga dady mukhtar kuwa a ciki yasa babu lpia yau a gidan kam, ai baba musa na barin wajen saiko dady mukhtar yaga da gudu su hjy furdauseey da hjy hadeeza sun sheqo sun fito daga gidan da gudu suna niyyar fucewa,, da gudun gaske kuwa dady mukhtar yaje ya rufe qofar da sarqa, suna isowa kuwa suka yi wani mummunan Karo da qofar, tuni fuskokinsu suka qara fashewa kuwa, amman Sam basu haqura da son fita gidan ba haka suka dinga d'alewa saman jikin gate d'in gidan uwa qadangaru, saidai tsawon gate d'in da sulb'insa ya dinga fyad'eso qasa kuma basu daddara ba nan take zasu koma,, shiko dady mukhtar tagumi yayi daga tsaye yana kallon su, dan zuwa yanzu kam ya shaida dutta qare su hjy hadeeza gamdakar sukai da baqaqen aljannu marassa imani masu kasar juna.....
a kuma can dakin zarah itama daidai sanda yunus ya shigo falon gidan ai nan take ta duqe qasa tana kwarara ihun, kankace mi tuni tayo qasan falon da gudu wanda heenduh dake shirin saukowa qasa tajiyo wannan ihun daga dakinta, wanda hakan yasa ta ida fitowa da sauri, hatta yunus ya furgita da ganin zarah yanda ta sauko qasa a guje,, tuni ta nufi kofa tareda bangaje khaleepa daya shigo falon a lokacin har yana watsar da gift d'in dayake riqe a hannunsa kuwa,, a rud'e suka biyota ganin yanda take ihun kankace me harta bud'e qofar gate d'in gidan ta fuce tahau titi tanata falfala gudu, da wani mugun sauri kuwa khaleepa da yunus suka shiga mota sukabita,,,yayinda suka bar heenduh nan tsaye hankalinta a matuqar tashe,,,,.
daqyar suka cimmata suka kamota suka sata a motar, ganin yanda take fuzge fuzge abun sai qara tuburewa yake hakan yasa khaleepa yanufi gidansu kai tsaye,, yana shiga anguwar kuwa yaci Karo da alhj Bala, dasauri ya kashe motor daidai gate din gidansu yaje Inda alhj Bala d'in yake tsaye sun gama gaisawa da abokinsa yana qoqarin wucewa gida shima,, khaleepa yayi qarfin halin sheda WA alhj Bala abinda ke faruwa da zarah wacce ke cikin mota tana sakin qara, dud ta fashe masa glass na mota kuwa hannuwanta sai jini sukeyi,, dasauri alhj Bala suka kamota suka fiddota a motor, alhj Bala ganin dayai gidansu khaleepa d'in yafi kurkusa yasa shi umartar khaleepa da su shiga gidan kawai da'ita Inda dud gida ne kuma, ahaka sukai mata talla talla suka shiga ciki da ita, dan sauqinsu ma dare ne babu mutane sosai a wajajen, kwata kwata kasa binsu ciki yunus yayi dan gani yake wannan personal life dunsu ne, kuma komi na buqatar sirri shiyasa kawai ya musu fatan
 alheri yajuya motor khaleepa d'in ya wuce da'ita gida.
wani tashin hankalin khaleepa da alhj Bala suka risqa sadda suka shigo harabar gate d'in gidan suka samu su hjy furdauseey zube a qasa suna billayi uwa macizzai wanda da qarfin gaske zarah ta qwace kanta daga wajen su khaleepa da alhj Bala dasuketa rirriqe da'ita , da gudu tayi sukuwa ta fada jikin iyayen nata, tuni suka kacame da fad'a suna yagin juna uwa mayunwatan

zakuna giggan ma juwa, kankace MI tuni sun qara 6ata jikinsu sunyiwa junansu jina jina wanda dasauri khaleepa ya'isa gaban mahaifinsa dake tsaye har lokacin yagaza mgn, nan ya riqesa hankali tashe yace "dady miya faru ne dasu momy suke wann... shugowar baba isma'il ne da baba yawale gamida dady salis harda ma mama zainab, dan da baba musa yaje gidan cewa yai kowa yazo inji alhj sbd gigita dayayi shima, to ganin su yasa khaleepa yin shiru yakasa ci gaba da mgnr, banda ma bugawa babu abinda zuciyarsa ke masa... su kansu su baba isma'il dasukaga halin da su hjy furdauseyy suke ciki saida suka d'umauta,,
daqyar dady mukhtar yaja su baba isma'il da nufin kamo hjy furdauseyy datayi nasarar d'alewa takai qarshe gate d'in tana niyyar durewa qasa dudda mummunan tsawon gate d'in kuwa amman bata kula ba, dan ita dai burinta kawai ta haura, banda bugawa fattt!! fattt!! babu abinda zuciyar khaleepa take sakeyi,, dasauri ya matsa ya kama gate din yana hawa ganin dayayi takusan sulalawa gasu dady sun kasa cimmata,, yana gab da'isa Inda take kuwa cikin ikon Allah sukaga kamar anyi sama sama da'ita an fyad'ota qasa jikake timmmmmm nan take qafafunta suka karairaye da hannuwanta sai gulu gulu suke suna yawo gamida zubar jini,, dasauri sukazo kanta dan har ta sume sbd tsananin azaba,, kuka khaleepa yake sanda ya durqushe gaban uwar yakasa furta komi sai faman girgiza uwar yake,,,,, daqyar su ka samu sukai musu talla talla suka shigar dasu cikin gidan anan falo wanda hjy hadiza da 'yarta zarah suketa sakin ihun kuka har lokacin suna fuzgar gashin kansu tareda dukan jikinsu suna yagansa da haqora wanda nan take suka sake yiwa jikinsu kaca kaca da jini,,, yayinda hjy furdauseyy ke a sume har lokacin.
dasauri baba yawale ya umarci khaleepa dayaje ya kawo masa ruwa cikin kwano, nan da nan da gudu kuwa khaleepa yaje ya kawo masa ruwan, baba yawale ya kar6a yadunga adduo'e a cikin kwanon ruwan yana tofawa yana gamawa kuwa ya miqe tsaye yawatsa masu hjy haddeza ruwan a jiki su dukknsu harda hjy furdauseyy da ta farfad'o lokacin, jin saukar ruwan adduo'e in nan a jikinsu kamar Ana babbaka su sukaji, nan take suka qara qwalla wani uban ihun suka zube wajen babu wacce ke motsi a cikinsu sama da daqiqa goma sha kuwa, banda sauke numfashin azaba babu abinda sukeyi,, zuwa can suka miqe zaune suka dinga bin jama'ar wajen da kallo (daya daga qa'idar sihirin nan da mlm lamma ya basu shine muddin akayi ba daidai ba tofa bala'oen nau'in azabobi ne gamida tonon asiri zasuyi tasiri ga wanda sukai abin ba daidai ba) mafarin knn hjy haddeza na d'aura idanunta kan alhj Bala mijinta nan take ta fashe da kuka tana fadin "alhj Bala ka yafemun bisa kalar mummunan cutarwar danai maka a rayuwa, ta hanyar bin malamai da na dungayi da 'yan tsubbu dud a kanka, wanda hakan harta kaini ga rabaka da' yan uwanka, kuma nai maka asirin da kaji kaqi jinunsu, snn kuma nice nayi asiri dahar na mallakeka, wanda komi nace kamin baka musu da rawar jiki kake mun shi, wanda ahaka wajen bin malamai na harna samu wani malamin tsubbu waishi mlm lamma yanaciga ba damun aiki a kanka kuma muna harkar alfasha dashi wanda ahaka ne har na samu cikin zarah dashi, sanin danai cewa kana son haihuwa ido rufe a lokacin shiyasa na fad'a maka ina dauke da cikin zarah a lokacin, wanda kai kuma kayi tunanin cikin Kane, shine a lokacin kuma mlm lamma yaqara mun wani aiki wanda saida aka yanka saniya goma, jar akuya goma, bunsuru biyar shima, Snn akayi aikin wanda aikin anyisa ne Dan dud wata qaddarar taka na gajeta na mallake ta, kuma hakan akayi,, kuma musabbabin abinda yaje famu cikin wannan tashin hankalin ayau bakomai bane face kai heenduh da iyayenta da kuma dud wani wanda keda saka hannunsa a lamarin auranta da khaleepa da'a kaudasa, haka muka fadawa mlm lamma kuma

ya'amunce yabamu magani da gargadin cewa kada a samu kurkure wajen aiki da maganin dan indai aka samu akasi khaleepa bai qetare maganin ba har wani ya qetara to zamu shiga taskun bala'e da musifa kamar yanda shi mlm d'in ya fada,, to munsan tabbas zarah tasaka maganin a ba daidai ba shiyasa hakan ta faru damu, Dan Allah alhj ku yafe mana koma samu sa'ida a jikinmu dan munsan alhakinku ne ke bibiyar mu..wayyo Allah,, suka sake fasa wani ihun nan take"
alhj Bala da tun sanda yaji hjy hadiza na wannan maganganun jikinsa yadunga rawa da karkarwar cin amanar da hjy hadiza tai masa a rayuwa, amman shine dan bata da kunya take neman gafararsa,,,, aida gudu sukaga alhj Bala ya fuzgo hjy hadeeza yadunga bugata da bango yana nanata da qasa tana ihun neman
ceto, wanda nanma zarah ta miqe babu zato sukaga taje gaban uwar ta danneta tareda shaqota daga kwancen da alhj Bala ya kaita wanda daqyar su dady mukhtar suka janyesa dan makasarta kawai sukaga yana bid'a .
zarah maye gurbin alhj Bala tayi ta sake shaqe uwar tana kuka take cewa "kincuceni kin batan rayuwa, ashe dama ni ba 'yar dady bace shegiya ce? wlh to nice ajalinku daga ke har tsinannen bokan mahaifin nawa dakikayo cikina wajensa,,, ganin da sukai tana niyyar qarasa uwar da shaqar mata maqoshi datai ne da zaqa zaqan akaifanta dahar tafara fasawa uwar wuyanta dasu, hakan ne yasa su dady sales saurin janye zarah daga jikin uwar tata wacce idanuwan hjy hadeeza sunfito luhu luhu tana tari tul tul tul na azababban zafin dake ratsata kota 'ina a jikinta kuwa,,,, zarah ko sai kuka take tana darjewa da cewa ita a suketa saitaga bayan uwar,,, hjy furdauseyy kuwa dud abinnan da akeyi ta makure kanta waje daya tana kuka sbd yanda takejin cikinta kamar ana faffaska mata 'yan hanji ana karkatsesu,, gashi ko motsi ta kasayi sbd jikanta babu Inda babu karaya a cikinsa,jiyowa sukai hjy furdausey na cewa daqyar cikin kuka "toke hjy hadeeza mima kika aikata? komi kika aikata bai kamo koda qafa qafar nawa wajen muni ba, nida har kisa saida na aikata..... laifuka munana babu wanda ban aikata ba, babu shakka inaji a jikina babu ni ba samun rahman ubangiji Allah domin wadanda na zalinta basu duniyar ma gaba daya,, wayyo kaicona ni furdauseey, nasani babu wanda ya jefani a wannan mummunan hanyar bayaga mahaifiyata kanta rasu,, ina roqon mata Allah daya qara mata nauyin qasa..... fashewa tai da kuka wiwi takasa ma cigaba da mgnr.
dasauri baba yawale yace"kashh subhanillah,,, furdausey ai komi mahaifiyarki ta aikata baici kimata wannan mummunan fatan ba ay, cikin kuka sosai hjy fursausey tace "nayi mata d'in yawale,, narantse da Allah bazan mata addua ba, Dan bata cancanceta ba, baka san abinda tayi a duniyar taba ne shiyasa kake cewa na daina mata wannan fatan,,,, kamar abin hauka sai kawai sukaga kukan hjy fursausey ya koma wata mahaukaciyar dariya, dariya take sosai kalar ta fitar imanin nan kuwa, nan take kuwa cikin haukar dariyar tata tahau watsa musu jimammen boyayyen sirrinta na munanan gsken kuwa, tundaga farkon zuwansu wajen marakusa itada uwarta sbd raba mukhtar da kowa nasa har kawo kisan da taiwa su baffa da inno ta hanyar guba data saka musu a abunci har kawo dai yau da dubunsu ta cika, tana gama fadan hakan tasake sakin ihun sbd yanda taji ciwukan jikanta ke mata wani mummunan addababben zunga da rad'ad'i.
daga baffa dake babbansu a wajen har kawo khaleepa dake qaraminsu Suman wucin gadi sukai dan tsakanin mamakin daya kashe su najin abinda hjy fusrdaseey ta gama furtawa,, su daga kan daddy mukhtar har kawo baba isma'il da baba yawale babu abinda sukafi jin shigarsa

jikinsu fiyeda yanda ta furta kisan su baffa, babu wanda ya ankara da ganin tashin dady mukhtar saidai ganin sa sukai ya dawo da wata sharbebiyar wuqa ya nufo hjy furdausey da'ita a guje,,,,, wani mugun ihun hjy fursausey ta saki dan ita kadai taga ya nufo da wuqar tsirara, tabbas tasan tata tazo qarshe yau dan abinda ta jima tanata shukuwa shine yake tanbayar ta yau haiqan,, gashi bazata iya ko motsawa daga Inda take ba bare ta samu matsera, dasauri su dady sales da baba yawale gamida khaleepa suka daddafe dady mukhtar din da jikinsa ke ciri yana fidda gumi gamida zubar da hawaye sharr sharrr,,, kamar yaro dady mukhtar ya dinga kuka riris yana fadin
"innalillahee wainnailaihirraji'un,, haqiqa kin cuci rayuwa ta furdausey,kinmin tabon dabazai taba gogewa ba a zuciya, kin rabani da dan uwa na na tsawon shekaru amman dud wannan bai miki ba saida kika dan gana da kashe mun iyayena ta hanyar zuba musu guba a cikin abinci... wani kuka ya fashe dashi tareda isa gaban baba isma'il ya riqesa da qarfi yana cigaba da kuka uwa lokacin yaji mutuwar nahaifansu, dan abun sabo fil ya zo musu,dan shima baba isma'il banda kukan babu abinda yake cuzga,,, hakama mama zainab data tuno zaman dad'in da sukai dasu inno,,, cikin rawar murya dady mukhtar yake cewa "wlh qanena bazan taba yafe haqqin su baffa fa koda dukiya ta zata qare gaba daya sainaga an zartarwa da furdausey hukuncin kisa itama sannan hankalina zai kwanta,, bazan yafe miki ba fursausey dan haka mataki na farko dazan dauka a kanki shine kije na sakeki saki uku...."!!!
ai wani kuka mai qarar gske hjy furdausey tasaki tareda fadin " tashiga ukkunta ta lalace, Allah tofin Allah wadai da rayuwarta,, haka take fad'a.
tuni khaleepa ya duqe qasa tareda dafe kansa yana kuka sosai, ko a mafarki bai taba tunanin mahaifiyarsa ce keda wannan munanan halayen ba, gaba daya jiyai duniyar tayi masa mummunan duhu,, banda dokawa babu abinda zuciyar sa ke ya matuqa gaya a lokacin jiyake kmr zaibar duniya ne sbd tsantsan tashin hankali .... wani qatuwar murya suka juyo awaje tareda bankado gate din gidan an shigo,,, kamun suyi wani motsi sai ganin mlm lamma sukayi dudus ya fado falon daga shi sai dan tohi a jikinsa,, hjy hadeeza na ganinsa tuni haukan ta yaqara tuburewa ta miqe tsaye tana qyalqyata dariya tana nuna mlm lamma tana cewa "hhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhhh zarah ga ubanki nan yazo zai tafi dake wajensa,,, katsewa mgnr tata tayi babu shuri, sanda taji mlm lamma d'in ya kwatsatsa wani uban ihun tareda Buda hannuwansa sama yana fadin"dan tsito ka sauqaqamun wannan bala'en da kk mun a jiki,,, waiiiii huhuhuhu waiiiii huhuhuhu, tuni sukaga an daga mlm lamma an bugasa da qasa tareda curesa aka kanannad'esa waje guda jini na fito masa ta baka ta hanci ta kunne, dan wannan faduwan da baqaqen aljannun sukai dashi qasa harsun fasa masa qwalwan kai,,,,
kowa ja da baya yayi a wajen ganin yanda wuta ta fara cin jikin mlm lamma,, da gudu sukaga mlm lamma ya miqe yana qwala ihu yake cewa "narantse da ubangiji Allah mai gaskiya bazan mutu a wukaqance nid'ai ba,,, babu zato kawai sukaga ya kwashi hjy hadeeza da zarah yafuce waje dasu a kafada a guje kuwa,suko ihu kawai suke suna neman barin jikinsa amman yariqesu gammm kmr danko,
da yake mlm lamma sangama sangaman mutanen nan ne,, to ganin haka yasa su dady mukhtar suka yo waje da gudu suka biyo su,, saidai ina gudu ba daya ba bare gudu kalar na turin iska, shiyasa nan da nan kankace qyat har mlm lamma yayi wankan tsarki ya afka dasu hjy hadeeza da zarah dashi kansa zuwa wata tsohuwar rijiya mai zurfin gaske dake can tsakiyar anguwar tasu dady mukhtar, wacce babu komi a rijiyar face gama gaman duwatsu dake cikinta,

dudda an rufe rijiyar ne da wani qarfe amman zuwan mlm lamma d'in duka daya da yayi mata da qafa yasa murfun ya 6alle har sukayi nasarar ruftawa ciki, wanda qara daya su hjy hadeeza da zarah dashi mlm lamma d'in sukai a cikin rijiyar basu qara wata ba,
tuni mutane suka fara taruwa a wajen ana salati,, dady sales ne yayi qoqarin fiddo wayarsa nan take ya kira fire service, 'yan kwana kwana,, babu bata lokaci kuwa saiga motor 🚑 ambulance ta' yan kwana kwanan ta shigo anguwar a guje tana jiniya,, kankace MI har an saka qugiya da fitilu an shiga an fiddosu dukknsu an kwantar nan qasa, gaba daya jikinsu ya ratattake har kwakwalan kansu sun zazzalo waje,, rai kuwa baqon duniya tuni yayi hijira daga jikinsu su ukun mlm lamma da zarah da uwarta hjy hadeeza, ganin wannan tashin hankalin ne na ganin yanda gawarwakin su hjy hadeeza cakud'e waje daya uwa sunyi hatsari mota ta murjesu ko fuskokinsu ba'a ganewa kuwa sun daddame, jini sai malala yake wajen, hakan ne yasa wasu daga cikin mutanen wajen suka dinga yanke jiki suna fad'uwa qasa a sume sbd tsabar furguci da tsoron ubangiji Allah dake qara ratsa zuqatan su.
yayinda wasu daga cikin mutanen kuma suka dinga guduwa sbd gigicewa..
ganin babu yanda za'ayi a kwashe su daga wajen ba tareda anbar wani 6angare ba na jikinsu yasa cikin dauriya baba yawale da sauran tsiraran mutanen wajen suka hada gawarwakin namomun su hjy hadeeza suka tattara waje daya sukai alwala, nan take sukai musu salla sannan aka haqa rami mai zurfi a wajen aka zubasu tareda maida qasa aka rufe su ruf iyakar ta tasu knn.
abinda yabawa mutane mamaki shine yanda qiri qiri alhj Bala yaqi shiga sallatar gawarwakin kuwa,,, haka dai kowa ya kama gabnsa suna mgn wacce ba'a rasa ba ga mutane ta cancanin miye musabbabun mutuwar tasu ma haka katsam.
su khaleepa wajen hjy furdausey suka koma, khaleepa na kuka yake fada Mata mutuwar su hjy hadeeza, ai tuni hjy furdausey taqara zarewa babu arziqi khaleepa da dady sales da baba yawale suka nufi asibitin su khaleepa da'ita dan qiri qiri kuwa dady mukhtar ya hanasu baba isma'il binsu shima yaqi zuwa kuma, Dan a duniya bayada maqiyi babban gske na bugawa a mujalla daya wuce hjy furdausey haka yakeji a ransa, dankuwa ko sunanta yatsani yaji bare ya tuna da sunyi wata rayuwa ma a baya.
koda khaleepa suka shigar da hjy furdausey emergency nan suka kwantar da'ita saman gado, wanda kusa da gadon nata harda wani crista shima yana kwance galabaice ba lpia.. tashin farko khaleepa daya fara buncike yaga dole sai an yankewa hjy furdausey qafafunta 2 da kuma hannuwanta dukknsu Snn zata samu nutsuwa sbd sugar din ta.
Dan haka yana kuka ya sanar WA su dady sales, to babu yanda suka iya haka suka yita tausar khaleepa d'in dayayi hakan kodan nema mata sauqi kuwa dan ihun kukanta kadai da takeyi gamida yagar naman jikinta d'anye tanaci ya'isa ya qara tada musu hankali, dole tasa khaleepa yayi mata allurar barci tareda Sanyo kayan aiki ya dawo yafara aikin cire mata qafafunta yana kuka riris, saida yagama tsab wajen qarfe uku na dare sannan yasa bandage ya nad'e wuraran tsab sannan yayi saurin komawa wajen su dady sales ya zube jikinsu yana kuka sosai gwanin tausayi,, sosai suka dinga rarrashinsa wanda daga qarshe suna nan wajen akayi kiran sallar asuba, daqyar sukayo salla a cikin masallacin sai wajen bakwai na safiyar ranar ne Snn suka baro masallacin, suka shigo room d'in da hjy furdausey take kwance wanda suna shigowa tana farkowa,, ganin datai jikinta ya koma dungu kawai ta fashe da kukan nadama na abinda ta aikata a rayuwarta kan kace MI tuni idanunta sun kakkafe tana kyarma,, da gudu khaleepa yaje

ya rirriqe ta yana kuka yake kiran "innalillahee.... momy ki tashi,,,, kitashi,,,,, kiyi haquri ki tashi indai kika tashi nai miki alqawalin zanje gaban dady na durqusa nayita roqonsa harsai ya yafe miki kinji,,,, haka khaleepa yaita sabbatu hatta su baba yawale da dady sales da 'yan uwan wannan kiristan dake jinyar sa basu San sanda hawayen tausayin khaleepa yadunga fito musu daga cikin qwayar udanuwan su ba,, daqyar dady sales ya tayar dashi daga wajen, wanda sosai baba yawale ya lura da hjy furdausey magagin mutuwa kawai takeyi, dasauri baba yawale d'in ya qara so daidai setin kunne ta yana laqafa mata kalmatusshahada, amman inaaaa tayi tayi tama bud'e bakin amman takasa kwata kwata, uwa an datse mata bakin kuwa haka takeji,, haka baba yawale yaita maimaita mata kalmatusshahada d'in nan amman tagaza kar6awa dudda ya fahimci tana son maimaitawan amman Allah bai bata ikon hakan ba,,, abin mamaki da al'ajabi ji sukai wannan kiristan dake kusada gadon hjy furdausey d'in shi kuma yana nanata kalmatusshahada d'in dayaji baba yawale nason hjy furdausey ta fad'a amman takasa,,, cikin mamaki baba yawale ya tambayi 'yan uwan kiristan mutumin nan wato mace guda daya namiji daya, baba yawale yace musu ko daman dan uwansu musulmi ne? nan take sukace masa a'a kawai dai sun sani yana yin wasu 'yan al'adu masu kama dana musulmai,wato na kullum safiya ta Allah yana bada sadaqar kud'i biyar goma ga qananun yara, snn in sallar su tazo wato kirsimate yana sawa a dafa abinci wanda babu nama a cikinsa ko tsoka daya, yasa adinga kaiwa gidajen musulman maqotansa, damuka tambayesa miyasa baisawa asaka nama a ciki dudda dai ga naman da yawa, sai yakance yayi haka ne gudun zargi, wato kada musulman ganin naman a cikin abinci yasa musu shakkun cin abincin gudun kada suyi tunanin ko naman alade kona kare ne ko kuma ma mushe ne a ciki,, koda suka gama gayawa baba yawale hakan sosai yayi mamaki, a ransa yake cewa "lallaikam gaskiyar hadisin dayazo Akan fad'ar cewa, zakaga mutum na aiki kalar na 'yan wuta baifi saura qiris ya rasu ba in Allah ya soshi da rahamarsa zaisa shi yayi aiki kad'an wanda zaisa ya shiga aljanna babu hijab wato ba shamaki, hakama mutum na aiki kalar na' 'yan aljanna zakaga saura qiris ya rasu zai aikata aiki kalar na 'yan wuta kuma y@ shiga wutar, wannan dud suna faruwan ne a cikin littafinka na kunfayakun, ya ubangiji Allah.

Jin da sukai mutumin yana gama maimaita kalmatusshahada d'in yayi shiru idanunsa a sama yasa yan uwan fahimtar ya mutu tuni suka fara kuka suna kiran jesus jesus jesus,, sunjima suna kuka dudda sun kira saurin 'yan uwansu kuwa da cewa azo da mota a dauki gawan dan bakin binneta,, koda sukazo zasu dauki gawar baba yawale yayi qoqarin fahimtar dasu cewa yanzun fa d'an uwansu ba kiristan bane Inda harma Allah yabashi dama ya ambaci kalmatusshahada to susamo malamin adini yai masa salla, amman qiri qiri sukace baza suyiba Inda sunsan d'an uwansu kiristan ne, ahaka suka fita baba yawale yabisu da kallo snn ya dubi dady sales yace "Allah yasosa da rahman sa dan haka komi zasuyi masa bazai sauyasa daga musulincin daya karba ba ynxun snn ya mutun.

dai dai lokacin ne sukaji

wani nishi mai qarfin gaske hjy furdausey taja sannan ta nimmuqe dungurmin jikinta daga haka tace ga garinku nan..... ta cika knn.

Allah sarki ay da gudu khaleepa yaje ya qanqame gawar tata yana kuka ma'ishi dan kwata yakasa mgn jijjigata kawai yake jikinsa na fidda gumi uwa yayi wanka,,, daqyar baba yawale ya janyesa shikuma dady sales yaja malullu6i ya rufe ta har kanta yana kallon ta da tunani a ransa yake cewa "ay shikenan to, iyakar taki ta duniyar knn furdausey, yanzun ina yawon neman

asirin naki yake? babu? Allah shi kyauta ya shiryi masu hali kalar naku kodan gobenku tayi kyau.
girgiza kai yayi shida baba yawale yayinda khaleepa ke dafe da bango har lokacin hawaye basubar fuskarsa ba,
kallon gawar baba yawale yake a ransa yace "hatimatussu'e mummunan makoma ta cikawa bada imani ba, wa' iyazu billah,, Allah ya tsaremu da 'ita,,.
daqyar baba yawale yasa khaleepa yayi shuru har suka tallafo gawar tata shida dady sales suka sakata a mota suka tuqo ta har suka iso ciki anguwar tasu kuwa da misalin qarfe 10 na safiyar ranar ....

By
Xexen Fasaha.
[4/18, 11:06 PM] Xainab Documen: 👁️👁️
🧻🧻
👁️👁️
DA SAURAN KALLO.

story and writing
by
Xayyneb 💤💤

my big daughter na ummu sulaimu haqiqa na tayaki murnar fara sabon novel dinki mai suna amra da afna WAKEDA hatimin nasara??,,
kai kai gskia wanda bai fara bin novel d'in nan ba yayi mazmaza ya shiga sahun nemansa dan kada girkakken daddad'an ma'anannan nishadaden soyayyen labari ya yabarsa abaya,,
ku nemesa nina fada muku, dan labarin na bada citta zazzafar kuwa ma, tafe yake kan tsari na jadawalin basira na fasihiyar marubuciyar nan ta mu ummu Sulaimu,,,,,.😍.
karku manta da sunan novel d'in wato shine,,,,,,,,,
AMRA DA AFNA WAKEDA HATIMIN NASARA?????

karku ku sake a baku labari ku maza ku garzaya kusha karatu Akan nera 100 d'inku kacal 👌a sauqaqe, *wanda dazarar ka biya 100 din nan bazaka qara* *biya ba har sai an gama wannan sabon salon labarin dakai.....*

wannan qasaitaccen labarin zaizo muku ne
daga kudin taskar marubuciyar.....

1_kibd'iyya
2-ta aure mijin
3-gimbiya meena
4-tattali
5-khairat matar cornel NK

6-sinadarin rayuwar aure

~7----_____----------now AMRA DA AFNA is loading.....~📲

domun hausawa na cewa biyan buqata yafi dogon buri,,,,
```kuyi maza ku garzayo kusha labari 👪daddad'a mai tarin ma'ana da kudin ku qalilan.```🐕.

~dedicated to my mom sadeeq hauwas~°

G agin datai bashida dai niyyar bud'e mata qofan ne nan tasake sakin wani qarar kukan wanda hatta zarah dake cikin d'akinta saida ta juyo ta, aiko da sauri saigata kuwa ta fito ta tsaya daga nn setin qofar dakin ta tana sakin wata dariyar mugunta tana fad'in "kai kai saurina da gobe dai kam saurin zuwa wlh, yanzu wata banza tasa aka gama qonamun rai a banza a wofi, to ashe itama natan nanan tafe? hehehe danasan hakan ma zata aiko aida banyi saurin b'ata ma raina ba dan gashi yanzu an wankemun shi tassss" hhhh may be duka kikasha ya tulloki waje ma ko? kaiiii huh,,,, abin gwanin burgewa, naji dadin ranar nan,
nan taita danqarawa heenduh zafafan maganganu masu dauke da qasqanci, amman ita heenduh kam sam zarah bata gabanta dan ita abinda ya dameta ya da meta shiyasa kawai taga babu dalilin da zaisa ma ta biye mata dan ita kam yanzun bata d'auki zarah mai cikkaken hankali ba yanzun,,, dan haka miqewa tai daga wajen ta goge hawayen fuskarta tareda watsawa zarah kallon tsana da qyama snn tace
"uwa da uba sun bani tsabtatacciyar tarbiryar dako ina naga dabban mahaukacin mutum ko kallon Inda yake bazan iya ba gudun kamuwa da jahilci kalar nasa kuwa, dan haka ina umartarki a shawarance da cewan kije ki samu karya abokiyan haushinki kuyi tayi amman badai niba heenduh na wuce class d'in musayar harshe da kishiya, kishiyar ma musamman ballagaza kamarki, kuma ki sani doctor na da kike taqama da wai kin samu power a gunsa kike wani tadamnun kai da hura hanci ko? to ki sani ganin damata ne na bar shige masa har yasa hakan ya faru, in yanzun nayi nufi maidosa gareni to ina mai tabbatar miki da cewa ruwa saisun miki wuyar had'iya kuwa a maqoshin ki cikin gidan nan, dan in baki wasa ba da kanki zaki bar gidan nan qafa ana kare, domin yaya na aronsa na baki, kuma aron nasa ma dana baki photocopy dinsa ne tare dake dan original dinsa na waje na damqe a tafin hannuna, so da fatan kin d'auki darasin karatun nawa ko? nina wuce dan ban iya jin zan tsaya sauraron wannan haushin naki ba na manyan karnuka"!!!!
tana gama fad'in mata hakan kuwa ta zagayeta tai shigewarta d'akinta.
aiko zarah cikin zafin zuciya na kalar zafafan maganganu da taji heenduh ta gama dandanqara mata su ata cikin ruwan sanyi yasa nan take kuwa taita sako ruwan bala'e tanata qunduma uban zagi na munanan ashar wanda sak 'yar bariki zakaji tana sakin kalar wannan zagin , tanayi kuwa tana dukan qirji bakinta na fitar da farin kunfa ata geffensa,,, ganin datai babu wanda yasan tanayi ne yasata had'iye masifar tata ta koma cikin d'akinta tana cigaba da zagin heenduh, dan qwarai maganganun data ya6a mata sun ta6a mata zuciyarta matuqa. jitai gidan yayi mata zafi tuni ta daura after dress saman kayan jikinta ta figi key d'in motarta ta shige
```

bayan ta kira hafeez tace su had'u a hotel d'in da suka saba had'uwa.
heenduh kuwa najin tabar wajen da wasu mintoci nan tayi saurin qara futowa ta koma bakin qofan dakin khaleepa daga ciki wajen qyauren ta raku6e ta zauna gamida dunqule jikanta waje daya ta sanya fuskarta cikin gwiyoyinta, zuciyarta naci gabar mata da zafi na ciwon fushin da yakeyi da'ita.
tarasa ma mike mata dad'i a cikin rayuwar ta, tana nan zaune harta fara jiyo kiran sallah daga babban masallacin dake anguwar,,, sake lafewa tayi wajen ta kwanta, babu zato taji qarar bud'e qofa kokan ta yunqura ta janye jikinta daga jikin qofar inaaa,,, dan har ta fad'i qasan farkon shiga dakin,,, "washh Allah na!!!"
abinda heenduh tace knn sanda ta miqe zaune tana luliya damtsen hannunta ta na dama data fad'i samansa,, binta yayi da kallo cikin mamaki na tunanin kaddaifa ace yarinyar nan tana wajen nan zaune tun dazun gashi yanzun duhun magrib harya fara,,, ganin datai ya d'auke kansa daga gareta yana qoqarin tsallaketa ya wuce wanda ga alama masallacin zaije Inda ga prayer mate nan da nurussubahe na cazbaha a hannunsa.
aiko da sauri ta ta yunqura tareda durqushewa gabansa ta rungume qafafunsa tsam tsam a cikin qirjinta tana matsar qwalla take fad'in "doctor please ka yafemun na rantse maka fa da Allah nace bazan qara maka rashin kunya ba, ka yarda dani bazan sake b'ata maka rai ba I will promise"!!!!
qwace qafafunsa yayi har tana fad'uwa qasa, baice mata komiba yayi ficewarsa masallaci"
tashi tai daga wajen tana share hawaye ga kuma yanda takejin kanta na wani mummunan sara mata kuwa a lokacin, toilet ta wuce ta shiga tareda yo alwala ta fito tayi sallar, tajima bata d'ago ba, tanata kai kukan ta ga Allah cikin sujjadarta ta qarshe na roqon Allah ya sanyaya zuciyar doctor d'in nata, ba'ita ta tashi ba daga wajen ba saida tayi sallar isha'e sannan ta miqe ta cire dogon hijab d'in jikanta, tayo wanka tadawo saman gadonta daga ita sai towel daure a qirjinta ta kwanta tayi lamo idanunta a rufe..... jitai wayarta dake gefenta ta d'auki ringing, bud'e idanunta tayi a hankali gamida tareda miqa hannunta ta jawo wayar,,, number sa'a ce tagani.
dasauri tayi qoqarin miqewa zaune ta daga wayar tunkan tace wani abu nan ta jiyo dariyar sa'a d'in cikin tsokana take cewa "uwargidan doctor khaleepa yakk ya amarci, na bugo ne na goge lefina nasan cinmutunci da zagi daga bakinki heenduh saidai na to she kunne Inda nai miki tonon silili, sorry qawata bazan juri ganin iyayenmu cikin damuwar rashin ganin kiba, na boye musu alhalin nasan Inda kike,, shiyasa tun ranar da kika dawo dudda nasan kin dawo wato doctor ya je ya d'aukoki naqi kiran ki na bari ne daman ad'an kwana 2 inkin huce saina kiraki dan nasan nida qawata bata 6aci ko? to kiyi haquri yiwa kaine shiyasa nai hakan"
wani murmushin dole heenduh ta qaqalo, dan kuwa tabbas tayi niyar wanke sa'a datai mata wannan tonon,, amman ina yanzu ta rusa budget d'in komi dan labarin kuwa yarigaya da yasha banban, dan yanzun Inda akwai abinda take buri bai wuce ace ta samu mafita wacce zata shawo kan doctor d'in nata ba, shiyasa tace " hmnn sa'a da knn kika sani, yanzun nayi sanyi, wlh ina cikin matsala sa'a please yaushe zaki shigo ne?"
sa'a tace "cab ke d'in ke daukar shawara? aini na daina baki shawara Inda ba dauka kikeba 'yar renin hankali kawai da shegen taurin kai uwa a garin arna kika fito"
marairaicewa heenduh tayi tace "yi haquri qawata, wlh komi dakemun yawo aka yanzun na ajiyesa waje
d'aya, please ki taimaka kizo dai d'in dan nasan bama bari na zaiyi nina zoba yanda yake fushin

nan dani, ay da saidai kawai ki ganni"
sa'a tace "to shikenan Inda kin kawo uzurinki, kinci sa'a da gobe zan koma amman zan daure nazo da wuri gobe d'in da safe insha Allah kanna wuce baucin"
cikin murna heenduh tace "yawwa qawata ta kaina ina jiranki"
a haka sukai sallama.
komawa tayi ta kwanta jitake ta qagara gari ya waye sa'a tazo, dan uwa ta jawo gobe da safe takeji saidai inaaa.
haka ta kwanta taita juye juye hardai tayi nasarar bacci ya dauketa.
washe gari Monday tunda wuri khaleepa ya fuce zuwa office zuciyarsa cikeda mamakin yanda zarah bata kwana gida ba, saima text datai masa nawai tana gidansu can zata kwana sai gobe zata dawo, ko replay bai mata ba a lokacin saima barcinsa daya shigayi bayan dawowarsa daga gidan su, da kuma gidan su heenduh, wato wajen mama zainab da baba isma'il gamida baba yawale daya biya yakai masa gasassun kaji, sanda ya fito daga masallaci yashiga mortarsa yanufi anguwar tasu iyayen nasu knn.
heenduh kuwa bacin ta gama komi tayi wanka ta shirya cikin wani milk d'in lace riga da zane sai faman walainiya takeyi cikinsa, nan ta dawo falo ta dake, zaune take saman kujera hannunta riqe da wayarta taga har goma da kusan minti arba'in sa'a bata iso ba alhalin ta mata text d'in address d'in gidan da anguwar dataje ta tambaye maigadinsu wani soja ne, kuma gashi sa'a d'in sai ce mata takeyi gata nan a hanya ta tafo amman kuma shiru kakeji har yanzu, d'an siririn tsoki heenduh taja tana qoqarin sake kiran number sa'a d'inne kawai taji sallamarta ta shigo falon gidan,, aida gudu heenduh ta miqe ta isa wajen sa'a suka rungume juna suna faman qyalqyata dariya.
saida suka natsu ne sannan ta miqe taita cikewa sa'a gaba da kayan ciye ciye danginsu kwad'ai.
saida sa'a taci dambun naman nan sosai da holandia yoghurt snn suka bar falon suka shige cikin lambun gidan suka zauna saman wasu blue d'in kujeru bayan sa'a ta daura jikkarta a tsakiyan tebur d'in kujerun.
shiru heenduh tayi tayi qasa da kanta dan tarasa ma ta Inda zata farowa sa'a mgnr ma kwata2.
dafata sa'a tayi tace kinacin tym dinki fa matar doctor kinsan da tafiya a gaba na kuma nazo kinyi shiru kinqi cewa komai"tayi mgnr tareda sakin murmushi.
sauke ajiyar zuciya heenduh tai snn ta kwashe komi ta fadawa sa'a dangane da abinda tace masan nan har yayi fushi, snn kuma da qofar da zarah ta samu ta sanadiyyar hakan tana mata cin kashi kala kala, dubanta sa'a kawai take kamin tace "komi ke kike jawo wa kanki shi heenduh, yanzun to da kikayi wannan katob'orar zancen wa gari ya waya knn? kefa knn, snn kin bawa kishiya kofar sanin babu jituwa tsakanin ki da mijunki har tana miki habaici,,, gskia in zaki chanza kawai ki canza qawata dan wannan hanyoyin da kiketa bi bamasu 6illewa bane kwata kwata, dan banda wahala babu abinda halayenki ke ja miki "
kamo hannunta heenduh tai tace" naji komi kikace kuma na rigaya danasan nayi kuskure tunma kan kizo, please sa'a kibani solution wlh gaba daya banjin dadin zuciya ta" taqarashe mgnr daqyar uwa zata fashe da kuka.
itama sa'a kamo hannun heenduh tayi cikeda tausayin ta kuma, sakin murmushi tayi tace "mafita daya ce dhe first solution shine kasan yanda zakiyi har kishawo kansa ya haqura, karkice kin gaji yaqi haquri, no daurewa zakiyi kina basa haqurin gamida yar kissar nan tamu ta

mata, dadai sauransu wanda a matsayinki na mace nasan kinsan sauran hanyoyin janyewa mijinki hankali koda kuwa bada yawwa bane,, zuge jikkarta sa'a tayi ta fuddo wani dan farin kwalban turare ta riqesa a hannunta tana jujjuyasa snn ta miqawa heenduh shi, heenduh ta karba wanda tun sanda sa'a ta fuddo kwalbar turaren taji gaba daya wajen ya kaure da wani qamshi mai tsananin sanyin dad'in gaske,,, "wannan fa na mine?" abinda heenduh ta cewa sa'a knn tana kara kallon turaren wanda takeji uwa ta shasa kuwa.
gyara zama sa'a tayi tace "wannan turaren da kike gani ba qaramin aiki yake ba, muddin kika shafasa a jikinki doctor yaji qamshinsa ko? hmnn sauran bayani kya bani shi daga baya qawata, dan nima mama ce ke sarosu a hadaddun nagartattun kayan mata datake sarowa daga manyan masu sayar dasu tana siyarwa, to shine ta bani guda daya, kinsan tsada ne dashi sosai wlh kwalban fa ta kusan 100k, dan manyan mata ne suke jure siyansa dan sanin amfanin su garesu ba kadan ba,, dan lokacin da'ina amarya tafara bani shi kiji in gaya miki qawata wlh bakiji sanbatu ba daga bakin my ba sanda muke tare....,, to yanzun na baki shi dan ahalin yanzun kin fini buqatarsa, yanda zakiyi amfani dashi ne cikin ruwan wanka zaki dunga zubasa kamar sau uku haka a kulum kinga yini guda knn zakiyi amfani dashi duka, to cikin yardar Allah kamshin zai bi jikinki ya zauna radam, kuma wnn turaren da kike gani matsayin ingantaccen maganin mata ne sama da goma.. kada nacikaki da surutu dai ga kuma tafiya a gabana, cewar sa'a d'in tana mai miqewa tsaye sargafe da jikkarta a kafada.
rungumeta heenduh tayi cikin farinciki take furta "wayyo qawata ngd ngd sosai Allah barki da my dinki"
sa'a tace "amin qawata komi kenan mayi waya ay"
daga haka heenduh taja sa'a cikin kitchen ta juye mata sauran snacks din datai mata gamida dambun nama dud a culors snn ta rako sa'a d'in har kusada gate suna bankwana snn ta dawo ciki bayan wucewar sa'a d'in.
haka heenduh ta dawo ta ajiye turaren da nufin sai gobe zata fara amfanin dashi, khaleepa kuwa sai da ya daidaici heenduh tayi barci sannan ya dawo gidan wuzin 12 pm, dan yana wajen abokansa su yunus yana fira dudda kuwa tana manne cikin ransa amman haka yake daurewa kawai danson ganin ta qara shiga taitayinta, dudda shima bada sonsa yake mata ko'inkula d'in nan ba amman dole tasashi mata hakan dan ramuwar gayya,,, haka koda safe da wuri ya fice dudda ya hangi zarah a kitchen kuwa amman Sam ita bata gansa ba danta juya baya sai hadar abinci take uwa taiki, dan zarah kam bata wasa da cikinta sam.
koda heenduh ta farka dasauri ta duro saman gadon ta tashiga bayi tayo wanka da turaren nan ta fito ta shirya cikin skirt da riga na wani material mai rawa rawa wanda gaba daya yabi jikanta ya manne d'af,, har mamaki take in tana kallon kanta a madubi yanda fatar ta taqara fresh, taqara kyau sosai hakama dukiyar fulanunta sun sake ciccikowa da girma suna tsaye curr curr gwanin sha'awa, gawani bud'ewa da hips dinta suke qarayi, dasauri ta ida daura scalp dinta ta fito tanufi dakinsa tana takun d'ai d'ai sai Baza qamshi take, tana tura dakin kuwa taga wayam alamun ya ficce, tsaye tai kawai tayi shiru, dudda bataji dadin hakan ba amman haka tahau gyara masa dakin nasa har zuwa toilet, tareda saka abin qamshi sannan ta baro dakin ta sauko qasa ta samu zarah kace kace ko wanka batai ba, sai soshe soshen kai tajeyi da daurin qirjinta kuwa tun na tashi barci.
tanaji sanda ta wuce kitchen dan samawa cikinta abin kari zarah sai habaici take mata tana zaginta amman ko kallo bata isheta ba, koda tagama hada breakfast din kuwa nan kitchen ta

zauna taci sa tareda wanke kayan datai amfani dasu dan bata son barin abu da datti koda kuwa cokali ne.
haka ta fito tai komawarta saman ta ta kwanta.
wasa wasa kuwa wajen dai tsawon sati daya knn khaleepa yaqi zaman gida kulum yana gidansu ko gidan mama zainab ko wajen su yunus muddin ya taso aiki kuwa, dan baison zuciyarsa ta raunana ne kan heenduh tun yanzu.
yau an tashi da hadari a safiyar ranar lahadi,da qarfe 9 na safen.
iska ake mai qarfin gske, wanda kan kace mi tuni ruwa ya tsuge shaaaaaa tanfar da bakin qwarya.
dasauri heenduh ta sauko daga gadon ta tayo waje, ta sauko qasa qasan falon, dan Inda akwai abunda heenduh ke sha'awa kuwa tun yarinta har kawo girmanta bai wuce son yin wanka cikin ruwan sama ba, dan haka dasauri ta qulle gashin kanta da band ja, tayo harabar gidan tashiga cikin ruwan tareda juya juya hannuwanta a ware fuskarta na kallon sama idanunta a runtse ruwan na sauka taaaaaaaaa kota'ina a jikinta tanata dariyan farin ciki kuwa, wanda kan kace mi tuni wandon ta na siliki da take sanye dashi iya saman rabin cinyoyinta yajiqe jagab gamida d'ashewa a jikin ta har ana iya hango sharp d'in hq dinta kuwa, yanda take juya mazaunanta kuwa uwa roba shima abin kallo ne,. ga rigar ta da take iya qirjinta danko arziqin halp best dunma bata kai ba, rigar ta manne mata mamanninta sosai wanda hatta kan nipples dinta jajaye kuwa ana iya hangosu,, gaba daya khaleepa dake tsaye saman benen dakinsa ya tsura mata Ido yana kallon ta yanajn tsigar jikinsa na mimmiqewa, jijiyoyinsa kuwa uwa ana tsinka masa su dan wani shocking dayaji a dukkan sansan jikinsa, runtse idanunsa yayi gam gam zuciyarsa na buga masa, numfashinsa na fuzga da qarfi, jiyai wata zuciyar tace "yanzu in mai gadi yana kallonta fa cikin filin nan yaya knn? dasauri kuwa ya bude jajayen idanunsa yakai dubnsa wajen mazaunin sojan mai gadin nasu yaga wayam babu kowa dan hatta tagogin dakin da yake ciki a rurrufe suke harda qofar ma,, sauke wata kalar qaqqarfan ajiyar zuciya yayi sai lokacin yaji hankalinsa yad'an kwanta,, da sauri kuma ya fara gangarowa waje shima ya nufi Inda take cikin ruwan, so yake ya fiddota a ruwan gudun kada lollipop d'in ta kamu da mura ko fever,
ganin satai kawai a gabanta tsaye kamar an jefosa,, ya zuba mata Ido yana binta da wani nataccen kallo sama da qasan ta kuwa,, lumshe idanuwa yayi gam jin yanda daddad'an wani ni'imtaccen qayataccen turare ke fitowa daga jikinta zuwa mashaqarsa wanda sosai qamshin yatafi dashi ba tareda ya ankara ba.
damm!! dam! dammm, abinda k'irjin heenduh ke bada kalar sautin bugawarsa knn.
ahankali taji jikanta yayi mata sanyi daga kalar d'imautaccen kallon da yake watso mata dashi,, sosai ruwan ya jiqesa shima sharkaf amman sam bai damu ba, heenduh zuwansa wajen gamida tsayuwarsa ne taji dud ya cike mata wajen da qwarjininsa, ahankali ta juya masa baya da nufin barin wajen taji an riqo qugunta ta baya an rungumesa tsamm,, kan tayi wani yunquri taji ya juyota gabansa ya matsoda ita cikin jikinsa ya rungumeta qam qam cikin mayalwacin qirjinsa yana sauke numfashi,, banda sunsunar dogon wuyanta zuwa tsakankanin qirjinta ta cikin rigar bai komi,,, tuni taji jikinta ya qara saki, da sauri ta riqe fuskarsa da tafukan hannuwanta jin datai yana shirin yin qasa da hannunsa zuwa hq dinta... ganin tana d'ari d'ari ne yasa bai jira komi ba ya sureta cikin jikinsa yanufi dakinsa da ita ya shimfid'ar da ita saman gado yana bin fuskarta da wani kasalallen kallo wanda hakan yasa heenduh saurin runtse idanunta gam, ahankali yaci gaba da binta sunsunar qamshin turaren nan nata wanda cikin

dabara ya rabata da komi na jikinta yaja blanket ya rufesu ruf, qarar saukar ruwan ne gamida wata tsawa da aka saki yasa heenduh gigicewa ta haye saman jikinsa ta qamqamesa jikinta na rawa,,, murmushi yasaki gamida daura hannuwansa saman nashanunta dasuke tsikarar masa qirjinsa a lausashe,, wani zazzafan kalar wasa khaleepa ya kwantar da heenduh yana mata, tundaga qasan ta har samanta babu Inda bai kai wa caffa ba cikin rawar jiki suka qanqame juna tareda hade bakunansu waje daya,,, sosai suke tsotsan juna kota'ina dan anjima kam ba'a hadu ba daman shiyasa suka haukacewa juna kowa na qoqarin ganin cewa ya farantawa dan uwansa, farin ciki kuwa cikin zuciyar heenduh fall wanda koda ba'a fad'a mata ba tasan doctor d'in nata ya daina fushi da ita yau kam,dan haka ta sake zage dantse wajen ganin ta faranta masa ta hanyar wasa datakeyi da hannunta a jikinsa kota'ina wanda kankacemi taji yafara mata sabbatuttuka kala kala kuwa, dan datakai bakinta a mamansa tana wasa dasu da haqoranta tuni ya'ida shid'e mata harda hawaye kuwa,, dasauri ta kamo fuskarsa tasaka ta cikin nashanunta taqara ja musu bedsheets ..... haka sukaita mukurkusar juna babu yankewa , dud sunbi sun rud'e sunbar hayyacinsu sai sabbatuttuka na dad'i sukewa juna, dan khaleepa kuwa cikin hawaye da baisan suna fitaba yake cewa "I really love you sugar lollipop na,,, please kada ki qarasawa nai fushi dake haka da yawa,,, wanda zaisa munisanci junanmu,, kinsan cewa dajin dad'in d'ayanmu muke rayuwa, please sugar na banda wacce nikeso matuqa a rayuwa ta sama dake,, kiyarda dani.... jin sambatun nasa yayi yawa ne yasata qara kamo fuskarsa ta tura masa sweet balloons d'inta d'aya a bakinsa, tuni bakin sambatun kuwa yasamu aikin yi ka jisa shuru kuwa, banda saukar numfarfashinsu bakkajin komi a d'akin... tun ana ruwa har aka jima ma d'aukesu tsab amman suna maqale da juna suna cigaba da farantawa junansu rai wanda basu ne suka sararawa juna ba saida wajen qarfe 2 na ranar.
koda suka nutsu still tana kwance saman faffad'an qirjinsa tana wasa da kwantaccen gashin qirjinsa, shi kuma hannunsa nasaman bazajjen gashin ta dayai mata rufi a jiki, kallon tsakar idanuwa kawai suke jifan junansu dashi suna murmushi.
sake yo sama yayi da'ita ya saddo da bakinsa a qirjinta yana qoqarin sake saka bakinsa a kansu dan ba qaramin tsokane masa ido suke yiba, muddin yana ganinsu free tofa babu sauran saqat na zaman lpia, uwa jinjiri ga mamansa haka doctor yake ga sweet balloons d'in heenduh wanda itama ta jima da sanin hakan, ganin hakan da tayi ne yasa tayi saurin barin jikinsa tajawo abin rufa to rufe rabin qirjinta tana qyalqyata masa dariya, dasauri ya bita nanko ta duro saman gadon sunata zagaye dakin kankace mi tuni yayi wani dogon taqi daya ya funcikota saigata saman jikinsa warwas,, fuzgota yayi ya matseta tsam tsam a jikinsa wanda had'uwar qirjinta da nasa baqaramin qara susutasa yayi ba, sunkuyowa yayi daga tsayen yana qoqarin cusa mata bakinsa a nata tayi saurin dakatar dashi idanunta sunyi narai narai tace "please sugar doctor na bafa kace ka yafemun ba" tayi mgnr tana goga masa qirjinta a saman nasa qirjin.
lumshe idanunsa yayi snn ya budesu, bai tsaya jiran komi ba ya sureta ya kwantas saman gado, bayan ya kwantar da'ita ya duqo ya zuba mata idanunsa wanda hakan yasa tayi saurin runtse idanunta cikeda kunya,,, jitai yace "ko dama can sugar baby na ba fushi nike da ke ba, adud abinda kikaiman kama daga zubda mun ciki da kikai kan kishinki da kuma guduwar da kikayi dudda raina ya baci hankalina kuma ya tashi, amman abinnan da kikace na kin barwa zarah ni baqaramin haddasa mun mummunan ciwo kalmar tayi cikin zuciya taba,, amman Inda na lura kinjima da zubda makaman yaqin naki to na haqura sugar lollipop na, daman na jajircewa fushin nawa ne gareki bada so na ba saidai dan in tabbatar miki da kurenki na mgnr

da kikai mun data 6atan rai since time, but forget it,,,,,, then komima h gonna sugar lollipop na OK?"
aikam dasauri kuwa ta rungumesa tana dariya qasa qasa sannan tace cikin shagwaba "to... to shine kaita dizgani da bani headache na kunya a gaban zarah ko? kaita gwasaleni kana hantara ta, naita Jin ciwo sosai a sanadiyyar hakan fa a zuciya ta, taqarashe mgnr tana turo masa red lips dinta a shagwabe.
murmushi yayi cikin kanne ido yace" inba haka na dinga gwada miki ba nasan bazaki shiga taitayinki ba snn nima bazan huce ba madam,,, dukan qirjinsa tahauyi cikin kukan shagwaba, shiko sai kama ta yake qarayi yana sakin kalar isassar dariyar nan tasa.
